https://www.youtube.com/channel/UCMylPCg0TCgTWAmy6HHvcEQ

*'KAUNARMU*

Mamuhgee

_*1*_

https://youtu.be/MJxY0y_SrOc

Labarin qaunarmu labarine akan soyayyar data shigi mutane biyu batareda sun ankareba duk da kasancewar banbancin dake tsakaninsu na kasancewar kowannensu nada abokin rayuwarsa Wanda suke ganin sune rayuwarsu saidai so yayi musu shigar sauri Dan kuwa tuni suka daina kallon waincan amatsayin abokan rayuwarsu.....SO NE WANDA BAIDA KATANGA YAYI MUSU SHIGAR SAURI...YAYA ZASUYI DA ABOKAN RAYUWARSU NA FARKO...

Zata sadaukar da farin cikinta dominsa,

Zai sadaukar da rayuwarsa dominta,

Zasu sadaukar da komai domin juna,

'yar uwarta wadda suka fito ciki daya,

Rana daya, awa daya saidai bambamcin mintuna biyarne a tsakanin fitowarsu duniya

'yar uwar tata zai aura Amma qaddara ta juyo da auren akanta bayan tanada nata abokin rayuwar dataiwa kanta tanada Kuma a uba suke kallonsa shikuma atasa duniyar baimasan dasuba

saidai qaddarar so ta sauya musu akalar rayuwarsu zuwa ga zazzafar qauna da bazasu iya juyowa su kalli bayansu ba bare abinda yayi sanadin auren nasu.....sun shirya yaqar maqiyan soyayyarsu batareda sun tabbatarda qauna da zazzafar soyayyar dasukewa junansuba...

*_BRG MUHD SAHEEB MARSHALL MAKARFI_*

And

*_KHADIJA MUFIDA NUHU MANDE FIFI_*

*_'KAUNARMU_*

Mamuhgee

*_1_*

BismillahirRahmanir Raheem.

□□□□□□□

https://youtu.be/MJxY0y_SrOc

HAMBURG garmany.

10:30am

Gyara zamanta tayi akan kujerar dake fuskantar ta Dr Fatima Omar yonas tareda gyara zaman glasses na idonta ta bude bakinta dake mata nauyi aduk lokacinda zatayi maganar 'yar uwarta sbd jin kunyar kanta da takaicin kanta akan yanda konyaushe 'yar uwartace ciwon ranta da damuwarta,

Duk yanda taso dauke Kai da danne alamarin ako yaushe sabo abin ke dawo mata sbd tsoron meyene zata samu agaba 'yar uwarta ta rabata dashi sbd wannan shine asalin dumuwarta da tsoronta sbd batasan mezata iya zama agaba ba itama akan hakan.

Kamar yanda tasaba kullum idan tazo gurin Dr Fatima yonas yauma farawa tayi da cewa"

Sunana AYSHAT HAMEEDA NUHU MANDE sunan Tawainiyar haihuwata KHADIJA MUFEEDA NUHU MANDE,

yan biyu mahaifiyarmu ta haifemu shekara ashirin dasuka wuce,

Mintuna biyarne kacal atsakanin haihuwar tamu,

Nice nafara fitowa duniyar kafin ita,

Nice na cancanci mafi yawan soyayya da qauna daga iyayenmu da danginmu kafin ita sbd nice nafara haskaka idanuwansu dasuka jima da jiran ganin wannan Rana dazasu rungumi nasu 'yayan suma kasancewar sun jima harsun fara manyanta babu haihuwa,

Bayan fitowata duniya iyayena sunyi farin ciki mara misali na samuwata Saidai SO da QAUNA Dana samu daga garesu na mintuna biyarne kacal sbd fitowar 'yar uwata duniya ya sauyamin komai har zuwa yanzu,

Itace sanyin idanuwansu,

Itace farin cikin gidansu da wajensu,

Saidai Allah dayafisu iko da ita bai sakota a duniyarba sai daukeda cuta ta *_RAUNIN ZUCIYA_* ma'ana _*WEAK HEART*_ _*(CARDIOMYOPATHY)*_

Wannan cuta datake daukeda ita ta qara rage kaifin qauna dake tsakanina da iyayenmu,yan uwanmu,likitocin da duniyama gabaki daya.,

Ciwon raunin zuciyarta yasa ba'a qaunar bacin ranta,baa mata fada,baa ganin laifinta,kowa qaunarta yakeyi,kowa sonta yakeyi Wanda tuni gata yayi mata yawa tako wane bangare musamman Kai tsaye mahaifiyar dadynmu ta yanke cewa asakawa 'yar uwata sunanta tanason ta gajeta

Ba 6ata lokaci taci sunan kakarmu da mahaifiyarmu wato KHADIJA MUFEEDA inda ni naci sunan Mahaifiyar mamanmu wato AYSHAT HAMEEDA.

Ta karbe soyayyar iyayenmu,

Ta karbe soyayyar kakanni da danginmu haka ta karbe sunan Mahaifiyar da rayuwarta Dan kuwa tun bayan fitowarta duniya mahaifiyarmu Bata qara lafiyaba munada shekara daya ta rasu tabarmu da dibbin kewa da maraicinta,

Anyiwa mufeeda aikin zuciya Wanda akayi cikin nasara da saa Saidai likitocin sun tabbatarda akwai yiyuwar asake mata wani aikin agaba wanda sukeda tabbacim ba lallai ta rayuba idan anyi.,

Wannan shine yaqara assasa wata sabuwar qaunarta mai tsananin qarfi a zuciyar kowa.

Muntaso cikin gata da kulawar mahaifinmu da kakarmu wadda tsufa yasa tuni Takoma gidan babbar yarta yayar dadynmu dake zaune a Lagos mukuma mahaifinmu ya daukemu muka dawo wannan qasar da zama,

Soyayya da qauna wadda mahaifinmu kewa mufeeda ta dabance wadda baa hadata da komai,

Ummy yayar mahaifinmu da hajja baza hada qaunarta da komai Dan kuwa ummy ko 'yayanta biyu maza kacal da Allah yabata Bata musu qaunar datakewa mufeeda,

Mufeeda Allah yayi mata gatanda bazance nasamu irinsaba Dan kuwa tako wane fanni Allah ya Bata duk wani Abu dakowa ke buqata,

Dukiya,

Arziki,

Gata,

Kyawu,

Kyawun jiki,

Farin jini,

Haiba,

Ilimi da wayewar rayuwa Amma Abu dayane bai horeta dashiba shine lafiya.,

Takasance lafiyarta qarantattace duk yanda takaiga holewa arayuwarta to lafiyace ke kawo mata tsaiko Dan kuwa ita mutumce mai tsananin son more rayuwa tareda abokai na wayewa dajin dadi,

Tun muna primary kowa da mufeeda yakeson qawance,

Kowa mufeeda yakeso haryanxu da muke a matsayin 'yan mata haka rayuwar take,

Nazama tamkar tsohuwa ko uwa sbd duwa da kishin 'yar uwata dake cin Raina tun ina qanqanuwata,

Ayanzu zuciyata cike takeda kishi tareda qaunar yar uwata Saidai abinda bansaniba shine tsakanin qaunarta da kishinta wanne yafi yawa cikin Raina??????

Wanne ne zai rinjayi waninsa acikin Raina Dan kuwa ayanzu nafara jin tsoron yanda tarabani da kamai na rayuwa mezata rabani dashi anan gaba????

Zan iya jurewa qaunarta ta rinjayi kishinta da jin zafinta kuwa kokuwa kishintane zai rinjayi qaunarta.????

Cikin sakin dogon numfashi Dr Fatima ta dakatar da ita ta hanyar miqa mata magani tareda glass cup na ruwa tana cewa"

It's time for break hameeda.

Jeki ki huta zamu Dora next time

Karki manta duk lokacinda kikaji zuciyarki na zafi gameda hakan Zaki iya zuwa ki sameni

I'm always here for you and always ready to listen to you okk?????

Gyada Kai tayi tareda sakin ajiyar zuciya Yana sake kurba ruwan ahankali kafin ta aje glass din tana kallon Dr Fatima ahankali ta furta"

Thank you mss yonas.

Murmushi Dr Fatima tayi tareda dafa hannunta tace"

Idan nadawo gida zanshigo

Karki Bari shedan tashiga tsakaninki da qaunar da kikewa 'yar uwarki,

Kece yakamata ace kinfi kowa qaunarta da tausayinta a duniya sbd kece twin dinta.

Gyada Kai tayi tareda miqewa tana sake cewa"

Thank you..ta dauki handbag dinta da wayarta dake kan table ta miqe ta nufi qofa ta fice.

Numfashi Dr Fatima tasauke sbd tausayin hameeda din da kishin yat uwarta yayiwa zuciyarta mugun kamu hartakai tanajin tsananin tsanaar 'yar uwarta wani lokacin wanda lura da hakan yasa tafara kulawa da mufeeda din ta hanyar sakata amayar da damuwarta kullum wanda Kuma hakan ba qaramin taimakawa mufeedan yakeba Dan tanajin sassauci idan tayi hakan Tasha mgani tana zuwa gida bacci yake sata maganin tana tashi zataji zuciyarta sakayau.

Dr Fatima Omar yonas maqwafciyarsu ce Kuma consultant ce ta bangaren tunani da karantar Dan Adam sune irin likitocin da idan Dan Adam baisan meke damunsaba idan ankaika gurinsu daga yanayin yanda kake amsa musu tambayoyinsu suke gano matsalarka.

Asalin 'yar qasar Ethiopia ce Batada miji ya dade da rasuwa yabarta da 'yaya biyu rak namiji da mace

Ameed da meena,

Ameed saurayine wanda shima Dr ne be wani jima da zama Dr dinba and ko shekara beyiba

Dan gayu me ji da kyau da gata da dukiya shima gashi dason rayuwar hutu da wayewa shiyasa aduniya Babu wadda yakeso kamar mufeeda wadda qawayenta da duk yawanci ma da FIFI MANDE,

Ameed na matuqar son Fifi itakuma amatsayin aboki Kuma Dan uwa ta daukesa sbd Dr Fatima data zamar musu tamkar uwa Dan kuwa ita kanta irin gata da qauna da Dr Fatima ke nuna mata yasa ma take kallonta tamkar mahaifiyarta haka take zuba mata shagwaba musamman idan ciwon na Fifi din yataso to tabbas kowa hankalinsa tashi yakeyi har mutanen Nigeria haka Dr Fatima zata tsaya tsayin daka a asibiti tamkar uwarta.

Meena ma Batada qawar datafi mata Fifi shiyasa kusan koyaushe suna tare musamman gurin yawon guraren shaqatawa sbd hameeda Bata shiga cikinsu.

Fifi a duniya bayan mahaifinta Babu Wanda takeso arayuwarta sama da 'yar uwarta hameeda wadda takewa kallon uwa Kuma 'yar uwa,

Qaunar datakewa hameeda qaunace irin wadda Allah ne kawai ya isa ya cire mata ita cikin ranta musamman sbd sanin ba lallai tayi doguwar rayuwa sbd ciwonta,

Tana Jim dadin rayuwarta da shaqatawartane sbd tunanin tabbas ita bamai jimawa bace a duniyar shiyasa Batada abokin fada Bata saka komai na damuwa aranta kowa natane sbd wata Rana Babu ita.

Ita mutumce mai tsananin son life musamman idan ta zauna takance idan har Allah yasa zata jima a duniya hartayi aure to Sam Babu abinda zai hanata auren miji irin ameed sbd itadai duk namijinda bai wayewaba ya iya rayuwar turawa Yana geaming ya handa muscles da abs to tabbas bazata iya aurensaba ita dai mijinta dole zai kasance kamarta Kuma wanda baifi yabata shekara uku zuwa huduba idan yabata shekaru to kardai su wuce biyar sbd me qarancin shekaru kamarta shine zai fahimci rayuwar Jin dadi yabarta suyi rayuwa yanda suke so kafin ta mutu tabarsa.

Ahankali ta bude idanuwanta dasuka Sha bacci ta miqe da sauri tareda cewa"

Oh shitt nayi latti sosai inada practical 10:00 and it's 9:40 yanxu.

Da sauri ta sauko daga kan gadon tana mayarda hular baccinta data zame gurin bacci ta nufi toilet da sauri tana adduar shiga toilet din ta fada tana cewa"

Maheeda zata kasheni da masifa wannan lattin danayi.

Sharp sharp tafito ta shirya cikin Marron Turkish gown me hadeda hula me gyale dazakayi rolling tayi rolling dinsa ta fesa turarenta na possess ta dauki Maroon channels handbag da loafers na Clark ta fito da sauri tana Kiran nurat me aikinsu akan takawo mata robar guava shake

Tana kawo mata ta karba da sauri ta bude zata saka a bakinta aka riqe robar tayi saurin juyowa taga hameeda ce tayi saurin Bata fuska tace"

Hameeda please kibarni Mana wlh nayi latti sosai fa....

Dadynsu ne yafito Yana waya idanuwansa suka sauka kan robar guava shake din sai hayaqin sanyi takeyi

Ya datse wayar Yana qarasowa gurinsu ya kalli robar yaga harda qanqara yakai hannu ya karba Yana kallon hameeda yace"

Hameeda kina kallo Zaki Bari Tasha wannan sanyin?

Kinmanta wayece itane?

Kallonsa tayi Takoma kallon Fifi din tana cewa"

Dady zan hanatane ka taho.

Kallon Fifi yayi Yasake kallon hameedar yace"

Ki ringa kiyayewa hameeda dukanmu bamason komai qanqantar ciwo yasamu mufeeda ok?

Miqa mata robar yayi Yana kallon Fifi datayi fuskar tausayi tace"

Dady nayi latti bazan iya tsayawa breakfast bafa.

Table ya nuna mata Yana cewa"

Ko exams ne mamana bazan taba barinki ki fita bakici komaiba indai I'm around.

Suna zama table din su duka hameeda datakai drink din fridge itama tazo ta zauna sai alokacin suke gaidasa ya amsa cikin kulawa Yana cewa"

Ummy takirani hajja ta sake 'dago rigimar wai sai andawo dake agabanta so takeyi taga aurenki kafin ta mutu.

Dariya tayi tareda kallon hameeda tace"

Hamee kinji nice hajja keson ganin aurena kifada mata raayina idan kunyi waya sbd dady yanzu ina kiranta ko ummy zata fara min kukan tanason ganina dady ba'a Nigeria zanyi aurebafa anan bana tunanin zan samu choice dina acan.

Murmushi yayi yace"

Mamana kifara zuwa Nigeria din tukuna zakisan choices naki duka suna can bama choice kadaiba,

And idan kina maganar life ne kije idan kinje Zaki bani labari sbd KHALID is also gonna be around.

Kallon Hameeda tayi tana dariya tace"

Hameeda ki shirya bazan iya zuwa badake ba I think it's time muje mu zauna dasu ammy right.

Chips hameeda ta tura cikin baki badan tanajin taste dinsa ba ta daga Kai tana qaqalo murmushi sbd yanda dadyn ke fira da fifin cikin tsananin kulawa sai can can yake jefota.

Cikin qarfin hali tace"

Dady 'yayan ammy shima wannan Khalid din Yana ciki???

Kallonta yayi cikin kulawa yace"

Hameeda yanzu duk bakusan 'yayan ammynku ba I tot kuna tambayarsu idan kunyi waya da ammyn.,

To dady ai bamusansu bane.

Babban danta tun kafin na auri mamanku ta haifesa MUHD SAHEEB MAKARFI yanzu baya Nigeria Amma Yana south Africa acan yake zama sai KHALID MAKARFI sukadaine yayanta so gskia yakamata kusan yan uwanku shiyasama dole ku koma gurin ummyn sbd abubuwa ma da yawa kamar wannan din.

#mamuh.

KU nunamin qaunarku ta hanyar dannamin subscribe @lafazitv□□□□

https://youtu.be/MJxY0y_SrOc

Littafin QAUNARMU na kudi ne akan naira 200 kacal.

Katura kudinka zuwa wannan account din...

2260792279

Maryam sani

Zenith Bank

Ka tura shedan biyanka ga wannan numbern

07067124863

Kokuma katura katin wayarka zuwa wannan numbern

.0903 234 5899*_ZAFAFA BIYAR NA KUDINE KA NEMI WAINNAN NUMBERS DIN KA BIYA KA KARANTA CIKIN AMINCI_*

07067124863

OR

09032345899

2

cigaba da cin abincin fifi tayi tana sauraran hirar su batace uffan ba da dan sauri take dan tuttura abincin tana lura da time,tana aje fork jakarta ta soma jawowa a

gurguje ta mike tsaye tace dady pls can i go now?waaro idanun sa waje yay,a shagwabe tace pls,se ya rankwafo kai yana kallon ta kamar me tunanin wani abu can yace emmm not until u give ne a hug,da yar dariyar ta ta taho ta rungume sa sosai yana me sakar mata murmushi cikin tsananin nuna kulawar sa yace akula ok? tace ok bye..dad i love u..bai amsa ba wani irin kallon kauna me fallasa tsananin so yake biyota da shi.. taku dayan biyu tayi sai ta juyo kamar wanda aka tsakure ta tace,"hamee?dago kai hamida tayi ta bita da sassanyar murmushi me ciwon datake jin shi har can kasar zuciar ta.."tace natafi schl..bye..Gyada kai Hameeda tayi Bata ce uffan ba ta mayar mata da murmushi

Me dan fadi..

tun kan ta maida kallon ta kan dinninh table taga dady shima yana shirin mikewa da alaman zai bar wajen cike da mamaki tace"dady har ka koshi?yace yes dear dama na zauna ne sabida mufida ta samu ta ci abinci,u go ahead ni zanje daki..

murmushin karfin hali ta kwakwalo tace ok Nan ya wuce ya haura sama tayi jugum tana bin bayan sa da kallo

In akwai abunda yake mata ciwo bai

Wuce wannan yanayin datake shiga ciki,nobody have her time,rabon dady yay zama na musamman akan dining table domin ta ita kadai bazata iya tunawa..."oh Allah its always about fifi nikam ko oho..wani lumshe idanun tayi hade da sauke nannauyan ajiyan zuciya can ta mike tayi wicewar ta daki..

Classic bentley stance code shiya sauke ta a kofar makarantar su batare da ta maida hanklin ta kan kowa ba ta haura fifth floor inda ake gabatar da practical din sun

Ta riga da tayi lattin mintuna talatin amma dake ta saba da halin ta na creating drama so tana bude kofar ajin tayi lumui cikin sanda tace hey guys,"anan kusan duka ajin suka juyo suka kalle ta,ganib hakan ya sata ta boye fuskanta ta tana toshe bakin ta ridicoliusly.

Kawarta maheeda ce ta watsa mata harara tana mata alaman shushhhh da hannu..kwabe fuska tayi a shashance tana duban lecturer da sauran daliban da duk suka tsura mata ido tace sorry tazo ta wuce sadaf sadaf ta nemi waje ta tsaya,sauke ajiyan zucia lab co-odinator yayi yace "and that was mufida mande, now lets get back to business. ,jin haka wani dariya ne ya kufce mata inda hanklin kowa ya sake dawo kan ta tun kan malamin sun yy magana ta mike tsaye ta rike kunnen ta kamar marainiya tana cewa sorry sir..rasa abun cewa yyi yana girgiza kai ya rasa ta meyasa fifi taki sa seriousness arayuwan ta

" ya bita da hararar jan kunne yace sit down,tana xama kuwa ta fashe da dariya duk ajin suma suka dauka da dariyar.

Wani hakurin ta sake bayarwa wannan karon da kyar dai aka agama practical din nan tare da ita cikin lumana...

Khadijat mufida nuhu mande,itace dalibar data fi kowa kokari a set dinsu duk dama bata dauki duniyar nan abakin komai ba,rayuwar ta kawai takeyi bata taba tsaurara tsanani akan dukkan lamarin ta ba.

Duk abunda xai bata nishadi da jin dadin rayuwa bata wasa da shi,great sense of humourn ta wajen iya mu'amala da mutane ya sa kusan kowani dalibi a makarntar ya san da zaman ta.

"Fifi mande" shine nick name din da kowa yake kiranta da shi tun suna shekarar su na farko,sosai sunan ya zaga ko ina in baka san ta dan wani abu ba dole zaka san ta dan wani abun dan duk inda shakatawa dajin dadin rayuwa yake to ita ne akan gaba

Aguje take biyo maheeda abaya dake tafiyar ta cikin masifa tana kukkuni

Mahee..maheeda pls now,juyowa maheeda tayi a masife Tace da Allah malama dakata min

Sau nawa na kira wayar ki?

Tace sau takwas..

Wani angry face maheeda ta sa tace and?...

matsowa kusa da ita tayi ta kama cheeks din ta tana mata murmushi tace and dady ne ya jawo komai wallahy...kinsan wani abu mahee?

Maheeda dake mugun son jin gulma tace what?..yatsinawa fifi tayi cikin iya zolaya tace nothing..in kina son ji ki biyo ni cike da takun ta na rigima ta wice gaba maheeda taja tsuka ta shiga biyo bayan ta..

Hadadden student cofee stall ta nufa nan take tayi odering kofuna biyu na shayin dayafi kowanne jin kayan hadi da dadi da tsada..

suna sha suna yar hirar su ahaka basa yin minti 10 batare da wani ko wata ta katse su da gaisuwa ba

dake mufida kusan favourite din kowa ne a makarantar so duk inda ta xauna sekaga mutane suna son mata magana in one way or the other,wani ajiyayyan numfashi ta saki tace wa maheeda gurl friend saura kwana nawa mugama karatun nan ma?Mahee ta yatsina idanun ta ta zuki shayin ta da alaman rashin kulawa,can tace 1 month i ques,wai meye ne zaki fada min kinsan na matsu inji kike ja min rai?..,dariya fifi tayi tace calm down dama nasan matsalar ki ai sarauniyar son jin gulma ..mahee tace whateva nan mufida ta matso kusa kamar me neman mata yar tsegumi tace ke maheeda ki shirya wannan karon ina so muyi abun da babu wanda ya taba yi a ranar graduation dinsa

Maheeda Tace kamar yay fa?

Tace i mean party ina son in hada babban get togher da ni da dukan abokai na amma kafin nan ina son muje yawon

Shakatawa ina son sauran ragowar college time dina ya zamto wanda bazan taba mancewa da shi arayuwata ba

..Maheee ta ce ehem?karatun fa?tace ohhh mance da wannan zamuyi catch up,.mahee dagaske nake miki

I want to go wild maheeda tace ure alwys wild,tayi kwafa ta maida bayan ta kan kujeran cikin dauke numfashi tace wannan karon ina nufin"wildest"..

Mahee tace hmmm to me kike shirya mana ne haka? shiru tayi sanda ta karashe shanye shayin ta tas sannan tace alot. Starting from today?..maheeda ta dan dube ta tace and hamida?

Tace oho wallhy bansan ko zata amince ba amma zan tabo ta inji,tace i hope she did nan suka gama yar hirarrakin su suka watse kowa ta nufi gida

Kafin satin ya kare ita da kawarta maheeda da meena yar gidan dr fatima yonas datake daukar ta kamar yar uwan ta da duk sauran gang na friends din ta suka taru suka harhada

Nau'i nau'i na shirye shiryen yadda zasu more rayuwar su a cikin wayannan kwanaki.

Ameed dake shi doctor ne so bai ciika samun lokacin kansa ba amma da shike yana matukar kaunar fifi hakan ya kukkusa ya mata alkwarin samun kulawar sa a dukkan wayannan kwanakin

Fifi tana sane da cewa zasu bar germany zuwa nigeria maybe na har abada amma se ta barshi aranta batare da ta nuna ma kawayen ta ba

 bayan tawainiyar ta hameeda da dad dinsu dr fatima ce da yayan ta Ameed da meena suke da masaniya akan tafiyar sun ahakan ma tanajin dan babu yadda ta iya ne,aranta ji take kamar in ta rabu da germany hala tayi tafiyar karshe kenan na har abada waya sani ko ma a nigeria zata mutu.

Tun daga lokacin takanyi abune ta inda kowa zaiji matukar nishadin wanda tasan hala bazasu taba mancewa da hakan aransu ba..

A karo na farko suka shirya fita su biyar yan mata maheeda meena harda hameeda da wasu kyafaffun yan mata guda biyu wato yesmin da arsala dukan su kowa tanajan sport car kaloli mabanbanta

Awani katafaren resort suka sauka ita da kawayen shakawatan nata All girls out so basu gayyaci wani namiji ba

ita yesmin yar gidan wani turkish tycoon ce arsala kuma brazillian ce gaba daya baya

Daga yanayin dressing dinsu zakasan suna matukar ji da wani abu waishi kyau kyaun jiki da asalin wayewa na iya kwalliya da daukar wanka uwa uba dukiya da wadata

Dukan su sanye suke da crazy jeans da brigt colour tops

Da manyan manyan sun glasses hannun su dauke da jakunan rataya na bvlgari wayayoin su masu tsadan gaske

saidai iya kokari sunyi wajen lullube kawunan su da muflers wasu da kananan veils wasu da hoodie ta inda da kaci karo da su dole zaka san cewa sudin musulmai ne

Kowaccen su ta sha kwalliyar ta na kece raini amma banda hameeda dake sanye da Egyptian jallabiya da pure red veil tayi roling kamar wacce ta fito masallaci

Tun suna gida da ta fito cikin nata haddenen shirin irin nasu fifi daddy ne ya umarceta data je ta sauya dresing dan dole.

Batayi musu ba tabi umarnin san amna Se ta ga mufida ta fito a kile amma bai ce mata uffan akan nata shigar ba and of course ta san bazai wuce dan yana gudun bata mata ranta ba ne

Hameeda ita ta fito odd a cikin su tayi daban sekace dukkan wajen ta girme su,shiru shiru zaka ganta kamar wacce bata da nacewa amma azahirin gaskiya zuciyarta ya fara hura wata wutar da takejin hala nan gaba bazata iya sassaita shi ba

wani irin surutayya suke yi a tsakanin su wanda ya nuna tsananin shakuwa jin dadi da hadin kai

Amma zuciyar hameeda cike yake da sake sake ganin dukan hankalin kowa akan mufida yake,ita kam ma har mancewa da zamanta awajen akeyi,a duk sanda akayi abun dariya ita murmushin karfin hali takeyi

Abu daya yake damun hameeda acan kasan ranta amma bata son bayyana ma kowa dan bata san tana ina zata fara ba.

Shin su dady basa kaunar nata farincikin ne ko ita ba yar su bace rayayya kamar yar uwanta fifi?

Cikin Wannan tunanin ta tsunduma sosai har aka kammala outing din kowacce ta shiga motar ta bata san anayi ba.

Tuki takeyi ita kadai tamkar wacce gangan jikin ta ne kawai ke motsi hankalin ta ya nitsa ne wajen tuno da asalin ciwon dake cin zuciyarta a kullum yana mata zugi.

#mamuh*_ZAFAFA BIYAR NA KUDINE KA NEMI WAINNAN NUMBERS DIN KABIYA KA KARANTA CIKIN AMINCI_*

07067124863

OR

09032345899

3

Wannan cuta da yar uwarta mufida ke dauke da ita shiya kara rage kaifin kauna tsakanin ta da dukkan wani abu me samar mata da kwanciyar hankli da salama a zuciyar ta

Ta zama tamkar batacciya marar amfani a duniyar mutanen da ta dauke su jigo kuma babban madogara a rayuwa kaunar da duniya take nunawa yar uwarta mufidan wani abu ne wanda za"ace har ta mutu batasa ran zata ci karo da shi ba

Son da mahaifin su yake nuna mata na musamman ne mufida Allah yayi mata baiwar da tasan ita batasaka ran samun irinsa.

Bayan kyau kyaun jiki ilimi wayewa Allah sai ya kara mata muhibba da tsananin farinjini

Tun hamida batasan kanta ba Rayuwar ta ya kasance a karkashin inuwar yar uwata mufida kowa yakan nuna tasa fifikor a bayyane batare da sun lura da halin da zasu jefa ta aciki ba. ayanzu haka zuciyarta cike yake da kishi da kuma qaunar yar uwarta saidai abunda bata iya banbancewa ba shine wanne ne yafi yawa acikin ranta?

A kullum ta zauna cikin tunani takan raya aranta cewa

Tana matukar kaunar yar uwata mufida kuma tanajin tausayin ta aranta amma ayanzu hakan baida wani amfani awajen ta

A duk inda takai wajen kololuwar son ta nuna nata son da kulawar sai taga iyayen su da yan uwan su da dukkan kawayen su suna mata irin shi koma wanda ya fishi

Ta lura Babu abunda zatayi ta birge kuma ta sha kokarin kin son hakan ya zauna mata araina amma sai takasa.

Itama mutum ce me ra'ayin son jin dadin rayuwa,shakatawa da matukar son nuna wayewar ta a fili kamar yar uwanta Fifi sai dai babu wanda ya lura da hakan bare abata irin waccan kulawar

Kowa ya mance da cewa mintuna biyar ne mabanbanta a rayuwan mu,tunda ni da ita munyi zaman mahaifa guda kuma muka fito acikin uwa guda

Aka yanke mana cibiya rana guda aka saka mana suna a rana guda sannan aka shayar damu nonon uwa guda.

Yadda yar uwata mufida take tsananin son life haka nima nake matukar so araina

Na dade da burika irin na mufeeda musamman babban burin ta akan kalar mijin data ke so tayi rayuwarta dashi wato namiji kamar ameed dan gayu me karancn shekaru young,rich,kyakkwa me aji mai ginannen jiki wanda ya kwarance a iya rayuwa da soyayya.

Zai kasance kamar ita ko kuma wanda ya fita da karancin shekaru wanda baifi uku zuwa biyar ba

Cikin sakin dogon numfashi ta rage gudun motar ta data keja ta danna horn abakin katafaren gate din gidan su tayi parking ta tattari yar jakan ta ta shiga ciki

Asalin damuwarta baifi tsoron meyene zata samu anan gaba wanda yar uwarta ta baxata rabata da shi ba

Sallama tayi ranta cike da kuncin hakan aranta mahaifin su dake zaune batare da ya dago kai ba yace wa'aliksam,bata karasa ba ya katse ta da cewa mufida kece? murmushin karfin hali tayi tace a'a hamida ce nan ya dago idanun sa yana me mata kallo mai kama dana tuhuma da tambayar ina ta bar yar uwarta mufida?

Hamida tace suna tare da kawayen ta amma tare muka kamo hanyar gida,yace meyesa zaki barta ita kadai baki da hankali ne call her now,yanayin yadda ya bata rai yasa Da sauri ta shiga dialing number mufidan yay ringing har sau biyu amma ba a daga ba...kasa cewa komai tayi ta tsaya tana kallon dady

ita kanta bata ji dadin yadda dadyn ya nuna rashin gamsuwar sa ba

Iya bayani ta masa kuma tasan ya fita sanin kalula irin na fifi,ta rasa meyasa ake yawan son nuna mata abunda bata fiye gane yuwar adalcin sa ba

Kowa yasan fifi tana rayuwar ta ne akan dokokin ta,she does what she feel like a lokacin da taga ya mata.. kuma banga lefin ta ba tunda su suka dora mata dukkanin gata da sakalci,sam basa iya mata fada kosu ce mata bari duk dan gudun kar ranta ya baci.

To meye ne nawa aciki shine ban fahimta ba.

sallamar ta ne ya dakatar da su gaba daya atare suka juyo suka tsura mata idanu,wani rau fifi tayi da idanun ta tana me aje jakarta akan table da dan sauri ta taho jikin dadyn su ta fada tana me dora kanta akan cinyoyin sa cikin sakaltaccen shagwaba cikin sanyin murya

"agafarce ni nayi latti ko?Girgiza kai daddy yyi ya dan shafa kanta cikin tsananin nuna kulawar sa tamkar ba shine yake shirin nuna damuwar sa akan rashin dawowarta yanzu ba

..shiru hamida tayi tana kallon su cikin tuno da Allah me kyautar kunci,ya dada ma kuma dole kace ka gode...

shiru me cike da tarairaya shi ya ratsasu hamida kuwa na cigaba da kwantar da wuyarta sulalewa tayi ta barsu awajen har takai bedroom din ta baxata iya bada tabbacin sun san ma tayi hakan ba

Haka rayuwar take tafiya a dadi babu dadi lamarin fifi da kawayen ta da dr ameed kai da gaba daya duniyar ma bai sauya ba

Wani abun ma gaba gaba yake yi musamnan tsakanin ameed da fifi inda yake nuna mata kulawar sa cikin tsananin nuna soyayayar sa agareta ita kuma fifi tana daukar sa ne a matsayin dan uwa kuma babban aboki

Rayuwar su atare gwanin ban sha'awa ce,"duk sa'in da suke tare sukanyi wasu abubuwan da in ka gansu ido da ido zaka ji ina ma inama kaine...

Hamida ma hakan takeji aranta dan ameed irin kalar mazan datake buri arayuwarta ne wanda anan ma yar uwanta fifi tayi mata fintinkau a zuciyar sa

Bayan windown hamida ne kawai agidan yake da lovely moonlight reflection kuma balcony ne ata kasan shi me dan fadi yana da step step na takawa

dake ba a ma yawan biyewa ta wajen akan iya zama akai a huta in waje yay sanyi

Hamida takanji matukar son tana kasancewa anan musamman can cikin dare dan ta dinga samun nitsuwa da daidaituwar tunani

Amma da ta doshi hanyar wajen sai ta shiga tuno da lokacin da ta same fifi da ameed sun jeru kafada da kafada suna kallon hasken wata suna hirar su irin ta masoya..

This is also her dream,and mufida is living it right behind her window.

Yawu ta hade tare da cewa hmmmm ta wuce dakin ta ta rufe kanta da damuwa ita kadai take mirginawa akan gadon ta,can ta mike tsaye ta bude right hand drawa ta dau wani tsohon family album ta xauna tana kallo

Tasan kwata kwata Basu wani jima da mahaifiyar su araye ba amma haka kawai takanji kewar ta da azaban kaunarta aranta duk dama tana harsashen da itama tana raye hala mufida zata zaba ba ita ba.

Cigaba da kare ma hotunan kallo takeyi tana dan shafawa da yatsun ta cikin wani irin yanayi me tafe da ssanyar sanyin zuciya.

Tabbas Mahaifiyar su kyakyawiyar mace ce kyaun ta da kalar fatar ta duk suka debo amma da alama mufida ta hada kamannin fuskn ta har dana kakar su hajja dan tafi su doguwar karan hanci da cikar suman gaban goshi

Kamar yadda mahaifin su yake da lotsawar gefen kunci na dimples haka ma mahaifiyar su take da su saidai na daddy a gefe daya ne na maman su kuma a duka site biyu

Nan ma fifi ce ta dauko kamanni mai kyaun ciki wato na mamar mu,nikuma dimple dina a site daya yake nunawa irin na daddyn mu.

Ta dade a kwance da hotunan agaban ta tana kallo cike da admiring wani karamin abun hannun winston diamond bracelet dake makale a hannun mahaifiyar su wanda yayi matukar daukar hanklin ta ya kuma shige ranta

Tasan ba komai bane awajen mahaifin su dan ya siya mata irin sa amma aranta so take abata shi kamar kyauta irin wanda zata sa arai taji tana matukar daraja shi in ta tuno shi.

Kasa kasa take sauke nishin gajiya da jin bacci can ta rufe album din ta maidasa maxaunin sa nan ta koma kan katifar ta ta nitsu jim kadan bacci yayi awon gaba da ita

Washe gari Ayanayin da bata son ta farkawa ta tsinci kanta

zagaye da duk wani yanayi dake dasa mata damuwa da jin kishin yar uwan ta fifi.

Ita kuwa fifi bata damu da komai ba hasalima babu damuwar komai aranta ayanzu face tsananin son mahaifin ta da yar uwan ta da zuciyarta yake wuni aciki kullum

Kamar yadda take bukata so tuni ta bude Babban shagalin enjoyn life ita da kawayen ta su na more rayuwar su yadda ya kamata.

Anan germany fifi bata da wasu shakikan kawayen da suka fi mata meena da maheeda

In tana gida kullum Meena na makale da ita dake dama su makwafta ne kuma kamar yan uwan juna suke ayanzu

Mahaifiyar su dr fatima yonas itama ba baya bace wajen nuna fifiko musamman wajen kulawa da lpyar mufida,sau dayawa in wani abu ya faru zakaga da ita da yaranta ameed da meena sun daga hankalin su matuka tamkar babu wani banbanci wajen kasancewar su jini daya.

Dr F.yonas ta kasance uwa kuma garkuwa agare su duka duk dama a hakan yanayin yake tafiya tsakanin rayuwar mufida da tawainiyarta hameeda.

Shiri ake yi sosai na komawar su nigeria

 a kullum kakar su hajja da yayar ddyn su ammy sukan so su bugo waya ko dan adada jadadda musu ranar gamawar su karatu

Ana washe gari zasu gama angama shirya musu komin su an kikkimtsa

To kowa ya kasance cikin farinciki amma banda hamida dake kokari wajen kawar da idanun ta akan abubuwan dake faruwa da ma wayan da suka gudana acikin yan kwanakin nan

Sosai aka bada fifi dama tayi shagalin ta,satin daya gabata ma ta hada wani kawataccen house party ita da abokan ta batare da an mata hani akan komai ba.

Dama duk mutumin da Allah ya axurta sa da abunda fifi take da shi na kyau ilimi da farinjini tabbas bazai taba rasa masu jin haushin sa ba,ciki kuwa har da ni yar uwan ta hamida

Duk da halayyar sakewa da maida komai ba komai ba irin na fifi ahakan takan samu sabani da yan matan ajin su

sau tari xasuyi ta daddaga kai ma juna wani bib har yakaiga ta jawo musu asara ankawo kararta gida wajen ddy

Saidai tunda nake ban taba jin mahaifin mu ya dau wani mataki ko ma yace xai mata fada ba.

Ranar da zasuyi exams na karshe daddy ya kasance cikin tsananin farinciki da nuna jn dadin sa a fili

dukan mu ranar ya hada ya mana addua amma muna iddawa suka fara nuna min yar hali

Kyaututtukar da aka yisu domina da wanda akayi domin mufida akwai kyaun bambanci.

Tabbas fifi ta fi hameda ilimi da samun jinjina da lambar yabo amma wajen sanya albarka akan kokarin su sanda dukanin dangi da yan uwa aka taru aka nuna ma hamida cewa nata nasaran kamar bakomai bane.

Abunda ya fiye ci mata baifi yadda ake nunawa a fili ba

Shiru shiru me nuni da alaman rasa gatan kuruciya shiya dulmuye hamida

Ta kasance a tsakanin su batacciya marar amfani sai dai in abun ya mata ciwo seta tsame kanta tayi nesa da su..

Ana washe gari tafiyar su mahaifin su ya biyo dakunan su cikin dare kowacce acikin su yana mata furucin nasiha da bankwana

Fannin hamida Kwata kwata befi tattaunar mintina talatin sukayi tsakanin ta da daddy a dakin ta ba

amma se ta ga tunda ya je dakin yar uwarta mufida ya dade yama kusa cin awa uku ahakn ma baisa ranan fitowa

Komawa room din ta tayi da sauri dake dama ta sauko ne ko zata samu smoothie me sanyi ta jika makwagoron ta

"Wayasan ko in anje nigeria wani abu zai sauya amma anya kuwa?ammy da hajja ma ba baya ba wajen nuna tsananin gata kulawa da kauna wa mufida,kikkimtsa kayayyakin ta ta cigaba da yi aranta tana me hoping komai ya zo da sauki acan.

Anan dkin fifi kuwa Bankwana me cike da kauna da tausayi shiya wakana tsakanin daddy inda tsabar nuna damuwar sa da son ta harji yake kamar da ransa zaiyi bankwana yama kasa fita a dakin daren ranan gaba daya ya kasa samun sukuni kanta ya dora akan kafar sa kwance akan cinyar sa tayi bacci

Sai Washe gari da safe ta shirya tsaf suka taho dinning yin kari a Tare suna saukowa hannun su sarkafe da juna

Sun samu hamida ma harta shirya kanta cikin wata turkish gown lavender purple tayi roling da golden veil tayi kyau sosai mufida kuwa dama ta fiye saka classic collection musamman white shirt da wandon falazon ta me fadi da tsayi yau kalar ja ta kwama tayi rolling da jan veil me tsantsi tayi kyau itama sosai

Confidently take takowa ata hannun daman dady akan takalmin ta na kamfanin gucci me da tudu dayan hannun ta rike da gucci side bag shima kalar takalmin ta.

Ko gaisawar kirki basuyi tsakanin su ba aka danna door bell inda duka hankalin su ya koma wajen dan ganin waye me shigowa

#MamuhKNM

https://www.youtube.com/channel/UCMylPCg0TCgTWAmy6HHvcEQ

Please SUBSCRIBE

4

cikin dauriya hamida ta taso ta taho har bakin kofar domin duba wanda yake wajen,tana budewa a tsaye taci karo da wani mutum Irin Mai bada sako gida gidan nan hannun sa dauke da manyan manyan akwatunan kyauta tare da mai gadi da security sun rakoshi

Kai tsaye Dagowa yay ya dubi hamida cikin harshen turanci yace mata good morning maam House no22 nuhu mande residence?

Ta gyada kai tace yes?

...nan ya mika mata biro ya umarce ta data sanya hannu a yar takardan su na register wanda yake nuni da isowar sako zuwaga maishi tana rantabawa ta mika masa tace thank you,security ne suka juya tare da shi

tsaye tayi tana me kare ma hadaddun akwatunan kyautar da aka killace su gwanin sha'awa agaban ta kallo

Saidai Tunanin abubuwan da suka wakana jiya da shekaran jiya dik su suka bijiro mata a zuciyarta inda take nazarin cewa kusan dukanin kyaututtukar data samu daga wajen su daddy da familyn dr fatima yonas bai wuce yan kayan sawa takalmi da katin gaisuwa irin na greeting card din nan ba

babu wani abu kwakkwara acikin kyaututtukan daya ya burge ta bare ma yaje mata har zuci

Amma Sanin yanayin yadda abubuwa suke a tsakanin ta da yar uwanta yasa a cikin yan kwanakin sai ta tsame kanta tayi gefe duk takurawar da fifi tayi mata akan su bude nata kyautattukar a tare haka taki fir

Aranta ba wani abu mai wuya bane iya cin karo da abubuwan da take so a cikin kyautattukar da fifi ta samu wanda ita ba'a bata ba kuma tasan hakan zai iya jefa ta cikin wani mummunan hali

Ayanzu Tana so ne hankalin ta ya dan dawo jikin ta kafin su isa nigeria tunda bawai sanin ya kasar dazasujen yake ba

A Labari kawai sukeji,bare ita da sau dayama daddyn sun ya taba gaya mata tarihin su waye ammy da yayan ta guda biyun da zasuje su tarar

Cikin wannan halin sake saken taji an dafo kafadun ta inda ta waigo cikin sauri da nitsuwa suna mai hade idanuwan su da yar uwarta tata cikin yanayin jefo tambaya a tsaye fifi take da alaman ta biyo bayan tane tace

Hamida Waye ne?

Tun kafin hamidar ta amsa idanun ta suka sauka akan tarin boxes dake gaban ta awajen

"cike da mamaki ta durkusa gabansu tace waw nawaye?waya kawo miki.. masha Allah..

Nan Hamida tai saurin cewa Bafa mani aka kawo ba

Mai bada sakone yazo shima bai gaya min komai ba sai dai in mun bude hala xamu gani

Nan fifi ta taimaka suka tarkato dukan su suka dauko box daya daya a hannun su suka shigo har gaban mahaifin su da shi saidai baice uffan ba har suka shiga budewa

Atare suka kai hannun kan wani dan madaidaicin katin da aka manno sakon tare da shi wanda sunsan dole anan ne zasu ga sunan wanda yayi sakon da wanda aka aiko ma

hamida ce tayi nasaran fara dora hannu ta akai dan haka ita ta dauki katin cikin warware makullin sa ta bude shi tsaf ta shiga karancewa

Sako ne me cike da nuna tsantsar so gata da kuma kauna wanda yayi mummunan fallasa girman irin kewar ta da za'ayi...

tsaban kalaman da aka rubuto sun tsaru cikin nitsatsiyar harshe mafi sanyayawa a cikin sassanyar yanayi hamida ta tsince kanta nan take ta shiga maimata kalaman ma zuciarta wanda yayi musabbin janyowa idanun ta cikowa da ruwan hawaye

Danne duk wani abun da takeji tayi ta karance har karshe,ina ma ace ko sau daya zata same irin wannan damar arayuwan ta

Waye zai so ta ya fifita itama ya turo mata wayannan kalmoni masu ma'ana wanda zai sa zuciyarta tayi saurin amincewa da cewa ita ma mutum ce wanda ta cancanci nuna kulawa da kauna

Duk yadda dadin kalaman suka karbu suka kuma sanyaya zuciyar ta suka ratsa ta hakan bai sauya mata jin komai ba dan kuwa babu sunan ta a jiki sunan yar uwan ta mufida ne Kenan sakonnin na mufida ne saidai bata ga sunan wanda ya aiko ba

Jiki a sanyaye ta mika mata batare da ta nuna yanayin data tsinci kanta na kishi da jin haushi akan fuskan ta ba.

Nan fifi ta amshe sakon tana kan tambayarta nawaye?wani shiru ne kawai ya ratsa wajen har fifin ta kammala karantawa dakanta ta dago idanuwan ta da zimman yin nazarin wanda zai iya aiko mata kyautar

charaf sai idanun ta suka sauka akan wani abu,shima a killace yake shikadai ana shi gidan a gurguje fifi ta dauko shi ta budeShi

Wani abun wuyar danyen dutsen safaya(saphiere)ne kalar sa ya shiga ja sosai yana faman sheki kamar asalin duwatsun diamond

Design din bana engine ko bugun kamfani ba bane asalin hannun kwarancewa ne ya tsara zaman zanen aka dedeta siffar duwatsun ta inda zaiyi matukar kyau wanda ko kallo daya bazai ishesa ba

Wannnan shine abun wuyar data gani a wani jaridar london times tace tana matukar sha'awar sa kuma tasan wa dady kawai ta nuna sukayi hirar kenan shi ya mata wannan sakon?tunda in ba shi ba babu wanda ta taba gaya ma wannan zancen

Daga yanayin yadda yay tsaye yana kokrin saka fuskn tausayi ta fahimci cewa tabbas shi din ne da wani irin gudu ta taho ta fada jikin sa ta saki wani irin kukan murna da tsananin kaunar sa

Tace. "Dukkan wayannan nawa ne? Nagode dady na Suna tayi dai hamida batace musu uffan ba

Wani shiru tayi agefe tana kallon su cikin tuno da Allah me kyautar kunci,..

Agaban ta mahaifin su ya tallafo fuskn fifin yana gaya mata maganganu masu dadin ji,yana me tabbatr mata cewa zai iya sallame dukan arzikin sa da komi nashi a duniya domin jin dadin ta da samun kwanciyar hankalin ta,kayan data sa ajikin ta kalar ja ne dan haka ta warware abun wuyar kamar zata kwama sai ta kuma ta fasa ta dawo tana kallon yar uwanta hamida dake kwakwulo murmushi da kyar

Da faffadan nurmushi fifi ta karaso wajen ta tana me damka mata abun wuyar tace hamida sakamin"ba musu hamida ta karbe,fifi tana ta surutun ta cikin bata labarin abunda ya wakana alokacin da sukayi hirar da daddy.

"Wani irin kishi da damuwa shi yake cin zuciar hamida amma ahakan ta daure ta shiga dannewa da tattausan lafazi tana amsata cikin sautin murmushin ta me fallasa tsananin kuna da ciwo

Warware abun wuyar tayi ta zago da shi a wuyar fifi tana malkaya mata last hook din abun wuyar,yadda ya xauna a wuyar fifin yay matukar kyau ya dada sawa takeji har can cikin ranta dama ace itace ta mallake sa..

Dauke kai tayi cikin sauke maganganun zuci a cikin dukkan tarin kyautattukan nan yanzu babu nata ko daya aciki?

Ta gama fahimtar cewa Bawai ana mata hakan dan ba'a son ta bane mancewa da ita akeyi agabanin farincikin yar uwan ta

Yaya zataji aranta me takeji duk babu wanda ya taba yin la'akari da hakan.

Zama sukayi dukan su suna cin abinci suna hirar ban kwana still wani shiru hamida tayi tana tura abincin bakin ta kadan kadan sakamakon rashin dadin sa datakeji abakin ta

Bayan sun gama sun fito zasu wuce nan ma su dr fatima yonas da yayan ta duka biyun suka tada nasu wasar inda gaba daya suka fi bada muhimmanci da kulawar su akan mufida,har hawaye sukayi ma juna alkwarin zasu na kirar ta sunyi shi yafi abun a kirga

10am na safiya suka isa aiport babban jirgin zirga zirga na kasan shiya kawo su nigeria aqashe garin ranan asabar karfe 2 na rana..

Kusan dukkan mutanen familyn sune suka zo tarban su,yayar baban su ammy khalid harma da kakar su hajja...

To Hamidar ce ta soma isowa garesu domin ta bar mufida acan baya tana famar tattara nata kayan.

Kallo daya ta musu ta gane su inda ta taho,nan suka tarbe ta da murna da fara'a ayayin da dukkan hankalin ta ita kuma ya koma kan kyakyawar hadadden namijin dake tare da su wanda take kyaun tsammanin cewa shine KHALID MAKARFI wato yaron ammy na biyu

zuciyarta ne ya shiga tsananin bugu ayayin da suka kalle juna suna masu sakar ma juna murmushi me sanyi

Su ammy da hajja kuwa sai tambayar ina fifi take?da alaman ita kawai suka fi so su gani so tsaban nuna zakuwar su da rawan jikin su ko hamidar ma bata iya samun damar nitsuwa ta amsa su dakyau ba

Haka kawai hamida taji khalid ya mugun dauke mata hankalin ta domin kuwa babu marabar sa da irin namijin data ke muradi a zuciar ta wanda takejin duk duniya da shi kawai zata ita rayuwar ta

Daga yanayin yadda suke satar kallon juna hajja tayi murmushi sbd Shi khalid dama yafi yayansa SAHEEB MAKARFI sakewa dason mu'amala da mutane Kuma gidan kaf yafisu rashin qyamar mutane yafisu fara'a da tausayi Dan komai na uwarsa ammy ya dauko

Sama sama suka gaisa da shi sai ya dan kawo Hannun sa zai karbe Troleyn hannun ta yana mikowa kamar daga sama yaji an wani tunkude sa a mugun razane ya dago kansa ya juyo inda yayi gamo da wata kyakyawar surar data dauke mai numfashi atake ta kuma tafiyar da shi sumewar tsaye yayi yana me tsura mata brown eyes dinsa cikin yanayin da ba sai ka tambaya ba

Hakika yasan yau yaci karo da muradin zuciyar sa

#Mamuh_*KNM*_

https://www.youtube.com/channel/UCMylPCg0TCgTWAmy6HHvcEQ

PLEASE SUBSCRIBE

5

Idanun sa kyar a kan wannan kyakyawar surar da ya zamo mai abu mafi haske tun tashin sa daga safe zuwa wannan lokaci..

Fifi kuwa Hankalin ta ba a kan sa yake ba sai kan yar'uwar ta mafi soyuwa a gare ta wacce ita kuma hamida gaba daya nata hankalin a kan na Khalid yake sakamakon taimakon da ya kawo mata wanda ita a zuciyar ta ji tayi kamar shima ya fahimci wani sirrin dake zuciyar ta ne da bai jima da darsuwa ba..

Da fara'ar ta cikin maido hankalin ta ga Hamida ta shiga daga mata hannu tana mata nuni alamar ta zo ta taimaka mata trolley din ta ya budu har kayan ta suna shiri zubewa ga kuma sauran tarkacen ta da take kan kwasowa daga jirgin..

Khalid dake daf da rike trolley din Hamida a hannun sa idanun sa gaba daya yakoma wannan kyakyawar surar rasa abin cewa yayi,yana iya fadawa zuciyar sa cewa tunda yake tunda yake mu'ammala da yan mata masu ji da kyawun fuska da kyawun dirir halitta bai taba dirar da idanun sa kan mace mai irin wannan surar ba,ba wai hasken ta ne ya rude sa ba a'a,tsantsar kyawun ta ne ya ja hankalin sa a haduwar idanun su na farko..

Hamida dake tsaye tana kallon ikon Allah ganin ita ce aka zo taimakawa da daukarwa kayan ta amma kuma an tsaya ana karema yar'uwar ta Mufida kallo,kallon da ko makaho ne ya san ba kallon da kowa kewa kowa bane,cikin wannan kallon akwai abubuwan fassarawa da dama sai dai in mutum bai da lura da la'akari akan abubuwa..

Ganin Hamida tayi tsaye ta kasa responding mata kuma har yanzu babu wanda yayi la'akari da zuwan ta sakamakon shigowar baya da ta yi kuma ba wani magana

tayi ba bare muryar ta ya ankarar da su cewa ta iso,shi kadai Khalid din ya san da zuwan ta acikin su sai hamida dake tsaye..

Maida dubar ta tayi ga Khalid din dan ganin wa ta buge a rashin sani nan take idanun ta ya sauka a kan kamanni jini da suke danyi da daddyn su..

Wani irin kallon karshe ta mai a kyau,idanun ta ko kiftawa basu yi ba ta ware su kyar a kan kyakyawar fuskar sa mai cike da abin kallo dan kuwa wannan kallo nasa da tayi babu abin da ya fado mata fiye da mijin dake cikin mafarkin ta..

Ba taba ganin khalid tayi ba sai yanzu amma da ganin haduwar sa ta ji wani bakon abu ya ziyarci zuciyar ta wanda bata san menene shi ba amma ta san akwai wani abu da yake rubutacce da zai faru a tsakanin su nan kusa ko anjima..

Magana ne ya fito masa ba tare da ya san ya fito ba hakan ya faru ne sakamakon wani abu da ya rinƙa tsikarar sa wanda bai san menene ba..

"Mu...fffida"!?ya kira sunan da sigar tambaya dan ya tabbatar ko ita din ce sai tayi mamakin yadda ya san sunan ta dan ita ba sanin sa tayi ba sai dai kiran sunan nata da yayi ya nuna mata ya san ta din ne..

Tun kafin ta amsa mai Ammy ta juyo gabadaya tana mai son tabbatarwa kan ta da gaske mai sunan da aka kira din ce ba gizo kunnuwar ta ke mata ba,a yayin da ta juyo din a wannan lokacin Hajja ta juyo itama..

Fuskantar juna da suka yi ne ya tabbatar mata da wadannan sune mutanin da take hira da su a waya kuma take kirgawa a matsayin nata na jinin ta,tana iya cewa bayan soyayyar mahaifin ta da na yar'uwar ta da take da shi a zuciyar ta,toh tabbas soyayyar wadannan mutanin ne ya biyo baya dan bata taso da sanin su ba amma muryoyin su ya saka mata kaunar su a zuciyar ta..

Wani irin runguma Ammy ta ma Mufida wacce ke tsaye tana kallon yar uwar ta dake ganin wani sabuwar shafi da babin tsaka mai wuya dake shirin tunkarar ta a nan Nigeria din..

Hajja ce ta matso kusa da su Ammy cikin farinciki da nuna tsantsar jin dadin ganin jikar ta mafi kusanci da zuciyar ta kuma takwarar ta wacce tausayin ta ne ya rikide ya dawo so da kauna a zuciyar ta..

"Mufida tah matso in gan ki in rike ki in rungume ki ko zan sami natsuwar zuciya,tun safe nake zullumin zuwar ku hankali na bai kwanta ba sai da na ji jirgin ku ya iso a yanzu kuma nake kara samin sukuni da na gan ki da idanuwa na,ban yi tsammani ba amma Allah ya ara min tsawon rai rabo na da ke tun kina jinjirar ki sai yanzu"..

Ihu zata fasa ko barin wurin zata yi ta koma cikin jirgin ya maida ta germany,rasa abin yi tayi,yanzu har a nan din ma babu wanda zai nuna ya san da ita bare ya nuna mata damuwar sa a kan ta bare a kai ga ana ririta ta ana tambayar ta nata lafiyar da rayuwar,a yanzu din ma still fifi ce ba ita ba?..

Take wani irin mugun tsana da kiyayya ya taso mata wanda a kan yar uwar ta duk wadannan abubuwan suka ta'allaka,ita shikenan haka tata rayuwar zata cigaba da tafiya..

Bata ida tunanin zucin ba ta ji su suna fadin Mufida zo mu tafi mun san kin kwaso gajiya ga yunwa...

Tun da Hamida take bata taba sanin tana da wani mummunar fanni a zuciyar ta mai karfi da yake kamar ya rinjayi daya kyakyawar fannin zuciyar ta ba sai yanzu dan kasa rike hawayen ta tayi sai da suka fito kuma ta kasa goge su sai juyawa da tayi ta basu baya tana mai warware nadin mayafin da tayi a kan ta dan ya taimaka wurin boye halin da ta shiga...

Yanzu Tsakani da Allah duk cikin su babu wanda zai tuna da wata wai Hamida? duk hankalin su na a kan Mufida kamar ita kadai ce mutum daya cikin zuri'ar su...

Kasa natsuwa Khalid yayi dan ba karamin dauke mai hankali fifi tayi ba musamman ganin irin shigar ta da yadda ta rinka exchanging tambayoyin da ake mata hakan ya bashi tabbacin ita din kamar shi ne

wato mace ce mai son rayuwa da faram faram bata da dagon kai da daukaka kan ta fiye da wasu halittun...

Tun a nan airport din Khalid ya sallamarwa kan sa ya sami abokiyar tafiya dan da alama ba iya son life kadai take da shi ba wanda shima yake da shi ba,hatta wasu dabi'un ta yana ganin zai zo iri daya da nasa dan haka ya dada saukar da kan sa fiye da yadda ya saba yi a cikin family din su...

Baki daya sun juya da zumar shigewa mota dan su kai gida fifi ta huta,shaf sun manta da Hamida har aka gama kwashe kayan fifi aka saka cikin booth itama zata shige ciki amma ganin kamar babu mutum daya cikin su sai ta tsaya ta hau dube dube

A nan cikin motar kuwa Ammy ce ke kiran sunan fifi akan ta shigo su tafi amma hankalin ta na ga yar uwar ta da ta hango ta chan tsaye..

Karasawa tayi gare ta ta dafo kafadar ta cikin farin ciki game da yi mata magana cikin yanayin jin dadin da take ciki..

"Hamee kin ga yadda su Ammy da Hajja ke murnar ganin mu kuwa,zo mu tafi gida dan duk mu suke jira "murmushin yake Hamida tayi sakamakon gama sauraron zantukar yar uwantan na wai su Ammy da Hajja na murnar ganin su

bayan baro baro ita kadai suka nuna a matsayin nasu yayin da ita aka ware ta kamar ba tare suka zo duniyar da ita mafi soyuwar nasu ba...

Kamar ba zata juyo ba sai daga baya ta juyo da murmushin da ya fi kuka ciwo zuciyar ta kuwa shake yake da kiyayyar yar uwar nata da take ma kallon katanga ce ma farincikin ta dan bayan ta karbe zuciyar daddyn su da na Ammy da Hajja har wanda take ganin Allah ya kawo mata shi shima fifi ta dauko hanyar kwace mata shi

Shin wai ita laifin me tayi ne da babu masu son ta da damuwa da ita ne?

menene aibun ta da bata samin kulawar kowa sai yar uwar ta kadai ke samu,shin ita a haka zata yi ta rayuwa komai nata fifi na samin sa ba tare da ta nema ba?..

Hankalin ta kamar baya jikin ta haka ta rinka bin bayan fifi har suka zo wurin motar wanda sai a sannan Ammy ta tuno da Hamidar amadadin ta ji wani iri ko damuwa batayi ba sai ta ce..

"Wai dama Hamida baki shigo cikin motar bane kika tsaya a waje kamar ba jinin ki kika hadu da su ba?..wannan tambayar ta Ammy ta kara tabbatarwa Hamida shikenan wani bakin cikin zata kuma fadawa ciki bayan wanda ta baro a germany...

Gyada kai kawai Hamida ta iya yi ta shige cikin motar ta zauna a kujerar baya yayin da fifi ta shiga na gaba,da so samu ne daga Ammy har Hajja so suka yi fifi ce a nan inda Hamida take amma ganin kamar ita ce ke muradin zama nan kusa Khalid sai suka bar ta dan kar su saka ta yawar magana...

Wani abin bakin cikin da ya sa Hamida jin zaman motar ya gundire ta taji ta matsu su zo gidan ta kebe ko zata sami sanyin zuciya shine,ita ce a tare da su a bayan seat din motar amma kaf hankalin su na a kan fifin ne

kowa sai son nuna mata so da kauna yake yi ta hanyar tambayar ta akan karatun ta,akan raywarta akan lpyarta a nan kusa da fifi kuma Khalid ne yake ta sakar mata murmushi yana nuna mata kulawar sa shima ta hanyar tambayar ta "if she will be comfortable da zaman nigeria din...

A haka har suka iso babbar gidan dake dauke da different parts ginin duplex mai ban sha'awa saboda tsarin da aka yi ma gidan kadai abin a zo a gani ne,wannan gini ya sa fifi kasa boye kyawun da gidan ya mata ta fitar da shi ta hanyar furta

"Wow,nice house"nan take kuma aka maida hankali hade da ba maganar nata muhimmanci..

Sai nan nan ake ta yi da ita har suka shiga daga cikin gidan inda nan ma wata duniyar ce abin kallo,mai aiki aka kirawo akan ta zo ta kwaso kayan fifi dake booth dan a kai mata wata killatacciyar dakin da aka gyare sa musamman saboda ita nan kusa da na Ammy da site din hajja..

Ana shigo da kayan ne Hamida dake tsaya a matsayin batacciya tayi ta kallon su har suka gama shigewa da kayayyakin fifi ciki

Khalid ne ya fito dan gyara parking din motar sa sai a sannan ya ankara da Hamida...

Yace."Ohh no"da dan sauri ya karaso gare ta yana furta

"Hamida ki yafe ni ban nuna maki hanya zuwa ciki ba ko?kiyi hakr yar uwar kin nan is so attractive,waidama dagaske ku yan biyu ne?dana ganta hankali na duk ya koma gare ta shi yasa na manta in nuna maki hanyar shiga cikin gida im deeply sorry"..

Wani fushi me hade da Faduwar gaba ne ya riske ta toh me yake nufi da yar uwar ita is attractive kuma?mswww fifi fifi fifi and ffi again,ji tayi kamar ta rufe idanun ta ta bude ta ga bata nan cikin gidan...

Janyo mata trolley din ta yayi zuwa ciki yana mai dan jan ta da hira,gabadaya zuciyar ta na ayyana mata cewa kar ta sake Khalid ya kufce mata sabida fifi wannan kuma nata ne ba zata barwa Mufida shi ba,dan duk cikin su shi kadai ya dan nuna ma ya san da ita...

Wani babbar bacin rai dataci karo da shi kuma shine ganin hanyar dakin da aka kai ta nan kusa da wani new abandoned room da yake shiru shiru kamar babu kowa sai ita kadai...

Dannewa haushin ta tayi Bayan ta mai godiya garin boye damuwar tane yasa tayi saurin rufe kofar dakin da key ta jingina bayan ta da kofar tana mai sauke nannauyar ajiyar zuciya akai akai wasu zafafab hawayen kunci na diga,jin kamar zuciyar ta zai fashe at any moment ya sa ta dauko karamar jakar ta ta hau lalubar maganin da Dr Fatima Yonas ta bata wanda dama kullum in ta tafi ta fadi mata

damuwar ta shi take bata ta sha,bude robar maganin tayi ta zuba guda biyu ta hau nemar bottle water din da ta sha a jirgi ta rage,tana ganin sa ta bude bakin murfin ta jefo maganin ta bi da ruwa...

Gadon dake gyare a dakin ta hau ta kwanta a kai idanun ta na kallon gefe daya hawaye na silalo mata har bacci ya dauke ta bata sani ba.

#Mamuh*_Mamuhgee_*

*Zafafa biyar na kudine ka nemi wannan numbern ka biya kudinka ko katinka*

07067124863

09032345899

6

A nan fannin su Fifi tunda ta shigo cikin dakin nata da ya sha kayan alatu taji sam takasa zama dan tamkar wata sarauniya haka aka tsantsara mata dakin sai da ta karewa dakin kallo ta yaba kyaun sa hade da maimaita kalmar "_wow cancadi"_.

Cire kayan jikin nata tayi ta nufi hanyar bandaki dan watsa ruwa,nan ma duk abubuwan bukata an tanadar mata wanda diya mace da ta amsa sunan ta mace yar gata ke alfahari da shi,haka tayi wankan a karkashin shower ta gama ta fito daure da fari kal din towel..

Sallah ta fara gabatarwa sannan ta hau kan kujerar gaban madubin ta,dama tayi tunanin jere cosmetics din ta gaban madubin ne amma zuwan ta dakin sai ta ga wadanda aka jere mata ma sun dame nata sun sha dan kuwa kaf babu cosmetics din da suka fito daga wani kamfanin kwalliya dake african

hatta jam baki da hoda duk products din La pariso ne daga kasar Persia hka komai suka fito ras dan a jeren su suke suffar su daban da na kasar nan..

Nan ma sai da ta yaba da kyaun koma ta kuma kara yarda da kaunar da ake mata a cikin zuri'ar nasu,lallai duk soyayyar da tayi tsammanin samun shi daga gare su ya wuce yadda ta tarar dan tun a wurin dauko su ta gasgata hakan..

Kwaliyyar ta ta cancanɗa mai daukar hankali dama akwai kyaun sai ga adon zamanin da ta dora a fuskar nata me sanyin haske..

Duk dakin nata ya gama amsawa da kamshin designers perfs din ta na matron daga haka ta saka suturar ta irin ta kullum bata canza ba wato shigar kananan kaya riga da wando ta kamfanin Dior sai ta dau kimono deep red ta dora a sama hade da saka head hoodies kalar rigar cikin da ta saka,flat foot wear ta saka ta dauko wayar ta cikin kazar kazar da karfin jiki ta fito da nufin tambayar inda yar uwar ta take..

Kicibis tayi da Khalid da shima fitowar sa kenan da zumar zuwa duba ta,anan suka shiga zagowa dan su hade a hanya wanda yake half way a balcony din gaban dakin hamida...

Dakatawa yayi ya tsaya kusan inch biyar da inda fifi take yana mata kallon da bai san yana yin sa ba

kwata kwata bai san yadda aka yi yake kasancewa a zauce ba musamman a duk lokacin da ya hada ido da ita...

Kasa karasowa kusa yayi yana tsaye ita kuma ganin sa sai da ya saukar mata da kasala domin kuwa white shaped long sleeves shirt ne a jikin sa mai two black straight line mai dauke da botara masu matukar tsada

wannan rigar ta shi ta bayyana asalin ginannen jijiyoyin muscles dinsa dan dama bai saka botins din duka ba ya bar na sama da mai bi mai a bude,kusan quarter daga sirrin faffadan kirjin sa a waje suke

ga wani irin glowing da haske da bared chest din nasa ke yi,kan sa ya sha gyara da mayuka har fiye dana dazu da ta gan sa..

Tace.."Ya rabbi"abin da ta furta kenan a zuciyar ta ganin kawai ya amsa sunan namijin da ta dade tana mafarkin mallaka a matsayin saurayi kuma miji a gare ta dan sak yanayin jikin sa bai da doguwar bambamci da Ameed abokin ta kuma dan Dr Fatima Yonas a germany...

Kasa boye abin dake zuciyar ta tayi kawai ta sanar da shi ya mata cikin sakin fuska dan ita bata iya boye abin da ya birge ta ko ya bata mata rai..

"You are looking good mr Khalid"

..wani dadi ya ji a ran sa yayi ado ta yaba dan dama dan ita yayi adon kuma kwalliya ta biya kudin sabulu data yaba,jin kan sa yayi kamar yau din rana ce ta musamman a gare sa...

Karasowa yayi gare ta yana mata murmushin manyan maza masu ji da kan su akan gabar su..

"Na gode Khadijatul Mufida"!ya fada hakan yana mai karkata kan sa wanda ita kuma ta ji kamar babu wanda ya iya furta sunan nata sama da shi

dan babu mai kiran sunan nata a haka gabadaya sai dai ko Mufida ko Fifi ko Fifi Mande..

Tambayar sa tayi inda yar uwar ta Hamida take,shi kan sa sai yanzu ya tuno da Hamidar sai ya mata jagora zuwa chan dakin Hamidar inda yake da doguwar tazarar gaske tsakanin matakakan dakin ta da na yar uwar nata..

Shi ya rinka yin sallama amma ba'a amsa ba kuma ya san bai gan ta ba a nan kasa tun bayan barin sa dakin da ya kawo ta mata kaya..

Kallon fifi yayi yana fada mata cewa hamida bata amsa ba sai fifin ta matso adame kusa da kofar ta mannu da nufin yin sallamar da kan ta, nan ma kamshin turaren tane ya kusan sumar da khalid a tsaye wani sanyin yanayi yaji wanda har cikin zuciyar sa yake jin dirinsa,bai san menene yake ji game da ita ba amma yana mutunta wannan abin ko ma menene shi...

Haka fifi ta rinka doka sallama wani na bin wani kusan sau hudu but babu amsa daga ciki,nazari tayi ta kira ta da pet name da ta saba kiran ta da shi koda zata gane itace dan haka ta hau kiran sunan _"Hamee"hamee,hamida_

Sai shiru nan ma duk haka bata sami amsa ba..

Da rashin jin dadi a fuskar ta ta juyo ta kalli Khalid da shi ba sunan Hamidar ko amsa sallamar ta ke gaban sa ba illa ita mai yin sallamar da kiran sunan wato ita kanta fifi..

Cikin matukar yanayin damuwa Tace hamida

"Bata amsa ba ko bacci take yi ne"?kallon ta yayi yana fadin.

"Kila baccin take yi"!!gyada kai tayi tana dan juyi tana dada kallon kofar daga haka har suka juya zuwa kasa nan main parlor din gidan inda a nan Mufida ta ga tsantsar gata dan abinci kala kala aka baza a babbar dardumar cin abinci duk dan saboda ita..

Farinciki ne ya buwayi zuciyar ta ta rasa ina zata saka kan ta da irin wannan soyayyar da ake nuna mata duk ita daya...

Ammy ce ta taso cikin fara'a ta tarbe ta tana mai yaba kyaun da tayi hade da yaba kamshin ta ita kuma ta rungume Ammyn tana fadin

"Ammy ai duk ke ce silar kyaun da nayi dan kaf kayayyakin dake gaban mirror din daki na ban taba ganin irin su ba ko da nayi amfani da su sai na ga ashe ni din bakuwa ce a fannin kayan ado,Ammy nagode da soyayyar ki gare ni na san ko da a

yau na mutu na bar duniya na ga masoya na kuma na yarda da kaunar da suke min suke kuma nuna min"!!

jin kalmar mutuwar da ta kira sai da Ammy ta ji bugun zuciyar ta ya dadu dan sam bata son jin wannan kalmar bare har ya kasance ya alakantu ne da fifi...

Dada rungume ta tayi tana danne hawayen dake kokarin fin karfin ta ya fito murya na rawa ta ce.

"A'a Mufida ta kidena cewa hakan ba zaki mutu ba har sai kin ga yayan ki,sai kin more su mu ma mun gan su,tare zaki rayu da yayan ki har girman su,da yardar mai rahama yayan ki ba zasu yi maraicin rashin uwa ba kamar yadda ke kika taso cikin ta ba Allah ya jikan mahaifiyar ki"..

Hajja da ta rigada ta ta fara hawaye tun bayan jin kalmar mutuwar da fifi tayi sai ta kasa hakura ta yi magana..

Tace"A'a Mufida ba yanzu zaki mutu ba kuma bana son kara jin kalmar nan ta fito daga bakin ki"..

Kallon ta fifi tayi ta kuma kallon Ammy da yanzu ta raba jiki da ita,ta kuma juyawa ta kalli Khalid da shima ya dan shiga wani yanayi sai ta basar da zancen duk da ta san ita din ba mai tsawon rai bane rayuwar ta mai iya datsewa ne any moment kuma ita so take ta saka murmushi a fuskokin kowa kafin ta rabu da su ba wai ta rinka saka su a damuwa ba,abaxata ta hau yin dariya tana fadin

"Ammy,Hajja, Khalid kun bani dariya,ashe haka kuke?wasa fah kawai nake maku dama gwada ku na yi dan in ga yawan son da kuke min kuma na gani,ta gwalo ido cikin wasa"sai dai Hajja ban gane miki bafa,fada min gaskiya hala dama kin matsu ne in tafi in baki wuri dan ki kwace min saurayi"?

da sigar tsokana tayi maganar..inda Duk ta saka su dariya ba kadan ba

duk da akwai kalmar rabuwar nan dai a wannan zancen nata but ta saka su nishadi..

Ganin duk sun sake ran su ya sa itama ta taya su dariyar har dai suka zazzauna aka hau serving nasu abinci..

Sosai fifi ta ci abincin dan ba zata iya tuno rabon ta da cin abincin gargajiya irin ta kasar ta Nigeria ba sai yanzu kuma da yake abincin da cikakkiyar soyayya aka bata shi sai ta ji kawai kaunar family din nata na kara ninkuwa a zuciyar ta fiye da da kafin ta san su in person..

Da suka gama cin abincin ne Khalid ya mata tayin fita zaga gari kafin dare,ai kuwa bata ja da tayin sa ba dan ita kan ta ta fi son haka,ko ba komai ta san zata fara ajiye tarihi da memories masu wuyar mantawa musanman tare da dan uwan ta kuma wani bangare na rayuwar ta wanda bata san ya zata fassara sa ba..

Da kazar kazar din ta ta tashi daga kan dardumar tana mai yi ma Ammy da Hajja godiyar saka ta jin ita din wata ce a gare su hade da yi masu sallamar sai sun dawo..

Sosai Hajja ta rinka gargadin Khalid akan kar ya kuskura yayi tukin ganganci da zai jijjiga jikin Mufida,shi dariya ma Hajjan ta bashi ganin yadda duk hankalin ta ya bi ya tashi akan kar a taba lafiyar takwarar ta,ita fifi in ta nata ne bata ki a yi ta rough driving din ba dan ta fi son hakan sbd ya fi dadi da saka annashuwa a gare ta a kuma zuciyar ta...

Juyawar su kenan da nufin fita Hamida ta bayyana a gaban su tana saukowa daga sama..

Tun daga kan babbar dardumar idanun ta ya nuna mata har an yi family lunch an gama kuma cikin nishadi aka yi sa dan ga yadda abinci ya barbarzu alamar mutani daban daban ke ba mutum daya abincin..

Babu inda hankalin ta ya kai sai ga fifi,wani abu ne ya taso ya tsaya mata a kirjin ta rasa abin yi tayi...

Idanun ta ne ya dawo kan yar uwar ta da mutumin da ta jima da mai masauki a zuciyar ta,bayan an gama cin lunch ba tare da ita ba yanzu kuma fita za'a yi ba tare da an damu da nemar ta ba...?

Idanun fifi ne ya sauka kan Hamida da ta tsaya cak a fourth to the last step ta kasa karasowa tsabar daurewar kan da ta tsinci kan ta a ciki...

"Hamee tun dazu nake ta nemar ki sai da fa Khalid ya zo ya nuna min dakin ki muka zo tare,kinyi bacci ne? munyi ta yin sallama baki amsa mu ba hope you are ok dan yanzu fita zamu yi ni da Khalid ya ce zai kai ni in zaga gari kafin dare,na san ba zaki taho ba ko na ce ki inaso dan haka mu sai mun dawo,go ahead am sure you will love the lunch da Ammy ta hada mana....na gargajiya ne mai dadi,just enjoy har mu dawo ok sis"!

karasa maganar tayi tana mai dan buga kafadar ta alamar comforting din ta take son yi cikin nuna tsananin damuwarta akan ta..

Hamida kuwa batace uffan ba

Bayan haka fifi ta juya ta fita Khalid na bin ta a baya suna magana kasa kasa suna dariya wanda ya kuma kunna wutar kiyayyar fifin a zuciyar Hamida...

Su Ammy dake daga cikin parlor din ne ta tsaya kare ma kallo,cikin kitsa maganganu ganin wai duk wannan abin da ya faru babu wanda ya lura da ita kuma ba a aika a kirawo ta ba haka suka ci abincin su cikin farinciki,ita kadai ce ake wa wariyar launin fata dan bata cancanci kaunar kowa daga cikin family members din nata ba,wannan bakin ciki da me yayi kama...?

Fasa saukowar tayi kawai ta koma dakin ta duk da haka bata sami natsuwar zuci ba sai kai kawo take ta yi a karshe zuciyar ta ya saka mata ta tafi dakin fifi dan ganin ko nan ma an nuna bambancin kamar ko da yaushe..

Fitowa tayi ta nufi hanyar babbar balcony din dake upstairs da nufin tambayar ma'aikatan gidan dakin fifi..

Tana tafe ta ga gilmawar wata sai tayi saurin kiran ta ta tambaye ta dakin Mufida ai kuwa ta kai ta har dakin inda da shigar ta ta ga abin da ya girgiza mata zuciya da ruhin ta dan in akwai aljannar duniya toh dakin fifi ya dace da wannan sunan...

Komai yayi ne kusan dukan abunda take muradi su aka zuba a dakin fifi abin nan ya sake tayar mata da hankali..

Danne damuwar ta tayi ta fita a dakin ta koma nata dakin,bata jin marmarin dandanar abincin gidan ma dan haka cookies din ta da ta zo da shi a jaka ta fiddo ta hau ci tana jin ciwo a zuciyar ta..

A haka tun tana dannewa kar tayi kukar bambancin da ake nuna mata har ta bar hawayen suka zubo,shaidan kam sai dada tunzira zuciyar ta yake yi ta rinka saƙe saƙe kala kala akan yar uwar nata daga baya ta dauko laptop din ta dan rage zugin da zuciyar ta ke mata dab wayar ta kam bai da amfanin komai dan in dai wai dan a kira ta ne dan jin ya take bayan ta bar kasar germany toh tasan yaudarar kan ta zata yi dan ba kiran nata za a yi ba

Ita kanta ta san izuwa yanzu favourite din kowa da kowa ta amsa kira ya fi sau a kirga daga saukar su hala har yanzu da suka fita da mutumin da take jin shi a zuciyar ta ma hakan ne...

Tunowa da yanayin farincikin da suka fita ciki dazu ya sa ta ji kamar ta masu mummunar addu'a amma haka ta daure ta maida idanun ta ga kallon da ba wani gane shi take yi ba dan hankalin nata ba a kan kallon yake ba...

#Mamuh*_Mamuhgee_*

*_zafafa biyar na kudine ka nemi wannan numbern ka biya kudinka ko katinka_*

07067124863

09032345899

7

fitar su agidan Khalid yafara tukinsa a hankali gudun kar ma wani ya gani aje a fadawa hajja,yana hawa kan titi ya kalli fifi ya ce da ita ta gyara zamanki da kyau yan mata zamu fara tukin mu ko?.. Murmushi suka maida ma juna

Ita a dadin ta dan dama hakan ta fi so,tun daga haka sai ya kara speed din motar yana tukin juye juye in yayi sai ya kalle ta ya ce speed din yayi sai ta girgiza kai suna dariya ahaka sai ya kara gudun,a haka a haka ya rinka kara speed har ya kure zuwa last speeding point din inda fifi sai ihun murna da dadi take ta yi dan tunowa takeyi da last drive din su a germany tare da kawayen ta.

Wurare da dama ya kai ta ya kuma bata dukkan lokacin sa cikin sukuni,bai yi rushing din ta ba komai a natse ya bar ta tayi,tun daga gidajen ganin kayan al'ajabi da aka bar su su bude a wannan lokacin dan har wuraren shakatawa sai da Khalid ya kai fifi kuma bai gajiya duk wani tambayar da zata mai akan abin da ta gani haka zai bata cikakkiyar amsa mai gamsarwa...

Su da suka ce zasu dawo kafin magrib sai gashi sai 7:24pm dai dai Khalid ya ja birkin motar da suka fita da shi.

Hannun sa cike da shopping bags da packaged eatery leathers duk na fifi Khalid dinne ya siyo mata dan kawai ya faranta mata..

Dawowar su yayi daidai da lekowar Hamida ta windown ta dan tun dazu ta damu tana ta duba lokaci tana leko window sabida bata ji muryar kowa cikin yan gidan ba,.

alama ne na cewa yar lelen tasu bata nan dan haka annurin gidan ma dole ya dauke na dan wucin gadi..

Tana kawo kan ta kuwa ta hango Khalid na bude ma fifi mota har fito tana mai dariya hannun sa ya saka a motar yana kwaso tsarabar outing din da suka futo..

Sosai hamida take ganin cikakken view din na duk abunda dake faruwa a nan farfajiyar gidan sakamakon hasken kwayayen lantarkin da ya dallare gidan ya haska ko ina..

Tsaye take tana kallon su wayar dake hannun ta ta dada damkewa dan saura kiris ya fado daga sama zuwa kasa kasa rike hawayen ta tayi kawai ta bar su suka rinka fitowa,babu murya bare wani reaction da tayi,wannan tsantsar hawayen bakin ciki da takaici ne ke bin fuskar ta wanda ya samo asali ne daga ciki cikin zuciyar ta..

Kasa cigaba tayi da kallon nasu kawai ta koma ciki hade da buga kofar window din wanda su kuma daga kasan suka ji karar bugun dan da karfi tayi kuma dama windown asalin metal ne mai kyaun gani da tsada..

A hanzarce duka suka dago kai suka dubi windown wanda babu alaman kowa,Kallon junan su suka yi suna mamakin wa zai aikata hakan?amma da yake abin dake gaban su ya fi karfin wannan yar hayaniyar sai suka cigaba da hirar su kamar ba gida daya zasu kwana su tashi ba..

"...Sai da aka fara kiran sallar isha'i sannan suka karasa ciki inda suka tarar da abinci shake saman dinning table alamar ba a ma ci abincin ba dan komai a shirye yake neat babu kowa,aranta tace kenan sun shiga yin sallar isha'i .

Murmushi tayi tana mai karbar wasu daga cikin kayayyakin nata shi kuma yana rike da wasu,haka ya raka ta har dakin ta ya ajiye mata kayan yana mai nuna mata kar tayi lattin fitowa dinner ta amsa ta hanyar gyada mai kai...

Bayan fitar sa ne ta sakawa kofar lock tawani daka tsalle da dariya dan yau is one of the best day da zata iya kirgawa na sakawa har cikin tarihin rayuwar ta

"kusan duk abubuwan da take bukatar sani a rayuwar Khalid din nata yau ta san kaso tamanin kuma ta san da sannu zata gama sanin sauran halayyar sa..

A tunanin ta da nazarin ta gaba kadan ita da Khalid din zasu yi sabon da ba a yi zato ba dan hallayar su kusan iri daya ne yadda take son morewa ta ji dadin rayuwa haka shima yake,ire iren suturun da take sha'awar sakawa shima haka ne..

Bata san ina zata saka kan ta dan tsananin farinciki da annashuwar da Khalid din ya saka ta ciki yau ba,mannewa tayi da jikin wardrobe din ta tana ta yiwa kan ta murmushi tana kara tuno awannin da suka gabata kafin yanzu..

Jin ana sallame salla ya sa tayi wuf ta shige toilet dan yin alwala dan dama ko magrib bata yi ba ga isha'i tayi har an idar...

Sai da tayi wanka ta kimtsa kan ta tayi sallolin nan ta fito ta nufi hanyar sashen yar uwar ta hamida dan ganin ya lafiyar ta yake dan a dazu da suka fita rabin hankalin ta na ga tunanin yar uwar tawainiyar ta

ganin yadda duk ta bi ta kasa sake jikin ta kamar ba cikin family din ta take ba abun na matukar damun fifi..

"....Tsayuwar ta da sallamar ta a bakin kofar dakin Hamida ya kai kusan mintuna biyar tana ta sallama da dan bubbuga kofar dakin amma ba a bude ba kuma ba wai dan ba a ji bane a'a kawai jin budewar ne kawai mai dakin bata jin yi..

Har fifi tagaji ta dubo number din Hamidar da zumar kiran ta aganin ta ko bacci take yi amma in ta ji karar wayar kila ta farka,sai kuma ta ga wani kiran ya shigo wayar ta,duba numbern tayi ta ga daddyn su ne dan haka cikin sauri ta daga kiran kuma a dai dai wannan lokacin ne aka bude kofar..

Ta karasa shiga dakin ne wayar na sagale a kunnen ta tana gaida daddyn nasu cikin shagwaba.

Ita dai Hamida tun da ta bude mata kofar ta koma ta zauna bisa sofa dake dakin bata kuma dago kan ta ta kalli Mufidar ba dan ta san wanda take wayar da shi ba kowa bane face daddyn su wanda ita ko digon missed call din sa bata sami arzikin samu ba..

Dadin mamakin Hamida shine lokacin da ta ji fifi tana cewa"Daddy ai gashi yanzu na daga kiran,dazu ma da ka kira muna tare ne da Khalid ya kai ni zagayan gari kuma ma ai daddy tun bayan saukowar mu in ban manta ba maganar mu da juna sau takwas fa ka kirani kenan and i have been ok tun dazu har yanz kadena damuwa kaji daddyna am fine wallhy...,ko ka manta tare da Ammy da Hajja da Khalid nake?duk fah cikin family nake sannan ga yar uwa ta abin alfahari na Hamida"

..dan shiru ne ya biyo bayan maganar da fifi tayi..

Hamida kan ta a kasa tana auna irin tsabar kiyayyar da ake mata a cikin ahalin ta kamar ba zama tare suka yi da Mufidar cikin cikin mahaifiyar su sannan aka haifo tare har suke rayuwa yau atare ba,ita ce ta zamo bare da ba a san tana raye ba?ko dai ta mace ne da har ba'a lura ba,8 calls daddyn su ya ma fifi ita tana nan tana ta jiran ganin kiran sa sau daya bai kira ba

even after seeing her 3 missed calls bai bi kiran ba sai fifi da ya kira ta har sau takwas..abun yanacin mata rai matuka

Waya ta ji a kunnen ta kuma shine ya ankarar da ita cewa a take muryar daddyn su ta ji yana ce mata

"Hamida ta yaya kuke?kina lura da yar uwanki kuwa? na ga kiran ki har uku amma bana kusa kuma da na dawo na gani sai nayi tunanin tare kuke da yar uwar ki dan haka na kira ta in ya so ita sai ta baki mu gaisa kawai,hamida tace hmmm.yace da fatar kema kina jin dadin gidan su Ammyn naku?murmushi mai ciwo tayi jin wai ashe ya ga missed calls din nata ma, amma bai biyo ta ba sai ya kira wacce ta fiye mai soyuwa a zuciyar sa sannan sai yanzu ne zaina tambayar ta akan jin dadin zaman gidan wanda in da zata sami dama da mutumin da ya cancanta toh da zata samar da shi irin rayuwar da ta fara ginawa a yan awannin da ta tsinci kan ta a ciki a cikin gidan da take ganin tana iya bugun kirji tayi alfahari da shi..

"Daddy komai alhamdulillah"iya kalmar da ya iya fitowa daga bakin ta kenan sai tayi shiru,ko me ya kuma ce mata sai ta mikowa fifi wayar tana tashi daga wurin dan bata muradin jin cigaban hirar tasu..

Sai da ta tabbatar sun gama sannan ta fito da fake face ta fuskanci fifin tana fadin

"So,ya outing din naku ya kasance"?ita kadai ta san karfin halin da tayi kafin tayi tambayar nan,tunanin ta kamar kullum fifi zata hau zayyano mata komai da ya faru ne dalla dalla sai dai yau ta ga akasin hakan

Dan fifi yi tayi kamar bata ji tambayar ba ita ta aiko mata da nata tambayar..

"Hameda meye ne wai ni kam, me ke faruwa da ke ne tun zuwar mu kasar nan? duk yanayin ki ya sauya kamar baki ji dadin tahowar mu ko dan nan kasar batamu bane ko?duk fah fara'ar ki ta dauke baki walwala hamida, baki sakin jikin ki dani na rasa gane maki Hamee

Please dan Allah ki sanar da ni damuwar ki kin ga duk duniyar nan baki da wata wacce zaki iya bayyanawa damuwar ki sama da ni,hamida ta a tare muka taho duniya, duk da ni din ba mai cikakkiyar lafiya ba ce kuma ina iya barin duniyar ma ako wani lokaci,

toh in baki fada min damuwar ki ba ta yaya kike so in taya ki saka farinciki a rayuwar ki, da fuskar ki wanda ba zaki taba mantawa da shi ba ko bayan na bar duniyar uhum?..fifi kamar zata yi kuka haka ta karasa maganar..

Kallon ta Hamida tayi tana jin maganganun yar uwar nata tsanake har yana son yin tasiri a zuciyar ta dan ta san bayan matsalar ciwon nan dake damin ta,inba don aan ware ta ba to da rayuwar su ba a haka zai ginu ba

dan sarai ta san Mufida bata da son kai bata da kyashi,amma wasu lokutan abubuwan dake faruwan be sai take ganin kamar fifin na da son kan ta da yawa wajen janye komai da kowa..

Matsowa fifi tayi ta riko hannuwar ta biyu cikin nata tana kallon cikin idanun ta hade da kuma yi mata tambayar

"Ko dai nan dakin bai maki bane mu yi musayar daki ke ki koma wancan nawa ni in dawo nan"?

kallon ta Hamida ta cigaba da yi kafin ta cire hannun ta cikin na Mufida ta mike tsaye tana fadin

"A'a fifi na,ko daya cikin tambayoyin ki babu wanda ke dami na,yanzu ki zo mu je mu ci abinci dan kin ga sai da daddy ya kuma min gargadin kar in rinka barin ki da yunwa in kular masa da ke,so mis Khadijah Mufida Mande can we go for our dinner now"?

sunan da ta kira ta da shi ne ya saka ta murmusawa dan da sigar tsokana ta fadi sunan..

Fifi Tana son sanar da mufida sirrin zuciyar ta game da Khalid amma sai ta ga kamar lokaci baiyi ba,gani take zai fi in ta bari abin ya kara karfi sai ta fadawa yar uwar nata...

Tare suka fito suna dan hira kadan kadan har suka karaso main parlor suka nufi dinning table..

Hajja ce ta fara ankara da Hamida sai ta dafe kai cikin jimami tana fadin

"Hamida kina gidan nan amma aka yi ta sha'ani amma baki fito an yi da ke ba kuma baki aiko kowa ya kawo maki abincin rana ba?ni dai bani son irin wannan dabi'ar taki da kika dauko ta turawa a ce mutum na cikin ahalin sa amma yana jan jiki da su kamar ba shine nasu ba"?kasa karasa zaman Hamida tayi ta tsaya a tsaye tana kallon Hajja har ta gama maganar ta sannan Ammy ta dora nata..

"Hajja ni wallahi mantawa nayi da ita da na aika mata da nata dazu, kin san sam yaran nan na zamani ba cika son takurawa rayuwar su suke son ana yi ba kin ga bai dace ana yawan shiga harkar su ba"!

kamewa Hamida tayi a tsaye tana nazarin zantukar nasu,da kamar ta juya ta koma amma sai ta ji hannun fifi a kan hannun ta da ta saka ta janyo kujera da niyar zama amma ta kasa...

Kallon ta tayi sai ta ga ita murmushi ma take yi dan haka sai ta fasa komawar kawai ta zauna ba tare da ta ce kala ma maganganun su ba..

Serving din su abincin Ammy tayi suka zazzauna har sun fara ci sannan Khalid ya zo shima yayi joining din su saidai duk hankalin sa akan fifi ita kdai yake,bayan ita kuma Hamida hankalin ta akan shi yake tana mai ambaton kaunar sa a ran ta..

Abubuwa kala kala sun faru a gun cin abincin sai dai duk ba a sako Hamida ciki ba sai ita fifi,dannewa Hamida ta rinka yi har aka kammala cin abincin ta mike tana masu sai da safe,bata jira amsar su ba tayi gaba dan ta san kara mata damuwa zasu yi..

Ammy ce ta bi ta da kallo kamar ta so dago wani abu game da hamida karar da fifi ta saki ne ya sa tayi saurin maida hankalin ta ga tana tambayar ta lafiya..

Ashe spoon Khalid ya saka cikin abincin ta ya dauke mata last sliced of cucumber din dake cikin abincin shine ta sake kara dan har ya kai baki zai saka..

Fada Ammy ta mai akan yana babba amma madadin ya faranta mata a matsayin ta na kanwar sa shine yake kuma tsokanarta...

Hajja kuwa ta kasa hakura da dabi'ar Hamida dan tayi ma abun bahaguwar fahimta gani take hamida miskila ce marar saurin sabo..

Tace "Wannan yarinya dai dabi'ar ta daban take,ana zaune ana hira amma ta tashi ta wuce ciki anya bata da wata damuwa kuwa?karasa tambayar tayi tana kallon Ammy..

Dage kafada Ammyn tayi alamar oho bata sani ba,daga haka suka maida hankalin su ga shirmen Mufida da Khalid har suna tambayar ta ina take son zuwa gobe dan bude ido..

Kasancewar bata san ko ina ba sai Khalid ya rinka zayyano mata wuraren bude ido da daukar hankali,daga nan ta rinka zabar inda zata kai ziyarar a washegarin..

A haka dai suka karasa hirar ta sallame su akan zata koma ta kwanta dan kan ta ya fara ciwo,ai jin kalmar ciwon nan ya sa suka daga hankulan su har abin ya ba fifi tausayi dan ta san duk son da suke mata da kaunar da suke mata dole watan wata rana haka zata mutu ta bar masu duniyar..

Rungume su tayi tana furta masu kalaman so da kauna hade da godiyar kulawar su akan ta,sannan ta wuce su suma suka wuce zuwa makwamcin su..

Anan ma Bata tafi dakin direct ba sai da ta fara duba dkin Hamida ta zauna tare da ita ta rinka jan ta da hira mai ban dariya sannan ta bata sassanyar runguma dacewa kar ta manta in tana da damuwa ko tana jin tana bukatar shawara kar tayi kasa a gwiwa wurin sanar da ita ita kuma ta mata alkawarin bata dukkan lokacin ta da hankalin ta dan ganin ta taya ta magance damuwar ta..

Da haka suka rabu Hamida na ta nazarin kalaman yar uwar nata,taji dama dama sosai kamar dai ta dauka tayi amfani da shi,can sai kuma ta fasa dan karfin kiyayyar da take ma yar uwar nata kamar ya fara rinjayar karfin soyayyar da take mata..

kuma ko ba dan haka ba tasan ita ba zata taba zuba ido ta rasa Khalid ba,tace makanta enough is enough fifi,fifi,fifi,kowa fifi toh abin ya isa haka

Anan ko da ace mutum daya ne zai saurare ta tasaka aranta Khalid ne.

Da Hakan zai fiye mata kallon su da saurarar irin kalar son da suke ma Mufida..

A fannin fifi kuwa kasa runtsawa tayi har sai da ta karema hotunan da suka yi tare da Khalid kallo,ta kalli hotunan nan sun fi a kirga sannan daga bisani ta kashe bed side lamp din dakin ta runtse idanun ta tana me sa kan ta baccin dole dan ba baccin take ji ba ta fi jin kamar begen Khalid ne ya fi dacewa da ta yi a daren ba bacci ba shi ya sa ta runtse idanun dan dole koda bacci zai sace ta in ya so ko a mafarki ne ta lazumci begen sa..

#Mamuh*_Mamuhgee_*

8

Da sassafe Hamida ta tashi ta bar sashen ta ta nufi

sashen Mufida dan aiwatar da wata kudiri da zuciyar ta tayi ta ayyana mata akan ta aiwatar da zarar ta farka daga bacci..

Kamar marar gaskiya haka tayi ta sanda tana bin hanya a hankali har ta zo kofar dakin nata ta ja ta tsaya ta hau bubbuga kofar a hankali tana kiran sunan ta a hankali kamar bata son a ji ta..

Sai da ta dan jima sannan ta ji an zo bude kofar dakin,ajiyar zuciya ta sauke tana hamdala dan bata so a zo a riske ta a wurin a fara jero mata ka'idoji dan ta zo da sassafe tada diyar gwal..

Ganin Hamida ce sai ta kuma murtsike idanun ta tana mata kallon mamaki dan bata fiye ganin Hamidar ta farka da sassafe haka ba..

"Lafiya me ya faru Hamee"?tura ta ciki Hamida tayi itama ta karasa ciki tana maida kofar ta rufe sannan ta jawo hannun fifi ta rike cikin nata suka samu wuri a kan gadon fifin suka zauna...

Kallon kurilla Hamida ta mata tana ta nazarin yadda zata kasance a tsakanin su bayan ta gama fada mata abin da ta nufo ta da shi..

Ganin kallon yayi yawa sai fifi ta tambaye ta ko lafiya,sai Hamida ta sauya fuska zuwa kalar damuwa ta saka idanun ta cikin na fifi sannan ta fara magana kamar haka..

"Fifi na matsala ce ta dumfaro ni babba amma ban san ya zan magance wannan matsalar ba, tun jiya toh bayan tafiyar ki sai na kasa samo mafita amma hankali na ya kawo min ke,tuno da karfin gwiwar da kika bani nasanar da ke matsala ta sai kawai na yanke hukuncin tunkarar ki sai dai kash,ko da na duba agogo,sai na ga har daya da mintuna talatin da tara ya buga,sai na fasa zuwa sanin cewa kin dade da yin bacci kuma baccin mai dadi ne dan baccin gajiya ne"!!

Hamida na kawowa nan sai ta ja tayi shiru tana kallon fuskar fifi dan samin amsoshi daga sauyin fuskar ta..

A ruɗe fifi ta kuma riko hannun Hamida tana jin babu dadi,saurin tambayar Hamidar tayi.

"Hamee dan Allah ki yi saurin sanar da ni wannan matsala da damuwar da ta dumfaro ki,ni dama na sani,sam akwai damuwa a tattare da ke amma kika ki sanar da ni,yanzu Hamida har kina iya boye min damuwar ki ba tare da kin sanar da ni ba?ina yar uwar ki jini daya"?..

Wani irin murmushi Hamida tayi haka dama ta tsara ganin fuskar fifi bayan ta tunkare ta da wannan batun..

Dada langaɓar da kai Hamida tayi kalar tausayi ta kuma matsowa kusa da fifi ta cigaba dan samo asalin amsoshin da take so...

"Fifi yar uwa ta...,na so a ce ni ce ke cikin wannan matsalar sai dai a'a..ba ni ba ce,saidai na yarda da wannan kalmar ta masoyin ka masoyi ne ko a ina yake haka makiyin ka makiyin ka ne ko a ina yake, _*KAUNARMU*_ ta asali ce,yadda nake son ki nake kokarin ganin farincikin ki kema haka din ne,da wuya ake samin yar uwa mai kyakyawar zuciya irin taki"..nan ma tana kawowa ta ja tayi shiru..

Dulmiyewa fifi tayi cikin kogin tunanin inda kalamar Hamida suka dosa dan ta matsu ta ji matsalar yar uwar nata ba dan ta gaji da jin yabon da yar uwar nata ta mata ba sai dan ta damu da son magancewa yar uwar nata matsalar ta..

Zata yi magana Hamida ta riga ta dan bata son shirin ta ya wargaje bata so fifi ta fahimce ta dan ba halin ta bane bata saba ba,ko da tana da matsala yana damin ta bata iya tunkarar fifi da shi dan bata da lokacin ta is either tana yawon bude ido da kawayen ta,ko tana gidan Dr Fatima Yonas,so yau na cikin kwanakin da zata iya kirgawa ta zauna one on one su yi wata muhimmiyar magana,and wannan ya kasance rana daya da ba zata so tayi sake ya kufce mata ba..

"A jiya bayan mun diro kasar nan na iske sakon wata aminiya ta a inbox di na sai na share dai har muka iso nan gida,bayan na yi wanka na bude na karanta tun daga farko har karshe,kusan sau uku ina karanta sakon nan nata,sai da na kammala kai na ya kulle na rasa ya zan yi dan tana tsaka mai wuya

kuma taimako take nema na gaggawa daga gare ni,fifi ko kin san menene wannan damuwar nata"?da sauri fifi ta girgiza kai tana son jin menene..

Murmushi Hamida tayi wanda a ido da zuciyar fifi gani tayi kamar murmushin da hausawa kewa lakabi da ya fi kuka ciwo ne sai ta ji ta kara tausayawa yar uwar nata dan ta shiga damuwa sosai...

Hamida tace

"Kawata Tana da yar uwa wacce suke ciki daya mahaifin su daya haka mahaifiyar su daya,tun yarintar su sun taso ne cikin kauna da kulawar junan su,suna kafa kafa da bacin ran junan su,basu son abin da zai taba dayan su,a haka suka taso cikin rayuwa mai inganci har girman su,ana haka sai yaruwar kawar tawa ta tsinci kan ta cikin son kula wani masoyi wanda wannan masoyin kuwa ba masoyin kowa ba face masoyin wannan aminiyar tawa,bata da masaniya akai tana chan tana dakon soyayyar sa tun haduwar ta da shi ta farko sai dai bata sami damar sanar da shi ba sbd alkunya irin ta mace,abin da bata sani ba shine,tun ranar da ta hadu da wannan masoyin nata yaruwar ta ta hadu da shi itama

Amma ita aminiyar tawa ita ta fara ganin sa kafin yaruwar nata ta gan sa,nauyin baki ya sa ba a jima ba ta gano cewa yaruwar nan nata ta gama fadawa soyayyar wannan masoyi nata kuma da alama shima yana shirin fadawa a tarkon soyayyar ta,duk yadda aminiyar nan tawa tayi dan ganin ta hana faruwar hakan ta yi amma abin ya ci tura dan tana chan tana tunanin madafa yaruwar nan nata ta fara niyar kawo mata labarin kusancin ta da wannan masoyin aminiyar tawa,bata kai ga kawo mata ba sai tayi tunanin sanar da ni dan in bata mafita,..iya tunani na yi fifi,ta bani tausayi kar fah ki manta masoyi ne da ta jima da soyayyar sa a zuciyar ta kuma take ta dakon sa sai dai alkunya da nauyin baki ya sa tayi delay akan fallasa masa sirrin dake ran ta,kuma kar ki manta,yar uwar nan nata ta riga da ta gama shirya sanar da ita abin dake tsakanin su da masoyin nan nata,tunani na ya ƙafe ƙaf,hankali na ya gama hango min iya mahanga,nazari na ya tsaya akan hanya,kai na ya kulle,tausayin ta ya gama mamaye ni dan shirun da tayi na nemar cutar da ita cuta ta har abada da in tayi wasa lallai zata zanawa kan ta tambari mai wuyar goguwa har abada dan tana ji tana gani yar uwar nan nata zata kasance cikin rayuwar da ya dace ita ce ta kasance ciki amma hakan bai yiwu ba, .

Mufida ina mafitar ki kan wannan matsala ta aminiya ta da yar uwar ta?me cece gudunmawar ki akan wannan labarin rayuwur tasu"?..

Kakkarfar ajiyar zuciya fifi ta sauke mai abubuwa da dama dan ba karamin tausayin aminiyar yaruwar nan tata tayi ba,labarin ya fi mata kama da irin labarun da ake sakawa a fina finai dan da wata ce ta bata wannan labarin toh nan take zata karyata ta dan bata ga ta yadda za a ce kana son mutum kayi shiru ka ki sanar da shi ka rinka boye abin dake zuciyar ka wai dan kar wata ta ji zafi da wani abu wai shi sunan shi alkunya?ita ba zata iya yarda hakan ya faru da ita ba,kasancewar yar uwar ta ce ta sanar da ita wannan labarin sai ta gasgata dan yar uwar ta ba zata taba tsara mata karya ba..

Rau da idanu fifi tayi tana jijjiga kai hade da alhinin wannan labari sannan ta yi nata maganar.

"Hamida yau da ba ke kika sanar da ni wannan labari ba,ba zan taba yarda da dan na fi ganin irin sa cikin fina finai,amma na san ba zaki zauna ki tsara min karya ba shi yasa na gasgata zantukar ki"!jin wannan kalama ta karshe da ya fito daga bakin fifi wato _"Gasgata"_ sai Hamida ta ji wani dadi ya mamaye ta dan ko da ta fara bada labarin tayi zaton fifi zata ki amincewa da labarin sai kuma ta sha mamaki dan haka ba karamin dadi ta ji ba..

Kara kyabe fuska Hamida tayi kalar tausayi ta tsurawa fifi ido tana jiran jin amsar ta..

Sai da fifi ta rinka shafa bayan Hamida tana bata magana akan komai zai wuce sannan ta cigaba da magana..

"Hamida kin ga dai rayuwar nan ita daya ce gare mu in aka bar ta ba dawowa ake yi ba sannan baya ga hakan akwai yanci kai,yanci zaben abin da kake so a rayuwar ka,toh dan me wannan aminiyar taki take daukar lokacii wajen yin wasu tunani?in ta zuba ido tana kallo yaruwar nan nata ta mallaki muradin rayuwar ta kuma suka kasance cikin farinciki shi kenan burin ta na son yin Tarayya da wannan masoyin nata a matsayin abokin rayuwar ta ya tafi kenan ba tare da ya sani ba?

matukar ta bari wannan damar nata ya tafi tabbas rayuwa ce zata yi amma cikin kadaici da rashin ingancin abokin da ya dace dan babu wani da namiji da zai zauna mata a zuciya sama da wannan masoyin nata,sbd haka tun kafin wannan yaruwar nata ta tunkare ta da zancen ita yakamata ta dau mataki dan kare faruwar hakan,ba sai ta bayyana mata ba amma dabi'un ta su zasu nunawa yar uwar nata cewa akwai wani sirri tsakanin ta da masoyin nata kin ga daga haka ita kan ta yar uwar zata rabu da su ba sai an yi hayaniya ba,let her go for what she want,ko ba haka bane yaruwa ta"?..

Kallon ta Hamida tayi tana hadiye shawarwarin ta tana kada kai daga bisani ta rungume ta cikin tsananin murna da farinciki tana fadin

"Tabbas _Kaunarmu_ daga min indallahi ne fifi,ni da ke din jini ne kuma Tarayyar mu tayi min amfani,yadda kika samo min maganin wannan damuwar wacce na dau tsawon awanni ina ta bugawa a kwakwalwa ta amma ban samo amsa ba,na yarda shi yasa kike da kaifin basira kike zuwa a layin farko ta fannin karatu,you are a genius twin sis i love you"!!

daɗa faɗaɗa murmushin dake saman fuskar ta fifi tayi tana jin dadin ta samowa aminiyar yar uwar ta maslaha mafi sauki kuma tayi kokari akan damuwar yar uwar nata..

Dagowa Hamida tayi ta shafa fuskar fifi tana kara gode mata da taimakon da ta mata sannan ta kara jaddada mata zata sanar da aminiyar nan nata shawarar kuma zata fada mata cewa nata yaruwar ce ta bata wannan shawarar..

Daga karshe bayan ta ma fifi godiya ta tashi da nufin fita sai kuma ta juyo ta kalle ta da murmushi mai ratsa zuciya sannan ta ce

"Na gode yar uwa ta Allah ya bar zumunci ya bar mu tare ba zan taba manta wannan abin da kika min ba yar uwa ta,InshaAllah wataran zan rama maki wannan kyakyawar ranar da kika min,kafin nan,ki koma baccin ki kin san daddy ni zai rike in har baki sami isasshiyar hutu ba

dan haka go back to bed twin sis sai mun hadu a wurin breakfast anjima"!gyada mata kai fifi tayi daga haka Hamida ta juya tana mata wani irin kallo..

Har cikin zuciyar Mufida ba karamin jin dadi tayi ba ganin ta warwarewa yar uwar ta damuwar ta,dama Hamida zurfin ciki ne da ita dan kullum shiru shiru haka take har takan yi mamakin yadda Allah ya halicci zuciya irin ta Hamida kamar bata da damuwa dan bata cika shiga sabgar da ba nata ba bayan ita da take yar uwar tama kan ta ita din irin mutanin nan ne da ake kira da extrovert masu son magana

Hamida kuma ta kasance kullum shiru sai abin da ya shafe ta take saka kan ta...

Komawa tayi ta kwanta dan cigaba da baccin dan dama bai ishe ta ba,bata dade ba baccin ya dauke ta..

A nan fannin Hamida kuwa duniya sabuwa dan ta samo abin da take so kuma ta samo facts da shaidar da ko da tace ga abin da take so babu yadda yar uwar ta zata ce ta mata kwace dan da kan ta ta bata shawarar kwato abin da yake nata ne..

Farincikin ta a ranar baya misaltuwa dan kasa bacci tayi har gari ya gama wayewa tayi abin da zata yi,wani hali da ba nata ba sai tayi sa a yau wato cancaɗa kwaliyya na zamani irin na yan mata masu ilimi da wayewa,shigar mutunci tayi ta dohuwar Asmaa abaya plain black mai kyau da tsada,tayi rolling veil din abayar ta saka loafas mai taushi ta fito kamar wata wacce bata taba zaman damuwa da kadaici ba...

Bata tsaya duba fifi ba dan ta san an zo an dauke ta zuwa dinning table,haka da fara'ar ta ta sauko ai kuwa ta fara hango su suna breakfast din su cikin walwala,ɗage kafadun ta tayi alamar abin bai dame ta ba ta karasa saukowa kasar..

Da zuwar ta ta sa hannu ta ja daya daga cikin kujerun dinning din ta zauna tana mai gaida su(cikin jama'u)..

Mamaki Ammy tayi ganin walwala a fuskar ta yayin da Hajja kuwa ta tsaya tunanin hala wa ya kirawo ta zuwa breakfast din tunda sun ga alamar ita din mai son kadaicewa ne ita kadai ko me ya faru yau ta zo tayi joining din su..

Shi kuma Khalid kallon ta yayi yana yaba kwalliyarta har ya furta mata..

"You look beautiful "wani dadi ne ya mamaye zuciyar Hamida amma tsabar rike aji irin nata sai ta dan murmusa kawai ta ce

"Nagode brother".daga haka ta kalli fifi tana mata faffadar murmushi itama ta maida mata da martani..

Abinci suka ci cikin jin dadi da walwala as family har suka kammala babu tashin hankali bayan yar hirar da aka rinka yi da fifi ba a sako ta ciki ita kam ko a jikin ta dan damuwar su yanzu ta maida shi gefen hagun ta ta dabbaƙa damuwar Khalid a gefen damar ta dan ganin bata yi sake ta rasa shi ba...

Sallamar ta fifi tayi akan zasu tafi yawon bude ido tare da Khalid har ta mata tayin tafiya amma ta ce a'a su tafi sai dai kar su manta su dau hotuna da dama dan in sun dawo ta kalla..

Allah sarki fifi sai ta dawo ta rungume yar uwarta tana mata sai sun dawo ita kam ban da murmushi babu abin da take mata,bayan tafiyar su ma bata koma dinning din ta zauna ba sai ta sallami su Ammy akan zata tafi kallon gidan tare da ma'aikatan gidan,basu hana ta ba suka kirawo wata amintacciyar ma'aikaciyar gidan suka umarce ta da ta raka Hamida su zagaya gidan..

Daga haka ta masu godiya suka fita,barin su Ammy da Hajja tayi cikin mamakin dalilin walwalar ta na yau amma da yake bata wani yi jiki da su ba sai suka share kawai suka cigaba da sabgogin su...

#Mamuh*_Mamuhgee_*

9

Sannu a hankali yar aikin nan ta rinƙa zagaye gidan nan da Hamida tana nuna mata sashe sashen dake cikin gidan ko wanne kuma sai ta mata bayanin mammalakin sashen, dan akalla mai aikin wanda aka fi sani da mama hasiya ta jima tare da su a cikin gidan zata kai sama da shekaru ashirin da shida zuwa da bakwai tana aiki a gidan kuma bata zamba da cin amana wannan ya daukaka darajar ta a idanun yan gidan ya sa aka yarda da ita har in abu na sirri ya taso ana iya yi a gaban ta dan an san sirrin nan zai kasance a killace..

Wani sashe suka zo mai bala'in kyau da tsari wanda bata taba ganin irin sa ba sai ta ja ta tsaya ahankli ta kalli matar ta ce

"Mama hasiya nan kuma sashen na waye ne?amsa ta bata kai tsaye ta ce

"Wannan sashen shine sashen ɗan uwan ku Khalid kuma tun yarintar sa har kawo girman sa a nan sashen yayi sa"..

Gyaɗa kai Hamida tayi tana tunanin ta shiga ne ko a'a, wani tunani tayi sai tayi shiru ta kyale ta dai cigaba da ƙare ma sashen kallo.

Muryar matar ne ya fargar da ita a inda take tambayar ta ko tana son a bude mata sashen ne ta shiga..

Tace "A'a mama hasiya,bana bukatar ganin yanayin sashen a yanzu,amma watarana nice aciki. cikin ranta tace ba iya gani zan yi ba har shiga cikin sa zan yi in zauna na har abada dani da khalid.

"da fara'a a fuskar ta ta ida maganar wanda ya so ya ɗan ɗaurewa mama hasiya kai ganin kamar jefa magana Hamidar tayi cikin magana amma lura da tayi da yanayin Hamidar na ba mai son hayaniya bane sai bata daukaka maganar ba ta basar..

Daga haka suka cigaba da bin sauran sashe sashe na gidan suna dubawa suna yɑr hira kaɗan kaɗan wanda a cikin hirar ne Hamida ke ƙaruwa sosai dan kusan a 100% ta san kusan 60% na halayyar yɑn gidan musamman inda ta fi buƙatar sani wato fannin labarin rayuwar Khalid dan shine ta fi bukata sama da komai..

Suna zuwa wani sashen kuma sai Hamida ta ja ta tsaya tana kallon mama hasiya tambayoyi cike taf a bakin ta da zuciyar ta amma bata furta ba tayi shiru..

Fuskantar hakan sai mama hasiya tayi murmushi dan ita kan ta tana da ɗiya mace mai hali kusan na Hamidar wato halin kau da kai ga abin da ba'a saka ta ciki ba kuma bata tambaya in har ba abin ya zame mata abin dole bane da zata sami ƙaruwa ba,dan haka sai ta hau yiwa Hamidar bayanin wannan sashen da mamallakin sa.

"Wannan shine sashen babban ɗan gidan nan kuma jigo jagorar gidan nan,magaji kuma masanin sirrin cikin gidan nan wato marshall MUHAMMAD SAHEEB kuma a halin yanzu baya ƙasar yana can South Africa inda ya fi yawan zama dan business din sa da kusan komai na rayuwar sa sun fi ƙarfi a can ɗin,amma duk lokacin da ya kawo ziyara nan ƙasar toh a nan sashen yake zama"!!

gyaɗa kai kawai Hamida tayi dan ko ba a faɗa mata ba ta san wannan shine old eldest son ɗin Ammy da daddyn su ke basu labarin sa,lallai wannan tsohon shine wai har yanzu yana zaune awata ƙasar gaskiya su Ammy sun mai sake da yawa..

Ko da mama hasiya ta kuma yi mata tayin shiga wannan sashen sai ta ce a'a bata so,a zuciyar ta kuwa faɗi take ita me zata shiga ta gani a sashen tsoho sama da tarikicen kaya irin tasu ta tsoffi,sashen yaro mai zamani ma wato Khalid an mata tayin sa bata karɓa ba sai na wannan da ta san da ta shiga zata fito da babbar story da zata faɗawa fifi in ta dawo su yi dariya dan ta san fifi ta fi ta wauta tana iya cewa zata zo sashen da kan ta dan ganin me ke ciki ko dan ta sha dariyar mai dalili..

Zagaye farfajiyar gidan suka yi har suka ɓullo ta asalin kofar babban falon suka shige tare ita mama hasiya ta wuce sashen ta ita kuma Hamida ta haura zuwa nata ɗakin dan ko da suka dawo babu wanda suka tarar a parlorn..

Hamida ta kai kusan mintuna talatin tana ta saƙa da warwara akan yadda game ɗin ta zai kasance dan a jiya ta rasa courage ɗin komai amma safiyar yau da tayi magana da fifi sai kawai ta ji kamar an yi tursasa mata wani karfin gwiwa ne tun safen har ya kawo iyanzu bata da shakku a zuciyar ta game da alaƙar da take shirin ƙullawa tsakanin ta da Khalid dan ta san Tarayyar su zata zamo abin alfahari..

Ko da rana yayi bata tsaya jiran ganin saƙon su na ta zo a ci abinci ko a aiko mata da shi ba ta sauko da kan ta ta kuwa same su zazzaune suna jiran dawowar su fifi..

Babu wata damuwa a fuskar ta ta sauko ta tunkare su tana fara'a ta jawo kujerar ta zauna sai duk suka bi ta da kallon mamaki dan yau gabaɗaya kamar an sauya ta daga Hamidar jiya da suka yi welcoming daga filin saukar jirgi ba..

Ganin irin kallon da suke bin ta da shi ya sa ta ɗan yi ƙaramar dariya ta kalli Ammy ta ce

"Ammy barka da rana da fatar kuna lafiya"!kallon ta Ammy tayi ta ce

"Lafiya ƙalau Hamida,ya zagayen naku ya kasance ne hope you enjoyed it"?faɗaɗa fara'ar dake saman fuskar ta tayi ta gyaɗa ma Ammyn kai daga haka ta hau buɗe food warmers ɗin dake jere bisa dinning table ɗin ta ɗauko serving spoon da zumar

ɗibawa ta zuba a plate amma wani irin magana da Ammy ta mata mai kama da faɗa faɗa ya sa ta dakata ta dago ta sauke idanun ta a fuskar Ammyn wanda ya saka Ammyn jin ba daɗi dan itakanta ta ji ajikin ta kamar ta zafafa abun da yawa sai ta sauke muryar ta ƙasa tana faɗin

"Kiy hkuri Hamida ba fada nake miki ba,kin gane,wannan abincin da nayi na yi sa ne dan in yi surprising yar uwar ki dan jiya cikin hirar mu ta sanar da ni cewa tana marmarin cin abinci irin wannan wai jiya ta ci irin sa a outing ɗin su da yayan ku Khalid sai na ga bai dace a ce mutum na da abu a gida amma yana cin na waje ba shi ya sa na shiga da kaina kitchen ɗin na girka mata,yanzu da haka ita muke jira ta dawo sai mu ci abincin dan na kira Khalid kuma ya faɗa min suna hanyar dawowa shi ya sa na sa aka jere su a nan,amma akwai wani variety ɗin a other food warmer kina iya farawa da shi kafin ki dawo!!..

Kallon da Hamida ta bi Ammy da shi ne ya sa Hajja riƙo hannun Ammy ta ƙarƙashin dinning table tana girgiza mata kai alamar bata kyauta ba duk da ita kan ta ba haka ta so ba,ta so a ce wacce aka yiwa abincin ce ta fara gani amma na yadda zasu yi dan ita kan ta Hamidar tasu ce...

Rasa abin yi Ammy tayi sai ta tashi tsaye ta hau bubbuɗe food warmers ɗin da ta ce na fifi ne ta ɗau wani serving spoon ta fara zubawa Hamida a plate,har yanzu kallon ta Hamida ke yi da tsantsar mamaki da alhini..

Ammy na gama zuzzuba mata ta kalle ta tana faɗin

"Bismillah"!girgiza kai Hamida tayi alamar ba zata ci ba,serving spoon ɗin dake riƙe a hannun ta ta saka cikin food warmer ɗaya dake kusa da ita tayi serving kan ta cikin plate ta saka spoon ta janyo cup ta tsiyaya chilled coco smoothie a ciki ta kwashe ta bar dinning musu area ɗin zuwa sama zuwa ɗakin ta...

"Duk bin ta da ido suka yi suna jin wani iri a zuciyar su duk su biyun,har dai suka rinƙa ba kan su laifin abin da Hamida tayi a yanzu na barin su zuwa ɗakin ta...

Sede har yau gani suke kamar adaidai suke game da lamarin su da fifi

Ko sau daya sun kasa nitsuwa su fahimce cewa sune asalin silar jefa hamida a cikin dukan wani hali datake ciki arayuwanta

***

Su fifi kuwa zagaye sai inda ba a ƙirƙiro ta ba amma kusan kaf wuraren buɗe ido sai da Khalid ya kai Mufida suka ba idanun su abinci rough driving kuwa fifi sai da ta saka Khalid raina kan sa dan tun da ya miƙa mata maƙullin motar bayan fitowar su daga wata resort ta riƙe sitiyarin motar,toh bata sarara ba haka ta rinƙa tuƙi tana yi tana jijjiga motar,sai tsoro ne kuma ya shigi khalid dan duk rashin jin sa ta fannin tuƙin ganganci bai taɓa kuskurewa yayi irin wannan tuƙin ba sai gashi mace na yin irin sa...

So yayi ya kai ta wani wuri da ba kasafai ya cika zuwa ba sai dai kiran Ammy ya hana sa dan saka shi dawowa da fifi gida tayi akan ta gama yi mata surprise ɗin da ta daɗe tana mata tun bayan fitar su..

Tunda surprise aka ce sai bai faɗa mata ba ya juya akalar motar zuwa hanyar gida sai ta tambaye sa lafiya sai ya nuna mata ba komai kawai wani emergency ne ya same sa kuma ba yadda ya iya..

Tun a hanya yayi ta bata haƙuri akan gobe zasu cigaba ita kam yaƴar son jin daɗin rayuwa ta nunar mai ba komai su koma gidan...

Suna hanya suka tsaya ya siyo mata ice cream vanilla flavour suka dawo gidan tare,duk ta matsu su dawo ta sha ice cream ɗin dan tun jiya take sha'awar ice cream ɗin..

Da shigowar su Ammy ta taso ta riƙo hannun ta tana mata sannu da zuwa haɗe da tambayar ta ya fitar tasu ta kasance har da tambayar da fatar dai Khalid bai yi tuƙin ganganci da ita ba cikin mota..

Haɗa ido suka yi ita da Khalid sai ya hau girgiza kai yana faɗin

"Ba zaki so ki san ya drive ɗin nan ya kasance ba Ammy,ga ta nan tambayeta meya faru?

!kallon ta Ammy tayi da mamaki sai kawai taga ta fashe da dariya har da riƙe ciki tana faɗin

"Ammy Khalid matsoraci ne kawai dannna karɓi tuƙi sai ya ruɗe wai ina tuƙi da too much speed kuma fah baki gani ba Ammy ahankli nake tafiya

"ta ƙarasa tana kuma kallon sa sai ya kaɗa kan sa yana faɗin

"Haka kika ce ko?toh ba zan fita da ke ba gobe sai dai mu fita tare da Hamida

"saurin marairaice fuska tayi tana girgiza kan ta haɗe da langaɓar da shi alamar ban haƙuri sai ya saka mata dariya yana faɗin

"Ammy yakamata abata kyautar ta kar ta ƙulle min ciki da abin dariya"!!jin haka sai fifi ta dubi Ammy tana faɗin

"Ammy surprise"?gyaɗa mata kai Ammy tayi tana jawo hannun ta zuwa kan dinning table ta zaunar da ita sannan ta saka ta rufe idanun ta da sharaɗin kar ta buɗe sai ta ƙirga uku..

Da murna fifi ta jijjiga kai cikin zumuɗin son ganin surprise ɗin,haka aka yi bata buɗe idanun ta ba sai da Ammy ta ƙirga ɗaya zuwa uku sannan ta buɗe idanun ta ta sauke sa kan abinci exactly irin wanda ta ci jiya a yawon buɗe idon su...

Bata san lokacin da ta taso ta rungume Ammy ba tana ta yi mata godiya sai kuma tayi saurin sakin ta ta dawo ta zauna ta fara yunƙurin zuba abincin amma Ammy ta hana ta ta karɓe spoon ɗin ta zuba mata da kan ta har zama tayi akan zata ciyar da ita..

Tana buɗe baki sai tunanin Hamida ya bijiro mata ko ya suka yi da aminiyar nan nata bata sani ba kuma tana son jin karshen zancen dan haka ta maida bakin ta ta rufe tayi wuf ta miƙe Hajja da yanzu take leƙo su dan ganin ko Mufidar ta dawo sai ta gan ta tana sauri sauri zata haura sama..

Kiran sunan ta tayi amma bata juyo ba ta cigaba da tafiya tana ce mata

"Hajja ina zuwa Hamida nake son dubowa yanzu zan dawo"!..

Haɗa ido Hajja tayi da Ammy dake riƙe da spoonful of abincin da ta ɗibo da bawa fifi a baki..

Ajiyar zuciya Khalid yayi yana juyawa da nufin tafiya sashen sa dan kimtsawa kafin ya dawo a yi lunch ɗin dashi shima.

Zama Hajja tayi tana kallon Ammy da alamar tambaya sai dai ta furta..

"Anya Hamida ba damuwa gare ta ba kuwa?kin ga yadda jiya ta rinƙa janye jikin ta daga gare mu sannan yau ɗazu ta sake jikin ta amma ɗazu kuma ta rikice kamar ba ita ba?ina ga ki kirawo min Nuhu in ji asalin abin dake damin yarinyar nan dan ina jin tsoro"

..kallon ta Ammy tayi bata ce komai ba ta ɗauko wayar ta da nufin kira sai wani kiran ya shigo..

Dubawa tayi sai ta ga ƙanin nata ne wato mahaifin su fifi dan haka ta ɗaga kiran ta miƙowa Hajja..

Hajja na sakawa a kunnen ta ta fara magana kamar ran ta a ɗan ɓace sai dai bata yi faɗa mai yawa ba..

Haƙuri ya bata dan shi dama kira yayi dan ya ji ya lafiyar yaran nashi sabida yayi ta kiran layin Mufida amma bata ɗaga ba sai ya kira na Hamida amma itama bata ɗaga ba shi ya sa kawai ya kira na Ammyn..

"Hajja ai duk jikokin ki ne hala bata jin magana ne kin san Hamida ta bambanta da yʻar uwar ta,

Hajja tace ah a Mufida ce ke da matsala itace wacce ya kamata tayi ta zaman shiru amma sai yʼar uwar ta ce ke yin waɗannan ɗabi'un?

Dady yace haka hamida take amma in kuka saba ba zaki ga shiru shirun ta a matsayin matsala ba dan haka halittar ta yake"ajiyar zuciya Hajja ta sauke dan tayi tunanin wani matsalar ne da Hamida ashe kawai tsabar kama kai ne..

**

Fifi ta daɗe tana ta sallama a ƙofar ɗakin Hamida sai dai babu amsa,deciding shiga ɗakin kawai tayi,tura ƙofar ɗakin tayi sai ta ga Hamida kwance kan gadon ta alamar bacci ya jima da ɗaukar ta,gefe guda a ƙasa plate da spoon ne wanda ta ci abinci da shi,tsugunawa tayi ta kwashe plate da cup ɗin sannan ta kalli Hamidar tana murmushi a same time ta ce

"Please Hamee ki yi ki farka i have a lot to tell you,yau...is one of my best days a rayuwa ta kuma na san Allah na jin addu'a ta and zai amsa min because is a positive wish"kallon Hamidar tayi na dan wani lokaci sannan ta juya ta fice...

Haka ta sauko ƙasan ta same su duk suna zaune har da Khalid,nan take ta ji damuwar ta akan yʼar uwar ta Hamida ya ragu dan ta ga fitilar dake haske mata duhun ta wato Khalid ɗin ta..

Zama tayi da annashuwa a fuskar ta ta fara ba ammy haƙurin tashi da tayi ta bar ta da spoon a hannu ɗazu,yʼar lele ce bata laifi bare ɗazu daddyn su fifi ya tuno masu da matsalar fifin sai duk suka ji jikin su yayi sanyi amma ganin ta ta fito cikin fara'a sai suka ga kar su saka ta cikin zargin wani abin..

A walwala aka ci abincin Khalid na ta labarta masu yadda fifi tayi da shi cikin mota ɗazu,duk sai su rinƙa goyon bayan ta suna mai dariya,da haka dai aka yi lunch lafiya aka kammala Hajja ta ja hannun fifi zuwa sashen ta wai tana so su yi hira ta jika da kaka,wannam hikimar duk dan kar su bar fifin cikin kaɗaici da damuwa ne ya sa Hajja bijiro da wannan tsarin dan kam ta...

#Mamuh_*Mamuhgee*_

10

Da isar su ɗakin Hajja Fifi ta hau koɗa ɗakin game da zuzuta kyaun d ɗakin yayi dan har wani qamshi yake fitarwa kamar ba na tsohuwa ba komai tsaf tsaf da shi..

Jawo hannun ta Hajja tayi ta zaunar da ita bisa kan silver colour royal bed ɗin ta da ya sha kayan ado na zamani kama daga kab throw pillows da aka zagaye gadon da shi kamar dai yadda ake gyara gado irin ta mutanin da sai dai wannan a zamanance aka gyare sa zanin gadon kan sa abin kallo ne.

Hajja ta gyra zama ta na ta famab murmushi dan ganin halin farin cikin da fifi ke ciki sai ta bar ta tayi ta kalle kallen ta tana yabe yaben ta har ta gama dan kan ta ta dawo ta zauna tana cigaba da yaba ɗakin Hajjan har ta so ba Hajjan dariya..

Riƙo hannuwar ta Hajja tayi tana kallon fuskar ta dake da ragowar murmushin da ya bayyana two sided dimples ɗin ta,hakan ya tuno ma hajja da mahaifiyar su fifin sai tausayin fifin taji ya kama ta sosai duba da irin rayuwar da yarinyar ta taso babu kula ta musamman daga uwa sakamakon bata raye sannan ga jarabtar da ubangiji ya mata na rashin cikakken lafiya,duk waɗannan dalilai ya sake jefa tausayin ta a zuciyar Hajja..

Nan da nan hawaye suka cicciko daga idanun ta amma bata bari fifi ta gama fahimtar dalilin cikowar hawayen ba bare ta tambaye ta,sabida ta gama sawa a abu mafi sauƙi a gare ta shine ta aiwatar da abin dake ran ta ayanzu game da rayuwar fifin dan a ganin ta hakan ne kawai zai fiye mata kwanciyar hankali..

"Hajja ɗakin ki kamar na amarya sabuwa fil,ji kamar ɗaki na ne"!!

kallon mamaki Hajja ta mata sannan ta ce da ita

"Da gaske ɗakin ya maki kina so a ce kina da irin shi ko fiye da shi ko!?da sauri fifi ta gyaɗa mata kai tana dariya..

Hamdala Hajja tayi jin da bakin ta ta ma furta sha'awar ta ga son samin ɗakin kan ta ba tare da ta cigaba da zama a ƙarƙashin su ba amma a ƙarƙashin mijin ta...

"Dama na jima ina son yin wannan magana takwara ta sai dai rashin wanda zan tunkara da maganar ya sa na barwa kai na amma sosai na damu da samun cigaban rayuwar ki a mataki mai inganci da ba zamu sami ɗar ko fargaba ba, amma tunda yanzu kin yi maganar da kan ki ina so ki faɗa min ra'ayin ki kar in maki shigar bazata,kina da wanda ya kwanta maki a rai ne da kike jin ba zai maki riƙon ƙasƙanci da son zuciya ba in an aura maki shi?

Fifi tace haajja aure?laahhh,abin dariya abin mamaki wai fifi da jin kunya sai ta faɗa jikin Hajjan tana ta ɓoye fuskar ta dan ba zata taɓa mantawa ba akwai ranar da suka zauna lokacin a germany suna lissafa irin mazajen da suke son aura ita da Hamida,sai bayan sun gama hirar har Hamidar ta wuce sai ta zauna da zuciyar ta akan in har Allah ya bata aron rai tayi aure ta sami ƙaruwa toh in mace ce sunan Hamida zata saka mata in kuma namiji ne sunan daddyn su zata saka mai har ta samo other name da za a rinƙa kiran baby girl ɗin da shi haka ta samo wanda za a na kiran mai sunan daddyn da shi...

Dariyar manya Hajja tayi dan ta ga amsar tambayar ta ƙarara a fuskar fifi tunma kafin ta amsa,sai ta rungume ta tana taɓa bayan ta game da ce mata

"Amma ni kam takwara ta wanene wannan saurayin ne da yake mana shigar bayan gida ba tare da mun sani ba,fata na dai ba baturen ƙasar can kika samo mana ko?dariyar itama fifin tayi tana cewa Hajjan toh in baturen can ɗin ne ma ba zata so shi ba..

Sai da fifi ta gama juye juyen ta sannan ta rufe idanun ta da tafin hannun ta tana faɗin

"Hajja ai kin san shi dama kike wani kwane kwane "...tana gama faɗin haka ta tashi ta fita daga ɗakin a guje wannan tabbaci ne na alkunya dake jinin matan arewa koda ba anan ta taso ba...

Ganin yadda ta fita da gudu sai Hajja ta fashe da dariya tana girgiza kai dan ko ba a faɗa mata ba ta san hasashen ta ne ya zamo gadkiya kuma da yardar mai duka zata ga tayi iya ƙoƙarin ta dan cika wannan hasashe nata..

Mezai fiye mata dadi ace an Hade mufiida da khalid,ita kuma hamida in Allah ya so ba sai akara ma yayan shi saheeb ba?

Da gudu fifi ta nufi hanyar balcony dan shigewa ɗakin ta dan bata san tana da kunya mai tsanani ba sai yau da Hajja wacce take a matsayin kakace ma a gare ta toh ina ga Ammy ce ta mata wannan maganar,lallai da ta daɗe bata bari Ammyn ta ƙara saka ta a ido ba..

Tana cikin wannan yanayin ta ji kamar ta bangaje mutum sai tayi saurin buɗe idanun ta ai kuwa tayi tozali da Hamida,take ta kuma jin wani kunyar sai ta matsa ta cigaba da tafiyarta..

Hamida da dama ita ta fito nema sai ta tsaya a tsaye tana mamakin dalilin farincikin fifi amma sai ta basar ta ɗage kafaɗun ta ta ƙarasa saukowa ƙasar ta ɗau abin da zata ɗauka ta juya ta hauro saman...

Zata wuce kenan ta ga fitowar Hajja cikin fara'a da ragowar dariyar mamakin fifi,ko bata tambaya ba ta san labarin gizo bai wuce koƙi,fifi ta fito ɗazu da fara'a a fuskar ta tana rufe fuska yanzu kuma Hajja ta fito da nata fara'ar..

Ɗage kafaɗa tayi alamar ba matsalar ta bane,gaida Hajjan kawai tayi irin gaisuwar barka da war haka,bata tsaya jiran amsa ba tayi gaba...

Muryar Hajja ta jiyo tana kiran sunan ta sai ta dakata haɗe da juyowa cikin mamaki ta kalle ta..

Da kan ta Hajjan ta ƙaraso ga Hamida ta riƙo hannun ta na hagu da babu komai ciki tana kallon ta daga bisani ta tambaye ta

"Wai nikam Kin ga min Mufida kuwa? ina ta jiran dawowar ta amma da gaske tafiyar tayi dan kunya ta wai ta ji"

ajiyar zucitayar Hamida tayi a zuciyar ta kuwa sai cewa tayi _"Hajja da abin ban dariya take toh ni ina ruwa na da wata kunyar ta da fifi ta ji har take tambaya ta ko na gane mata ita,ai wannan tsakanin su ne,yanzu dama dalilin da ya sa ta dakatar da ni kenan ashe?ohhhh,,fifi,fifi,fifi ko nauyin ta basu ji kan su tsaye suke nuna mata wariyar soyayya,ko da yake ai komai ya kusa zuwa ƙarshe illar in na kasa cigaba da haƙurin ne amma da zarar na daure toh zan mori haƙurin da na daƌe ina yi"_..

Jin tsyi shiru sai Hajja tayi saurib bijiro da tunan kafin ta dubi Hamida ta ce da ita cikin raha

"Hamida dama maganan aure ne?ko dai ke ma haƌa ku zamu yi ne dan na ga kin fiye son rayuwar kaƌaici nidai wannan salalan ba ajina ba?

Hamida taja tace haajja aure kuma?

Hajja tace eh

Daa wai nace mubawa mufida khalid ke kuma tun da ba wani shkuwa kukayi ba ai sai ahada ku da yayanku ko?kuma wannan haƌin shine zai yi daidai da tsarin rayuwar ki..

Wani kallon durus tayi ma hajja kanta na wani irin juyi,idan da za a ba Hamida dama da tace babu wanda yakai hajja iya nuna fifiko da sonkai dan babu cigaba a cikin lafuzan ta hala nata tsufar a haka ya zo mata da hauka,tana tambayar ta tun ma bata amsa ba ta kuma jefo wata tambayar da bata san ma'anar sa ba ikon Allah...Hajja..?wai waye na saheeb din nan tsoho shekaru aruru?Allah tir..Allah ya sawwaka itace za'ace ta auri wanda yazo duniya tunma kafin a aure mahaifiyar su?

Dariyar bazata Hamida tayi tana girgiza kai tana mai raba hannun ta daga na Hajja haƌe da furta

"Hajja kenan,zokije fifi na ƌakin ta ƌazu ta wuce ni zuwa ƌakin ta,sannan maganar ki ta biyu Hajja ni ban gane mata ba zai fi kyau in na raka ki ƌakin ki kika huta dan da alama kin gaji da yawa bayan tsawon lokacin da kika ƌauka baki ci abinci ba kina jiran dawowar....,fifi ko?"a kalmar Hamida ta ƙarshe sai da ta ja misali kafin ta

ƙarasa sakamakon wani baƙin cikin da ya mamaye mata zuciyar ta tuno da cewa saura ƙiris ta yarda ɗan kada yayi girma a gaban ta ba dan tayi saurin yiwa tufkar hanci ba...

Ko jiran jin ta cewar Hajja Hamida bata yi ba ta janyo hannun ta ta kai ta ɗakin ta tana mai dangana ta da gadon ta haɗe da ƙare ma ɗakin kallo dan sai yanzu take shiga,duk da ba mai yawan magana ce ba ita,ta tsinci kan ta da complimenting ɗakin Hajjan..

A nan kuma Hajja ta kasa haƙura ta so ta kuma tado da maganar da ke ran ta amma Hamida bata bata damar yin maganar ba sai ta juya tayi ficewar ta..

Tuntuni Tana ɗakin ta tana shan banana smoothie tana tunano zantukar Hajja na ɗazu abin na mugun bata dariya dan ta fi danganta rashin natsuwar zuciyar Hajja da yanayin tsufa inba haka ba ina ita ina auren wani wai saheeb?

Nan take kuma tunanin zagayen su na ɗazu ya bijiro mata a lokacin da suka kai sashen sa,wani dariya ne ya taso mata nan ta tuno da yadda mama hasiya ke mata tayin shiga sashen tana ko, dariyar ce ta taso mata a fili ta furta

"Wai in shiga in gani?kaji munafurci suce kawai dama ni an zabamin shine ita kuma an zaba mata kyakkawa,toh me nake da buƙatar gani a sashen tsoho sama da karikitai?gaskiya mama hasiya da abin ban dariya take sosai, ni dai na san wannan babban ɗan Ammyn in har yanzu bai yi aure bama toh lallai akwai matsala dan bana jin akwai macen da zata wani aure sa wa ke son tsoho,lallai..sanda ya gama zamawo asalin tsohon za'a kuma bada hamida?.."dariyar hasashen kamannin sa tayi haka ta rinƙa ƙyaƙyatawa har ta ji dariyar ta ishe ta sai ta miƙe tana faɗin

"Ya zama dole in sanar da fifi wannan abin dariyar na san ta sarai ko son binciken ta kaɗai zai saka ta shiga sashen in ya so bayan ta dawo sai ta faɗa min ya sashen yake..

Ko tsayawa batayi ba ta fita ta nufi ɗakin fifi,babu doguwar sallama ta shigo kawai..

Fifi dake duƙunƙune cikin bargo ta ɗago kai dan ganin wa ya shigo mata,sai ta ga Hamida ce nan take ta kuma rufe fuskar ta..

By now attitude ɗin fifin shikansa na son shiga sahun abubuwan ban dariyar da Hamida take cin karo da su a yau..

"Tace hjiya fifi taso ki faɗa min menene ke faruwa na ga kamar ke da Hajja wasan ɓuya kuke yi"!!da sauri fifi ta taso ta zauna yayin da Hamida ke gyara zamanta bisa kan gadon..

Saurin tambayar Hamida tayi halan me Hajja ta ce mata,ita kam Hamida da dariya a fuskar ta ta hau yi mata bayanin yadda suka yi da Hajja ita kan ta fifi sai da tayi dariyar Hajjan amma ta ba maganar Hajjan ma'ana akan ko dai Hamida itama yi mata za a yi irin nata.. ?

"Faɗa min yʼar uwa ta,ina jin ki shin me Hajja ta faɗa maki ne da kike ta jin kunyar ta?Hamida tayi tambayar tana mugun danne dariyar takaicin ta..

Sai da fifi ta ɗau lokaci sannan ta riƙo hannun Hamida ta hau bayyana mata komai da ya faru ɗazu tsakanin ta da Hajja ta kuma ɗora da bayyana mata ko wanene wannan mai sa'ar da ta kasa bayyanawa Hajja shi ta gudo,still da yadda zancen ɗin da suka yi a tsarin su na cewa ita za'abawa khaleed ita kuma saheeb

Dan Fizge hannu Hamida tayi daga riƙon da fifi ta mata ta tashi tsaye dan take take ganin kamar duhu ya fara ziyartar idanun ta,bugun zuciyar ta ya ɗan dakata sannan ya cigaba a bugu fiye da ƙima,take ta ji kamar zata faɗi,ba shiri ta juya ma fifi baya tana tare hawayen dake shirin zubo mata da hannun ta,ɗaya hannun ta na bakin ta tana kare bakin ta daga sakin kukar da ke shirin fin ƙarfin ta..

Cikin dauriya Tace"Na taya ki murna fa Allah ya tabbatar da alkhairi"

iya abin da Hamida ta iya faɗi kenan daga haka ta tura ƙofar ɗakin Mufida ta fita da sauri tana haɗa hanya burin ta ta tsinci kan ta a ɗakin ta..

Har ta wuce sai ta dawo da baya jin wani irin baƙin tattaunawa dake tashi daga ɗakin Hajja tsakanin ta da Ammy..

Natsuwa tayi ta kasa kunnen ta tana sauraron su ba tare da sun san tana wurin ba,har suka gama zantukar su mai ɗauke da nazarorin su da fasahohin su suka yi jawo bakin zaren aka tsaya a matsaya ɗaya...

Juyawa tayi ta ga gidan na mata juyin fanka,kan ta ta dafe da hannuwar ta biyu ta hau dube dube a balcony ɗin ko zata hango ruwa dan ta sha ko zata sami damar kashe wutar da ya banku a ciki cikin zuciyar,amma bata gani ba kuma babu alamar zata samu...

Kusan da dafe dafen bango ta ƙarasa ɗakin ta,tana shiga ta saka lock ta zame a ƙasa tana ta juye juye tana fifita da hannuwar ta biyu sai shakar numfashi take kamar mai matsalar asthma ganin hakan bai gamsar da ita ba sai ta hau zubda hawaye tana numfashi cikin sauri sauri,tari ne ya sarƙe mata nan take ta hau yin sa babu ƙaƙƙautawa idanun ta sun canza launi daga farare zuwa jajazir.

Kwanciya tayi a ƙasa ta hau birgima dan har yanzu bata ji numfashin ta ya mata yadda take so ba..

Kimanin mintuna ashirin Hamida bata samu daidaituwar numfashin ta da ƙyar dai ta sami ikon sakin wani kuka

tun da ta ji kamar zuciyar ta ya ɗan sassauta sai ta cigaba da kukan,yi take yi tana tuno lokutan datayi sadaukarwa da yawa a rayuwar su ita da fifi har kawo yanzu...

Kirjin ta ne ta ji yana mata nauyi da zafi nan ma ta rasa ina zata saka kan ta ta sami sassauci,danne ƙirjin tayi da hannayen ta biyu tana jan numfashi hawaye na fitowa wani na korar wani...

A nan ɗakin Mufida kuwa ba ƙaramin kaɗuwa tayi da mamkin hamida ba,taga ta shigo tana yar fara'a batayi tsammanin zata ga shauƙi da zumuɗin ya yanke bayan ta bayyanawa Hamida sirrin dake zuciyar ta amma sai ta sha mamaki ta ga akasin haka.. Seta ke gani kamar mufida bata ji dadin zabin ba?

Dama wazai so tsoho?wani damuwar tuno da cewa ko itace na bayarda zatayi ba to amma me zatayi?wannan ai duk shirin su ammy da hajja ne.

Miƙewa tayi ta tsaya a tsaye tana kallon inda Hamidar ta tsaya daxun a yayin da ta juya mata baya tana mata wani irin amsar da bai yi kama da kalaman da kawai ya dace su fito daga bakin ta ba..

Mamaki kan mamaki ne ya saka fifi a gaba,duk iya inda hankalin ta da tunanin ta zai kai akan wannan abin da ya faru yanzu yanzun nan tayi ƙokarin kai hankalin ta nan amma bata sami abin da take so ba..

Juyawa tayi ta ɗauko gyalen ta ta yafa a kan ta ta saka takalmin ta ta fito da sauri dan zuwa jin matsalar Hamida gani take wannan reaction ɗin nata bai yi kama da abunda da mutum zai gani ya kawar da kai ya ƙyale ba dole ne dai akwai matsala dan Hamida ba haka take ba...

Cikin saurin ta ta fito tana tafiya sai ta ji a jawo ta ko da ta duba sai ta ga Ammy ce,cikin inda inda ta fara yunƙurin yin magana amma Ammy ta riga ta da fara'ar ta tana gyaɗa mata kai..

"Na sani,na sani,Hajja ta faɗa min komai,kuma na kasa haƙuri har sai kin bayyana mana da bakinki wanene wannan ɗin dan ni duk hankali na ga mutum ɗaya ya koma and i know it's that person,yanzu kin ga ba batun kunyar Hajja ko ni zaki ji ba,ki zo mu tafi sashe na dan ki bayyana min abin dake zuciyar ki a matsayi na na uwa a gare ki ai na cancanci jin ra'ayin ki,so come let's go my dear"Ammy na gama faɗin haka ta riƙo fifi da karfib tsiya suka hau tafiya ita kuma ba zancen kunyar ce ke damin ta ba a yanzu abin da ya fi damin ta shine ta san wani hali yar uwarta Hamida ke ciki..

Ɗan ja da baya Mufida tayi tana rau da ido cikin rashin jin dadi tace ma Ammy akan itafah ga inda ta fito da niyar zuwa amma amsar da Ammy ta bata shine

"Kibar wannan Hamida zata zo anjima itama aiko?itama akwai maganar da muka yi akan ta duk zan mata bayani amma bayanzu ba.let's concentrate on yours.."daga haka ta kuma riƙo hannun fifi suka cigaba da tafiya..

Duk da zuciyar ta na faɗa mata a'a ta fara zuwa ta ji damuwar yar uwar ta amma maganar Ammy na daɗa buga mata ƙararrawa akan ai ta ce zasu yi wata magana akan Hamidar tare,sai kawai tayi shiru ta cigaba da bin Ammy har suka isa ɗakin ta...

#Mamuh_*Mamuhgee*_

11

Zaunar da Fifi Ammy tayi tana kallon fuskar ta nadan wani lokaci sannan ta fara magana cikin kwantar da murya dan ta sami cikakkiyar hankalin fifin..

Ita kam fifi na ta bin Ammyn da kallon mamaki dan a zuciyar ta tambayoyi ne kala kala sai dai Ammyn bata bar ta ta sami ikon yin sa..

"Mufida kina ji na?,ɗazu Hajja ta kirawo ni ta sanar da ni matakin da ta ɗauka akan ki na haɗa auren ku sai dai ko kafin ta furta maki wanda ta zaɓar maki ke har kin nuna ta hanyar yin na'am da shawarar ta a ƙarshe har kika fita cikin kunya hakan ya tabnatar mata da cewa kina son abin da take maki sha'awar samu,toh ni yanzu ina so in kuma tabbatarwa ne,da gaske kin yarda da alakar dake tsakanin ku da yayan ku Khalid ya shiga wata matakin rayuwa wato matakin aure"?

karasa maganar tayi tana janyo hannayen fifi dan samin hankalin ta da yaddan ta dan basa so su yi mata ba dai dai ba..

Yin ƙasa da kai Mufida tayi cikin jin nauyin Ammy da tambayar da ta aiko mata..

"Mufida amsa min bana son kina jin nauyi na ko kin manta ni ɗin Ammyn ki ce"? girgiza kai fifi tayi tana mai buɗe bakin ta cikin jin nauyin Ammyn ta ce

"Ammy ai shi bai ce komai ba"!!shiru Ammy tayi tana sauraron ta a zaton ta akwai cigaban maganar amma ta ji shiru sai ta ɗago ta kalli Mufidar cikin jin daɗi dan ta san in har ita tayi na'am da zancen toh shima Khalid ɗin ya zama dole ya amince dan bai da matsala dama sun jima da jiran ganin ya kawo masu mace da sunan matar da zai aura anma babu labari shi yasa da Hajja ta tunkare ta da maganar kawai ta ji hankalin ta itama ya kwanta da shi dan ta matsu ta ga jikokin ta ko zata mori albarkar yaya itama tunda auren na danta na farin bai yi working out ba toh yanzu addu'ar ta bai wuce ta sami jikokin daga tsatson Mufida ba...

Hajja Tace..."In dai Khalid ne wannan ba abin da zaki ɗaga hankalin ki bane saboda ya jima da bari mana zaɓin matar sa a hannun mu,yanzu dai menene kike son sani game da shi da baki sani ba wanda bai faɗa maki ba"!?

murmushi fifi tayi tana daɗa sunkuyar da kan ta ƙasa kafin ta amsa kamar da Ammy takeyi..

"Ammy kaɗan na sani daga rayuwar sa kin ga kamar ban san komai bane so kusan komai akan sa nake son sani"cikin jin nauyin su duka ta ƙarasa maganar nata.

Ajiyar zuciya Ammy tayi sannan ta kuma faɗaɗa murmushin ta tana gyara zaman ta..

"Kamar dai yadda kika ji ana kiran sa da Khalid,toh asalin sunan nasa kenan Khalid,kwata kwata shekarun sa bazasu wuce 27 years ba bai ma gama kaiwa ba sannan shi ne ɗa na biyu a cikin gidan nan babban yayan sa shine Saheeb wanda ba a nan yake ba,Khalid yayi karatun su both primary and secondary schools ɗin sa a nan ƙasar ne so bayan ya kammala ya nuna interest ɗin sa a fanin karatun gynaecology wato ya zaɓi ya zurfafa karatun sa a fannin sanin matsalolin mata.

duk da ban raine su tare da Abban su ba sakamakon barin mu da yayi a daidai lokacin da muke buƙatar sa dan kuwa Allahn da ya bamu shi ya karɓe sa,hakan bai sa nayi ƙasa a gwiwa ba kakar ku Hajja ita ta ƙara ƙarfafa karatun Khalid ɗin sai ya zaɓi ƙasar Cyprus a inda yake son zuwa yin karatun,bamu hana sa ba iya fatar alkhairi da muka mai,wani abu shine Khalid ya kammala karatun sa ne a dan kankanin lokaci dan ya karasa yana da shekaru ashirin da biyar abin da ba kasafai ya fiye faruwa ba,so ya dawo kuma alhamdulillah ya sami aikin sa yana aiki a nan cikin gari sai dai ba ko da yaushe yake zuwa ba sai har in shine on call kuma a halin yanzu yana kan cigaba da karatun sa dan zama cikakken consultant so zuwan ku ne ya sa yake zaune a gida kuma ya haɗu da hutun sa da ya shigo..

Kuma he really wants you to feel at home that was why ya zaɓi kai ki wurare daban daban tun dawowar ki kuma daga dukkan alamu shima ya gamsu da ke dan naga kamar jinin ku ya zo ɗaya daga yanayin da yake sake maki"..ɗan dakatawa Ammy tayi tana sauraron jin ta bakin fifi..

Fifi sai ji tayi kamar an kara rura mata wutar ƙaunar Khalid a zuciyar ta ina ma a ce karantar fannin zuciya yayi da sai ya magance mata damuwar ta amma duk da hakan bata ji ƙaunar sa da ya mata shigar farat ɗaya ya ragu ba..

Can Tace "Ammy, baki sanar da ni komai akan social life ɗin sa ba irin meyafi so,abokan sa da dai wasu abubuwa da suka shafi personal life ɗin sa"..

murmushi Ammy tayi tana shafo fuskar fifi sannan ta cigaba..

"Well,Khalid...,ina ga ba sai na tsaya faɗa maki tsarin rayuwar sa ba dan ke kan ki shaida ce akan hakan kin gani kuma kina iya faɗawa wasu,sannan akan abokan sa...,Khalid na da abokai but mostly sai lokaci zuwa lokaci suke haɗuwa kinsan yanayin aikin nasu kowa na concentrating ne akan aikin sa,game da abincin da Khalid ya fi so kuwa,ina iya faɗa maki Khalid is a simple person komai yana ci muddin abin nan na ci ne,ba kamar yayan sa Saheeb da ba komai yake ci ba"...

Kallon Ammy fifi tayi tana gyaɗa kai alamar ta gamsu da duk bayanan Ammy tace Hamida fa,itama ai tare zaayi mana auren ko?sai tayi shiru aranta tana tunanin

"ya ita kuma zata kasance in aka ce ita zata yi aure ba tare da Hamida ba?bata taɓa mafarkin hakan ba ta fi planning ranar auren su ya zo daidai komai su yi tare amma ba a rabe ba..

Yin wannan tunani sai ta ɗago ta kalli Ammy directly ta jefo mata tambayar dake zuciyar ta...

"Ammy ya labarin na Hamida"?shiru Ammy tayi tana ɗan kasaƙe for a while sannan ta amsa tambayar..

"Dear ban manta da Hamida ba ai dama na faɗa maki za mu yi maganar nata bayan naki so yanzu bari in fayyace maki nata dan surprise ɗin da Hajja ta mata ne

"..nan take fifi ta zaƙu a faɗa mata dan sanin ko wa ita kuma aka zaɓar mata dan dan tasan bazata taba yin aure ba tare da yaɾar uwar ta ba..

"Kin ga kasancewar Hamida mai ɗauke kai ne ga duk wani al'amurar rayuwa,ba ni kaɗai na hango hakan ba har kakar ku Hajja ta hango hakan,tana da shiru shiru bata cika magana ba babu ruwan ta,so haɗa ku da za a yi da yayan ku Khalid sai Hajja ta ga me zai hana itama a mata hakan dan ɗabi'un ta ya zo sak irin na wanda take hasashen haɗa sun,sedai shi ba anan yake ba

kuma...."!!!sai tayi shiru sai fifi ta girgiza mata hannu cikin zaƙuwa tana son Ammy ta ƙarasa mata bayanin...

Kawar da kai Ammy tayi tana takaicin furucin da zata furtawa fifi dan bata san yadda zata ɗau maganar ba amma dai dole ta sanar da ita dan ba zai yiwu ta ɓoye wani sirri ba alhalin haɗin da suke son yi haɗi ne na har abada..

"Mufida wanda muke son haɗa sa aure da yaɾar uwar ki Hamida yana da mata,kuma sun share shekaru da yawa suna tare sai dai..."!!nan ma Ammy tayi shiru sai fifi ta ƙyale ta bata ce mata komai ba...

Sai da suka ɗau lokaci a hakan sannan fifi ta sake tambayar su haɗe menene matsalar da ajiyar zuciya Ammy ta furta bakomai sunan sa..

"Muhammad Saheeb,yayan Khalid ne, shine mutumin da muke son haɗa Hamida aure da"!!fata na hadin y zame mana alheri

wuf Mufida ta miƙe tsaye tana kallon Ammy baki buɗe...

Ammy duk ta gama azawa ki wani abu ne

Dariya ne ya cunkushe a zuciyar fifi sai dai bata son yin sa a gaban Ammy kar Ammy ta ji wani iri,haka ta rinƙa tarar dariyar dan kar ya fito,a ƙarshe dai ɗagawa Ammy hannu tayi alamar zata je ta dawo...

Bin ta da kallo Ammy tayi tana mamakin reaction ɗin fifi dan ta ɗauka zata ga tayi negative reaction ne sai ta ga akasin haka...

Mufida na fita daga ɗakin Ammy bata tsaya ko ina ba sai ɗakin Hamida wacce ke kwance ƙasa tana baccin wahala..

Da zuwar ta bata tsaya tunanin bacci yƙar uwar nata ke yi ba kawai ta hau tapping nata a baya tana kiran sunan ta..

"Hamee...,Hamee na ki tashi...common wake up i have a gist for u,dan Allah ki tashi".jijjiga ta fifi ta rinƙa yi tana assasa mata akan lallai lallai sai ta farka daga baccin dan kawai ta labarta mata abin da Ammy ta sanar da ita..

Daga cikin baccin da bai jima da ɗaukar ta ba Hamida ta ji muryar fifi sai ta buɗe idanun ta a hankali ta zuba su a kan fuskar fifi dake ta dariya kamar wacce ta ga abin dariyar..

Fifi na ganin ta farka sai ta riƙo hannun ta tana mai cigaba da yin dariya tana magana..

"Hamee wai kin san wani babban albishir da su Ammy zasu maki kuwa?tayi maganar tana kuma ƙara ƙarfin dariyar ta...

Bin ta da kallo Hamida tayi dan in dai wannan ne special package ɗin,toh ta san da zaman shi...

Tace "Hamee me?na yi tunanin zaki matsu dan son sanin wannan zancen?girgiza mata kai Hamida tayi tana kawar da fuskar ta gefe..

Kai tsaye fifi ta hau bata labarin komai sannan ta ɗora da sunan wanda za a haɗa su auren..

"Hamee wallahi na fi dacen miji kin san fah wai har mata gare sa kuma ta ƙi yarda ta haihu over years,though Ammy bata sanar da ni gabaɗaya labarin sa ba amma daga wannan ɗin ma na gane cewa Ammy ta matsu ta sami grandchildren you see in aka haɗa ni da yaya.....Khalid ke kuma aka haɗa ki da...."!!!wani dariyar ne ya tasowa fifi ta rinƙa yin sa har Hamida ta ji kamar ta ɗauke ta da marin da ubangijin ta kaɗai ya san halin da zuciyar ta ke ciki game da wannan lamarin,ba fah ita aka roƙa aka nemi yardar ta da izinin ta ba kai tsaye aka nuna mata iko,amma ita fifi da yake yʻar so ce yʻar gida ce bayan Hajja ta yanke hukunci har sake tuntuɓar ta Ammy tayi dan jin ra'ayin ta wai kar a mata dole..

these people are unbelievable ta furta aranta .ta ja tsaki,ba ma su suke sanar da ita ba? Mufida ce yar aikan su akan maganar dan kawai bata da daraja da ƙima...

Duk wannan dariyar d fifi take bai dame ta ba dan dana ta ji shirun sua ɗazu,so wannan ba abu ne da zai ɗaga mata hankali ba duba da irin rayuwar da ta taso a ciki na kaɗaici da rashin samun kulawar kowa a kan ta..

Murmushi mai ciwo Hamida ta yi tana kallon Mufida dake ta ƙunshe dariyar ta,sai ta girgiza kai kawai dan wani lokaci in ta gwada nauyin ƙiyayyar da take yiwa Mufidar sai ta ga ya rinjayi ƙaunar da take mata hakan ya sa take ta ƙoƙarin ganin shaiɗan bai kai ta ƙarshe ba ta yadda in ta tashi barakar ta abin ba zai yi muni ba

sai dai daga dukkan alamu yazama dole ne tayi introducing Mufida zuwa ga other side na halayen ta dan ta san ba komai mutum ke yi ya tafi haka nan kawai ba...

Tae wai za a aura min

"Yaya Muhammad Saheeb ko"?sai fifi ta gwalalo idanun ta waje tana tunanin a ina Hamida ta san wannan labarin..

"Kina mamaki ne dan na san da shi ɗin dama za a haɗa ni, kuma kin san me fifi? hakan bai dame ni ba a hakan ma,ina son shi"!!

baki buɗe fifi ta rinƙa kallon Hamida jin cewa wai tana son shi a hakan ita da baya cikin jerin tsarin mazajen da take burin aura sai kuma yanzu wai har ita ce mai cewa ya mata a hakan..

Lallai Hamida ta sauya amma meyasa Kika ce kina son shi a hakan Hameeda"?

Gyaɗa mata kai Hamida tayi tana kallon ƙwayar idanun ta dan duk inda jarumta yake Hamida ta nemo sa ta ara ta yafawa kan ta bata so fifi ta ga gazawar ta har tayi taking advantage ɗin gazawar nata ayau dan ji take kamar hakrin ta ya riga ya kare..

Tashi fifi tayi tana yar dariyar rashin fahimta tana girgizawa Hamida kai cikin tsokana tana faɗin.

"Ni Mufida,yanzu Hamida duk irin burin nan da kika ɗaura akan samin namiji ƙerarre mai muscle duk sun tafi abanza kenan?tsohon nan mai mata zaki aura kuma wai kina son sa a hakan?unbelievable"!!

sai dariya dama on normal basis ya aka iya da dariyar tsokanar fifi bare yanzu da ta sami dalili...

Tsanar ta ne kawai ke ruruwa a zuciyar Hamida,ji take kamar ta kawo ƙarshen wannan masifar yau yau ta hanyar shakure ta,Mufida kowa Mufida kowa Mufida,daurewa tayi ta danne ɓacin ran ta ta cigaba da ɗora murmushin yake har Mufida ta gama tsokanar ta da zata yi ta ɗora da yabon nata husband to be ɗin wato Khalid...

Ƙala Hamida bata ce da fifi ba har ta gama ta dawo ta rungume ta tana masu fatar alkhairi su duka sannan ta tafi dan ta matsu ta san ko ta sami ƙarbuwa a zuciyar Khalid ɗin..

Bayan fitar ta ne Hamida ta kira Dr Fatima Yonas cikin kuka tayi narrating mata abin da ake ciki,babu abin da ya wuce shawarwari da sauƙaƙa zuciya da Dr Fatima Yonas ta ba Hamida ƙarshe ta mata fatan alhari da alƙawarin inshaAllah ko da bata sami damar halartar bikin ba Ameed zai zo..

Zama Hamida tayi tana ta saƙe saƙen ta ita kaɗai da zuciyar ta,hawayen dai na kan zubowa amma zuciyar ta bai karaya ba tana nan tana jiran ji ko za a same ta a sanar da ita wannan shawarar ta musamman ko kuma daga wanda fifi ta sanar da ita shikenan...

****

Bayan an kammala dinner har an bar wurin cin abincin sai Hajja ta kira attention ɗin Mufida ta aike ta da ta kirawo Hamida dan tana da magana ta muhimmin ga dukkan su...

Tashi fifi tayi ta nufi ɗakin Hamida ta sanar da ita saƙon Hajja,biyo ta tayi suka dawo tare

A gaban Hajja duk suka zauna Mufida ta fi kasancewa kusa da ita,nasiha sosai Hajja ta masu sannan ta ɗora da sanarwar da ta sa aka yi a cikin family game da batun auren,kuma jadadda masu tayi akan a tsarin su kwata kwata ba su son bikin ya wuce wata guda,dalilin barin sa ya kai har wata gudan kuma shine dan su ƙara fahimtar junan su ne da abokan da zasu yi rayuwa da su..

Duk kan su a ƙasa Hamida dai ta san ba dan ita aka yi wannan tsarin ba sai dan fifi dan ita kam an gama cutar ta mijin da ake shirin haɗa ta da shi batun wai su fahimci juna kuma duk wannan bai taso ba dan shi kan sa ba a ƙasar yake ba bai da lokacin kan sa bare nata toh ta yaya zata wani fahimce sa,again her life is about to get ruined so bata jin daɗin komai a duniyar ma...

"Hamida ina ra'ayin ki akan wannan tsarin da muka maku ke da yʻar uwar ki"ta ji muryar Hajja a kan ta sai ta kalli Hajjan da murmushin dole ta ce

"Komai kuka tsara yayi Hajja"daga haka ta tashi ta bar wurin duk da ta haɗu da Ammy a hanyar ta na komawa ɗakin ta hakan bai sa ta tsaya ta ma Ammyn magana ba...

"Kin ga irin halin yɘar uwar taki da ya sa muka ga sun dace da Saheeb kenan,kullum mutum na zaman kaɗaici"?..murmushi fifi tayi tana tunano irin kallon da Khalid ke aiko mata ɗazu da suke cin abinci...

Kwanciya kawai tayi jikin Hajja tana ta murmushi wanda ita ta san me ke saka ta murmushin...

****

Kwanaki na ja fahimtar juna na ƙara ninkuwa a tsakanin fifi da Khalid haka mizanin ƙiyayyar fifi a zuciyar Hamida babu abin da ya ragu sai ƙaruwa sabida son kan da aka dade ana nuna mata yau ya fito mata karara duk wani shiri na musamman da ake yiwa fifi ita bata sami wannan rahamar ba,haka duk hankalin su ya koma kan fifi ba Hajja ba ba Ammyn ba,wannan ya janyowa Mufida baƙar tsana a zuciyar Hamida wanda da wuya wannan tsana da ƙiyayyar ta gogu a zuciyar Hamida..

A zahirance Hamida na nuna amincewar ta da auren amma a baɗini kuwa ubangiji shikadai yasan me ta kulla zata aiwatar ta dai ɗauke kan ta daga dukkan abin da zai ɗaga mata hankali har ɗaurin auren da ta san ita kaɗai zata yi zaman aure babu wani miji sabida da shi da babu abu daya ne wurin ta...sede hakan bazata taba bari ya afku ba

#Mamuh*_Mamuhgee_*

12

Rai bace cikin ɗan ɗagin murya da ala dai ba cikin dadin rai take maganganun ba dan har kasa zama wuri ɗaya tayi,ta juya nan ta juya can kafin daga bisani ta yi wata magana cikin tsawa mai nuni da oder take bayarwa..

"Nan da kwanaki goma sha biyu nake son ganin ka a ƙasar nan,ni na haife ka ba Muhibbah ba dan haka a matsayi na na mahaifiya a gare ka tun kafin rai na ya sosu da kai Saheeb,ka dawo gida ka halarci ɗaurin auren ka dan ita kan ta yarinyar dole

aka mata ba dan zuciyar ta na so ba sai dan ita ɗin mai biyayya ce,for the very last time kar ka yarda in kuma yin magana da kai akan wannan issue ɗin am i clear"? shiru ne ya ratsa tamfatsetsen ɗakin nata kafin daga bisani tayi magana...

"Sai ka zo Allah ya kare min kai ya dawo mana da kai lafiya take care"!!tana kaiwa nan ta sauke ajiyar zuciya haɗe da sauke wayar daga kunnen ta..

Juyowa tayi ta kalli Hajja dake ta sauraron ta tun farawar wayar naya har yanzu da ta dire wayar daga kunnen ta..

"Wai zai zo ɗin"?Hajja ta tambaya da sanyin gwiwa sai Ammy ta ce

"Eh Hajja,zai zo idan bikin ya rage saura kwana biyu inshaAllah".gyaɗa kai Hajja tayi tana magana

"Allah ya kawo mana shi lafiya".da amin Ammy ta amsa daga haka suka cigaba da tsare tsaren bikin dama ba wata bidi'a za a yi sosai ba abin da fifi ta zaɓa are just three,na fari bridal shower na biyu family get together ne sai walimah,kuma in aka yi la'akari kusan duk taron cikin gida ne..

Tsarin ta sak tsarin turawar da ta taso a ƙasar su bata son yawan hayaniya in ba ita ta so ba toh kuma sun gama tsarin su akan duk yadda za a yi bayan bikin ita da angon ta zasu gudu zuwa honeymoon a can zasu yi abin da ran su ke so..

"Yanzu ki aika a kirawo ita Hamidar dan a mata ɗan taƙacciyar bayani akan rayuwar mijin nata dan ina ga takwara ta har yanzu kamar bata sanar da ita ba kamar dai yadda kema baki ƙarasa mata bayanin ba,kin ga ai haƙƙin ta ne ta san da wanda zata yi rayuwar zaman aure da shi dan in takwara ta ce na san bani da ɗar akan hakan sun saba da junan su"!!.gyaɗa kai Ammy tayi tana sauke ajiyar zuciya..

Wayar ta ta ɗaga ta kira layin Hamida,bugu uku Hamida ta ɗaga sai bata tsaya jiran komai ba ta ce da ita ta same ta a ɗakin ta.

Sauke wayar tayi daga kunnen ta tana yi wa Hajja bayanin ai tana zuwa..

Kafin ta zo ɗin ne suka cigaba d tattauna lamarim bikin dan sun saka an yi iv na soft copy an yaɗa ma yan uwa da abokan arziƙi sbd a zamanin yanzu wannan ɗin shine dai ya fi saurin kaiwa wurare fiye da hard copy..

Suna cikin hirar sallamar Hamida ya ankarar da su,shigowa ɗakin tayi bayan an mata iso ta nemi wuri ɗan nesa da Ammy ta zauna sai Hajja ta ƙure ta da kallo ganin kamar tayi rama fiye da da da suka zo,bata kawo komai a ran ta ba illa rashin

sakin jikin Hamidar da take kallon ta da shi but ta san in har aka yi auren nan toh komai zai zo ƙarshe ko ba komai miskilanci da ɗauke kan ta zai sauka..

Gaida su tayi tana yin ƙasa da kai haɗe da cewa ammy

"Ga ni Ammy"..sai da ta gama kallon ta ta ga kamar ita bata gyaran jikin sai ta tambaye ta surprisingly..

"Hamida ina gyaran jikin da na sa ana maku ke da Mufida"?wani irin abu ne ya tasowa Hamida ya tsaya mata a ƙirji sai take tambayar kan ta a zuciyar ta..

"Wai mutanin nan...,are they for real?ni Ammy ke tambaya ina gyaran jikin da ta sa a mana?wai ma tukun yaushe aka yi hakan?ina fifi ce kaɗsi centre of concern ɗin su?ita kaɗai ake yiwa gyaran ita kuma da yake bare ce a gare su bata cancanci wannan kulawar ba,"girgiza kai kawai tayi ta ce da Ammy..

"Ammy fifi kaɗai ake ta yiwa ni ban ma sani ba sai jiya da na gan ta a wun cin abinci"!!kallon mamaki Ammy ta bi ta da shi tana jimamin hali irin na Hamida mutum so quite and ignorant haka,..

"Amma ai kin san dole tunda baku haɗuwa akwai abin da ake mata kuma ya kamat a matsayin ki na babba ke ce kika cancanci fara zuwa duba lafiyar ta,toh in wata matsalar ce ke damin ta shikenan kin ɗauke kan ki bski damu da ita ba"? kallon fuskar Ammy Hamida tayi tana mamakin son kai irin na Ammy..

Yanzu ita da fifi har wani fidda babba za a tsaya yi alhalin duk tare suka faɗo duniyar sai bambancin mintuna biyar da ke tsakanin su amma Ammy kawai tsabar bata son a ga laifin ɗiyar so fifi sai ta juya ignorance ɗin su akan ta akan duk dai laifin ita ce ba su ba ba Mufidar ba..

Ƙala bata ce da su ba har Ammy ta gama yin faɗar ta Hajja ta ɗora da nata sannan suka hau yi mata bayanin abin da ya sa aka kirawo ta wanda Hajja ce ta jagoranci bayanin..

"Ba komai ne ummul aba'isin ɗin kiran ki nan ba Hamida sama da yi mski bayani na musamman akan wannan mijin naki da zaki aura,kin ga dai yabawa da hankalin ki da tunanin ki da muka yi shi yasa muka ma ɗan uwan ki kwaɗaiyin auren ki,baki san shi ba bai san ki ba amma haɗin ku zai zamo alkhairi ga kowa,shi dai ba mai son magana bane kuma bai da matsala bare damuwa,kasancewar sa mai ɗauke kai ga abubuwa ya sa auren sa na fari da matar sa Muhibbah ya zamo kamar cutarwa,kwata kwata bata da lokacin sa bata zama yana south africa tana Los Angeles mafi yawan lokutan su sukan yi sa ne ta waya,basu cika haɗuwa ba sai shekara shekara,kusan shekarun su goma da aure kenan amma tun bayan shekarar su ta farko da suka yi sa cikin zaman lafiya basu ƙara samin zaman lafiya ba,dan ni abin da zan iya kiran zaman nasu da shi kenan,ta yi gaban kan ta ta tafi wata

dunuyar tana kula da businesses ɗin late mahaifin sa"..kaiwa nan Hajja ta ja ta tsaya..

Kan Hamida na ƙasa zuciyar ta na mata zafi da raɗaɗi dan wata sabuwar ƙiyayya ce ke samin gurbi da mazauni a zuciyar ta game da auren nan da ita kan ta ɣar uwar nata,tsabar son kai wai har shekarar su goma da aure ita wancan matar nasa bata da lokacin sa tana business ɗin ta sai ita ce mai zaman gida marar aikin yin da zata na kula da tsoho kamar shi,ai ko da bata san shi ba a ido ta san in ba a yi wasa ba ya haife ta because a shekarun da Hajja ta kirawo mata akan shekarun sa da aure ita a lokacin ina take?sannan kwata kwata tana ten years as at then toh shi ɗin a shekaru nawa yayi auren?..

Muryar Hajja ta ji a kunnen ta tana ƙarasa mata labarin.

"Shi ɗin Brigade ne na sojoji,kuma dalilin da ya sa ya bar mahaifar sa zuwa ƙasar south africa shine,akwai wata shekarar da ta gabata kusan shekaru ashirin da suka wuce an sami wata tarzomar da ta tayar da ƙura a tsakankanin ƙasar nan Nigeria da Cotonou,duk sojojin da ake kaiwa wannan boarder ɗin sai dai su yi iya yin su ba tare da sun yi nasara ba,wasu su dawo da rai wasu a dawo da gawarwakin su wasu kuma ba ma za a gan su ba,toh a wannan shekarar ne aka umarci head division ɗin wannan yankin da ya saka hannu wun bada gudunmawar sa kuma a haɗa da na ƙasar chad dan ganin ko za a sami nasara dan in har aka bar tarzomar ta cigaba toh zata iso nan ƙasar gabaɗaya ta addabi ƙasar,a lokacin yayan ku Saheeb bai jima da fara aikin sa ba sai wannan buƙata ta taso,da zuciya ɗaya ya amshi umarnin da aka basa daga sama ya nemi addu'ar mu suka nufi wannan yankin Cotonou ɗin wanda suka shafe kusan watanni shida suna jeji sai a na bakwan ne suka fito da babbar nasara mafi yawan yabo ya sauka akan yayan ku Saheeb,wannan jarumta nasa ya sa ya ɗaukaka har ya sami cigaba sosai fiye da shekarun sa,toh ana haka ne wata tarzomar ta kuma tasowa a ƙasar south africa inda a nan ne kuma ya ƙara samin ɗaukakar fiye da na farin,toh kuma tun daga wannan sai suka buƙaci da ya cigaba da zama a can dan ƙasar na fuskantar barazana ta maƙiya kusan akai akai,zaman yayan ku a ƙasar ya sauƙaƙa yawa yawan faɗace faɗacen da ake samu akai akai dan sun haɗa kai da sojojin ƙasar ta yadda da zarar an sami ɓaraka ko ana gab da samu toh zasu baza battalions ɗin su nan kuma za a fito da nasara"!!kuma jan fasali Hajja tayi Hamida na sauraron ta kamar tana sauraron wa'azi..

"A shekarar da suka fito da wata nasara ce Allah ya nufa suka haɗu da matar sa Muhibbah wacce itama aiki ne ya kai ta can ɗin dan businesses ɗin mahaifin ta ya kasance mai faɗi ne ƙasashe daban daban take zuwa yin sa, a wannan karon sai suka haɗu suka saba,toh mu a nan gida dama a matse muke da yayi auren dan ya fara manyanta amma bai maida hankalin sa a nan sai da ya haɗu da ita ɗin ne sannan ya kawo maganar,ba a ɗau lokaci ba aka yi auren zaman su a nan wata

guda suka tattara suka koma south africa da zama,bayan shekara ɗaya kuma sai ya kawo mana ziyara duk muka ga kamar ba shi ba,yin duniyar nan mun yi ya fayyace mana matsalar sa amma ya ƙi,ko da muka tuntuɓe sa da maganar inda matar take sai ya ce ai tana ƙasar Los Angeles wai tana kula da businesses ɗin mahaifin ta da ya rasu ya bar mata.a wannan lokacin hankali na ya gama tashi nayi tunanin samin mahaifiyar ta dan mu zauna a warware matsalar amma haka Saheeb ya hana ni ya ce min shi bai da matsala da wannan haka na ƙyale ba dan ina so ba"..

"Bayan ya koma da shekaru biyu ya kuma dawowa shi kaɗai nan ma da aka yi tambayar duk ɗaya ce,tana wata ƙasar tana kula da businesses ɗin mahaifin ta,a lokacin na san Saheeb bai yi dacen macen aure ba dan bata da niyar zama da shi bare ta haihu,daga ni har Ammyn ku duk mun matsu mu ga jinin sa a duniyar nan amma shi a wurin sa ba haka bane,a lokacin na ɗaga hankali na akan zancen ina ta nemar haɗa sa da jikokin aminai na amma haka zai ce duk basu mai ba shi hasalima bai da matsalar komai da matar sa akan me zai kuma yin wani auren,a ƙarshe dai komawa can south africa yayi kuma tun daga wannan komawar ne bai sake dawowa ba kusan shekaru shida da rabi kenan kullum sai dai a yi magana da shi ta waya in muka matsu da son ganin sa sai dai ta video call abin na damu na yana damu na a zuciya ta,yana jika na amma ya nesanta da ni ga mahaifiyar sa ya tsallake ta ya gwammaci zaman wata ƙasar duk dan baya so a ba matar sa laifi"..

"A ranar da mahaifin ku ya sanar da ni kun cika shekaru goma sha tara a duniya a ranar ne na saka sa gaba akan ya turo ku ku dawo tunda shi ɗin bai da niyar dawowa dan tun bayan rasuwar mahaifiyar ku shima ya ƙi yarda a mai maganar aure ya zaɓi zaman can germany akan nan,tun lokacin nake damin sa akai akai dan na san ba za a rasa wacce za a haɗa ta da Saheeb ba amma ya min nuni da cewa ai karatu kuke yi sai dai kuna gab da kammalawa kuma da zarar kun kammala zaku taho"..

"Kasancewar takwara ta ta fi yawan magana da ni ya sa na rinƙa damin ta da ta dawo gida,ku dawo gida kar ku gama yin girman ku a ƙasar da ba taku ba,toh alhamdulillah kun kammala karatun naku kun dawo gida Allah ya tsara maku mabambantan rayuwa ita Mufida ta dace da Khalid ke kuma muka maki sha'awar Saheeb sbd ɗabi'un ku kusan ɗaya,ke tamu ce muna da iko akan ki ba kamar matar sa ba da ikon da muke da shi a kan ta ƙalilan ne"!!..

"Dan haka muka ga dacewar ku kuma mun san kema a yanzu da kika ji labarin sa kika san ko shi ɗin waye zaki ga hangen da muka yi kuma ba zaki taɓa yin nadamar zaɓin mu ba"..

Ƙaƙƙarfar ajiyar zuciya Hamida ta sauke bayan ta gama sauraton Hajja,ajiyar zuciyar na ɗauke ne da abubuwa masu wuyar fassaruwa amma dai ta barwa kan ta duk da zuciyar ta na mata zafi ganin irin mizanin da aka ɗora nata martabar akai,ƙasƙancin sa ya ɗare abin misali..

Wani baƙin cikin ta haɗiya sannan ta saka murmushin da ya fi kuka zafi da ciwo tana faɗin.

"InshaAllah zaku same ni mai bin umarnin nan naku da amana da gaskiya Hajja"!!.wani sanyi Ammy ta ji a zuciyar ta har ta fidda ƙaƙƙarfar ajiyar zuciya haɗe da tashi cikin sauri ta rungumo Hamida jikin ta..

Abin mamaki yanzu dan na yarda da auren nan ne ya sa Ammy ta rungume ni haka?abin da tun da muka iso ƙasar nan bata taɓa yunƙurin yi min ba akasin fifi da ba zata iya ƙirga yawan hugs ɗin da ta samu daga wurin Ammy ba,oh ita Aysha yanzu wai ba dan ta cancanci hug ɗin ba aka bata shi ba sai dan ta yarda da zaɓin su..

Hawaye ne ya sauko mata daga idanun ta tayi saurin gogewa tana jan hancin ta sai muryar Ammy ta ji tana ta yi mata addu'a haɗe da bata tabbacin ba zata taɓa nadamar wannan haɗin da zasu mata ba.

Jin Ammyn kawai take ta yi har ta gama ta kuma jaddada mata ta tabbatar ta tafi inda ake ma fifi gyaran jiki dan itama a mata..

Gyaɗa kai kawai tayi ta sallame su suka rinƙa saka mata albarka tana jin su ita dai tayi gaba..

Tana hanya tana ta nazarin kalamomin su har ta zo ta wuce apartment ɗin da ake wa fifi gyara sai kuma ta dawo tayi peeping ta hango ta tana ta danna waya tana murmushi..

Komawa da baya tayi ta nufi nata ɗakin ta kwanta dan zuciyar ta bai mata daɗi,kasa baccin tayi sai ta tashi ta ɗau maganin ta ta zazzago guda biyu ta nemo bottle water ta haɗiye maganin..

Bata jima ba bacci ya sace ta bata farka ba sai 7pm kasancewar bata sallah sai ta sauko zuwa ƙasa dan a yi dinner da ita inda a nan fifi ta rinƙa mitar Hamida ta manta da ita yanzu sai dai su haɗu a wurin cin abinci in ta zo kenan bayan haka basu haɗuwa kuma ita a hana ta fita a apartment ɗin sai dai in ya zama dole..

Nan ma duk jin ta Hamida ke yi kowa ya kwaso blame ɗin sa kan ta ake sauke sa ba komai in yanzu sun mata wataran ba zasu yi ba..

A haka aka cigaba da shirin bikin su Hamida da fifi wanda tun a washegari Hamida tayi joining fifi aka cigaba da yi masu gyaran jikin sai dai bata tsira ba still akan nuna bambancin dan bayan an gama sai Ammy ta kira fifi separately ko me suke

girkawa Allah ne masani ita dai ta san babu wani ƙaunar Mufida a zuciyar ta ko na ɗigo ne but su sun kasa ganewa,bambancin da suke nuna mata bai haddasa komai sai ƙiyayyar masoyiyar tasu wato Mufida...

#Mamuh*_Mamuhgee_*

13

Ana saura kwanaki biyar da bikin su fifi sai shaƙuwar su da Hamida ya ninku ya fi da duk da ita Mufida ta fi alaƙanta shaƙuwar tasu da yanayin bambancin rayuwar auren da zasu fuskanta,duk dama ta san cewa gida ɗaya zasu zauna amma apartment ɗin kowa daban ba lallai bane su rinƙa haɗuwa kullum ba in an gama bikin..

Lokaci zuwa lokaci sukan zauna zama ta musamman tsakanin su su zanta mafi yawan hirar tasu takan karkata ne a ɓangaren kewar junan su da zasu yi bayan bikin,though sau da yawa hirar ta su takan ƙare ne da faɗa wanda fifi ce mai yawan janyo sa dan takan so ƙure Hamida akan zaɓen mijin ta ita kuma Hamida bata ba fifi hankalinta ɗin ta iyakar in an gama masu gyaran jikin sai ta tashi tayi gaba abin ta ƙarshe Mufidar ce ke zuwa ɗakin Hamida ta bata haƙuri sai su shirya hakan bai hana washegari in sun kuma haɗuwa ta ƙara tsokanar ta ba sai dai Hamidar da girgiza kai ta ce mata Allah ya shirye ki fifi..

A yau ne suke saka ran zuwan daddyn su dan kusan one week ago suke ta waya da shi ya sanar da su zai zo inshaAllah cikin kwanakin nan..

Tun safe suka kasa sukuni musamman fifi da ta fi zumuɗin ganin daddyn nasu dan dama tayi kewar sa fiye da tunani..

Har kasa natsuwa tayi saboda zumuɗi sai da Khalid ya ja hankalin ta da hira sannan ta sami natsuwa shima ya tafi ɗauko daddyn..

A cikin gida kuwa har girke girken da aka yi fifi na a ciki dan sosai ta ce tanaso daddyn ta yayi tasting abin da ta girka da kan ta..

A lokacin da daddyn su ya iso gida tare da Khalid haka fifi ta kanainaye sa ta ki barin sa ya sha iska tana ta yi mai surutai akan yadda tayi kewar sa,hakama su Ammy da Hajja da suka matsu da ganin sa sai dariya suke ta yiwa fifi akan yanzu kenan da take da yɑncin ganawa da daddyn nata take mai haka ina ga in ta yi aure kuma ita da mijin and da zarar sun tsokane ta da haka sai ta saka kukan shagwaɓa tana kallon Khalid da kwana biyun nan sam tadena gane masa

Sau dayawa ta rinƙa tambayar sa ai ba zai bari ta rabu da daddyn ta ba ko? shi kuma da dariyar sa zai amsa ta yana ce mata ai babu mai raba ta da daddy da su Ammy..

Azuciyarta tana dannewa ne kawai amma Halaye khalid gaba daya ya sauya mata in ya amsa ta se tanajin kamar ba shiba

Sai da aka ci abinci aka natsu sannan aka dawo parlor domin cigaba da hirar da aka faro tun akan dinning,sam Hamida takasa sakin jiki tayi da su sai ta nemo excuse ɗin da ta san zai bada babbar muhimmanci ta gudu zuwa ɗakin ta ta kwanta sabida duk yadda kwanakin bikin na ƙaratowa the more fargabar ta na ninkuwa..

Kusan raba dare suka yi suna hirar su duk kuma saboda fifi ne dan ta ce wannan shi ne best moment ɗin rayuwar ta da ba zata yarda ya tafi haka nan ba sabida ita dai tun tasowar ta daga ita sai daddyn su sai Hamida suke rayuwa a cikin gidan banda ma'aikata,a yau da suka haɗu duka with exception of saheeb wato mijin yar uwar ta da ita kan ta yar uwar nata sai ta ga wannan kamar dama ne babba da zata yi amfani da shi dan barin memories ɗin ta a zukatan ahalin nata...

Wasa da dariya anata hira Sai kusan 11pm fifi ta raka daddyn su masaukin sa inda nan ma ta rinƙa labarta mai abubuwan da Khalid ke mata tun zuwan su da irin kula ta musamman da yake bata tun zuwan su,shi kam daddy bai da abin cewa sama da yiwa Allah godiya dan ya kawo mai saka ɗiyar sa farinciki a rayuwar ta ba kuma zuwa kaɗai yayi ba tsayawa ma zai yi na har abada..

Da ta dawo ɗakin ta kuwa sabon babin hira taso ta buɗe ta musamman ita da angon nata Khalid dan kiran da ta mai ya kai sau uku bai dauka ba,can yazo

yadauka bata gane masa ba in sun yi good night sai ta sake kiran sa a haka dai har aka yi final good night duk suka kwanta bacci..

A washegari suka haɗu a ɗakin Ammy ta saka su gwada ɗinkunan su na bikin har ma da na events ɗin da za a yi,duk babu wacce kayan nan bai yiwa kyau ba dan dirin jiki da kyan halitta Allah ya hore masu shi..

Ita fifi da ta gwada na ƙarshen ƙin cirewa tayi ta bar shi a jikin ta sai da aka shigo ɗakin da sallama ta ɗago kai ta ga Khalid ne nan take ta fara nemar abin da zata rufe jikin ta da shi da alamr bata so ya ga kayan dan in ya gani toh ba wani birge sa da take son yi da zata yi a ranar event ɗin kayan..

Dariya Ammy ta mata itama Hamida ta ɗan dara tana mata gwalon Allah ya kara wai angon ta ya ga kwalliyar ta tun kafin ranar bikin,abin sai ya ba fifi haushi amma da yake bayan ya shigo Ammy ta kora sa waje dan kar ya ga kayan fifin sai ta ji sauƙin abin bata saka tsokanar yar uwar nata a ka ba...

****

Da safe yau ma family breakfast aka yi dan an san daga yau ɗin ba lallai bane a kuma haɗuwa on special breakfast haka ba sai dai in bayan biki..

Ana cin abinci ana hirar yaushe rabo Hamida dai bata yi gigin saka masu baki a hirar tasu ba dan ta san ko ta saka toh ba wani ƙwarjinin da zata yi duk hankali na ga fifi..

Suna gama breakfast ɗin tayi gaba abin ta sai dai a yau Hajja ta yi magana akan ƙyaliyar Hamida na damin ta,toh ana ta fifi sai kawai aka ce hala yanayin fargabar ta kenan ita tunda ko wacce amarya na da nata sigar fargabar in bikin ta ya zo toh maybe nata a haka ya zo na son kaɗaicewa ita kaɗai..

Bayan an gama hirar fifi ta tafi ɗakin Hamida wacce ke kishingiɗe tana danna wayar ta da hannu ɗaya babu wani sutura a jikin ta sai ƙaramar armless top marar kauri ƙafar ta tayi crossing ɗaya kan ɗaya,hakan ya bada damar viewing elegant

well groomed skin ɗin ta da ya sha gyara yana ta ƙyalli da walwal..jin fifi abayan ta ya sa ta boye abunda takeyi a wayar tana me cusawa a kasan fillow

Ƙare mata kallo fifi tayi sannan ta ƙaraso ciki tana murmushi ta zauna kusa da Hamidar ta taɓa ta..

Kallon ta Hamida tayi sannan ta tashi ta zauna sai fifi ta kuma kallon ta har abin ya saka Hamida tsarguwa sai ta nemo outer top ɗin rigar ta saka tana kallon Mufidar haɗe da tambayar ta ko lafiya da irin wannan kallon..

Murmushi kawai fifi ta mata sannan ta fara magana cikin gaskiya da gaskiya..

"Hamee ni kin san me ke dami na ne,wallahi ba komai ke dami na ba sai ganin irin wannan gyarar da aka maki kika fito tas da ke amma wai a ce wannan tsohon ne zai ga gyaran abin na taɓa min zuciya yar uwa ta,ban da yadda zan yi ne da na taimaka maki,ba ƙaramin tausaya maki nake yi ba,duk yanayin ki ina ankare da su kawai ƙyalewa nake yi dan na ga kamar kin fi buƙatar ki zauna ke kaɗai ne dan ki jajanta rayuwar da zaki shiga ciki,wannan dalili ya sa nake barin ki ki bar mu ko da hira ake yi sai dai a yau na ga damuwar taki har ta ɗare na kullum shi ya sa na biyo ki,shin Hamida akwai wata matsalar dake damin ki ne a zuciyar ki da baki son sanar da kowa"?.

Kallon ta Hamida ke yi cikin wani yanayi me wuyar fassara da sa tsoro wanda babu alaman shi akan fuskan ta sai a ziciyarta

har fifi ta gama maganar ta sai ta sauke nannauyar ajiyar zuciya tana girgiza kan ta cikin halin ni ban da wani damuwa..

Hakan bai gamsar da fifi ba sai da ta kuma nanata mata tambayar a wannan karon sai Hamida ta yi magana da bakin ta bayan riƙo hannuwan fifi da tayi cikin nata.

Tace"Fifi na kar ki damu kan ki akan matsalar da bata nan,ni ban da matsalar komai dan dai kawai a yan kwanakin nan nakan yi tunanin irin kewar ki da zan yi

bayan bikin nan dole dama wataran duk shaƙuwar mu dole mu rabu in ba mutuwa akwai aure kuma auren babu inda baya kai mutum hala mu rabu wata rana,alaƙar dake tsakanin mu ba ta fuska bace kaɗai,Mufida alaƙar mu ta jini ce wacce ko bayan rabuwar mu in an yi bikin nan wannan alaƙar tamu ta jini ita zata cigaba da ƙarfafa _Ƙaunarmu_ dan haka yaɗar uwa ta kar ki damu advantage ɗin auren mazajen namu kenan,gida ɗaya zamu zauna kuma in muka so a rana sai mu haɗu fiye da ɗaya,so calm down my dear auren nan ba zai raba mu ba ok"?ta ida maganar tana ɗage girar ta..

Gyaɗa kai fifi tayi dan duk abin da Hamida ta faɗa mata a yanzu gaskiya ne babu ƙarya cikin ta..

Rungume junan su suka yi Mufida yaɗar shagwaɓa sai kuka take ta yi ita kuma Hamida na rarrashin ta dan ita danne nata hawayen tayi...

Sai da suka natsa suka ɗan yi hira Hamida na kuma jaddada mata kar fa ta ɗaga hankalin ta akan behaviours ɗin ta ba komai bane kawai kewar ta da zata yi ne da na su daddyn su,da hakan fifi ta sami relief ta saka a ran ta in ma an gama bikin ba zata yarda su gudu zuwa honeymoon ɗin ba har sai sun jima sbd yaɗar uwar ta kar ta yi zaman kaɗaici...

****

Yau ce ranar da za a yi family get together inda a cikin gidan farfajiyar gidan aka taru aka gabatar da shi bayan an ƙawata farfajiyar gidan da decorations wanda ya kasance adon royal blue aka yi amfani da shi dan su kan su amaren kalar kayan da suka saka kenan sai sauran yaɗan uwa da abokan arziƙi da suka halarci event ɗin,su ma royal blue ɗin suka saka bambancin nasu da na amare shine na amaren an haɗe sa ne da off white head turban da aka masu ɗaurin sa sannan doguwar transparent designed net ɗin da aka ɗora masu saman asalin rigar jikin su ma ya kasance off white,takalman su da purse ɗin su duk off white,makeover aka masu sosai da ya fito da su..

Duk babu wanda zai gan su ya ce bai yaba da su ba,basu da kamanni dai amma da an gan su annga jini,ita Hamida in tayi murmushi gefe ɗaya dimple ɗin ta ya fito ita kuma Mufida in tayi murmushi duk two sides ɗin su bayyana..

A haka cikin kwanciyar hankali suka yi event ɗin su aka yi coverage da hotuna,masu selfie na ta yi ƴayƴan abokan mahaifin su Khalid duk sun taho sannan friends ɗin sa maza da mata sun zo wurin ciki har da close colleagues ɗin sa..

A fannin ammy Da zarar an yi tambayar ina amaryar Khalid sai a hau nuna ta su kuma su yi ta zuzuta kyawun ta dan dama ita ɗin mai kyau ce ko ba ado...

Lafiya ƙalau suka gama event ɗin aka koma cikin gida washegari ma aka yi bridal shower duk da ba su da friends amma close ones sun halarci event ɗin dan a jiya suka sami friends yawanci ƴayƴan abokan daddyn su da na mahaifin su khalid ne suka dawo bridal shower ɗin..

Dama in ka taho da kayan ka toh zaka cire a baka dress of the day da ya kasance mini peach chiffon inner da outer top ɗin sa kasancewar cikin ɗakin Ammy aka yi event ɗin kuma duk mata ne sai abin ya bada armashi nan ma haka aka yi aka gama..

Next day aka yi walimah da ya afku a cikin gidan kuma ya sami albarkar jama'a da dama dan marigayi mahaifin su Khalid ya tara jama'a sbd irin zaman kirkin da yayi da su,haka matayen abokan nasa ma suna mutunci da Ammy sosai Haka shima walimar aka yi aka gama sa lafiya

misalin 6pm daidai ana gama sa daidai Ameed da Meena suna shigowa cikin gidan,wani irin annashuwa fifi ta tsinci kan ta ciki wanda baya misaltuwa dan bata san har da Meena zata zo ba..

Welcoming nasu alka yi zuwa cikin gidan aka gabatar da su.

Duk wannan bidirin babu wanda ya kawo maganan zuwan angon Hamida wato marshall Muhammad Saheeb Maƙarfi,sai sha'anin biki kawai ake ta yi..

Hira sosai suka sha da Meena dan Ameed kam ya bi ayarin ango Khalid suna hira though basu san juna ba amma dalilin fifi sun saba..

*****

Next morning

Duk wata shiri irin ta musamman da ya dace a ma amare an zauna an ma su fifi da Hamida misalin ƙarfe goma ne dama ɗaurin auren sai Mufida ta rinƙa hirar ta da ɗaukar selfies tare da Meena da wasu dake ɗakin waɗanda ba zasu wuce sa'oin juna ba,in tayi wanda ya mata kyau sai ta turawa angon ta Khalid amma setaga kamar ma baiya bada hanklinsa sosai,

Hakura tayi daga baya tabarsa atunanin ta hidimar biki ne ya sha masa kai

Suna kan ɗaukar hotunan nasu aka fara shirye shiryen ɗaurin aure inda nan fifi ta bar duk wani abin da take yi ta riƙo hannun Meena ta natsu tana sauraron mallamin dake kan huɗubar sa da nasihohin sa har ya gama..

Sai a lokacin tasake duddubawa tana qoqarin Kiran wayar hameeda data bace Mata tun dazu Bata ganta ba Dama tanason ganinta Dan kebewa tayi Mata tambaya sbd ganin wani irin sauyib data tashi dashi a yau din na tsantsar yalwan farin ciki Dan zata iya cewa ta jima batagan hameeda cikin sakewa da annashuwaba kaman yau din.

Ɗan shiru ne ya biyo baya sai ta kalli Meena da tensed face sai Meena ta gyaɗa mata kai alamar it's all gonna be ok.. Karta damu

Bata gama tunanin ba sai ta ji gyarar murya a microphone sai a sannan ta sami relief ta yiwa Meena murmushi..

Ba a ɗau 3 seconds ba sai ta ji an kira sunan ta nan gaban ta ya faɗi sbd zaƙuwar da tayi ta ji an ce ta mallaki Khalid sai murmushi Meena ta mata

The next name that follows shine _Muhammad Saheeb Maƙarfi_..

Shiru tayi tana jiran jin a kira nata ango amma kuma sai me!?sai jiyo mallamin tayi yana faɗin

"jama'a ayi hakuri Adakace mu"..

Wani irin ras gaban mufida ya fadi

takalli meena

Tanason mgn saikuma takasa take ta ji kan ta ya sara kawai ta fara ganin dishi dishi bata ƙarasa jin yadda aka karasa wajen ɗaura auren ba ta koma ta mannu da bangon ɗakin idanun ta widely out tsaban fargaban da bata san mafarin sa ba

nan take hankulan matan ɗakin ya tashi banda mace ɗaya da yanzu ta shigo tana ce da su an dakatar da daurin aure kowa ya nitsu Mufida haka ta zauna shiru kamar statue babu uhm babu uhmuhm

Meena ce ta hau tambayar ya haka?

Wasu tambaya suke yi ko an sami akasi ne daga gun maɗaurin auren ko ya manta sunayen angwayen ne..

Matar nan dai na tsaye sai da surutur tayi yawa sai ta ɗan tsawatar masu ta ce

"Duk ku natsu,ina Hamida take?sai a yanzu aka fara waige waige inda Hamida take,nan hankula ya kuma tashi dan babu ita babu alamar ta..

Wata ce cikin masu duba Hamidar ta ce

"Mama ɗazu fah tana nan ana mata kwaliyya muna selfie tare da ita ina ta shiga"? gyaɗa kai matar tayi tana jinjina lamarin sannan ta ce

"Hamida da Khalid sun gudu,ba su gidan nan,ba su cikin anguwar nan kuma babu trace ɗin su"..

Babu wanda ya lura sai jin ƙarar faɗuwar mutum suka yi nan take aka juyo dan ganin wa ya faɗi,ko da suka juyo Mufida ce kwance a ƙasa kamar marar rai ga kwalliyar ta da ya shimfiɗu a saman fuskar ta ya mata kyau amma daga nesa kamar bata numfashi...

#Mamuh*_Mamuhgee_*

14

Rikicewa gidan biki yayi a nan waje maganganu aka rinka yi da masu tir da sigar da Hamida da Khalid suka ɗauka da masu tausayawa Mufida dan shagulgulan da aka yi a kwanakin bikin ya nuna irin ƙaunar da ke tsakanin Mufida da Khalid sai dai kuma yau da wannan abin ya faru,jama'a sun kasa bambance irin wannan lamari..

Kusan rabin yʻan biki sun fara tafiya saboda yadda bikin ya kasance akasin burin da aka dora a bikin amma yau da yake bikin ne sai abubuwa suka sauya.

An bar gidan biki da abubuwan al'ajabi wanda ake ganin ba a taba samin irin hakan a wuraren hausawa ba kamar yadda yake faruwa a wuraren kudu..

A sashen su Ammy kuwa haka Ammy ta rinƙa ji kamar ta saka kuka ba dan komai ba sai dan irin wannan abin maganar da Khalid ya bar mata because ba ta kan Hamida take ba duk laifin a yau ta alaƙanta sa ne da Khalid kuma abin na ran ta..

Hajja kan ta kasa taɓuka komai tayi murna ya koma ciki duk burin bikin takwarar tata kuma jikar ta abin ya wargaje,bambancin fushin ta da Ammy shine ita laifin Hamida take gani while Ammy ta ɗau zafi sosai akan Khalid kuma ta shirya mai..

Daddyn su fifi kuwa rasa abin faɗi yayi dan da a ce yau wata ce hakan ya faru da ita toh ba zai ji ciwo a ran sa kamar yadda yake tsananin jin ɓacin rai ba a yanzu da abin ya shafi rayuwar sa(Mufida kenan)..

Tun ana neman na haƙuri har aka zafafa abin tun safe har dare amma babu wani kyakyawar outcome.

Yʻan sanda da jami'an tsaro duk sun shigo lamarin amma babu wani sakamako mai daɗi da aka samo..

Hankula duk sun tashi tsoron Ammy bai wuce kar wani abu ya faru da Hamida ba dan ita ce mace da ko da wani abin zai faru ita ce abin a tausayawa..

Matuƙa Ammy ta ɗau zafi hakan ne ma ya sa daddyn su fifi bai nuna nashi ɓacin ran ba gudun kar abin ya fi haka amma ba dan baya jin zafin abin a ran shi ba..

Da ɗai ɗai dama aka bar gidan bikin gidan ya dawo shiru babu hayaniyar kowa kamar ba gidan biki ba abin dai abin ban mamaki da tausayi.

Misalin 10pm daddyn su fifi ya sa aka tafi dubo masa ita dan tun faruwar abin ƙulle kan sa yayi a ɗaki yana ba kan sa laifin gazawar sa a uba,yana ganin kamar ya kasa samarwa ɗiyar sa rabin ran sa farincikin ta wanda tunda ta taso tun yarintar ta har kawo yanzu komai take nema sai ya tafi ya samo mata shi..

Sai dai abin mamaki yadda ya gaza wurin samo mata farinciki mai daweamuwa har ƙarshen rayuwar ta...

Yana zaune a ɗakin sa yana ta tunanin yadda duniyar ta sauya masu su duka a cikin ƙanƙanin lokaci sai aka yi sallama wanda muryar Ammy ne.

Shigowa ɗakin tayi rungume da Mufida a jikin ta da duk ta fita hayyacin ta ta sauya kamanni kamar ba amaryar da few hours ta baza murmushi da annashuwa ba..

Kasa hada ido da ita daddyn su yayi sai kawar da kan sa gefe da yayi yana danne zuciyar sa dan kamar hawaye ne ke son ciko mai a idanun sa kuma ya san yana barin hawayen ya zubo toh fah zai kuma karyawa ɗiyar tasa gwiwa..

Suna ƙarasowa cikin ɗakin Ammy ta zaunar da ita sai ta bi Ammy da kallo idanun ta duk ya koɗr dan tun bayan faɗuwar da tayi aka yayyafa mata ruwa ta farka babu abin da ya mata daɗi sama da yin kuka kuma shi ta rinƙa yi har sai da ta ji kamar zuciyar ta na mata nauyi fiye da misali sannan ta ɗan sarara..

Girgiza mata kai Ammy tayi alamar ba tafiya zata yi ba tana nan tare da ita sannan ta saukar da kan ta ƙasa ta zauna shiru.

Zama kusa da ita Ammy tayi bata dai taɓa ta ba amma tana tsammanin faɗowar ta jikin ta da zarar hawayen ta sun fara zubowa..

Kusan mintuna goma suna zaune shiru,babu wanda ya tanka ko motsawa,sai chan daga bisani daddyn ya kira sunan ta a hankali.

"Mufida"!!kan ta na ƙasa amma sai da ta ji sunan har cikin zuciyar ta,take taji zuciyar ta ta karaya sabuwar kuka na son kufce mata amma dai ta danne ta amsa mai.

"Na'am daddy"!.shiru ya biyo baya sannan daddyn nasu ya daure ya hau yi mata nasiha akan yanayin rayuwa da yadda Allah ke tsarawa bawan sa rayuwar sa,duk tana sauraron sa tana tanƙwara zuciyar ta dan kar hawayen ta ya fito,amma maganar sa ta ƙarshe sai da ta karya mata zuciya har ta kasa haƙuri ta saki marayan kuka..

"Kuma ki sani matar mutum ƙabarin sa,dan kin rasa Khalid ba kin rasa miji bane hakan na maki nuni ne da ba alkhairi bane a gare ki kuma wani wanda shine mafi alkhairi a gare ki na nan Allah zai haɗa ku"..

Kuka sosai take yi bayan sauraron wannan kalamai nasa,bata san ta faɗo mai ba har tana maganganu cikin kukan nata ba sai da Ammy ta zo ta ɗaga ta ta rungume ta ai kuwa ta damƙe Ammy gam gam tana ta kuka yanzu ne ma take asalin kukan daga zuciyar ta sanin ta rasa Khalid kenan har abada dan ko bata san dalilin sa na gudun ta ba ta san tunda tare suka ɓace da Hamida a rana ɗaya toh ba ƙaramin abu bane kuma a ran ta bata jin son da yake mata na da ƙarfi because da yana da shi toh da ba zai ɓace a neme sa a rasa ba a rana mai albarka irin wannan ranar da ita da shi suka ɗau lokaci suna tsara sa ba...

Lura da daddyn su fifi da Ammy tayi kamar kuka zai yi sai ta janye ta suka bar ɗakin dan ita kan ta jarumtar ta ya ƙare ƙiris ya rage ta saki nata kukan dan wannan irin babbar embracement da Khalid ya saka ta ciki bata taɓa fuskantar sa ba..

A ɗakin Ammy haka fifi ta buɗe sabon babin kuka gwanin tausayi dan duk wanda ya kalle ta sai ya tausaya mata..

A haka tana kukan Ammy na rarrashi Hajja na zaune gefe rungume da ita bata sani ba bacci ya sace ta..

The next morning wuraren ƙarfen goma na safe sai ga mai gadin gidan ya shigo a guje kamar ya ga abin ƙi yana haki yana kallon Ammy dake zaune a kujerar dinning ita ɗaya tana tunanin fifi da kusan sau uku tana zabura cikin baccin ta jiya ƙarshe sai da aka kirawo family doctor ya zo ya duba ta cikin daren ya mata abin da ya dace sannan aka sami sukuni..

Kallon sa Ammy tayi ta tambayi lafiya,sai a sannan ya iya buɗe baki ya faɗa mata ai Khalid ne ya dawo yanzu tare da Hamida..

Rass gaban Ammy ya bayar dan haka ta tashi ta wuce mai gadin ta nufi hanyar ƙofa ta leƙa ta ga su ɗin ne abin su..

Dawowa ciki tayi da sauri ta nufi sashen Hajja ta faɗa mata abinda ke faruwa itama Hajja cikin tsinkewar zuciya ta tashi ta fito zuwa parlor..

Daga ɗakin Hajja Ammy ta nufi ɗakin ƙanin ta daddyn su fifi ta ce da shi ya sauko zuwa parlorn ƙasa ga su Khalid nan sun dawo..

Tashi yayi ya fito tana gaba yana bayan ta suka sauko ƙasan,step ɗin daddy na ƙarshe yayi daidai da shigowar su parlorn..

Sai bai ƙarasa saukowa ba ya tsaya a nan last step ɗin ya ƙurawa Hamida ido yana nazarin ta yadda ta zamo so selfish..

Ammy kuwa bin su da ido kawai tayi tana jinjina kai dan ko ɗazu sai da aka kawo masu feedback akan fah ba a gan su ba ashe suna hanya...

Tsayawa suma suka yi a tsakar parlorn ganin all eyes on them sai ya ja hannun Hamida ya maida ta bayan sa shi kuma ya fuskanci iyayen nasu..

Riƙe hannun ta da yayi a idon Ammy da daddy sai gaban Ammy ya faɗi tsoro ya shige ta firgici ya rinƙa ziyartar ta akai akai..

Suna tsaye kamar an dasa su Hamida na a bayan sa kan ta ƙasa shi kuma ya buɗi baki direct babu ɓuya ya ce

"Ku yafe mana"!!wani dum gaban Ammy ya bayar dan bata yi tunanin abu mai kyau bane ya faru a tsakanin su ba..

Babu wanda ya tanka masu sai Hajja dake zaune ce ta dube su ta ce

"Na me"!?sai ya kuma haɗo jarumta da tattaro qarfin hali da zare tsoro da kunyarsa sbd shine namiji Kuma shugaba sunyi alqawarin shine zaiyi bayani ba wani kwana kwana tunda dai sungama komadai menene. amsa kakar ta su yayi

"Na gudun da muka yi,ku yafe mana"!!sai Hajja ta ji ran ta na kuma ɓaci a ce a shashancin namiji mace ta saka kan ta ciki..

"Gudun da kuka yi?me ya sa kuka dawo bayan kun zaɓi gudun"?tambayar da Hajja ta masu kenan wanda ya dirar masu ba tare da sun shirya ba sai Khalid ya ce

"Mun dawo ne dan dalilin gudun namu ya riga ya gabata"!!turus Ammy tayi tana sauraron su yet Hajja ce ta kalle sa ta ce

"Wani dalili kenan da ya gabata har ya sa kuka waiwayo daga gudun naku"?dama tambayar da yake so ya ji kenan sai ya ce

"Auren mu,ni da Hamida"!!Ammy was like what??aure?shi da Hamida?wani irin madness ne wannan..

Kasa haɗa ido yayi da Ammyn nasa dan ya san tambayoyi da dama na yawo a zuciyar ta sai kawai ya hau bayani because ya san ko yayi shiru he owe them an explanation..

"Ammy,Hajja,Daddy ku yafe mana ba fushin ku muke so ba a yanzu,albarkar ku zai fiye mana dan in har babu albarkar ku auren nan namu da muka yi ba zai yi tasiri ba"!!dum gaban daddy da Ammy ya bayar jin wai har sun yi aure ba wai zasu yi ba but how??..

"Ni da Hamida mun gudu ne dan samarwa zukatan mu abin da muka daɗe muna muradi kuma shine auren junan mu ba auren mabambantar ra'ayoyin mu ba da aka zaɓar mana"!cutting nasa Ammy tayi a tsawace ta ce

"Mabambantar ra'ayoyin ku da aka zaɓar maku,Mufidar ce ba ra'ayin ka ba"?shima a hanzarce ya maida mata da amsar

"Yes Ammy,Mufida was never my choice,Hamida ce zaɓi na kuma ita na so tun asali"!!kan su ne ya ɗaure sai kawai Khalid ya cigaba da maganar sa

"Eh Ammy,Hamida ce zaɓi na ba Mufida ba"wani tsawa Ammy ta daka mai but sai daddy ya dakatar da ita dan cin ribar zancen dan haka ta haƙura tayi shiru nan fah Khalid ya hau warware masu ai tun kafin su haɗu a ranar da su Hamida suka taho nan Nigeria shi ya riga da ya san ta kuma sun san juna haka suna soyayya toh da suka yi realising cewa su ɗin families ne sai abin ya ƙara ƙarfi dan haɗuwar su a wata experience ne da ita Hamidar ta tafi yi a ƙasar Cyprus sai suka haɗu toh shine suka ƙulla alaƙa wanda daga baya ya girma for almost a year,a ranar da suka haɗu kuma a airport sai basu sami damar bayyana kan su ba a matsayin waɗanda suka san juna ba,abu ɗaya da ya shiga tsakanin alaƙar su ta soyayya shine shigowar fifi rayuwar su,duk yadda fifi ta ɗau alaƙar tasu ba haka bane shi a wurin sa dan ya fi ɗaukaka relationship ɗin su a matsayin ƙanwar sa ta jini kuma twin sister ɗin macen da ya fi so a rayuwar sa..

Ana haka suna soyayyar su a ɓoye ba tare da sun bayyana ba akan suna jiran right time su kuma basu sani ba ashe iyayen nasu na hango masu wani abu ne daban..

A cewar Khalid,ranar da labarin ya riske su ne shi da Hamida suka hau nemar hanyar hana faruwar auren amma lokaci ya ƙure ba yadda suka iya sama da bariwa Allah komai dan in suka ɗaukaka maganar toh hankalin fifi zai tashi kuma ba lallai bane a yarda a bar su su mallaki junan su ba,shi yasa suka yi shiru kawai but ganin lokaci na ta gabatowa kuma ba lallai bane su mallaki junan su ba sai kawai suka yanke shawarar guduwa a rana bikin ba tare da sun bari an gano su ba dan kar a yi yunkurin nemo su ba tare da sun mallaki junan su ba..

A jiyan bayan gudun su ne suka tafi wani wuri aka ɗaura masu aure kuma yanzu da haka suna a matsayin mata da miji ne..

Yana rufe bakin sa hawayen dake maƙale idanun Ammy ya zubo Hajja kuwa kasa ko da motsi tayi sai Ammyn ce ta kalli Khalid ta ce da shi ya matsa mata ta ga fuskar Hamida,cikin sanyin jiki ya matsa mata sai ta ɗan tako kusa da ita ta tsaya ta ƙare mata kallo sannan ta buɗi baki cikin sanyi ta ce

"Ta ya aka yi ke kika fita kika bar gidan nan ba tare da mun sani ba"?shiru Hamida tayi daddy na kallon ta da sauraron ta,sai da Ammy ta kuma maimaita tambayar ta sannan Hamida ta ce mata

"Ammy a lokacin da ake ƙara yiwa fifi kwaliyya ne bayan an gama yi min nawa,toh na ga hankulan mutani na kan ta ana ta ɗaukar hotuna sai na ɗau hijabin ta na saka na janyo shi ya rufe min fuska,shine na sauko na bi hanyar ƙofar baya na fita a nan na ga yaya Khalid cikin wani taxi sai ya ɗaga min hannu na tafi na same shi muka tafi inda aka ɗaura mana auren toh a gidan limamin muka kwana ni na kwanta a ɗakin matar sa shi kuma ya kwana a ɗakin baƙi,sai yau da safe muka ɗau hanyar dawowa gida dan mu nemi yafiyar ku"!!kai ayar bayanin ta yayi daidai da isowar daddy gaban ta a harzuƙe abin da bai taɓa yin sa ba,ɗaga hannun sa yayi da nufin marin Hamida cikin ɓacin rai da raɗaɗin zuciya yayin da ita kuma ta runtse idanun ta tana jiran saukar marin dan ta shirya masa tuntuni..

Muryar fifi ne ya dakatar da daddy daga aiwatar da abin da yayi niya..

"Daddy dakata...,please"!!muryar ta a karye ta jawo hankalin sa abin da basu sani ba tun zuwar su Hamida gidan akan idon ta ne har kawo wannan warwararriyar bayani nasu duk tana ji kuma tana kallon su..

Ƙarasa saukowa tayi sai Khalid ya kawar da kan sa gefe Hamida kuma ta saci kallon fuskar fifi amma sai ta ga babu hawaye face tawakkali..

Riƙo hannun daddyn nasu tayi ta saukar tana girgiza mai kai alamar kar yayi komai ya bar shi kawai..

"Daddy babu abin da zaka yi da zai sauya destiny ɗin mu,ko ka manta jiya da kan ka ka min nasihar matar mutum bata wuce sa dan haka yar uwa ta Hamida ita ce matar yaya Khalid ba ni ba kuma Allah ya san da haka dan shi ya tsaro mana hakan a rayuwar mu dan haka daddy,Ammy da Hajja ku yi haƙuri abin da zai faru ya faru bamu isa mu sauya sa ba ok"?ta ƙarasa da murmushin dole wanda ya karya zuciyar Khalid sai ta kalle su ta ce da su

"Na taya ku murna ubangiji ya dawwamar da farinciki a rayuwar ku"!!tana kaiwa nan ta juya ta koma ciki,duk jikin su sai yayi sanyi fifi dake haba haba da mutani babu ruwan ta da damuwa dan ta san ko ta sakawa kan ta ba lafiya ce da ita ba,wai yau ita ce ta komo haka...

Kasa aiwatar da komai suka yi dan duk inda maganar kamun hankali yake Mufida tayi sa,hukuncin su ba komai zai gyara ba sai dai ya ɓata dan haka Ammy ta kalle su ta kuma tana girgiza kan ta kafin ta ce da su

"Sai ku tafi apartment ɗin shi Khalid ɗin Allah ya bada zaman lafiya"!!dama an gyare two apartments ɗin da na Khalid da na yayan sa Saheeb so amare kawai ake jira su tare...

Bayan Ammy ta gama magana ta juya abin ta daddyn su kam baya jin ganin fuskar Hamida bare ya mata fatar da Ammy ta masu dan haka wucewar sa yayi haka Hajja ta tashi itama ta bi su da kallon ta girgiza kai sannan ta wuce..

Kʼarshe komawa apartment ɗin Khalid ɗin suka yi inda suka tare a matsayin ma'aurata even though akwai matsalar family dake kan su hakan bai hana su raya daren ranar ba...

A fannin fifi kuwa wuni tayi cikin zugin zuciya da rarrashin kan ta wanda abin ya ishi su Hajja har Ammy ta ce mata

"Mufida ki ɗau shawara ta a ɗaura maki aure da yayan ku Saheeb dan kina buƙatar mai kula da ke fiye da wanda mu muke maki a yanzu duk da ya zo jiya amma ya koma immediately auren ku na iya faruwa in ya so daga baya in ya dawo sai kuyi assuming duties ɗin ku ko ke ki bi sa can inda yake kin ji"?Hajja tayi na'am da wannan shawarar dan haka ta gyaɗa kai ita kam fifi ba a hayyacin ta take ba sai ta saka murmushin dai mai galabaitar da zuciya ta ce

"Ammy duk yadda kika yi zaɓin ki daidai ne a gare ni kuma ni zan maki biyayya sbd nariga na rasa zabina har abada Don kuwa ko mutuwa hameeda tayi Khalid ya haramta ga rayuwata har abada,

Farin ciki da rayuwar auren danake fata da buri har abada na rasashi"!!?rungume ta Ammy tayi ba tare da ta bar hawayen idon ta ya fito ba tace"

Khadija da yardar Allah aurenki da SAHEEB sai kinyi kukan farin ciki domin saikin kasance cikin Mata masu Saar aure.

'dan juyowa tayi takalli hajjn idanuwanta na cikowa da hawaye tana maidawa tayi murmushi mai tsananin ciwo ahankali can qasan maqoshi ta furta"

Mai matan???

Nida bantaba Sharing komai arayuwataba sai iyayenmu shine yanzu zance cikin tsofi muna gogayyar miji nida matarsa.

Har dare suna tare da ita suna bata magana da ƙyar dai bacci ya ɗauke ta,Ammy ta sanar da daddyn su tunanin da shawarar datayi da alhaji Abbas wani qaninta namiji daya rage Mata shima ya manyanta sosai

Akan mganar auren saheeb da fifin

ya ce in dai ta yarda shi bai da matsala Dan shima kam zaiso auren fifin da saheeb dama tun farko shi sukaso hadata dashi Amma ganin yanda take da Khalid yasa sukace shi din sbd ganinsu so ne atsanakin nasu Ashe ashe,

albarka Hajja ta saka mai dan yayi jarumta da tawakkali..

Washegari a cikin gida misalin ƙarfe goma na safe aka ɗaura auren MARSHALL MUHAMMAD SAHEEB Maƙarfi da KHADIJA NUHU MANDE ɗaurin auren da aka yi sa cikin shiru ba tare da hayaniya ba ko gayyata dan basu buƙatar kowa sai su...

A ranar bayan an ɗaura auren Mufida ta ƙulle kan ta a ɗaki ta sami damar fitar da damuwar zuciyar ta dan kuka tayi sosai har sai da numfashin ta ya rinƙa sama sama sannan ta sararawa kan ta ta watsa ruwa ta fito da alwala tayi nafila raka'a biyu tayi addu'ar da zata yi sannan ta kwanata bisa sallayar.

Tunani takeyi aranta gameda yanda rayuwar ta juya cikin sauri,

Itace da auren tsohon datakeyiwa 'yaruwarta maganar aurensa,

Shin ita wane farin ciki ko Jin dadin rayuwar aure zata samu a auren Wanda ya tsofeta?

QADDARA TA RABATA DA WANDA TAKE TUNANIN SHINE ABOKI MAHADAR RAYUWARTA,

MIJINDA 'YAR UWARTA DASUKA FITO CIKI DAYA,

RANA DAYA,

AWA DAYA MINTINA BIYARNE A TSAKANINSU ZATA AURA AURENSA YADAWO KANTA BAYAN TANA TUNANIN BATADA WANI ABOKIN RAYUWA KAMAR KHALID,

WACE QADDARACE WANNAN?

SHIN MENENE MAKOMAR RAYUWAR AURENTA DA WANDA HARYAU BATAGA KALARSABA.

Ahankali ta rintse idanuwanta dasuka fara bushewa da kuka tana Kiran sunayen ubangiji sbd yanda zuciyarta ke zafi da nauyi.

a nan bacci ya ɗauke ta dan ta sami sassaucin cunkushewar zuciyar ta..

#Mamuh*_Mamuhgee_*

15

Da safe aka kawo abinci sashen su Hamida daga Hajja kuma saboda Khalid ba dan Hamida ba dan halin da Hamida ta nuna a shekaranjiya ya saka Hajja jin wani iri tana mace amma tunanin ta irin na da namiji har yau abin bai bar kan ta ba..

Bayan an kawo abincin a ajiye masu aka fita dan basu tashi daga bacci ba sai wuraren 11am tun sallar subhi da suka yi suka koma sai yanzu suka farka kenan an

yi ɗaurin auren Mufida da Saheeb ba tare da an gayyace su ba musamman shi Khalid ɗin..

Cikin shigar atamfa riga da zani haɗe da babban mayafi Hamida ta fito ta tarar da angon nata yana jiran ta sun je su gaida su Ammy su kuma yiwa Hajja godiyar abincin da ta aiko masu da shi dan sun san dama Ammy na fushi da su ƙila sai anjima zata saurare su..

Shima Khalid din a yau yayi shigar alfarma ya fito a angon shi half kaftan da hula shirin da bai taba yi ba kenan tunda ta san shi dan ko a ranar bikin nasu wani irin kaftan ya saka da bai fiddo sa ba..

Murmushi shimfiɗe saman fuskar su suka nufi sashen Ammy inda ta amsa gaisuwa kawai ba tare da ta kuma tanka masu ba har suka ƙaraci zaman su suka wuce zuwa sashen Hajja da tunanin ita zata tarbe su da sanyin fuska tunda ta aiko masu da abinci sai dai ba yadda suka yi tsammani bane dan yadda ta ɗaure fuska ta kawar da kan ta gefe kaɗai ya tabbatar masu har yanzu fushin take yi da su kuma fuskar su kan sa bata jin ganin sa..

Tashi suka yi suka nufi sashen daddyn su,inda aka sami bambanci kenan dan shi ya amsa gaisuwar tasu ba yabo ba fallasa kuma ya masu fatar alkhairi haɗe da sanar da Khalid batun ɗaurin auren da aka yi na ɗan uwan sa da ƙanwar sa yana mai ce da shi ya kira ɗan uwan nasa ya masa fatar alkhairi..

Ko da Khalid ya ji wannan zance babu inda bai yi sanyi ba a jikin sa dan bai yi tsammanin farat ɗaya za a ɗau hukunci mai zafi haka ba,yayi tunanin za a ba Mufidar damar zaɓar abokin rayuwar ta ne dan har ya fara tunanin haɗa ta da wani abokin sa na kusa mai ɗabi'u kusan irin nasa amma an riga an gama tunda aka aura mata yayan sa sai dai matsalar shin tana son yayan nasa kuwa ko dai haɗin iyaye ne?

Tambayar da ya rinƙa kai kawo kenan a zuciyar sa amma ya san bai da wannan ƙimar na tambayar daddyn dan laifin sa na nan bai goge ba da saura ko da zai gogen amma sai ya ɗau lokaci shi ya sani,wannan dalili ya sa ya ja bakin sa yayi shiru har daddyn ya gama nasihar sa a gare su ya sallame su suka fita bai bar tunanin ya lafiyar fifi ba kuma a wani hali take...

Suna fita Hamida ta ja hannun sa zuwa old room ɗin ta tayi saurin saka lock ta cire mayafin ta da dama ya ishe ta sbd rashin sabo..

Dariyar ta da ta rinƙa dannewa ne ya fito fili sai da ta dara har tana riƙe cikin ta mijin nata na kallon ta sannan ta matso kusa da shi ta rungume sa tana mai cigaba da ƙarasa yar dariyar da ta rage mata..

Shi dai Khalid bai san me ya saka ta dariyar ba kuma hankalin sa da tunanin sa na ga fifi ko a wani hali take,wannan dalili ya sa bai ce mata komai ba har ta zo ta rungume sa sannan ya sami damar tambayar ta..

"Me ya faru ne love kike dariya haka tun ɗazu"?jujjuya kai ta shiga yi tana murmushi sannan ta ce

"Miji na dariya ta manufofi biyu gare ta,na farko aurar da fifi da aka yi ga wannan tsohon da aka so a haɗa ni da shi,na biyu kuma murnar samin ka da nayi a matsayin miji na da na rasa ka in har a ranar nan an aura maka fifi ni kuma aka aura min wannan tsohon amma Allah na amfani da zuciyar mutum ne ba kalaman sa ba shi ya sa ya bamu ikon mallakar junan mu a matsayin ma'aurata bai bar mu mun zalunci wani ko wata ko wasu ba ya bar mu tare dan Allah kaɗai ya san abinda ke zuciya ta da ban mallake ka ba miji na,na godewa Allah da ya bani kai kuma ya mallaka min kai please don't ever leave me i will die if you forsake our love"!!da ɗan muryar kuka ta ƙarasa maganar dan wani irin azababben so ƙauna da shauƙin mijin nata dake shigar ta bata san ya zata iya rayuwa a doron ƙasar nan ba tare da shi ba..

Khalid dake sauraron ta cikin mamaki da jimami sai ya kasa faɗin abin da yayi niyar faɗi musamman da ya ji yanayin muryar ta ya sauya kamar kuka take yi sai shima ya ƙara tightening hug ɗin yana mata alƙawarin duk wuya duk runtse suna tare babu mai raba su sai hukuncin ubangiji..

Cikin zurfi a tunanin maganarta cikin ransa nazarin maganarta,

Shin sunkuwa San waye Marshall dasuke kiransa da tsoho?

Tabbas basuda masaniyar waye Marshall Amma bazai fadaba zai Bari su gani a idanuwansu.

Kusan mintuna sama da biyar suka kwashe suna a haka sannan ya raba jiki da ita ya ɗauko mata mayafin ta ya yafa mata dan su koma sashen su su ci abinci..

Har sun fito hannun sa cikin nata sun zo giftawa sai ta ji zuciyar ta na raya mata yin wani abu a ɗakin da suka wuce yanzun nan dan haka ta ɗan ja da baya tana ce ma Khalid

"Baby ka tafi ina so in gana da yar uwa ta zan zo in a jiffy"!!shi babu abinda ya zo mai rai jin ta ce zata gana da yar uwar ta sai ya gyaɗa mata kai ya ce zai raka ta amma ta ce ta yafe mai ya tafi ita zata zo daga baya.

Sai da ta tabbatar ya tafi gabaɗaya sannan ta koma da baya ta nufi ɗakin fifi bakin ta ɗauke da sallama sai dai bata ji an amsa ba so ta tura ƙofar ta shiga..

Hango fifi tayi kwance saman sallaya tana bacci fuskar ta ya ɓaci da hawaye sai tayi murmushi tana jin wani sanyi a ran ta..

Ƙarasawa gare ta tayi tana taku ɗai ɗai har ta zo ta tsuguna tana ƙare mata kallo,tunowa tayi da ranar da fifin ta kawo mata ziyara ta gama tsokanar ta sannan ta gaya mata wai tausayin ta take ji duk kyawun jikin ta wannan tsohon ne zai mora,sai tayi murmushi haɗe da lumshe idanun ta sannan ta cigaba da maganar zucin ta tana faɗin yanzu wa yayi asarar kyau da da surar jiki?ke Mufida dan ke kika ƙare da tsohon da kike murnar ni zan aura oh na tausaya maki dama haka rayuwa take yau kayi dariya gobe ko anjima ka yi kuka...

Ina tsananin sonki yar uwata fiyeda komai da kowa a duniya

Sai zuciya Batada qashi bansan ya zanyi na Hana zuciyata tsanarki ko kishinki ba sbd sune sukeda haqqin sakamin qiyayyarki yar uwata duk da nasan ba laifinmu bane Amma we'll have to pay the price for abinda iyayenmu keyi,

Zan nuna baqin cikin danai shekaru Ina boyewa tareda dannewa Ina qunsa kodan Su girba abinda suka shuka

I'm sorry my Fifi.

Kuma murmusawa Hamida tayi tana sauke ajiyar zuciya haɗe da furzar da iska daga bakin ta..

Tapping bayan fifi tayi ba tare da ta ce mata komai ba har sai da fifi ta buɗe heavy eyes ɗin ta ta ɗora su kan fuskar Hamida dake ta baza murmushi..

Tashi zaune Mufida tayi tana gyara hijabin jikin ta sannan ta zauna bayan ta matsa nesa kaɗan da Hamida..

Kallon behaviours ɗin ta Hamida tayi sai ta taɓe baki tana ɗan yin fari da ido unexpectedly sai kalmar zuciyar ta ya fito sarari..

"Na ji an ɗaura auren ki da...yaya Saheeb wai ko"!?ɗago kai Mufida tayi ta kalli Hamida sai ta ga sai murmushi take ta yi babu alamar damuwa a fuskar ta..

"Toh nothing big,kawai zuwa nayi na musamman dan in maki fatar alkhairi da samin miji irin naki wanda ban taɓa gani ba tunda nake a rayuwa ta ina maku fatar samun zaman lafiya mai ɗorewa har ƙarshen rayuwar ku"!!tana kaiwa nan sai ta miƙe tsaye ta juya leaving fifi to be staring at her kamar stranger..

Ɗan dakatawa tayi bata fitan ba sai ta juyo irin surprisingly ɗin nan ta kalli fuskar fifi,cikin son ƙure haƙurin ta ta ce

"Oh na manta,kina cikin jimami ne shi ya sa kika kasa yi min ni fatar alkhairi da nawa auren amma ba komai na fahimta ai na san ba zaki min baƙin ciki ba da nawa mijin dan bai zamo namijin da ya kwana biyu kuma second hand ba,jini ne ke yawo a jikin shi sabo fil yana ji da ƙarfi dan akan gaɓar sa yake lafiyayye ne ya haɗa duk abinda nake burin miji na na aure ya haɗa and guess what?i have been appreciate him for everything,though na tausaya maki yar uwa ta da kika yi rashi rashin da har abada kin yi sa dan ke da sanin dadin aure ina ga sai ko a aljanna in ana yi but a nan duniyar kam,

I'm sorry Fifi karkiga laifina laifin wainda suka zaba Mana wannan halinda muke cikine,,have a nice day ahead"!!tana ƙarasawa ta fita tana ɗan dariya haɗe da rufowa Mufida ƙofar ɗakin..

Tunda ta fara yaɗa mata wannan maganganun sai ta sanƙare zaune tana tunanin anya Hamida yar uwar ta na jini ce wannan ko dai an musanya mata da wata ne dan bata yi kama da Hamida ba ko daga yanayin maganaganun ta ya bambanta da na Hamida because ba ƙaramin abu ne ke saka Hamida tankawa mutum ba in yayi mata magana,sai ga wannan Hamidar ba tankawa kaɗai tayi ba hasalima ita ce ta janyo maganar kuma tayi sa ta tafi ba tare da ta jira amsa ba,anya wannan yar uwar ta ce kuwa?..

Wani sashe na zuciyar ta ne ya amsa mata _"Eh ita ce mana ko baki ji tana ta yaba mijin ta bane?mijin da kika daɗe kina tunanin zai zama naki amma a yau ya zama nata,kuma baki ji ta ce she has been appreciating him for everything bane?kenan ita ce dai yar uwar taki Hamida yar ywar tawainiyar ki"_..

Kuka ne mai ƙarfi ya ci ƙarfin fifi wanda ta bar zuciyar ta ya rinƙa tunzira idanun ta suka rinƙa fitar da hawayen,kuka tayi sosai har sai da ta fara shiɗewa sannan ta kwanta ruf da ciki numfashin ta na sama sama da ƙyar ta iya nemo wayar ta ta kira Ammy,jim kaɗan sai ga Ammy ta shigo a rikice hankali tashe..

Samin ta a halin da take ciki sai da ya tsorata ta because ɗazu bata ga kukan da tayi ba bayan ɗaurin auren sai yanzu..

Natsuwar Ammy ɗaukewa yayi ya hau nemo layin family doctor ɗin su akan ya zo ya duba masu Mufida dan al'amarin yana bata tsoro yanzu..

Kafin zuwan doctor ɗin har ɗakin ya cika da Hajja da daddyn su fifi hankalin kowa tashe,duk tunanin su ko auren da aka haɗa ne ya ɗaga mata hankali har ta shiga damuwa irin haka..

Bayan gwaje gwajen da Dr yayi ya san yadda yayi calming Mufida har ta fara bacci sai ya jawo attention ɗin su inda ya fayyace masu cewa ran ta na yawan ɓacin akai akai daga shekaranjiya zuwa yau kuma duk wani mummunar outcome da zai faru toh sune sanadi dan sun san condition ɗin ta amma suke ƙyale ta tana experiencing irin wannan pains ɗin a lokaci kusan ɗaya..

A ƙarshe wasu special bulk laxatives ne ya rubuta masu da wasu magungunar akan su samo mata dan su zasu rinƙa taimaka mata in ran ta ya ɓaci tunda su iyayen sun kasa samo mata kwanciyar hankali...

Bayan tafiyar sa Ammy ta zauna a gadon ta dake bacci ta rungumo ta jikin ta ta rinƙa kuka tana maganganu wai ta kasa samarwa ɗiyar ta farincikin da take so she feels like she failed as a mother..

Daddyn su da niyar sa ya koma tun jiya in da komai ya tafi yadda ya kamata,amma faruwar wannan abin ya sa dole ya zauna a nan ɗin duk da ya so ya koma gidan sa a nan Nigeria ɗin amma condition ɗin fifi bai yi warranting nasa matsawa ko nan da can ba...

Hajja ce ta rinƙa rarrashin Ammy itama tana share ƙwallar ta cikin tsananin tausayin jikar nata dan duk yadda ta ƙiyasta azabar da fifi ke ji a zuciyar ta abin ya fi haka basu taɓa shiga tashin hankali ba irin ta wannan kwanaki duk a sanadin Khalid..

****

Fifi bata farka ba sai wuraren magrib,buɗe idon ta na farko a fuskar Ammy ne da yanzu ta gama share hawayen ta..

Dama ita take ta kallo tun ɗazu kafin ta farka toh yanzu da ta buɗe idanun ta sai Ammy tayi saurin matsowa kusa da ita ta ɗago ta ta haɗa ta da jikin ta tana bata haƙurin laifin su ita da Hajja haɗe da yi mata alƙawarin in har ta ce bata son auren nan yau sai a warware sa dan da zaman rayuwar takura gwara zaman ingantaccen rayuwa.

To Ammy's greatest surprise sai fifi ta ce a'a kar a ma auren komai a bar shi Allah ne ya sauko mata da wannan jarabtar a daidai wannan lokaci dan ya gwada imanin ta kuma ba zata kaucewa wannan jarabta ba har sai ranar da ya ƙare...

Zantukar ta ba ƙaramin daɗaɗawa Ammy zuciya yayi ba sai ta ji wani sabon so da ƙaunar ta ya shiga zuciyar ta bata taɓa ganin yarinya mai tawakkali kamar Mufida ba wannan ya sa ita kuma tayi alƙawarin kare ta har iya inda ƙarfin ta ya ƙare...

Ita Mufida a zuciyar ta tana jin raɗaɗin abin da yar uwar ta ta mata ɗazu amma ta danganta hakan da ƙaddarar ta ne kuma bata isa ta sauya nata ƙaddarar ba ko da kuwa hakan na nufin saɓawa _Ƙaunar_ da take yiwa Khalid ne da yar uwar ta...

Tun daga ranar Ammy ta maida kular fifi ɗakin ta komai nata ya dawo sashen Ammy cin abincin ta shan maganin ta ruwan shan ta hatta da murmushin ta Ammy na kula da shi dan kar su rasa ta ba tare da sun shirya ba...

Kimanin kwanaki bakwai kenan komai nata baya tsallake sashen Ammy tana iya cewa tun ranar da Hamida ta zo ɗakin ta ta mata wannan maganganun bata sake ganin ko shadow ɗin ta ba har yau kuma hakan ya fiye mata dan tana tsoron haɗa ido da ita bata san me zata kuma jefar ta da shi ba..

Khalid kam bata gan sa ba kuma bata son ganin sa dan ganin sa daidai yake da karayar zuciyar ta ita kuma ba so take ta cigaba da saka iyayen nata da kakan ta cikin damuwa ba akan ta sake jiki tayi kamar ba abin dake damin ta duk da ba kamar old self ɗin ta ba magana jefi jefi take yin sa ba sosai ba amma a cikin maganar sai ta saka abin da zai ba mutum dariya ko kaɗan ne but ita ba zata yi dariyar ba sai dai ta ɗan murmusa a hakan ma family ɗin nata na jin daɗin sauyin da suka gani tattare da ita....

#Mamuh*16*

Yau da farinciki fifi ta tashi so tun safen ta yi wanka

ta saka doguwar rigar ta cikin waɗanda Ammy ta fitar mata a matsayin irin suturar da zata rinƙa sakawa duba da yanayin ya canza da da yanzu ba ɗaya bane,auren wani ne akan ta presently..

Zaman jiran shigowar Ammy ta zauna yi dan ta roƙe ta alfarmar fita zuwa zaga gidan zaman wuri ɗaya ya ishe ta ga ba abokan hira wayar nata ma Ammy ba kasafai ta cika barin ta tana taɓawa ba gudun kar a yi wani kiran da zai ɗaga mata hankali.

Jim kaɗan da zaman ta Ammy ta shigo da wani babban tray cike da kulolin abinci da plates har huɗu da kofuna,fuskar ta cike da murmushi ta ƙaraso ciki da sauri fifi ta miƙe ta tarbe ta tana gaida ta da ƙoƙari.

Zama suka yi kusan a tare fifi na ta yiwa Ammy sannu da ƙoƙari haɗe da tambayar me ya sa bata kira ta sun yi tare ba sai Ammy ta mata nuni da ai bacci take a lokacin shi yasa bata tada ta ba...

"Ammy what's the surprise all about"?murmushi Ammy tayi mata tana shafo fuskar ta sannan ta amsa mata

"Family breakfast zamu yi yau kin sa yau juma'ah ne kuma haka al'adar gidan nan take"!!gyaɗa kai fifi ta mata tana tashi tsaye dan raka ta zuwa kwaso sauran abincin because a babbar falon ta za a ci abincin..

Jere kayayyakin abincin suka yi zuwa wani lokaci sai ga daddyn su da Hajja sun fito aka zazzauna a ƙasan carpet ɗin falon,ganin Ammy na serving ɗin su abincin ya tabbatar mata da su kaɗai zasu ci abincin ban da su Hamida..

Cikin son juna suka ci abincin suka gama aka kwashi kayan abincin aka mayar kitchen sannan aka koma main parlor aka cigaba da hira inda a cikin hirar ne fifi ta roƙi alfarmar barin ta ta fita dan zaga gidan zaman wuri ɗayan ya ishe ta da fari dai Hajja fargaba ne ya shige ta kar su haɗu da Khalid ta tuno wasu abubuwan da zai ɗaga mata hankali amma ganin kamar ana danne mata hakkin ta da yawa sai ta ƙyale bata ce komai ba..

Ammy ce ta ce mata ba damuwa sai dai kar ta kai kan ta sashen angon nata ta bari har ya dawo ya zo ayi siyan baki sannan a kai ta..

Ita dariya ma maganar Ammyn nasu ya bata sai dai bata dara ba ta murmusa kawai tana mai tashi dan fita zuwa zagayen.

A hankali a natse ta sauko zuwa farfajiyar gidan ta hau tafiyar ta ita kaɗai tana dube dube,duk idanun su Ammy da Hajja na kan ta daga windown sama suna monitoring ɗin ta dan kar wani abu ya faru da ita..

A haka har ta ɓace masu dan ta zaga wani sashen da basu san hanyar da ta bi ba..

A zagayen nata ne ta isa wani sashe da bata san ko na waye ba da kamar ta wuce sai ta dawo ta buɗe ta shiga ciki..

Da shigar ta idanun ta yayi mugun gani dan kuwa Hamida ce sanye da kananan kaya tana magiyar Khalid ya miƙo mata abin rufe jikin ta da ya ɗauke shi kuma yana daga nesa babu kaya a jikin sa yana mata wasa da abin rufan yana mata dariya...

Silently ta koma da baya ta turo masu ƙofar sashen tana danne abin da ya fara ziyartar zuciyar ta tana ƙoƙarin nemar hanyar komawa inda ta fito.

Da ƙyar ta samo hanya ta nufi sashen Ammy,da shigar ta bata tsaya ko ina ba sai cikin bedroom ɗin Ammyn ta kwanta akan gado sai hawaye shar shar tana nadamar bin shawarar da zuciyar ta ya bata akan komawa ta shiga sashen da bata san zai ɓata mata rana ba..

Kuka tayi sosai sannan ta nemo wayar ta ta kira layin Meena wacce tun ranar bikin ita da yayan ta Ameed suka koma gida basu sami damar ganawa ba..

Ringing kaɗan Meena ta ɗaga suka gaisa ta ji kamar ta fallasa zuciyar ta ma Meena nan take ta bi shawarar ta hau zayyanewa Meena abin da Hamida ta biyo ta ta mata a kwanaki shida da suka wuce,nan dai Meena ta bata shawarwarin da ya kamata sannan suka yi sallama...

Kuma nemar layin wata aminiyar ta tayi cikin turawar ƙasar germany da suka yi karatu tare,sai dai bata sami damar yin kiran ba sakamakon shigowar da taji an yi cikin ɗakin nata.

Ɗago kan ta tayi sai ta ga Khalid ne da Hamida a bayan sa cikin kwanciyar hankali kamar ita ɗin bata da wata damuwa a rayuwar ta abin mamaki twin sister ɗin ta blood ɗin ta..

Hankalin Khalid tashe ya nemi wuri kusa da fifi ya ɗan tsuguna yana ƙare mata kallon tausayi.

"Mufida ya jikin ki,ban sani ba sai yanzu Hajja ke sanar da ni da fatar kin sami lafiya"?kallon sa tayi sau ɗaya sai ta kawar da kan ta kawai alamar ba son ganin sa take ba bare amsa maganar sa..

Ya san dama da hakan dan har yau yana jin wani iri a zuciyar sa akan abin da ya faru a kwanakin nan ya san ba nan kusa zata gafarce sa ba amma hakan ba yana nufin zai karaya bane da nemar yafiyar ta ba..

Hamida dake kallon mijin nata yana nuna damuwar sa akan yɗar uwar nata sai ta ji wani baƙin ciki ya ziyarci zuciyar ta ga ƙasƙantar da kan sa da yayi yana tambayar ya lafiyar ta ga wulaƙanta sa da tayi abin sai yayi wa Hamida ciwo a rai..

Basu ankara ba ta ƙaraso gab da mijin nata ta saka hannu ta riƙo nasa daga baya ta sauke idanun ta tar akan fifi,cikin calm tune kamar ran ta bai ɓaci ba ta ce

"Ya jikin ki yɗar uwa ta da fatan kin sami lafiya,Allah ya ƙara inganta ki da lafiya sis i really felt bad a lokacin da Hajja ta sanar da miji na abin na damu na so sorry gaisuwar mu ya zo a ƙurarren lokaci"!!ɗago kai fifi tayi ta sauke a fuskar Hamida wacce itama ita take kallo..

Kallon kallo suka aikawa juna daga bisani kawar da kai Mufida tayi tana danne hawayen ta sai Hamida tayi murmushin da ita ta san manufar sa tana tashi riƙe da hannun mijin ta..

Kuma kallon fifi tayi fuskar ta ɗauke da murmushi ta san ko ba komai itama Mufidar na ɗanɗanar kwatankwacin raɗaɗi da zaman kaɗaicin da ta taso ciki tun yarintar su har kawo yanzu..

"Allah ya ƙara lafiya zan dawo in duba ki anjima for now ki ɗan sami hutu kin ji"?ta ida tana ɗage mata gira ɗaya sama..

Kamar ta ce da ita a'a bata buƙatar zuwan ta a karo na biyu amma sai tayi shiru dan maganar tata in ta fito toh kuka ne zai biyo baya..

Kan Khalid a ƙasa Hamida na riƙe da hannun sa suka fita daga ɗakin but kafin su ƙarasa fita sai da Hamida ta juyo ta kuma jefar fifi da wani irin kallon da Mufida ta kasa gane manufar sa..

Fitan su da mintuna biyu zuwa uku Ammy ta shigo tana tambayar yaushe ta shigo bata lura ba,kasa amsa Ammy tayi sai faɗawa jikin ta da tayi ta rungume ta tana ta sauke ajiyar zuciya dan hawayen da ta ƙi bari su sauko..

Kasa fahimtar ta Ammy tayi sai rungume ta itama suka kasance a haka har ta ji kamar fifin tayi bacci sai ta leƙo fuskar ta ta ga idanun ta a rufe,shafa fuskar ta tayi sannan ta kwantar da ita ta fito tana admiring kyawun ta..

Ɗakin Hajja Ammy ta nufa tana labarta mata sauyin yanayin da ta gani tattare da fifi nan Hajja ta fara tunanin ko dai su Khalid sun mata wani abin da ya ɗaga mata hankali ne a dalilin basu permission ɗin ziyartar ta..

Sanar da Ammy tayi abin da ya faru nan hankali tashe Ammy ta ce

"Hajjaa me ya sa kika yi hakan"?kallon ta Hajja tayi cikin halin ko in kula ta ce

"Sun matsa min suna son sanin halin da take ciki musamman shi Khalid ɗin sai kawai na sanar da su inda take ban san haka abin zai juya ba"zama Ammy tayi next to Hajja tana girgiza kai

"Hajja sun ɓata mata rai ajiyar zuciya ta rinƙa yi ta kasa yin kukan bare raɗaɗin zuciyar ta ya ragu bana son ran ta ya rinƙa ɓaci haka Hajja please a kiyaye gaba"gyaɗa kai Hajja tayi because ta gano kuskuren ta..

Tun daga wannan rana Ammy ta ƙara ɗaukar zafi da su Khalid iyakar ta da su amsa gaisuwar su amma abin da ya shafi sakin fuska sam basu samu daga gare ta ba ƙaramin damin khalid abin ke yi ba dan bai saba zama cikin fushin mahaifiyar sa ba sai dai matar sa na iya ƙoƙarin ta wurin ganin ta ɗauke mai hankalin sa ga duk waɗannan matsalolin dake fuskantar su..

Kimanin watanni uku da faruwar wannan lamari amma babu abin da ya sauya hasalima abubuwa sabbi ke faruwa akai akai dan irin secret silent intimidations da Hamida ke yiwa fifi ya wuce tunanin ɗan adam kwata kwata ta sauya kamar ba Hamida ta da ba bata ragawa fifi ko kaɗan amma duk wannan abin da ke gudana a iya tsakanin su hakan ke faruwa bata taɓa yarda Ammy ko Hajja ko mijin ta sun gane tana treating fifi very bad ba secretly bare daddyn su da ya ɗan jima da komawa germany sakamakon business ɗin sa..

Duk tsawon wannan lokaci da Hamida ta ɗauka tana threatening fifi dai dai da rana ɗaya fifi bata taɓa ɗaga kai ta kalle ta ba bare ta tankawa threats ɗin ita iyaka in ta zo ta mata wani lokacin sai ta rufe kan ta tayi kuka har sai ta ji sanyi a ran ta because mostly takan manta da tana da aure sai Hamida ta zo ta mata rashin kirkin ta ta tafi sannan take tunowa da auren nata,bata taɓa faɗawa Ammy ko Hajja ba duk da daddyn su kan kira ta akai akai dan jin ya lafiyar ta amma har su wayar su gama bata faɗa mai wani abin da Hamida ke mata dan ta ɗau hakan a matsayin nata ƙaddarar rayuwar ne..

Some times Khalid kan so ya tubkare ta amma sam bata basa chance kallon sa ma bata ɗaga kai tayi sai dai in ya laƙanci zata zo kusa da inda yake yayi targeting ɗin

ta ita kuma ta lura sai ta sauya hanya,bata yarda wani abin ya shiga tsakanin su ba tun ranar da abin ya faru..

A halin yanzu da abubuwa suka saka fifi a gaba sai tayi tunanin ɗaukar shawarar ƙawar ta Meena dan kar tayi asarar rayuwar ta duba da yadda family ɗin ta ke ɗawainiya da farincikin ta sai take ganin kamar in ta yarda munanan maganganun Hamida suka yi tasiri a jikin ta toh tabbas zata asararwa family ɗin ta da kan ta..

Bata da wani option sama da ta ɗau shawarar Meena dan haka ta shirya sanar da Ammy ƙudirin ta kuma ta san Ammy ba zata hana ta ba dan ita kaɗai ta san irin ciwon da take ji a zuciyar ta a duk lokacin da Hamida ta zo ta mata magana son ran ta ta tafi...

#Mamuh*17*

Ammy na shigowa ta taso ta zo ta faɗa jikin ta tana murmushi,da murmushin itama Ammy ta tarbe ta tana mamakin farincikin ta na yau dan a kwanakin nan ba kasafai ta fiye sakin jiki tana dariya ko fara'a ba sai ya zama dole.

"Baby me ya faru na ga yau kamar annashuwa kike ji"!gyaɗawa Ammy kai tayi tana lumshe idanun ta har suka zauna kafin ta tafi straight to the point ta bayyana Ammy abinda take so..

"Ammy so nake in koma makaranta tunda zaman wurin ɗayan yakan ɗan ishe ni ba dan bana jin daɗin kasancewa tare da ku ba sai dan ina tunanin tunda ban da wani abin da nake yi a nan sai zaman gida kuma baki yarda in taya ki aiki,so please kar ki hana Ammy komawa ta makaranta zai kawo min cigaba a rayuwa ta fiye da da tunda kin ga bana komai kuma dama ina manta wasu abubuwan amma in na koma makaranta na maida hankali na sai in fito da sakamako mai kyau ko Ammy na"?tayi maganar tana daɗa kwantar da kan ta a jikin Ammyn..

Shiru Ammy tayi tana sauraron ta har ta gama,ba hana ta take son yi ba hasalima jin dadin shawarar nata tayi ko ba komai ba zata rinƙa ƙarar da lokutan ta cikin tunani ba,matsalar yanzu shine wa zai rinƙa kula da ita a makarantar kuma wani irin makaranta ya fi dacewa da ita inda ba za a rinƙa ɗaga mata hankali ba..

Shiru ta sai ya saka fifi jin wani iri a tunanin ta ko Ammy bata yi na'am da shawarar ta bane sai ta kuma lafewa jikin Ammyn tana shirin shagwaɓa..

Murmushi Ammy tayi ta shafo kan ta ta bayyana mata fargabar ta amma fifi na nuna mata ai ba komai ita ɗin ai ta girma ba zata yarda hankalin ta ya rinƙa tashi ba zata kula da kan ta..

Da ƙyar Ammy ta yarda da kalaman ta dan cewa tayi sai an samo mata masu kula da ita amma ta tuɓure akan ita kan ta tayi girman da zata iya kula da kan ta,sai Ammy ta ce mata ba komai dama lokacin siyar da form ne sai cewa fifi zata yi magana da daddyn su duk yadda ake ciki zuwa nan da 2 weeks ta san komai zai kammalu...

Runguma sosai fifi ta kaiwa Ammy tana ta yi mata godiya da fatar gamawa da duniya lafiya,sai da Ammy ta dara ganin yadda fifi ta karɓi ragamar Ammyn ita kuma ta zamo kamar ita ce fifin dan irin adduo'in da fifi ke mata bai da maraba da addu'ar da uwa ke wa yayan ta..

Throughout ranar fifi ta yi sa ne cikin annashuwa da jin daɗi bata yarda ta saka damuwar Hamida ko wani a ran ta ba,kiran Dr Fatima Yonas tayi ta faɗa mata ai zata koma makaranta kuma burin ta na son zama cikakkiyar ƙwararriyar mai kare rajin haƙƙin ɗan adam wato Human right archivist na gab da cika,murna sosai Dr Fatima ta mata haɗe da fatar alheri da samin nasara a ƙarshe ta tambaye ta ya Hamida take dan sun ɗan jima basu yi magana ba ko ta waya..

Wani abu ne ya ziyarci zuciyar fifi jin sunan Hamida da Dr Fatima ta kira amma sai ta danne zuciyar ta ta amsa mata da tana nan lafiya ƙalau a haka suka ƙarasa hirar tasu suka yi sallama..

Kiran Ameed tayi shima ta faɗa masa ya mata murna da barka tun kafin abin ya kasance,Meena ce mutum na ƙarshe da ta sanarwa shima sai bayan hirar su da suka yi suka gama..

A iya nazari da lissafi fifi ta lissafa kwanaki goma sha huɗu kenan rabon ta da Hamida abin da ko a mafarki aka faɗa mata zata ƙaryata wai ita da yar uwar ta ta jini sun zamo ko ga maciji basu yi kuma suna zaune gida ɗaya..

Tun ranar da Ammy ta sa aka yi musayar kayan ɗakin su akan ai kayan fifin aka kai ɗakin da Hamida ke ciki presently ita kuma na Hamida na sashen fifi sai ta sa aka je aka kwashe kaf hatta da akwatinan fifi sai da ta sa aka musanya akwatinan da yake sashen Hamida da ta ƙi aka kwasa aka kai mata wanda su Ammyn ne suka yi na fifi kuma aka dawo mata da su amma waɗanda angwayen suka yi sai ba'a canza ba dan dama an sami sauyin angwayen,toh ranar da Ammy ta saka aka yi wannan kwashen ba ƙaramin ƙiyayyar fifi ta jefa a zuciyar Hamida ba wato ita bata yi deserving abu mai kyau ba kenan,tun ranar da fifi da ta fito ta leƙa ta ga abinda ke faruwa ta ce da Ammy ai ba wani amfani sauya kaya amma Ammy ta ce no sai an

sauya ai ita Hamidar rufe ido tayi ta aure Khalid so dan me tunda yanzu itama da nata mijin ba za a saka mata kayan da yake mallakin ta bane,tun ranar da ta hangi Hamida bata kuma ganin ta ba har rana mai kamar ta yau..

Da maganar su da Ammy yanzu ya kai kwanaki tara bata dai san ya ake ciki ba but tana ankare da kwanakin kuma takan yiwa Ammy godiyar ƙoƙarin da take yi akan ta time to time ita kam Ammy bata cika son jin hakan ba dan gani take kamar fifi bata gama sakin jiki da ita ba..

****

Fannin rayuwar su Hamida ita da mijin ta soyayya ake yi ba ji ba gani kamar akan su aka fara soyayya,duk damuwar family ɗin nasu baya hana su nunawa junan su kulawa da soyayya dan shirin tafiya zuwa wani wurin shaƙatawa ma suke tunda plan ɗin su yayi failing ba yadda suka tsara sa ba akan bayan bikin zasu tafi honeymoon toh yanayin bikin ya sa suka ɗan dakata har sai yanzu da abubuwa suka ɗan yi masu sauƙi..

A kullum dai kafin Khalid ya tafi aikin sa zai shiga ya gaida Ammyn sa da Hajja but iyakar amshin su bai wuce lafiya ba bayan haka babu canji tun faruwar lamarin har kawo yanzu,haka zai tafi aikin sa ya dawo ya kuma shiga gaida su da gida babu bambanci abin na damin sa ba kaɗan ba.

Ko ga kan matar sa Hamida duk haka ne basu sauraron ta ita dai abin bai wani ɗaɗa ta da ƙasa dan mijin ta ya gama yi mata komai tunda ya ɗaukaka soyayya da ƙaunar ta a zuciyar sa da ruhin sa,she doesn't care about irin attitude da suke bata a gidan..

Tana ƙoƙarin yiwa mijin nata hidima da sauke haƙƙoƙin da ya rataya akan ta na aure,a wannan fannin kam Khalid bai da matsala dan bayan matsalar family ɗin sa da irin ƙibar da zai yi sai ya fi wanda yayi a yanzu.

Bai cire rai ba ya san watan wataran iyayen nasu zasu yi accepting relationship ɗib su da auren su kuma su yafe masu,yana buri da addu'ar zuwar wannan ranar...

Sun shirya tafiyar su dai dai ƙarshen wata wanda yake daidai da lokacin da fifi zata fara zuwa makarantar ta,burin Hamida bai wuce su kai ziyara ɗakin Allah ba a

matsayin umara after that sai su zarce zuwa ƙasar Oman dan jin daɗin honeymoon ɗin su.

Zaɓin ta ya zamo na Khalid dan haka ya amince aka yi processing masu visa suka haɗa kayayyakin su ɗan kaɗan a cewar Khalid ta bari in suka tafi can zasu sayi wasu kayayyakin...

Ana washegari zasu tafi Khalid ɗin da kan sa ya shiga sashen Ammyn sa ya gaida ta ta amsa mai kamar kullum sai ya fara nemar yafiya da afuwar ta akan tafiya zasu yi shi da matar sa ya san tana fushi da shi amma ta yafe mai dan ya ga haske a wannan tafiyar tasu duka su biyu tunda tafiyar hanya ce ba lallai bane su dawo a raye in kuma ta Allah ta kasance akan su yayin da take fushi da su ba zai ga rahamar ubangiji ba..

Ba ƙaramin shigar ta kalaman sa yayi ba sai ta ji zuciyar ta na gaza cigaba da fushin da shi abu ne da bata saba yi masa ba,bata da wani zaɓin da ya wuce sassauta fushin nata ta mai addu'a shi da matar nasa ta masu fatar alkhairi da farinciki mai ɗorewa a rayuwar su..

Kasa natsuwa yayi sai ya je ya rungume ta yana murna kimanin watanni uku kusan na huɗu kenan Ammyn sa bata sauraron sa yau ta saurare sa sai ya ji kamar an sauke mai nauyi a zuciyar sa..

Ko da aka sanar da Hajja bata wani yi freaking out ba sai addu'ar Allah ya kai su lafiya ya dawo da su lafiya that's all so duk da bata sauya ba amma ya ji daɗin addu'ar ta gare su..

Next target ɗin sa shine ya gana da fifi ya roƙe ta dan gani yake ko Ammy ta yafe masa haƙƙin fifi dake kan sa kaɗai ya isa ya hana sa jin daɗin rayuwar sa da Hamida amma duk iya ƙoƙarin sa na son su haɗu haƙar sa bata cinma ruwa ba dan Mufida bata da lokacin su tana can tana murnar samin gurbin karatun ta a Abuja university da lectures date ɗin ta fixed sati ɗaya mai zuwa,jin daɗin wannan gurbi da ta samu bai bar ta ta saurari labarun su Ammy ba bare ta san me labarun nasu ya ƙunsa ba..

A washegari tun asubahi jirgin su Khalid ya ɗaga zuwa ƙasa mai tsarki sun tafi cike taf da adduo'in Ammy da na daddyn su Hamida da Khalid ɗin ne dai ya kira ya sanar da shi dan jin ko zai sassauto shima duk da dai dama ba wani ɗaukar zafi yayi sosai ba irin na su Ammy ba...

****

Wuraren 8am fifi ta fito cikin shirin ta na tafiya makaranta inda ta sami su Ammy zazzaune ana cin breakfast ga nata nan rufe ana jiran zuwar ta..

Fuskar ta ɗauke da fara'a ta ƙaraso tana gaida su,suna amsawa tana zama cikin sauri ta tambaye su ya daren su suka amsa da lafiya..

Sauri sauri ta ci abincin ta tashi wai zata tafi sai Ammy ta aje spoon ɗin ta tana kallon ta da mamaki

"Baby ina zaki tafi ba ki kammala cin abincin ki ba fah"!dariya ta ɗan yi ta zo ta bayan Ammyn ta rungume ta tana mata kiss ta ce

"Ammy na duba lokaci ki gani tara saura kuma ina da first lectures ɗi na by 10am beside na ƙoshi sosai kuma in ma yunwar na ji ai zan nemi school cafeteria in ci abinci sannan in cigaba da attending lectures ɗi na"!!a dame Ammy ta miƙe tana faɗin

"Wait for me ina zuwa"!bin ta da kallo fifi tayi tana jinjina irin ƙaunar da take mata sai Hajja ta yafito ta da hannu,saurin ƙarasawa tayi sai tayi murya ƙasa ƙasa ta ce

"Kin san Ammyn ku,abinci ta je kawo maki,kar fah ki bari karatu ya sha maki hankali ki ƙi cin abincin dan tun jiya take ta haɗa maki ta ce yʼar ta zata fara zuwa school dole ranar farkon ta ya zama abin tarihi a rayuwar ta dan haka ta dage ta maki girki mai daɗi so ki tabbatar kin ci abincin kar ki dawo da shi ta gani kin ga ai ran ta ba zai yi daɗi ba ko"?gyaɗa kai fifi tayi tana murmushi haɗe da jin son Ammy na kuma shigar ta..

Suna haka sai Ammy ta fito da wata ƙaramar basket mai cover ɗauke da food warmer da wani watter bottle kamar na yʼan primary school..

Yau da Mufidar da ne da ta tsaya ta yi dariyar ta son ran ta dan wannan shirin Ammyn shirin yʼan primary ne amma kasancewar rayuwa ta sauya ta zuwa ɗaya fannin ta sai kawai ta murmusa ta ƙarasa ga Ammyn ta amshi basket ɗin tana mata godiya da alƙawarin zata cinye abincin duka..

Har bakin mota Ammy ta rako ta da Hajja suna mata addu'ar nasara a ranar farkon ta sai da Ammy ta gargaɗi drivern da yayi tuƙi a hankali daga nan gida zuwa cikin university ɗin ba doguwar tafiya bace dan haka kar yayi gudu da fifi su tafi a hankali...

Murmushi kawai Mufida ke ta yi masu dan suna bata dariya da over protectiveness ɗin su,waving nasu tayi suka maida mata motar ya tashi suka fita su kuma suka dawo gidan suna tattauna yanayin rayuwar gidan da ya sauya ba yadda suka so ya tafi ba kafin bikin..

A nan Ammy ke ɗago zancen Saheeb akan ya kamata ya zo su ga juna da fifi ko da sau ɗaya ne in komawar zai yi sai ya koma amma ya zo ya gan ta damuwar ta kenan,Hajja ma ta matsu ya dawo dan tayi kewar sa ba kaɗan ba..

****

A fannin fifi kuwa tana iya cewa ranar ta na farko a makaranta rana ce da ba zata taɓa mantawa da shi ba a tarihin rayuwar ta dan abubuwan al'ajabi,ban mamaki da ban dariya ta rinƙa gani wanda a germany bata taɓa experiencing irin wannan school life ɗin ba kasancewar can kowa minding business ɗin sa yake yi amma nab ko baka da niyar magana wani sai ya saka ka yi..

Ƙalau ta ida lectures ɗin ta aka dawo da ita gida,tun daga farfajiyar gidan Ammy ta san an sami nasara a makaranta..

Biyewa fifi tayi ta fito tana amsa kiran ta,rungume Ammy tayi ta hau labarta mata abubuwan ban mamakin da suka faru a idon ta yau,ita da Ammy suka rinƙa dariya sai farincikin Ammy ya ninku ya ɗare na fifi duba da yadda yau kaɗai ta sake tana dariya abin da ta jima rabon ta da yin sa..

Har dare in fifi ta tuno wani abin sai ta rinƙa dariya ita kaɗai kusan kaso saba'in cikin ɗari na damuwar ta ya tafi kuma tayi farinciki da faruwar hakan..

Bayan sun gama dinner ta je ta kwanta har ta riga Ammyn bacci a cewar ta ta zamo yˇar makaranta dole ta rinƙa minimizing time ɗin ta kar ya rinƙa tafiya ba tare da ta aiwatar da abu mai muhimmamci ba..

A kwana a tashi ga mai rai ba wuya,fifi ta cinye semester ɗaya har tana gab da zana jarabawar ta saura sati ɗaya hankalin ta duk ya karkata ne ga karatun ta bata son disappointing Ammy da Hajja duba da irin so da ƙaunar da suke mata she want to make them proud...

Ko da Ammy ta sanar da ita tafiyar su Hamida sai ta share zancen ta masu fatar more tafiyar tasu lafiya ita kuma tayi facing damuwar ta dan bata so ta fara jarabawa da layin baya duk da ma bata san nature ɗin jarabawar nan ba amma ta dage sosai sai shirya mai take da makaman karatu..

Rannan da dare tana karatun ta misalin ƙarfe ɗaya na dare sai Ammy ta farka ta gan ta gaban littafi saman table abin sai ya dami Ammy ta taso ta zo ta rufe

littafin,ɗago kai fifi tayi sai ta ga Ammy ta ɗan ɗaure fuska sigar kar ma fifin tayi tambayar dalili ko magiyar a bari ta ƙarasa..

Bata jira ta cewar ta ba ta ja hannun ta ita kuma tana murmushi ta bi Ammyn,Ammy bata dakata ba sai kan gadon ta inda ta saka fifi kwanciyar dole ta rufe ta ta je ta kashe wutar ɗakin ta bar na gefen gadon ta ce da fifi

"Go to sleep dare yayi"gyaɗa mata kai tayi tana murmushi mai sauti sai kuma ko me Ammyn ta tuno bayan ta juya baya ta kuma Juyowa ta kalli fifi da idanun ta biyu ta ce

"Baby yayan ku zai dawo nan da kwanaki uku kuma sashen sa na buƙatar gyara ina tunanin assigning wasu su mai gyaran amma babu yarjewar ki shi ya sa nayi delaying dan na ga hankalin ki na kan karatu kar in takura ki ya kika gani kin yarda su shiga su yi gyaran"?kasa fahimtar Ammy fifi tayi ita meye haɗin ta da Khalid da ake nemar permission ɗin ta wurin gyara masa sashe sai ta dubi ta ce

"Ammy ai matar sa zaki tambaya ni ina ruwa na da sashen su"!kallon ta Ammy ta yi sai ta ce

"Da zan so hakan amma matar nasa ba sanin wurin baccin sa tayi ba bare lafiyar sa tana can wani ƙasar daban but ke da kike nan nake nemar yarjewar ki"gaban Mufida ne ya faɗi jin zancen Ammy..

Wai ashe da ita ake yi da aka ce yayan su zai dawo,kaf tunanin ta ya ta'alaƙa akan Khalid ne,ashe wai nata mijin ake nufi.

Dafe goshi tayi ta kalli Ammy sai ta juya mata baya kuma gaban ta na cigaba da faɗi,Ammy sai tayi tunanin hala kunya ce ta kama fifi sai ta ƙyale ta ta kashe hasken dake gefen ta ba jimawa bacci ya ɗauke ta,ita kam ko gyangyaɗin kasa zuwar mata yayi fargaba ne tattare da it da alhinin irin yanayin mijin nata da zata gani in ya zo ohh ita Mufida auren tsoho bata taɓa mafarki ba da ƙyar dai baccin ya ɗauke ta bayan doguwar tunane tunane...

#Mamuh*_Mamuhgee_*

18

Zazzaune suke bisa dinning suna breakfast Ammy sai bin fifi da kallo take dan son gano wani abu amma haƙar ta bata cin ma ruwa ba dan ƙeƙashewa Mufida tayi bata yarda sun haɗa ido ba sai abincin ta da take ta ci tana hira da Hajja suna ɗan ɗariya ƙasa ƙasa.

Suna yunƙurin kammala cin abincin sai Mufida ta ji kamar an tsikare ta wuf ta tashi tana cewa Ammy tana zuwa sai suka bi ta a da kallo har ta haura saman abin na basu mamaki..

Bayan tafiyar ta ne Ammy ta labartawa Hajja abin da ya faru a daren jiya tsakanin ta da fifi,abin gwanin ban dariya sbd wautar fifin..

Shigar fifi ɗakin Ammy dan ɗauko wani handbook ɗin ta sai kuma kamar ta hango wani dan haka ta dawo da baya ta ɗan yi facing window,nan ta hango clear view ɗin abin da idanun ta ke hango mata a nesa..

Tsayawa tayi tana kallon sa almost months kenan rabon da ta gan shi,ta dai san last time da Ammy ta mata magana akan sa shi da matar sa shine wai sun tafi honeymoon apart from ranar wata magana mai ƙarfi da ta shafe su bata kuma ji ba..

Ajiyar zuciya ta sauke ta kawar da kan ta ta ɗau handbook ɗin nata tayi zaman ta a ɗakin bisa kujerar karatun ta ta buɗe tana duba abin da ya faɗo mata ɗazu da take cin abinci har ta kasa haƙura ta tashi..

Kimanin mintuna talatin tana karatun ta bata tashi ba sai da ta kammala sannan ta mayar da littafin ta miƙe ta sauko zuwa ƙasan..

Da zuwan ta Ammy da fara'ar ta ta sanar da ita dawowar su Khalid har sun shigo sun gaida su amma lokacin tana sama so presently Ammy is directing to go and welcome them since da kan sa shi Khalid ɗin yayi requesting Ammy ta bar fifin ta zo dana akwai wani muhimmin abu da yake so ya mata,toh ita dama Ammy tun ranar da ya sanar da ita tafiyar su ta ɗau sassauto da zafin ba dan komai ba sai dan yanayin rayuwa da ganin shi ɗin jinin ta ne...

At first fifi was like scared ne ko fargaba ne na haɗuwa da su dukan ko ya nene bata sani ba,so tana ta son shashantar da zancen amma wani iri tsananin kewar 'yar uwarta na damunta tundaga qasan ranta sbd tun haihuwansu Basu taba yin nesa da junaba ko banxatar da junaba sai yanzu Wanda tasani kowannensu abin na qwaqwalar zuciyarsa da radadi mai zafi.

tashi tayi ta fita cikin faɗuwar gaba ta nufi apartment ɗin su Hamida tana addu'ar samin sanyin zuciya dan kuwa har ciwo ciwon kai take ji..

Da sallama ɗauke a bakin ta ta shiga main entrance ɗin sashen amma shiru sai ta kuma kimtsa kan ta tayi sallama ta shiga asalin parlor ɗin,this is her first time na shiga sashen haka ta rinƙa bin sashen da kallo tana yaba kyawun wurin tana takawa zuwa ciki a natse..

Bata san daga ina magana ke fitowa ba amma ta ɗan ji hayaniya da alama ƙaramin sa'insa ne ya kaure a inda hayaniyar ke fitowa..

Tsayawa tayi a tsakiyar parlorn tana ƙare ma parlorn kallo a hankali,duban ta ta maida ga wall ɗin parlorn sai ta ga wani babban enlargement mai ɗauke da hotuna kala uku na Khalid da Hamida suna murmushi cikin yanayin jin daɗi..

Rintse ido tayi cikin faduwar gaba kafin ta juya ta kalli ɗayan nan ma sun yi kyau,haka ɗayan da ta kalla nan ma sun kyau ba kaɗan ba,idanun ta na kan wannan last photo sai ta ji muryar Hamida na faɗin

"Mine ba fah zan yarda da wannan sigar ba fah,na ce wannan nake so amma baka ganewa,hankali na kuma ya biya me ya sa kake son haramta min"!!.daidai sun fito parlorn kenan ana jayayya Khalid na saka wani abu cikin aljihun sa yana ƙarasa fitowa cikin parlorn Hamida kuma na turo baki cikin shagwaɓa da ɗan ɓacin rai..

Basu san fifi na parlorn ba sai da Khalid ɗin ya gama maganar sa da Hamida cikin ɗan ɗaure fuska.

"Luv amma kin san wancan bracelet mai haɗe da wrist watch ɗin nan na farko da na siyo kin ce kina so,na damƙa maki right?wannan bai maki ba yet this one da na faɗa maki mai shi shima kika ce kina so and you knew ba naki bane,wannan ma ba naki bane duk na mutum ɗaya ne amma na baki ɗayar so why still insisting on this one again?haba Luv be just akan wannan lamarin i just can't give this one to you"!! rai ɓace Hamida ta ƙaraso cikin parlorn da nufin saka mai rikici da rigima duk dan ya bata dan bata ƙaunar ya mallakawa wacce yake da nufin mallakawa ɗin..

Har ta buɗe baki da zumar fara yi mai rikici sai kawai tayi tozali da fifi dake tsaye tana sauraron conversation ɗin su tana wondering rigimar nasu ko akan menene..

Wani haɗe rai Hamida tayi ta aikawa fifi wani irin kallon da sai da ya ƙarawa fifi fargaban ta a zuciya amma ta ɗan kawar da fuskar ta ta buɗe baki ta gaida Khalid..

"Yaya Khalid ina kwana"!!nan take ya juyo ya gan ta tsaye sai ya ji nauyin ta hakan ya tabbatar mai da cewa lallai ta ji duk conversation ɗin su dan haka ya sake fuska ya tunkare ta yana amsawa..

"Zo ki zauna mana kina tsaye yaushe kika shigo"!!wani takaici ne ya mamaye zuciyar Hamida kawai tayi folding hannuwar ta a ƙirjin ta tana bin su da kallo..

Kasa zama fifi tayi ta tsaya a tsaye tana girgiza mai kai akan ba zata zauna ba idanuwanta nakan hameeda datakejin kaman taje ta rungumeta sbd take taji kamar zata fashe da kukan kewar hameeda din

Khalid ɗin ya rasa ya zai fara yi mata magana akan haƙurin da ya jima yana son bata but sai tayi cutting tunanin sa off ta hanyar ce mai

"Yaya Khalid Ammy ce ta ce in zo wai kana nema na shine na zo"!!gyaɗa mata kai yayi yana saka hannun sa dan fiddo da agogon hannun da ya ɓoye ma Hamida.

Ai kuwa Khalid na fiddo wannan ƙaramin packed gift box ɗin nan ɗan madaidaici da zumar miƙawa Mufida a matsayin tsarabar da ya siyo mata Hamida ta waro idanun ta,rai ɓace ta ƙaraso gare su ta fauce abin kafin ya gama miƙowa Mufida..

Rai ɓace tana kallon Mufida cikin tsananin baƙin ciki da kishin dake cin ranta na fifin tsawon shekaru tace'

"Wallahi a'a,ba zan yarda ba akan wani dalili zaɓi na zaɓin rai na ka ɗauka ka yi ƙudirin damƙawa wata shi alhalin ka san ina so kuma yanzu na gama yi maka magiyar ka bani amma ka ƙi but ka ɗauka zaka damƙawa fifi akan me"!??tsayawa kallon ta Mufida tayi haka shima Khalid ɗin ya bi ta da kallo bai taɓa tsammamin Hamida zata iya bada wannan reaction ɗin ba akan mere wristwatch da bai kai nata da ta karɓa da fari tsada ba..

Bakin sa cike da magana da niyar hana ta cigaba da fiddo maganganun dake zuciyar ta dan wannan maganganun ya san zai yi leading ma wani matsala ne babba dan yana gudun in bai dakatar da Hamida ba yadda ran ta ya fara ɓacin nan toh komai na iya faruwa..

Bai gama nazarin sa ba ya jiyo muryar Hamida cikin tsantsar ɓacin rai daya fara karya muryanta tana cewa'

"Ka daina yi min haka rai na na ɓaci a ce kana nawa ɗin ma amma ban da iko da kai ban isa in mallaki abin da nake so ba daga gare ka sai an raba min shi da

wata,ta yaya kake tunanin ba zan yi fushi ba?meye hakan"?Mufida na tsaye na kallon yadda ta rufe ido tana faɗa kamar bata san gaban wa take ba..

Hamidar da ta fuskanci jimami fifi ke yi akan maganganun da ta gama faɗa yanzun nan sai ta ƙara fuskantar ta rai ɓace cikin haɗe fuska ta ce

"And you,,na yi ƙarya ne?ba gaskiya na faɗi ba kike kallo na?komai ba so kike ki mallaka ba a duniyar nan?ko ina kowa kina so ya zama naki mijin nawa ma ban isa in mallake sa ba ni kaɗai sai na raba sa da ke,abin hannun sa da nake so nake kuma da iko akan sa shima ban isa in mallaka ba ni kaɗai sai an ƙidaye min wanda ya cancanci zama nawa all because of you"!!da zuwan Khalid gaban su da jawo Hamida jikin sa bai fi blink of an eye ba..

Abinda yake gudu ne ke gab da faruwa dan babu irin kishin da Hamida ke yi akan Mufida da Khalid bai sani ba,komai akan irin kishi da haushin Mufida da matar sa ke ji dan haka yayi saurin janyo ta jikin sa sbd kar ta cigaba da maganar amma ina tayi nisa sai fizge jikin ta da tayi tana hana sa kuma riƙo ta dan ba ƙaramin ɓaci ran ta yayi akan wannan abin da,duk da ta mallaki Khalid ɗin amma bata da cikakkiyar iko akan sa akwai abinda ya fi wannan ciwo a ce mijin ka na ɓare ɓaren ba wata da ba matar sa ba kyautar abinda ita da take matar sa ke muradi,ai wannan masifa ce,kenan in ta cigaba da yin shiru shikenan tana zaune tana ji tana gani shi kan sa mijin zai zamo under control ɗin Mufidar kenan since she is the ƴar so...

Mufida na ƙare mata kallon mamaki dan bata san musabbabin wannan maganganun ƴar uwar nata ba..

"Ai sarai kin gane me nake nufi kuma me nake magana akai,komai ke jawo sa and you should be asked for that"!!cikin mamaki da fargabar kalaman Hamida Mufida ta ce

"Me ya faru Hamida"??wani irin kallon banza ta aikawa Mufida da shi sannan tayi ƙwafa ta ce..

"Tambaya ta kike ko?ok yanzu zan sanar da ke,Mufida you are a thief asalin ɓarauniya mai kwashewa mutum komai,you are a thief who steals what is rightfully hers and not hers,baki da wani abin da ya zama mallakin ki duk sacewa kika yi kika maida sa naki kuma baki da ranar daina satar,you are a thief Mufida"!!dum dum gaban Mufida ya bayar cikin ƙaraje da rashin natsuwa Mufida ta kasa haƙuri ta tari numfashin ta

"Hamida me na maki da kike aibata ni haka kuma ki rasa irin kalmar da zaki yi amfani da shi wun aibata ni sai da ɓarauniya?me na maki da tsauri haka Hamida"?? datse mata maganar Hamida tayi ta hanyar ɗan ɗaga muryarta dake rawar kukan takaici da bacin Rai tace'

"Ai dama ba zaki sani ba Mufida,in tambaye ki mana?ina sbd jin daƈin da kike yi har kasa tantance abin da ya dace ki mallaka da wanda bai dace ki mallaka ba kika kasa zama ki tantance?tukunna a lokacin da kike jin daƈin ai baki san akwai abinda ba naki bane da bai kamata ya zamo naki ba right?everything ke everything ke sbd ke ce fitilar kowa"!!

kuma datse ta Mufida tayi cikin tashin hankali Khalid kam na gefe yayi yayi tayi shiru amma ta ƙi sauraron sa instead ta taso mai da ɓacin rai akan ko ya bar ta tayi maganar ta ko a ji su a gidan yau ɗin nan..

"Hamee wai meke faruwa ne na kasa samo ma'ana a cikin kalaman ki"!!..dakatar da ita Hamida tayi ta hanyar ɗaga mata hannu tana fashewa da kukan mai tsananin radadi tanafaƈin'

"Save that name for someone kar ki kuma kiran wannan sunar dan baki cancanci kiran sa ba,tsakanin ki da Allah kin taɓa zama kin lura da wasu abubuwan dake faruwa da ke a rayuwar ki?am sure baki taɓa ba dan baki da wannan lokacin you are so occupied da soyayyar family ɗin mu,duk wasu jin daƈi a kan ki ya ƙare ɗiyar so,i cried all years duk a dalilin ki ke kaƈai Mufida,you stole everything komai"!!a ruƌe Mufida ta ce

"Me na sace maki Hamida"!?a tsawace Hamida ta amsa mata rai ɓace

"Komai Mufida,kin sace min komai da nake mafarkin samu,komai da ya dace in mallaka Mufida you own it,can you believe that you have been leaving my dream?

Ni marainiyace gaba da bayana Banda kowa aduniya tunda na rasa mahaifiyata sbd nasan ita kadaice tasan ciwo da zafina bazata taba wareni kamar Mara galihuba,

Banda kowa Banda komai I have no other choice than to fight for myself Kota wace hanyace Koda kuwa ta hanyarda bai dace bane sbd kune kuka bani wannan choice din,

ohh Mufida kin gama sace min komai na duniyar nan kin ƙwace min komai na rasa me na tare maki kika zaɓi yi min haka"!!a ɗan tsawace Khalid ya kira sunan ta

"Hamidaa just shut up"!!itama a tsawace ta mayar mai da

"No ba zan yi shiru ba,gata nan Mufida ce silar faruwar komai da yake faruwa da ni a rayuwa ta,she stole everything for me and i don't want to forgive her"!!hawaye ne cike taf a idanun Mufida jin zafaffan kalaman da Hamida ke faɗa mata..

Ƙarasowa kusa da su tayi ta tsaya suna fuskantar juna ita da Hamida sai da Mufida ta sauke wata nunfashin kukan zuciya mai nauyi sannan ta ce cikin tsananin rawar murya da rashin ƙarfin gwiwa ta ce

"Hamida ina son sanin asalin abinda na maki a iya rayuwar mu da zaman da muka yi ni da ke"!!wani irin kallo Hamida ta bi fifi da shi sannan ta hau yi mata magana cikin faɗa da haushi..

"Yanzu zan fayyace maki asalin abin da kika min a rayuwa wanda bai da bambanci da baƙin taɓo duk da na so _Ƙaunarmu_ ta ɗore amma kika san yadda kika yi kika datse wannan ƙaunar tamu"!!kuma yi mata wata tambayar fifi tayi gaban ta na faɗi

"Hamee ta yaya na datse _Ƙaunarmu_"?..

"Ta ko ina Mufida,Mufida kin mamaye min komai,soyayya,kulawa,rarrashi d ƙauna duk kin mamaye komai kin riƙe,ni ba mutum ba ce?ban dace a so ni bane?ban da yɑncin samin gata ne?ke kaɗai ce mutum mai jini a jiki da kika cancanci gata? Mufida tun da muka taso da zuciya ɗaya na riƙe ki a matsayin yɑr uwa ta ta jini ba yɑr uwar dangantaka ba,tun yarintar mu Mufida kika fara ƙwace min abinda nake so,attention ɗin daddyn mu duk ke kika samu ni ban samu ba ban yi complaining ba,karatu ni ba a maida hankali akan nawa ba ke har special classes ake baki a gida ni kuma ko oho dan an fi ƙarfi na ni ban da gata,abincin ki sai an ɗanɗana kafin ki ci gudun kar ki ci ya maki illa ni kuma kai tsaye ake bari na na ci abincin haka,sutura sai wanda kike so kike sakawa kan ki tsaye ba a maki gyara bare a hana ki ni fah? idan zan saka wanda rai na ke so toh sai daddy ya maida ni in canza zuwa wanda ran sa ne ke so i never complained,soyayya da kafa kafa da ake yi da ke kar ran ki ya ɓaci Mufida ni bana samu ni ban taɓa ɗanɗanar sa ba,kaf su Ammy da Hajja da ke suke magana in suka kira a waya dan ke ce tasu ni ko daidai da rana ɗaya ban taɓa ganin kiran su ba ni ba mutum ba ce?ranar da muka iso ƙasar nan imagine wai hankalin kowa akan ki ya komo ni dake tsaye an manta da ni ba a san ni ba sai ke,wai fah har wucewa aka yi da ke aka shige mota za a tafi a bar ni ana ta maki wasa da dariya ana gwada maki soyayyar da family ke nunawa yɑyɑn su da yɑn uwan su,mun dawo gidan nan aka kai ni wani irin pit wai ɗaki aka ce shine nawa naki kuwa kamar ta princess Cinderella komai an tsara maki dan ke ce kaɗai aka sani ake considering a matsayin ɗiya,abinci sai an tabbatar wanda ran ki ne ke so sannan za a girka kuma ba a ci sai an tabbatar kina nan za a jira ki sai kin zo sannan a ci ni fah?wa ya damu da ni wa kuma ya san ina raye bare a ba ni abinci,dawowar mu ƙasar nan ke kaɗai ce kika rinƙa experiencing soyayya da ƙaunar family ɗin mu ni ban samu ba,masoyi na abin alfahari na da nake muradin aure kafin in aura shima aka nemi a baki shi dan ni ban dace da shi ba sai ke tunda

ke ce kika nuna soyayyar ki gare sa a fili,auren namu ma a sace aka ɗaura sa dan kar soyayyar ki da kulawar ki ya sami tangarɗa we ran away,muka dawo muka yi bayani a tunanin mu za a yarda da auren amma sai aka juya mana baya aka ɗau fushi da mu dan mun yi tempering da tunanin ki,babu wanda ya damu da mu a gidan nan daddy,Ammy da Hajja duk babu wanda ke sauraron mu akan karon farko da na tashi nayi standing ma right ɗi na,ni ce wacce bata dace da jin daɗin rayuwa ba aka ɗau wani a matsayin wanda za a ba ni tsoho mai mata wanda ni da ke duk mun san irin mijin da nake so,a lokacin da aka ce za a haɗa ni aure da yaya Saheeb Mufida kika maida ni abin tsokanar ki safe rana dare baki tunanin negative impact ɗin da tsokanar ki ke min a ƙwaƙwalwa ta kawai ana nuna maki so and you think ke ɗin angel ce that deserves everything right?muna nan ni da ke Ammy ta aika aka kwashe duk kayan ki dake sashe na aka maida maki ni kuma aka kwaso nawa aka kawo min,ni da ke ɗin ba abu ɗaya bane?ba uterus ɗaya muka zauna ba?ba rana ɗaya aka haife mu ba?komai naki ba nawa bane?Ammy ta kawar da fuskar ta akan hakan ta min abinda ta min dan ni ba mutum ba ce i never complained,now miji na ya siyo abu na gani na ce ina so ya bani amma ya hau jayayya da ni akan abinda nake tunanin ina da iko da shi ashe still ban tsira ba Mufida kina nan kina bibiya ta da farinciki na kina yunƙurin ƙwace min,for goodness sake Mufida me zan maki ne a rayuwar nan dan ki rabu da ni hakan nan in ji daɗin sabuwar rayuwa ta??uhum?tell me please"!!hawaye ya gama ɓatawa Mufida fuska kaca kaca haka Hamidar mai magana itama fuskar ta jiƙe yake da hawaye sakamakon tuno da irin rayuwar ƙinci da tayi a baya all because of Mufida..

Numfasa fifi tayi tana kuma matsawo kusa da Hamida ta kawo hannu ta riƙo ta tana tambayar ta murya a karye.

"Hamida yaushe duk waɗannan abubuwan suka faru?ban sani ba baki sanar da ni ba ban taɓa gani ba,Hamida all these happened amma baki tsayar da ni kin sanar da ni ba?why"?fizge hannu Hamida tayi ta amsa mata.

"Yaushe na sami lokacin sanar da ke?kina da lokaci na ne?soyayyar family ɗin mu ya mamaye ki baki da lokaci na baki taɓa lura da yanayi na ba ta yaya kike tsammanin zan iya tsayar da ke in nuna maki wannan abin?already akwai third party a tsakanin mu Mufida tell me how did you think i have been feeling lately all those years"!!kuka sosai Mufida ke yi Khalid kan sa a ƙasa Hamida kam hawayen ne kaɗai ke fitowa amma babu kuka tsantsar ɗacin da ran ta ke mata...

Mufida bata haƙura ba ta kuma matsowa ta riƙo hannun Hamida tana kallon ta ta fara magana da sansayyar murya..

"Amma Hamida for once kin taɓa tunanin kira na ki faɗa min ni da ke?Hamida all my life na yi sa ne ina so maki farincikin rayuwa kamar yadda kike so min Hamida

ban taɓa kawowa a rai na wannan kulawar da ake ba ni yana taɓa maki zuciya ba,ban san ana treating ɗin ki a haka ba,zuciya ta da tunani na bata taɓa kawo min ana ɓata maki irin haka ba tun yarintar mu har girman mu,Hamida ban san irin rayuwar da nake yi kike so ba believe me i swear,Hamida kina ganin kamar da niya nake ɗauke kai na akan ki??no, Hamida ban san halin da kike ciki ba,har zuciya ta ban san kina jin zafin wannan abin ba,Hamida ban taɓa lura ba Allah ne shaida na ban taɓa lura da yanayin rayuwa ta mafarkin ki bane,Hamida komai nawa naki ne komai naki nawa ne,ki yafe min na maki katsalandar a rayuwar ki soyayya da kulawar daddyn mu Ammy da Hajja duk na tara a kai na ni kaɗai ban bari kin mora ba Hamida ki yafe min am so sorry and i promise to make it up to you Hamee tun yanzu zan sanar da su Ammy da Hajja su canza su daina saka ki jin irin wannan feelings ɗin am coming"!!?duk a ruɗe take maganar zata juya Hamida ta wani finciko ta a hasale ta ce

"Stop this i don't like it,ki daina wannan pretence ɗin i hate liars and pretenders,Mufida duk wata so da zai fito daga wurin su Ammy,Hajja da daddyn mu a ƙarƙashin alfarmar ki bana so ki je ki cigaba da more goodies ɗin ki all i want is you to leave me and my husband alone na roƙe ki Mufida ba dan hali na ba na haƙura da jin daɗin family ɗi na dan na san ba zan samu ba sai a dalilin ki ni kuma bana so dan haka ki rabu da rayuwa ta da na miji na please Mufida"!!!a yanzu sosai kukan Mufida ya fito sarari ta kasa ɓoye sa,zafin da take ji a zuciyar ta ya sa ta kasa tsayawa ta juya da zumar kawa sashen Ammy amma sai me..

Ammy ce da Hajja ke share hawaye suna jan hanci abinda ya kuma girgiza Mufida kenan dan ta tabbatar suma sun saurari abinda ya faru sai kawai ta ƙarasa ta faɗa jikin Ammy tana matsanancin kuka tana kuma nanatawa Ammy abinda ya faru Ammy ba abinda take yi sama da kuka mai sauti,hankalin ta in yayi dubu ya tashi bata taɓa kawo maltreating Hamida suke yi ba da soyayyar da suke nunawa Mufida..

Hajja da tayi making attempt ɗin rungumo Hamida jikin ta bayan ta ƙarasa shigowa cikin parlor kawai Hamida ta ture hannun Ammy ta haura sama abin ta Khalid kam ya tsaya ya rinƙa ba su Ammy haƙuri tunanin sa basu ji daɗin maganganun Hamida bane sai da Ammy ta tura sa ya je ya lallaso Hamidar kafin ta kai fifi ɗaki dan kan ta har ya fara sara mata jikin ta na ɓari...

Jiki sanyaye Hajja da Ammy suka koma apartment ɗin su da nadama mai tsanani duk rayuwar da suka yi da su Hamida a gidan nan basu taɓa sanin suna zaluntar ta ba sai yau da ta furta da kan ta..

Abu kamar wasa fifi zazzaɓi ya rufe ta tun safiyar nan har dare haka Hamida sai da ta ji sauyi a jikin ta dan zazzaɓi ne mai tsanani ya rufe ta amma taurin zuciya ya sa ta ƙi yarda Khalid yayi nursing ɗin ta..

Kamar wasa kwana biyu kenan da faruwar wannan abin amma komai ya taɓarɓare Ammy da Hajja ba yadda basu yi ba akan Hamida ta sake jiki da su suna jawo ta jiki amma sam Hamida ko sauraron su bata yi dan ta san fake affection suke nuna mata ba dan son ran su ba..

Rannan Hajja ta ga abin ya fi ƙarfin ta ƙiyayyar kamar ta gama ginuwa a zuciyar Hamida game da yar uwar ta sai ta kira daddyn su Hamida tana sharɓe kuka tana mayar mai da abinda ya faru sannan tayi requesting ɗin sa da ya dawo Nigeria ya zo su haɗu su gyara wannan ɓarakar...

****

A rana na ukun ne da faruwar hakan Hamida ta fito farfajiyar gidan ta tana nemar wanda zata aika ya karɓo mata saƙon mijin ta a sashen su Ammy dan ko sashen ta daina zuwa sbd zafin da zuciyar ta ke mata game da su..

Rasa samin ɗan aika ya sa ta fito zuwa farfajiyar gidan dan nemo ko da driver ne ko mai gadi dan aiken sa..

Tana tsaka da dube duben ta idanun ta ya hasko mata wani mutum daga baya yana taaye hannun sa riƙe a ƙugun sa sanye da sport suit yana bada direction,tsayawa tayi tana kallon mutumin daga baya dan bata san waye shi ba a gidan bata taɓa ganin sa ba..

A sannu mutumin ya juyo a natse cikin kamewa ya fuskanci hanyar ɗaya apartment ɗin dake kusa da nasu

Atake kwarjininsa da haibarsa tareda wani kamewarsa da tsantsar kyawun fuskarsa da fatarsa dake bayyana tsantsar hutu da dukiya data gama kamesa ya cika gurin hartana Dan sauke kanta qasa sbd cika idanuwansa

yana tafe yana amsa waya kan sa direct yana kallon hanyar da zai shiga..

Sbd cikin Daren Koda ya iso baa shiga da kayansaba sai yanxu da safen

Wani irin suman tsaye Hamida tayi ta ƙame tana bin wannan mutumi da kallo da bata san ko wa nene shi ɗin ba,gaban ta ne ke faɗi da ta rasa dalili,ai kuwa tana

tsayen sai ga Khalid ya fito da ɗan sauri yana dube dube sam bata san da zuwan sa ba sai ji tayi yana

"Luv kin ga min Marshall ba a ta nan wurin"?

dum ta ji gaban ta ya faɗi jin sunan da ya kira kasa kallon sa tayi sai sashen da take kallon an wuce ɗazu..

Tunowa Khalid yayi akan Hamidar fah bata san Marshall ɗin ba sai yayiwa kan sa murmushi ya ce

"Na manta Luv baki san shi ba am sure ya shige part ɗin sa dan yanzu na hango sa yana wucewa ina kiran sa amma yana waya bai ji ni ba am coming bari in duba shi"!!

tsinkewa zuciyar Hamida yayi jin an kira wannan mutumi da Marshall kenan yaya Saheeb..

"Inalillahi wa'inailaihir raji'un"!!shine kalmar da Hamida ta rinƙa nanatawa a zuciyar ta tana tsaye Khalid ya wuce ta zuwa apartment ɗin dake next to them batareda ta iya motsawa ba..

#Mamuh*_Mamuhgee_*

19

Jiki sanyaye Hamida ta nemi hanyar komawar ta sashen ta gaban ta na cigaba da faɗi tana cigaba da nanata innalilahi wa'inailaihir raji'un idanun ta na mata mugun hasashen..

Da shigar ta parlorn ta zauna daɓas akan kujera tayi shiru tana kallon gefe ɗaya tana tunanin yadda tayiwa kan ta tuwon tulu gashi a yanzu ta rasa marar kwashe ta..

Me idanuwanta keson nuna Mata???

Mijin Fifi yafi nata??

Ko yanxuma kenan Fifi ce ke gabanta??

Hawaye ne ya hau zarya a fuskarta fuskarsa da haibarsa na sake cika idanuwanta..

Share hawayen tayi ta hau jujjuya kai tana girgiza ƙafa rasa madogara tayi kawai ta tashi ta shige ɗakin ta bata jira komai ba ta saka lock ta rufe ɗakin ta faɗa kan gado ta saki kukan raɗaɗin zuciya da zafin rai..

Kimanin mintuna arba'in da wani abu Hamida na rufe a ɗaki tana sharɓe kuka tsakanin ta da Allah wanda ita ta san dalilin yin sa,tana nan tana kukan har bacci yayi nasarar cin ƙarfin ta bata ankara ba sai ji tayi ana tapping bayan ta ana kiran sunan ta..

Ɗan buɗe idanun ta tayi ta sauke akan fuskar Khalid dake kan ta fuskar sa cike da damuwa ƙarara..

Tashi tayi ta zauna ta zuba mai idanun ta da ya sauya daga farare tas zuwa rage red..

Shima ita ɗin yake kallo yana tunanin me ya ɗaga mata hankali har haka da idanun ta suka sauya suka kumbura sannan jikin ta yayi zafi kamar wacce fever ya ma kamun sauri..

Kawo hannu yayi ya taɓa jikin ta ya ji zafi rau sai yayi saurin kai hannun sa goshin ta nan ma zafi rau,hankali a tashe ya hau tambayar ta me ke faruwa amma kasa amsa mai tayi sai bin shi da wani irin kallon tsarguwa take yi wanda ya fara bashi tsoro shima..

"Luv me ke damin ki ne i hope ba zazzaɓin ne ya kuma dawowa ba"?ya tambaye ta a ruɗe sai ta kawar da fuskar ta daga kallon sa ta ɗau wasu seconds sannan ta girgiza mai kai sai ya kuma yunƙurowa zai tambaye ta amma ta dakatar da shi ta hanyar ɗaga mai hannu sannan ta ce

"Bacci nake son yi"!!gyaɗa mata kai yayi sai ya kwantar da ita a kan gadon ya jawo duvet ya lulluɓe ta yana manna mata kiss a goshin ta ya tsaya yana kallon ta..

Ganin bai da niyar fita ita kuma a matse take tayi nazarin ta sai ta lumshe idanun ta dan dai ya ga tayi bacci ya fita..

Shi kuma ganin ta fara bacci ya matso ta ya zauna kusa da ita duk tana jin shi ya hau kwararo mata addu'ar samin lafiya har da na fatar Allah ya sa albarkar sa ne a tare da su..

Tana gama tabbatar da cewa ya fita ta tashi da sauri ta je ta rufe ƙofar ɗakin da double lock ta dawo ta zauna..

Ji tayi kamar zafi na mata yawa alhalin akwai air split a bedroom ɗin but zafin da take ji ko mutumin dake cikin kango sai haka..

Cire kayan jikin ta tayi ta nufi toilet ta kunna shower ɗin wanka dan ba zata iya zama cikin bathtub ɗin ba tsabar rashin natsuwar zuciyar ta..

Wankan nan ana iya kiran sa da wanka baƙin ciki because the more the water is dropping on her skin the more her mind is leaving her soul..

Fuskar mijinta ya fado Mata tareda duk wani abinda ya shafesa ta lumshe idanuwanta cikeda so da qaunarsa saidai tsananin kishin yar uwarta da irin mijin data samu Wanda a gani na ido yafi nata Yana yaqi gurin danne son nata mijin,

Bayan ta gama wankar ne ta fito ta shirya cikin simple abaya ta wuce kitchen ta haɗa masu lunch..

Bata kira Khalid a waya ba bare ta sanar da shi abincin su is ready,rather tayi zaman ta ta ci nata ta bar mai nashi ta tashi tayi ficewar ta zuwa zuwa garden ɗin gidan tayi zaman ta a nan

Ita wato ko yanxuma Bata sauya Mata ba Fifi is always ahead of her,

Meyasa su hajja suka zabarwa Fifi Marshall???

Hawayen tsananin kishin fifin suka gangaro mata tanajin wani irin nauyi cikin ranta.

****

"Baby ki ci abincin nan mana kin taɓa ganin inda mutum ya warke garau kuma baya cin abinc?ana haka"?shiru fifi tayi,tun ranar da yaɗar uwar ta ta mata confessing abinda ke ran ta ta kasa natsuwa haka ciwon da take ji a zuciyar ta har yanzu bai warke ba yana nan yana daɗa yaɗuwa,ita dai ta san har ga Allah zuciyar ta ɗaya take yiwa yaɗar uwar nata so amma ta rasa yadda aka yi tana raye tayi witnessing

irin wannan blast ɗin ta yaya ma aka yi duk waɗannan abubuwan suka faru amma basirar ta ya shafe bata lura ba..

Ko a mafarki bata taɓa kawo rana irin ta ranar nan zata zo ta riske su a rayuwar su ba mostly a labarai take jin ana irin hakan amma ashe it has been designed for her tuntuni ranar da abin ya faru ne dai Allah yayi zai zamo mata eye opener..

Hawaye ne ya fara bin fuskar ta sai hankalin Ammy ya kuma tashi dan a kullum sai dai in fifi bata farka daga bacci ba amma in har idanun ta biyu daga silent tears sai kuka mai sauti hatta da abinci in aka mata maganar sa sai ta saka kuka dan tunowa take da yanzu Hamida na nan na mata kallon selfish person...

Da ƙyar Ammy ta rarrashi fifi ta tashi ta ci abincin dan har an kawo mata ɗakin..

Zama tayi tana kallon abincin sai ta ji appetite ɗin ta yayi ceasing sai ta kalli Ammy ta girgiza mata kai alamar ba ci zata yi ba..

Girgiza mata kai Ammy itama tayi tana faɗin

"Baby not now again rabon ki da abinci tun daren jiya kuma shima liquid sips ne ta yaya zaki warke baki ci abinda zai saka maki ƙarfin jiki ba?uhum?amsa min?ki mana adalci Hajja na can na zaryar sashen Hamida tun ɗazu amma bata same ta ba duk dan mun gyara kuskuren mu amma ke baki son yarda ki taimaka mana why"?jan hanci fifi tayi sai ta kalli Ammy ta ce

"Ammy kina ganin Hamida zata yafe min laifin da na mata kuma yafiyar har abada"?tausayin ta ne ya mamaye Ammy sai ta rungume ta tana amsa mata da eh Hamida zata yafe mata mana ai ba da sanin ta hakan ya faru ba..

Sai da fifi ta ɗan natsa sai ta kuma kallon Ammy muryar ta na rawa ta ce

"Ammy exams ɗin mu saura kwanaki kaɗan,bana concentrating a karatu na ina so in ɗan zaga gidan maybe in sami ikon tuno wasu abubuwan"..

Ɗaga ta Ammy tayi bata ce ƙala ba ta rako ta har main parlor sai fifin ta ce mata ta huta ita kaɗai zata tafi..

Fita tayi ta fara tafiyar ta a hankali tana yi tana tuno irin rayuwar ƙuncin da yaɗar uwar ta tayi duk a dalilin ta,a ko da yaushe in ta tuno wannan abin takan yi takaicin irin rayuwar da take yi ta yaya yaɗar uwar ta jinin ta ta girma tun yarinta har auren ta a irin wannan baƙin ciki ba tare da sanin ta ba,abin na taɓa mata zuciya..

Tana tafe tana tunanin ta bata san har ta zago zuwa hanyar garden ba sai ji tayi kamar ta jefa ƙafar ta a wani soft place,hakan ya sa ta dawo hayyacin ta ta kalli ƙasa sai ta ga grass carpet alamar garden ta zo..

Ɗan kalle kallen ta tayi ta hango wani kujera sai ta ƙarasa nan ta zauna tana mai haɗe hannun ta da goshin ta wuri ɗaya..

Bata ɗago ba sai da ta ji hawayen idanun ta na nemar tado mata da matsalar zuciyar ta mai wuyar sha'ani sannan ta ɗago ta kalli garden ɗin for a while..

Juya kan ta da zata yi ta hango yaɾ uwar ta zaune tayi crossing ƙafa ɗaya kan ɗaya tana kallon anterior view ɗin ta..

Ai bata tsaya wani tunanin ba ta tashi da gudun ta dan dama ta jima tana son ta gana da Hamidar amma bai faru ba sakamakon rashin lafiyar da ya lulluɓe ta tun ranar da abin nan ya faru..

Hamida dake zaune a zahiri amma a baɗini duniyar tunani ta dulmiya,kawai sai ta ji an faɗo mata from no where..

Ɗago kai tayi sai ta ga Mufida a jikin ta tana kuka tsakanin ta da Allah

Wani irin tsananin so da kewar fifin ya taso Mata harta daga hannu zata rungumota sai kishinta ya motso Mata mai qarfi ai kam bata wani jira ba ta ture ta daga jikin ta tana kakkaɓe jikin ta haɗe da jefawa Mufida wani irin mugun kallo..

Ita dai bata damu da kallon ba ta kuma zuwa dan rungume ta amma nan ma ta ƙara datse nufin Mufidar tana gargaɗin ta akan kar ta kuskura ta matso ta..

Abin bai ɓatawa Mufida rai ba dan ta san zafin laifin ta ne ya sa Hamidar yi mata hakan.

"Hamee ki saurare ni,i am ready to receive your punishment ko ta ya nene na yarda zan karɓi hukuncin ki in dai zai goge baƙin tambarin da na dasa nawa a zuciyar ki kin ji"?wani dirty look Hamida ta aikawa Mufida da shi kafin ta ja tsaki ta wuce Mufidar tana tafe tana maganganu ciki ciki ita kaɗai ke jin sa..

Durƙusawa Mufida tayi a wurin tana kuka mai taɓa zuciya a duk lokacin da ta tuno irin raɗaɗin da ta sakawa yar uwar ta a zuciya sai ta ji kamar kukan nata kaɗai bai isa ba..

Sai da tayi kukan sosai sannan ta tashi tana tangaɗi ta koma sashen Ammy inda da zuwan ta ta sami wuri ta kwanta,forcing kan ta tayi dan bacci ya ɗauke ta kar damuwar ya mata yawa..

Ko da Ammy ta shigo ta gan ta a haka bata yi gigin tada ta daga baccin ba dan ta san labarin gizo baya wuce koƙi dole kukan baƙin cikin yar uwar ta ne ya saka ta baccin dole..

Fitowa Ammy tayi tana share hawayen ta dan abin na damin ta ganin da hanun ta ta taimaka wurin nesanta Hamida da Mufida wanda a matsayin ta na uwa a gare su bai kamata ta bayyana soyayyar ɗaya akan ɗaya a fili haka ba kamar yadda ta rinƙa nunawa a baya..

Ta kan zauna tayi kuka cikin dare idan fifi tayi bacci ba dan komai ba sai tuno irin wariya da bambancin da ta rinƙa nunawa Hamida kamar ba tare aka haife su da Mufidar ba..

Tabbas da ace Khadija na Raye da bazata bambamta yayanta ba sbd ita ta haifesu,

To su yanxu me kenan sukayi???.

Tun ranar ita da Hajja suka rinƙa zaryar zuwa duba ta dan nemar afuwar ta amma sai ta tsiro da hanyar guje masu kar na su haɗu bare su karanta mata fake love ɗin su gare ta...

Musamman yanxu dataga mijinda suka zabarwa Fifi tasake tabbatarda sun qara fifita fifin,

Sashen Hamida Ammy ta nufa bayan doguwar sallamar da ta tsaya tana yi a bakin ƙofa ba tare da an amsa mata ba sai ta yanke kawai bari ta shiga ciki..

Da shigar ta sai ta hango Hamida zaune a ɗan kishingiɗe kunnen ta sagale da earpiece bakin ta na nanata abinda take sauraro a earpiece ɗin wanda waƙar maher zain ne na number one for me cikin album ɗin sa,shigowar Ammy daidai inda yake baitin _"my mamma is alright is a brand new day i will like to put a smile on your face every day"_..

Sanyi gwiwar Ammy yayi zuciyar ta ya karye duk wannan maraicin ita da Hajja ce sanadin faruwar sa dan tun yarinta da suka taso tare da daddyn su basu damu da son jin ya lafiyar ta yake ba sai dai na Mufida..

Kasa cigaba da tsayuwa Ammy tayi haka ta fita ta koma sashen ta tana nadamar ƙiyayyar da suka dasa a zuciyar Hamida game da su sannan inda abin ya fi muni shine ƙiyayyar yar uwar ta da suka taimaka wurin haddasa sa a zuciyar ta..

Maimakon ta tsanesu suda sukai komai Amma yar uwarta ta tsana.

****

Kwanaki uku kenan a tsakani Hamida da Mufida babu fahimtar juna sai sabuwar ƙiyayyar juna tun abin na faruwa a tsakanin Hamida da mijin ta a sashen su har ya fito fili Mufida ta gane son ta ne yar uwar nata bata yi already ƙiyayyar da take mata ya rinjayi soyayyar da take mata dan haka ta sakawa zuciyar ta haƙurin dole akan bayan wasu lokuta zata kuma komawa ta roƙi yafiyar yar uwar nata maybe by then ta huce..

Ana jibi monday exams ɗin su Mufida Ammy ta rinƙa ƙarfafa mata gwiwa dan dai tayi ta kammala lafiya ta dawo gida ta natsu dalilin da ya sa bata sanar da ita dawowar mijin ta ba kenan kar fargaba ya hana ta concentrating a karatun ta,duk yadda zata yi kar su haɗu for now tana yi because bata san ya reaction ɗin Mufidar zai kasance ba in har things turn out to be in a negative way...

****

Da sanyin safiya ta fito zata tafi inda ya fiye mata daɗin karatu wato garden,tana tafe tana nazarin abinda ta karanta a daren jiya..

Tana tafe tana karatun tana ɗan rausayawa unknowingly kawai ta juyo tayi ido biyu da wani mutumin da bata taɓa ganin sa cikin gidan ba..

Cak ta tsaya a wurin hannun ta dogare da ƙirjin ta littafin ta riƙe a ɗaya hannun ta idanun ta akan wannan mutumi sbd sanin Babu wani Wanda ke rayuwa a gidan bayansu..

Shi wannan mutumi dama morning workout ya fito yi as usual kuma yanzu ya kammala zai koma cikin gida..

Gama juyowar sa ke da wuya fifi ta nemi natsuwar ta ta rasa hatta da handbook dake hannun ta saura ƙiris yayi slipping daga hannun ta ya faɗo ƙasa sbd tsananin faduwar da gabanta yayi lokacinda idanuwanta suka hadu da nasa wanda yasa jikinta Neman daukar rawa..

yana zuwa zai wuce ta kuwa ta ƙara girman idanun ta ganin kamar ta so sanin sa amma kamar ba shi bane..

Da zuwan sa zai wuce ya ga mace tsaye ta ƙame kamar soldier tana kallon sa sai ya buɗe baki ya furta

"Excuse me if you wouldn't mind"!!ja da baya tayi ta matsa mai ya wuce ta da ɗan gudu gudu in form of jugging..

Sumewa ne kaɗai ya rage fifi bata yi ba da ba a germany ta taso ba inda nan ne ƙarshen masu workouts,

Maza masu abs sune best mazan datake tsananin so da birgewa tagansu kala kala Amma Bata taba ganin Wanda jikinsa yayi building kamar wannan ba,

Zufan dake gangara daga jikinsa kawai was very neat and shiny,

But waye wannan ɗin!?

Who is he????tambayar da tayi wa kan ta kenan amma babu amsa sai ta cigaba da bin sa da kallo..

Ko me ta tuno kuma oho sai ta taɓe baki ta ɗage kafaɗar ta ta ƙarasa zuwa garden ɗin tayi zaman ta da zumar yin karatu sai dai karatun nan bai yiwu ba because tana yi rabin hankalin ta na ga tunanin wanene wannan gentile good looking man ɗin..

Ƙarshe tashi tayi ta ƙarasa sashen su Ammy na mata tambayar ya karatu amma kasa amsa ta tayi sai shiru da ta mata..

Suna nan zaune suna halin shiru ita da Ammy sai aka doko sallamar da sai da ya shiga ciko cikin kunnuwar Mufida ta ji nan take natsuwar ta ya fara yunƙurin barin jikin ta...

Bata gama alhinin wannan sallamar ba ta ji muryar Ammy na faɗin

"Yau da wuri ka shigo,na ga baka cika fitowa da wuri ba hope babu wata matsala"!?hankalin fifi sai ya dawo ga conversation ɗin su har suka gama magana tana kallon bakinsa a sace yanda yake magana cikin cool and matured tune dinda ya gama kashe jikinta musamman dataketa son tantace wane mizani zata kallesa sbd bata gama sanin wayeba.

yana fita fifin ta rufe idanuwanta ahankali ta bude ta yaqi da shaqar kamshin turarensa na Armani daya gama kame sanyin AC na dakin ta kalli Ammy a hankali ta ce

"Ammy waye shi wannan ɗin"?murmushi Ammy ta mata tana shafo fuskae ta a hankali sannan ta amsa mata

"Baby kin ga illar rashin sani shi ya sa na matsu ku dawo,yanzu jinin naki ma baki san shi ba sai an nuna maki,toh dama ban so ku haɗu tun a yanzu ba sbd jarabawar ki amma tunda Allah ya ƙaddari yau zaku haɗu ina ga sai ki kai mai gaisuwar barka da dawowa kusan 4 days kenan da dawowar sa"!!shiru fifi tayi tana jiran cigaban sharhin Ammy sai kuwa kamar Ammyn ta sani ta cigaba..

"Yayan ki ne baby SAHEEB ne"!!, gaban Mufida ne ya faɗi at once..

"What did Ammy just said?yaya na Saheeb ne?what"?tambayar da ta yiwa zuciyar ta kenan tana ƙara hasashen yanayin sa..

Tashi tayi ta sallami Ammy wanda sallamar ya ɗan tsorata ta tunanin ta ko Saheeb ɗin bai yi ma fifi bane...

Da shigar fifi ɗakin Ammy tayi wurgi da littafin hannun ta ta warware mayafin kan ta ta zo gaban mirror ta tsaya tana ƙarewa kan ta kallo daga sama har ƙasa,sai da ta share mintuna biyar tana kallon kan ta a mirror sannan ta jijjiga kai tana furta

"Ya salam,

"wani irin reaction ne ya riske ta ta kuma kallon kan ta sai ta rainawa kyawun ta da wayewar ta da zamanancin ta dan in aka tsaya aka yi comparing nata da wannan da Ammy ta kira sa da yayan ta Saheeb wanda kuma a addinance shine mijin ta for now toh ita ɗin mummuna ce abinda ya ɗaga mata hankali kenan ta rinƙa tunanin anya Ammy ba tsolanar ta take yi ba kuwa ta yaya mutumin da suka ji labarin sa suka kuma daɗe da tagging nasa old man zai yi turning out to be a gentile,handsome and well kept man like this har ma kyawun sa na nemar ɗare nata kyawun,anya ba tsokanar ta Ammy ke yi ba kuwa..

Kasa samin kan ta fifi tayi sai da ta ga in fah ta cigaba da wannan tunane tunanen da ba lallai bane gaskiya ne ba toh zata yi biyu babu because ba zat sami cikar burin ta ba sannan tayi causing mistrust a zuciyar family members ɗin ta akan ta..

So tun ranar wanda ya kasance saturday fifi bata kuma bi ta kan tunanin wanda aka ce mata yayan ta bane dan ta san hasashen Ammy ne ba asalin wanda take jin sunan sa bane is not even possible a ce shine wannan..

Ranarda taji hajja tayiwa ammy mgnar tarewar Fifi din gurin saheeb hankalinta ya tashi matuqa Amma taqi nunawa

Hankalinta bai sake tashiba Saida taji ammy na cewa abari aji ta bakinsa idan matarsa ba yanxu zata dawoba.

Concentrating tayi a karatun ta har ranar litinin da tayi shirin ta na musamman dan fara zana jarabawar ta,good wishes Ammy ta mata ta fito driver ya wuce da ita zuwa makaranta dan attending exams ɗin ta...

#Mamuh*20*

Yau kimanin kwanaki takwas kenan da fara jarabawar fifi kuma ana saka ran gobe zata kammala da hukuncin ubangiji.

Yanayin jarabawar ya sa bata da isasshen lokacin zama tayi hira da su Ammy bare har ta sami lokacin tunanin wani abin..

A wannan tsawon kwanaki tara zuwa goman abubuwa da dama sun faru a gidan wanda fifi bata da masaniya akai..

Cikin wadannan abubuwa akwai wasu halayyar Hamida da ba a san ta da su ba amma ta rinka yin sa a boye,wannan abin ba komai bane sai salon da ta dauko wurin ganin ta sami wani abinda take so..

A natse cikin kamun kai da wayewa take haduwa da Saheeb a garden kullum safe in ya tafi morning workout ɗin sa ita kuma sai ta tafi ta zauna tayi concentrating akan wani pamphlet da take yawo da shi a hannun ta kullum da sunan dubawa take yi..

Haka kawai ta ji duniyar nan babu wanda take son gani kullum safiya zuwa yamma sama da fuskar Saheeb,abin mamaki kamar mantawa tayi yʻar uwar ta Mufida ke aure da shi kuma ita ke da wannan dama da ikon ba ita dake auren ƙanin sa ba..

Kamar kullum yau ma tana zaune tana duba pamphlet ɗin nata sai mijin ta ya zo dan dama yana ta nemar ta bai gan ta ba sai yayi tunanin zuwa nan dan tun rana da idanun ta ya mata tozali da Saheeb ta fara sauyawa Khalid abincin da suka saba ci tare ta yanke sai dai ta ci nata ta bar mai nashi,wankan da ake yi tare shima ta datse,hirar dare da ake yi kafin a yi bacci nan shima ta yanke sa dan bata da lokacin sauraron hirar lokacin ta na wani abu ne chan daban,toh shi kuma bai ɗau abin da muhimmanci ba ya fi alaƙanta sa da ƙila conflicts ɗin da ya faru ne tsakanin ta da yʻar uwar ta..

Da zuwan sa ya zauna kusa da ita haɗe da ɗora kan sa a kafaɗar ta yana lumshe ido sai a sannan ta san ya zo dan idon ta na kan Saheeb a kaikaice..

Harga Allah cikin ranta batada wata soyayyar 'da namiji bayanta mijinta khaleed Saidai Sam takasa dauke idanuwanta daga kan Marshall ne sbd son gano wani aibunsa dazai nuna mijinta yafi na Fifi Wanda shine yasa zuciyarta Sam kasa sukuni da walwala.

Ko da ta juya ta ga shine sai tayi saurin ɗaga kan sa daga jikin ta tana ce mai

"Miye kuma haka Kuma ka manta a waje muke?shagwaɓe fuska yayi ya kalle ta ya ce

"Luv Ina ruwanmu da waje tunda Babu kowa a gurin?sai ta bi shi da wani look tana ja da baya kaɗan kafin ta tashi rai a ɗan jagule dan ya hana ta ƙarasa abinda ya kawo ta..

Yana kallon ta ta tashi ta wuce dan bata yarda kowa ya san da wannan abinda take yi ba iyakat ita da mahaliccin ta..

Yana kallon ta tana wuce sa ya jiyo kiran yayan sa sai ya maida hankalin sa wurin itama ta tsaya a inda take dan jin muryar sa..

Ƙarasawa Khalid yayi zuwa wurin da yayan sa ke tsaye,da zuwan sa ya gaida Saheeb cike da ladabi da biyayya dan akwai tazara sosai tsakanin su kuma baya da haka tarbiyar gidan dole na ƙasa ya ba na sama da shi mutuncin sa..

Tana jin yadda Khalid ɗin ke gaida Saheeb tattare da mutuntaka sai kawai ta ja wani tsaki ta wuce ran ta na ɓaci idanun ta na kawo ruwan hawayenda ke sulala zuciyarta ganin mijinta shine yake qasqantarda Kai ga mijin Fifi.

Tare suka ƙaraso Saheeb ɗin na sanar da shi yana so yau su tafi site wato wani ginin da ake yiwa Saheeb a nan cikin Abuja..

Da murna Khalid ya ce ya yarda zai bi shi har driver ɗin sa zai zama yau dan sun daɗe basu haɗu ba kasancewar ranar da ya kamata su haɗu aka sami akasin ɗaurin auren nan sai ta waya suka cigaba da magana dan ya koma toh yanzu da ya dawo ne Khalid ɗin ke son faranta mai dan ya san yayi laifi kuma shi yayan nasa ba

mai damuwa bane yana iya yiwuwa yana da matsala amma bai furta ba ya barwa kan sa..

Hamidar da yanzu ta ƙarasa cikin sashen su kunnuwan ta suka jiyo mata inda Khalid ke faɗin ai har driver ɗin Saheeb zai zamo a yau,wani baƙin cikin ne ya kuma turnuƙe mata a zuciya wannan karon kasa dannewa tayi tasaki wani irin kuka Mai qarfi tana zubewa kan kujera da qarfi

Ko da ya shigo ya sanar da ita abinda yayan sa ya ce sai ta mai banza kamar bata jin sa sai da ya kuma maimaitawa sannan ta kalle sa a karkace ta ce

"Ai na ji kuma na fahimta ba kurma bace ni da zaka faɗi magana ka kuma nanatawa duk dan in ji ka ba"!!a yanzu wannan amsar da ta bashi sai ya ji abin wani iri bata taɓa responding mai magana a haka ba sai yau bai san dalilin ta ba amma ko menene dalilin ai bai cancanci irin wannan kalamai daga gare ta ba...

Miqar da ita tsaye yayi cikin yanayi na tsananin damuwa da kulawa yace"

Luv menene please tell me sbd Sam nakasa gane kanki

Please tell me meye matsalar?

Idan maganar Fifi ne inaga mun wuce gurin right?

Kallonsa tayi da sauri hawayenta na sake saukowa cikin rawar murya tace"

Fifi is always ahead of me,

Meyasa bazaa daina qina da wareni ba acikin family na sbd Fifi?

Meyasa mijina zai zai zama bawan mijin fifi sbd mijin Fifi yafi nawa..

Kallonta yayi da wani irin zallar mamaki da tsoro yace"

Hameeda me kike fada?

Meye ruwanki da mijin Fifi ko Kuma wani Abu kaman hakan tunda dai mijinta baifi nakinba.....

Cikin fita hayyaci tace"

Yafi nawa tunda yafisa komai

Dukiya,ilimi, wayewa hutu, kyau soyayyarsu ammy da hajjo da komai da komai ma.....meyasa mijinta yafi nawa zuciyata quna takeyi I can't take ita Kun taru kun hainceni Kun boyemin Asalin wayene Marshall sbd tun farko baaso ya aureniba.....

Cikin kaduwa khaleed ya girgiza ta Yana cewa"

Hameeda ki daina wainnan zancen kishin Fifi ne ke cinki zai gurbata tarayyarki da yar uwarki please stop wannan kaman kina Mata hassadane...

Ture hannuwansa tayi tana kuka tace"

Kaima da kake nawa bayanta kakebi,

Harda Kai aka taru aka boyemin baa fada min gskiyar waye saheeb ba you lied to me khaleed....you hid this from me..

Daskarewa khalid yayi agurin cikin tsananin firgici da tashin hankali tareda tsananin tsoro idanuwansa suka ciko da wasu irin hawayen nauyinda zuciyarsa ta dauka ya kasa furta komai sbd nauyinda bakinsa yayi.

Atake tadawo mutsuwarta tareda Dana sanin maganarta cikin sauri ta riqo hannunsa tana hawaye tace"

Baby I'm

I'm sorry ba abinda nake nufiba kenan plea....

Bata qarasaba ya janye ya nufi daki da sauri haryana buge qafarsa da kujera ko gani bayayi sosai.

Jininsa daya buge qafarsa ta durqusa agurin tareda fashewa da sabon kuka tana cewa"

Da gaske hassadar Fifi nakeyi???

Ni meyasa ko yaushe Fifi ce abakin kowa?

Daqyar yayi wanka yafito ya wuceta a palon jikinsa duk a sanyaye Saidai zuciyarsa acike takeda damuwa da bacin Rai Saidai kamar yanda yayi alqawari hameeda itace farin cikinsa zai tsaya tsayin daka Dan ganin bai Bari wannan halinda aka jefata ya Bata rayuwartaba zai zame Mata bango Kuma abokin rayuwa na qarshe.

Basu dawo gidan ba sai dare lis dan yawo ya rinƙa jan yayan nasa yana gargaɗin sa shi kuma yana mai nuni da ai faranta mai yake son yi dan rabon su da juna shekaru da dama,toh sai Saheeb ɗin bai ja ba ya ƙyale Khalid ɗin har sai da dan kan shi ya bar su suka dawo gida...

Har sashen yayan nasa ya raka sa ya kira sashen su Ammy da a kawo wa yayan nashi abinci,sai da aka kawo ya tabbatar yayan nashi baya buƙatar komai sannan ya mai sai da safe ya nufi sashen su..

Bai yi mamaki ba ganin an kashe light ɗin parlor dan ta saba sai ya ƙarasa ciki ua hango ta kwance tana danna waya..

Da sigar zolaya ya ce da ita

"Luv ba sai kin kira ni ba na san kewa ta kika ji kuma kin ga ban dawo da wuri ba shi ya sa kike son kira na right"!?ya ɗage gira ɗaya sama sai ta taso da sauri tafada jikinsa tareda qanqamesa tana fashewa da qaramin kuka batareda ta iya furta komaiba.

Sake shigarda ita jikinsa yayi Yana sauke numfashi ahankali.

Haka suka cigaba da yin rayuwar zaman shiru a gidan nan sam Hamida bata da lokacin Khalid kullum safe tana garden tana kallon Saheeb kuma da zarar lokacin tashin sa yayi sai ta bar wurin dan kar ya gane ta kuma daidai da rana ɗaya bai taɓa sanin da zuwan ta ba sai dai yayi abinda ya kai sa ya gama ya wuce..

In ma fannin abinci ne in ta gama bata saka mai a food warmer sai dai ta bar mai haka nan duk inda ya kai ya kawo da yunwar sa in ya dawo daga aiki haka zai yi reheating abincin ya ci kamar bai da mata,sam sam zaman su ba wani daɗi,kyautatawa sai wanda ta ga damar yi take mai,lokacin sa ma bata da shi sai ta ji dan kan ta ta saurare sa,haƙƙin sa kam ya manta rabon ta da ta ba shi sai dai da ya matso ta ta ɓata fuska ta ce she is not in the mood..

Duk wannan abinda ke gudana babu wanda ya san da shi daga ita sai shi ba ƙaramin gasa mai aya a hannu Hamida ke yi ba kuma bai da ikon yin magana dan yana tunanin wa zai tunkara da wannan batu a wurin sa kamar abin kunya ne a ce shi da matar sa amma bai isa ya ji daɗi ba..

Batun zamantakewar ta da su Ammy kuwa babu abinda ya sauya dan nesanta kan ta da su take yi ba kaɗan ba har ta kai ta kawo in Hajja ta zo sashen ita Hamidar ta manta bata rufe ƙofa ba da ta ga Hajjan sai tayi saurin tashi ta wuce da zarar ta gaishe ta abin na damin Hajja har da Ammy ba kaɗan ba dan da zuciya ɗaya suke son jawo Hamida jikin su amma ita gani take kamar yi suke yi na ganin ido shi yasa ta ƙi sakin jikin ta da su..

****

Yau monday yau ne fifi ta yi nasarar kammala jarabawar ta na first semester kuma da farinciki ta dawo gidan dan papern ya mata daɗi bata yi zaton zai zo mata da sauƙi haka ba.

Ranar Hajja ta shawarce ta ko zata tafi ta kaiwa yʼar uwar ta ziyara ƙila ta yarda da ita su tsaya su yi magana tunda su dai bata tsayawa su yi wata doguwar magana bata zuwa sashen su su kuma in suka tafi sai ta tashi ta bar su..

Fifi dai bata gamsu da shawarar kakar nata ba dan ita kaɗai ta san irin zafin da ta ji a lokacin da Hamida ta ture ta daga jikin ta haɗe da bata wani dirty look ranar ta ji ba daɗi bata san ƙiyayyar da yʼar uwar nata ke mata ya kai haka ba sai ranar shi ya sa ta yanke hukuncin bata kuma zuwa wurin ta sai dai ta cigaba da yi mata addu'ar saukowa dan ba iya nan ta tsaya ba hatta da silent intimidations ɗin da ta ke yi mata a baya ta cigaba da yi har yanzu bata daina ba kawai dai bata sanar da su Hajja ne dan kar abin ya kuma taɓarɓarewa Hamida ta kuma tsanar ta...

A daren ranar ta fito parlor bayan kowa ya kwanta bacci ta zauna ta saka system ɗin ta a gaba tana duba wani abu gudun kar ta tayar da Ammy ya sa ta dawo parlor dan ta sake ta yi abin ta da kyau..

Kimanin mintuna talatin tana ta abinda take yi sai ta tashi tana rufe system ɗin alamar ta gama ta cire shi daga chargi tana naɗewa ta saka footwear ɗin ta tana miƙa tana salati..

Juyowar nan da zata yi sai ta ga mutum a hanyar water dispenser yana ɗiba ruwa dan sha..

Saurin gyara rigar baccin jikin ta tayi duk da riga da wando ne kuma bai bayyana tsiraicin ta ba amma sai ta ji faɗuwar gaba ya riske ta..

Wanene wannan ɗin da ya tsallake kitchen ya ratsa har main parlor ya zo shan ruwa,sai da ya juyo shima ya lura da ita dan akwai tazara tsakanin ta da shi kasancewar parlorn babba ne..

Shaƙewa ya so yi da ruwan dan yayi zaton ghost ne bai taɓa jin tsoro irin wannan ya riske shi farat ɗaya ba..

Sai da ya ƙare mata kallo ya tabbatar mutum ce kuma itama kamar a tsorace take sai shi ya riga ta magana.

"Am sorry"daga faɗin haka ya juya ya fice abin sa ita kuma ta haura a guje dan ganin fuskar mutumin ranar nan da ta yi wanda Ammy ta ce wai shine yaya Saheeb ɗin da suke jin labarin shi...

Da tunanin shi ta kwanta tana ƙoƙonta anya shine ko dai wani Saheeb ɗin ne dan wannan bai yi kamar shine Saheeb ɗin da suke tsammanin gani ba..

Gari na wayewa ta nufi sashen Hajja da yanzu ta idar da sallah tana azkar ta zauna jiran ta har ta ɗan taƙaita suka gaisa bata yi nauyin baki ba ta tambayi Hajja ko waye wannan da ya zo ɗin,Hajja ta tambaye ta dan neman ƙarin bayani nan ta mata kwatancen sa sai Hajja tayi murmushi ta bayyana mata ai shine yayan nasu almost same amsa da Ammy ta bata ne Hajja ta bata sai ta kuma tambayar Hajja wai shin shekarun sa nawa..

A nan sai da Hajja ta dara ta ce ba tsakanin ta da mijin ta bane wannan,haka fifi tayi tayi Hajja ta faɗa mata amma Hajja ta ƙi ƙarshe ma kora ta tayi dan kawo mata zancen wai ya ce matar sa zata dawo daga jibi zuwa juma'a sai fifin ta kama jiki dan Muhibbah yaɗar gayu ce kuma ta girme mata ba kaɗan ba..

Wannan zancen Hajjan ne ya kori fifi ta miqe ta nufi qofar fita da sauri ta bude tareda ficewa gaba daya daidai shikuma ya budo qofar zai shigo qirjinta ya sauka a kirjinsa sosai Wanda ya haddasa musu Shirin faduwa sbd baisan da itama hakama itama

Sukayi baya ya dafe bango da hannunsa daya yayinda dayar hannun ya riqeta sbd yanda tsoro da firgici yasa ta qanqamesa tana rufe idanuwanta.

Ahankali ya dago ya kalli fuskarta akaro na farko dayaji razanar zuciya Bayan kallon wata 'ya mace,

Itama ahankali ta bude idanuwanta ta sauke Masa zuciyarta na tsananta harba Wanda haryanaji a qirjinsa datake Kai.

Hajja ce ta Dan daga murya tace"

Meyake faruwane agurin wai naji shiru???

Saurin sakinsa tayi shikuma ya fuske tareda dauke Kai ya fada dakin da sallamarsa data sake fadar da gaban fifin ta waiwayo ta kalli bayansa tana Jin wani zazzabi nason kamata

ta koma ta kwanta a gadon Ammy tana ta tunani da ƙiyasta ya matar nasa zata kasance dan in har shi yayi appearing a haka ba a tsohon da tayi tsammani ba ya matar nasa zata kasance ga shi Hajja ta ce yaar gayu ce...

Ba ƙaramin halin tunani da jimami fifi ta shiga ba sakamakon waɗannan abubuwan al'ajabi da take gani a gidan right now tunanin Hamida da yanda komwi ke Naman lalacewa a tsakaninsu Yana damunta saikuma na wannan ɗin da wai shine mijin ta da na matar sa da wai zata zo abin na ta mata yawo har bacci dai ya ɗauke ta,tsabar ta saka abin a ran ta sai ta rinƙa ƙananan mafarke mafarke kala kala a baccin nata game da matar yaya Saheeb ɗin ƙarshe da ciwon kai ta tashi ta rinƙa tsaki tana jin haushin ɗorawa kan ta damuwar wasu,da haka ta bar gadon babu Ammy a ɗakin ta wuce dan yin wanka a lokacin har 11am yayi...

Kamar ko yaushe tayi wankanta na yamma tana Shirin zuwa gurin hameda ammy takirawota kicin fuskarta Babu alamar Wasa ta nuna Mata qaramin tray da aka jera combo juice nasu fruits marasa zaqi tace'

Dauka kikai sashen mijinki Yana jira Kuma idan kinkai ki jira yagama ki kawomin kayan.

Kallon ammyn tayi tasake kallon kayan kafin takuma kallon ammyn taga Babu Wasa ko sauqi a fuskanta saitaji jikinta yayi sanyi har zata dauka saita fasa tace"

Bari nadauko mayafina....

Kije ahaka jira yakeyi and karnaga qafarki anan sai ya gama infact ki zauna acan zakuyi mgnar inda kikeson zama.

Rau Rau tayi da ido zatai mgn ammyn ta wuceta tana sake tsuke fuska sbd taga idan Bata tashi tsayeba akan Fifi idan muhibba tazo da matsala.

Part din ta nufa tayi knocking ahankali Kai tsaye yace"

Com in Yana amsa waya.

Murda qofar tayi ta tura ta shigo wani sanyin AC da qamshi suka daketa ta qarasa shigowa tareda tura qofar tana kallon qasa sbd bazata iya kallonsa ba.

Shima dagowa yayi yayi Mata kallo daya ya maida kansa kan kallon laptop Yana cigaba da wayarsa.

Ajiye Masa tray din tayi hannuwanta na Dan rawa ahankali ta furta"

Ina wuni cikin siriryar muryanta data Kuma sashi dagowa ya kalleta da idanuwansa dasuke wasu blue blue.

Kamar bazai amsaba yace"

Lfy klau sit.

Zama tayi adarere tana kallon yanayin tsarin palon a takure ga zuciyarta dake wani irin tsallen rashin sukuni.

Yana gama wayar ya ajiye ya rufe laptop dinsa bai dagoba ya zuba combo din a cup ya dago ya Dan kalli gefenta ya hango zallar yarintarta da kuruciyarta sai kawai ya dauke Kai Babu abinda ya fado Masa sai ranarda aka haifesu Amma shine su ammy basuyi wani dogon tunanin nisan shekarunsu ba aka ɗaura Masa aure da ita alhalin zai Isa haihuwarta insha Allah.

Kamar bazaiyi mgn ba cikin wani irin class yace"

Kije.

Ahankali ta dago ta Dan kalli gefen fuskarsa dake kwance fresh da qananun gashinda suka mugun kwanta cikin siriryar muryar basarwa tace'

Ammy tace nadawo da kayan.

Shiru yayi kamar baiji ba kafin yace"

Ok ki dauka na gama.

Tashi tayi cikin mamakinsa da Dan Jin haushinsa na yanda yake wani basarwa ta dauki kayan ta fice batareda tace Masa komaiba.

#Mamuh*21*

Dawowa sashen su tayi tana jin mamakin sa har ta shiga kitchen bata ankara ba sai da ta ji kamar ta buge abu sannan ta dawo hayyacin ta ta kalli abinda ta buge..

Ɗan tsaki ta ja tana dire tray ɗin saman babbar fridge ɗin kitchen ɗin tana mai zama saman wani stool mai juyawa amma bata bari ya juya da ita ba sai ta zauna still ta dogara hannun ta da saman kitchen table dake nan kamar round dinning table,sannan ta tallafe kumatun ta da hannuwan ta biyu ta yi shiru tana kallon direction ɗaya..

"Ni kam wannan wani irin mutum ne shi?daga haɗuwa da shi har yana nuna min jin kai yana wani basarwa hala bai san Ammy ce ta tursasa ni kai mai abin shan ba ƙila shi ya sa ya min wannan jan ajin,toh amma ai nima kyau ne da ni ko?ina da kyau mana toh da me yake taƙama"?wata zuciyar ta amsa mata da ai shi soldier ne ko kin manta..

Jan iska tayi sannan tayi breathing out tana girgiza kai sai ta kuma faɗawa wata duniyar tunanin daga bisani ta kalli agogon dake manne a kitchen ɗin ta ga 6:40pm magrib na gabatowa sai ta sauko daga kan kujerar ta nufi hanyar upstairs dan kaiwa Ammy sakamakon aiken ta da ta yi..

Wani abin al'ajabi da ya faru shine tana haurowa ta yi kicibis da fuskar sa sai ta ga kamar tsananin damuwar sa da ta saka a ran ta ne game da shi ya sa ya zo yake mata gizo.

Har zata wuce sai ta kuma kallon sa ta ga yayi blinking idanun sa haka ya tabbatar mata da shine a zahiri ba mafarki ba..

Saurin wuce sa tayi tana jin faɗuwar gaba matsananci da bata san dalilin sa ba,bin ta da kallo yayi har ta gushewa ganin sa ya girgiza kai yana mamakin ɗabi'ar ta kamar ta ga dodo har da gudu,shi kam su Ammy sun haɗa shi da aiki wannan yarinya a matsayin matar sa abin na bashi mamaki har yau,dan shi har yanzu da ya kalle ta tunowa yake yi still da lokacin da aka haife ta ita da yar uwar ta Hamida aka bashi su ɗai ɗaya ya riƙe su,wai an wayi gari ɗaya cikin yaran ne kuma aka aura mai at his age ya san ko a haihuwar kaji ya haife ta ya kuma haifi wacce zata girme mata..

Ƙarasa saukowa yayi yana ta nazari a zuciyar sa game da irin rayuwar da zai yi tare da fifi a ƙarƙashin inuwa ɗaya a matsayin mata da miji..

Da gudu ta shigowa Ammy ɗaki har sai da Ammyn ta ji tsoro ta kalle ta da mamaki ta ce

"Me ye kuma haka baby,ko kin manta kina da aure ne yanzu da kike guje guje haka"?kallon Ammy tayi sai kuma ta ji bata jin sanar da ita abinda Saheeb ya mata kawai sai ta yi murmushi ta ce

"Am sorry Ammy i was eager to see you"!!kallon zargi Ammy ta bi ta da shi har sai da ta ji ta tsargu sai ta shashantar da zancen ta hanyar jan hannun Ammy ta kai ta saman sallayar da take shirin hawa dan bada farali..

Kallon ta kawai Ammy ke ta yi har ta je ta kwanta bisa gadon Ammy ta ba Ammy baya sai Ammy ta girgiza kai kawai bata mata magana ba ta tayar da iƙamar ta dama fifi na fashin sallah sai tayi kwanciyar ta kawai...

2 hours later

A dinning table yau Ammy ta ji a yi dinner sai ta sa aka kawo duka abincin nan har wanda za a kaiwa Saheeb ta ce a bar shi a kawo nan shima zai yi joining ɗin su..

Fifi dai na jin Ammy amma da so samu ne da ta roƙi alfarmar kar a bar ta a nan a bata dama ta wuce da nata sama ta ci a can dan ta san ko presence ɗin sa kaɗai ya isa ya hana ta sakewa bare ta ci abincin har ta ƙoshi..

A gaban ta Ammy ta kira sa a waya ta ce mai ya zo su haɗu a dinning ta girka mai favourite ɗin sa,sai ko ba a jima ba yayi sallama ya shigo direct ya nufi sashen da dinning ɗin yake nan ma ya kuma doka sallamar sai da fifi ta ji sallamar a kan ta dan ba normal voice da mutani ke amfani da shi wurin yin magana shi yayi amfani da shi ba..

A matsayin sa na babba kuma elder person yayi sallamar,yana ƙarasowa dan gaida su Ammy kafin ya zauna fifi ta rinƙa kallon sa ƙasa ƙasa..

Har ya zauna bata sani ba sai muryar Ammy da ta ji tana umartar ta da ta yi serving yayan ta..

Duban ta ta maida ga Ammy sai Ammy ta kuma maimaita mata ta tashi tayi serving yayan ta shima Saheeb ɗin sai ya dubi Ammy ya kuma dubi fifi wacce a dai dai lokacin idanun ta ya kai gare sa dan ganin ya zai yi reacting da jin wai ita ce zata yi serving nasa abinci..

Sai ta ga idanun sa akan ta yana kallom ta abin sa ya bata mamaki tayi tunanin attitude ɗin da ya bata ɗazu zai bata yanzu amma sai ta ga akasin hakan,a zuciyar ta sai ta rinƙa muhawwara da kan ta akan ai ƙila ko halin sa kenan abinda ya maki ɗazu nan gaban mahaifiyar sa ce ba zai yi hakan ba..

Taɓe baki tayi kawai ta tashi a natse dama atamfa ce a jikin ta ɗinkim doguwar riga A-shape dan har yau bata gama zama gwana a ɗaura zani ba dama dama skirt takan ɗan saka sa wasu lokutan but ta fi yin free da doguwar riga..

Gyara ƙaramin gyalen kan ta tayi ta hau tafiya a hankalin dan table ɗin babba ne kuma yana da faɗi in har so kake kayi serving abinci comfortably toh sai dai ka zagaya dan in ka tsaya a inda kake ba zaka ji daɗi ba..

Takun da take yi shi ya saka sa kai idanun sa gare ta ya rinƙa kallon ta a hankali cikin hikima har ta zo gab da shi ta tsaya,sai kuma ƙamshin ta ya shige sa nan ma still ya kuma aika mata wani irin kallo ita kuwa matsanancin faɗuwar gaban da ta rinƙa samu ne ya sa ta kasa natsuwa ta tambaye sa me zai ci sai kawai ta fara bubbuɗe wadatattun food warmers ɗin ta ɗau babban serving spoon ta fara ɗibar mai abincin tana zubawa..

Sai da ta zuba mai abinci kusa 4 dishes a plate ɗaya ko wanne da inda take zuba sa da ta gama ta rasa ya zata ce mai ta gama zuba mai sai ta dubi Ammy..

Abin mamaki sai ta ga idanun Ammy da na Hajja a kan su da har su sun fara cin nasu abincin amma suka dakata suna kallon dramar ta su kamar ba komai suke yi ba..

Ammy na ganin ta kalle ta sai ta kalli Hajja wacce itama da sauri ta kawar da kan ta daga kallon su ta maida ga abincin gaban ta..

"Hajja kin ƙoshi ko in ƙara maki"!?sai Hajja ta amsa mata da ya isa hakan daga nan suka cigaba da cin abincin su ba tare da sun kuma kallon sashen su fifi ba sai dai sun ƙunshe dariyar su a ciki kar ya fito but ba ƙaramin dariya fifi ta ba su ba duba da yadda ta tsaya kamar soldier a tsaye ta kyaɓe fuska kamar zata yi kuka shi kuma yana kallon ta kamar tana abinda ba daidai ba..

Tayi tayi Ammy ta ɗago ta kalle ta dan ta taimake ta ta mai mgn amma ko a kuskure Ammy bata ɗago ta dube ta ba haka Hajja kuma ba wai basu san tana buƙatar taimakon bane,sune ankare sai dai suna ganin in suna shiga al'amarin ta har yanzu da mijin nata ke nan toh ba zasu saba ba kuma ba zasu san juna su fahimci juna ba...

Fifi na nan tsaye kamar an dasa ta Saheeb na zaune yana kallon ta yana girgiza kai dan mamakin saurin girman da ta yi farat ɗaya shi sam bai ma san ana wata drama a wurin ba bare ya ɗauke kan sa daga kallon nata..

Ita kuma bata yarda ta haɗa ido da shi ba bare ta ga reaction ɗin sa addu'ar ta Allah ya sa ya juyar da kan sa ko wani abu ya shige mai idon da zai ja hankalin sa ya ga abincin ita kuma ta gudu..

Kusan mintuna biyar babu abinda ya faru sannan ita ta fara gajiya da tsayuwar sai kawai ta yi shahada ta buɗe baki cikin fargaba ta ce mai

"Abincin ka...ur food....i just serve it kalla gashi"!!kalaman nata are not coordinated wanda ya saka su Ammy kasa riƙe dariyar dake ta cin su suka sake ta.

Sai a sannan Saheeb ya farfaɗo daga kallon ƙurillar da yake yiwa fifi wanda a wurin sa kallon saurin girman ta yake yi yayin da su Hajja ke tunanin ko ya razana ne da kyawun fifi har ya kasa daina kallon ta shi yasa ran su yayi fari tas...

Gyara murya yayi yayi saurin kai idanun sa ga abincin sai kuwa fifi ta sulale ta baya ta gudu ta haura upstairs..

Ba wanda ya ankara sai da Ammy ta ɗago dan kallon ta sai ta ga wayam ba kowa a wurin,ƙara danne dariyar ta Ammy tayi ta dubi Saheeb da yake shirin fara cin abincin sai ta ɗan murmusa ta cigaba da cin abincin nata.

Hajja ce ta ƙura mai ido tana kallon sa sai ta ga yadda ya lumshe ido da ya kai spoon ɗaya,sai ta ji tausayin sa ya mamaye mata zuciya Allah kaɗai ya san rabon sa da cin girkin mahaifiyar sa,matar nasa bata da lokacin kan ta bare nasa ta yaya zai sami abinci irin wannan,cigaba da kallon sa tayi mutumin that is worth marrying his daughter out amma yana cin girkin mahaifiyar sa kamar wani ɗan shekaru goma sha wannan irin aure nasa na farko da shi da babu duk ɗaya ne a wurin ta shawarar auren sa da fifi yayi ma'ana kuma yayi amfani ko ba komai ta san fifi ba zata kunyata su ba in dai fannin kula da shi ne da cikin sa...

Sai da ya ci kusan rabin plate ɗin sannan ya kalli Ammy cikin jin daɗi a ran sa ya ce

"Ammy na it's awesome i love d dish"!da fara'a Ammy ta kalle sa ta tambaye sa

"Da gaske yayi daɗi"?gyaɗa mata kai yayi yana kuma kai spoon ɗaya bakin sa sai kawai ta ce

"All thanks to Mufida ita ta girka i only gave her directions"!!ƙamewa spoon ɗin yayi a bakin sa bai ƙarasa saka sa ciki ba haka bai fitar da shi waje ba take ya ji kamar ba shi ba..

Kallon sa Ammy tayi tana murmushi tana ganin yadda ya sauya amma tayi kamar bata gan sa ba..

Ai kuwa ɗan halas sai ya fiddo spoon ɗin waje da abincin ciki ya mayar cikin plate ɗin ya ɗau tissue yana goge bakin sa haɗe da tashi yana faɗin

"Na ƙoshi Ammy tnx sai da safe"!bin shi da kallon mamaki suka yi sai Hajja ta juyo da sauri ta dubi Ammy tana bata kallon meye hikimar ta na yin haka sai Ammy ta ɗan murmusa ta ce

"Hajja rabu da shi na san ya ji daɗin abincin kuma da sani na na ce mai fifi ce ta girka ba dan komai ba sai dan in ƙara janyo su kusa da juna kin dai san auren nan nasu ba a natse aka yi sa cikin kwanciyar hankali ba dole akwai gaps da yawa a tsakanin su da sai dai mu da muka haɗa su zamu taimaka mu cike masu gaps ɗin wannan dalilin ya sa na bar shi ya ɗan nitsa cikin cin abincin sannan na ce mai Mufida ta girka duk da ba ita ɗin ba ce amma Hajja believe me wannan hikimar da na yi zata janyo su kusa ke dai ki tsaya ki ga me zai faru next"!faɗaɗa murmushin fuskar ta Hajja tayi tana gyaɗa kai alamar gamsuwa,da haka suka ƙarasa cin abincin nasu suna tattauna irin dramar da Saheeb da fifi suka yi...

*****

Fifi na shiga ɗakin Ammy sai ta faɗa saman gado ta rinƙa sauke ajiyar zuciya tana jin fargaba na shigar ta ta yaya tsoron Saheeb yake mamaye ta ne haka a sannu? girgiza kai tayi kawai ta rufe idanun ta da tafin hannuwar ta ta rinƙa tunane tunane ta yaya Ammy ta ƙi taimaka mata wurin yiwa Saheeb mgn bayan ta gama zuba mai abinci alhalin ta san bata iya yi mai mgn..

Lkc ta ɓata tana tunanin abinda ya faru gashi ta gama kwaɗaituwa da girkin Ammyn amma bata ci ba duk sbd wannan yaya Saheeb ɗin..

Juyawa tayi ta lumshe idanun ta tana tuno abinda ya faru a tsakanin su tun safen yau har ɗazu,juyi ta rinƙa yi har Ammy ta shigo ta rinƙa murmushi tana kallon ta daga bisani ta kira sunan ta a ɗan firgice ta juyo ta kalli Ammyn sai ta ce da ita

"Baby daga yi serving yayan ki abinci kuma shi kenan sai ki gudo nan ɗaki ba tare da kin ci ba"?shiru fifi tayi tana sauraron Ammy kamar ta ce mata a matse take tana son ɗanɗana abincin amma sai mgnr Ammy yayi intruding.

"Kin san me ma kuwa"?sai fifi ta girgiza kai Ammy na murmushi ta ce

"Yayan ki ya ce abincin ya mai daɗi sosai dan ce mai nayi ke kika yi so u have to improve in ur cooking skills dan yana son girkin gargajiya kawai dai bai cika samin irin na gargajiyar bane amma yana matuƙar so"!!

Huhh..is Ammy for real!?toh ita meye ruwan ta da Saheeb da Ammy ke ta nanata mata yanda yake son girkin gargajiya?ita fah har yanzu tana ganin abin a almara wai Saheeb ɗin nan ne mijin ta...

Share tunanin tayi kawai ta hau sauya kayan ta zuwa na bacci duk Ammy na lura da ita sai da ta zo zata kwanta Ammy ta ce ya haka sai tayi tsaye tana kallon ta nan Ammy ta ce mata ai Saheeb baya kwanciya sai ya sha warm nscafee if not ya rinƙa damuwa kenan dan haka ta je ta haɗa mai a kitchen ta kai mai and she should make sure ya sha kafin ta dawo..

Mamakin Ammy ta rinƙa ji sai ta ga kamar Ammyn ta daina son ta amma ba ɗabi'ar ta bane yin jayayya da Ammy ba sai kawai ta ɗau hijabin ta ta saka ta fito ta nufi parlor ta wuce kitchen tana haɗa nscafee ɗin tana tunanin ko ya zata kasance a tsakanin su in ta kai mai ɗin ita wlh cika idonta yakeyi yayi Mata kwarjini da yawa..

"Ko damuwa da rashin cin abinci na Ammy bata yi ba wai in zo in kai mai toh ni fah"?ta tambayi kan ta,kamar zata zauna ta ci abincin ta sai kuma ta fasa ta ɗau ƙaramin tray ta ɗora mug cup ɗin ɗin ta nufi hanyar sashen sa...

Tana tafe haske na haska mata sashe biyun da na yar uwar ta Hamida da na yaya Saheeb ko ta ce wai nata ita da wata..

Tuno da Muhibbah da ta yi sai ta ɗan ji wani iri haka dai ta ƙarasa ciki,bata tsaya ko ina ba sai inda ta gan sa ɗazu ko da ta isa wurin sai bata gan shi ba,bata tsaya wani tunani ba ta nufi hanyar wani ɗaki ta tura ƙofar ɗakin da sallamar ta..

Saheeb dake tsaye yana gyara carving ɗin sa na fuska ɗaure da towel gaban mirror da nufin in ya gama ya shiga wanka sai kawai ya ji sallamar mace bai bada izini ba ya ga shigowar ta..

Daga ita har shi sai da suka razana da gudu ta juya mai baya shi kuwa cikin ɓacin rai ya furta

"Goddamn it meye haka ke ba a koya maki in kika yi sallama ki tsaya a baki izinin ba tukun ki shigo"?ya mata tmbyr ba wasa a tare da shi.

Jikin ta na ɓari bakin ta na rawa ta ce da shi cikin tsoro

"Ka...k..ka yi haƙuri...coffee na kawo maka"!!kasa ƙarasawa tayi akan Ammy ce tayi assigning ɗin ta sai tayi saurin nemar inda zata aje trah ɗin kafin yayi slipping daga hannun ta dan hannun nata kyarma yake yi...

Tsaki ya ja yana wurgar da hand clip ɗin ita kuma ta fita cikin sauri ta koma sashen su gaban ta na faɗi tana ta numfarfashi kamar ta yi gudun tsere..

Ko da ta shigo sai ta ga har Ammy ta yi bacci dan haka ta hau gadon kamar matsoraciya ta kwanta ta ƙanƙame jikin ta cikin blanket haɗe da runtse idanun ta ko baccin dole zai ɗauke ta dan ta daina ganin gizon fuskar ta sai dai ta kasa baccin sai juyi dama da hagu daga baya da ƙyar baccin yayi nasarar fizgar ta bayan ciwon kai ya mamaye ta....

#Mamuh*22*

Da sanyin safiya Ammy ta tada fifi akan ta tashi ta yi wanka,sai abin ya mata wani iri is somehow wired Ammy da ba cika son tashin ta a bacci take ba sai ta ji dan kan ta ta tashi amma yau ta tayar da ita..

Bata yi musu ba ta miƙe ta tafi toilet tayi wankan ta gyara kan ta a ciki ta fito ta nufi mirror dan gyara jikin ta,Ammy ta riga ta fita zuwa ɗakin Hajja dan yi mata gaisuwar safiya inda daga gaisuwa kuma suka zauna hira har ta manta da ta saka fifi yin wanka..

Da ta gama gyara jikin sai ta nufi wurin closet ta buɗe ta tsaya ƙare ma kayan cikin closet kallo tana nazarin wanda zata saka,amma haka ta gaji tsayuwa bata samo wanda ya mata ba duba da irin yanayin sanyi na garin sai tayi tunanin saka hoodies da summer outfit kawai since ba fita zuwa ko ina zata yi ba..

Ciro wata leather summer Cardigan tayi mai ɗan tsayi da wata blue women jeans ta zuba su kan gadon sai ta dawo ta saka inner wears sannan ta saka kayan a sama ta saka hular ta ɗau wayar ta tana selfie dan turawa ƙawayen ta na germany..

Tana kan ɗaukar na uku ta ji turo ƙofa sai bata juya ba tunanin ta Ammy ce sai ta cigaba da ɗaukar hotunan amma sai ta ji ba a kuma motsawa ba sai ta juyo tana faɗin

"Ammy tun ɗazu ina kika shiga almost an hour"!!mgnr nata ne ya sarƙe sakamakon haɗa ido da tayi da Marshall kawai sai ta ji kamar an saka mata battery ana controlling movement ɗin ta..

Kasa natsuwa tayi shin gaida shi zata yi ko dai ta juya baya ne?,tana tsaye ta kuma kallon sa sai ta kawar da kan ta tayi shiru shima yayi kamar bai san state ɗin da ta shiga ba ya waske kawai ya buɗe baki ya tambaye ta inda Ammy take sai ta amsa mai da

"Nima ban san ina ta tafi ba"!!sai ya ga kamar ta mai amshin rashin kunya duk da sigar da tayi amfani da shi wurin amsa mai ba sigar rashin kunyar ba ce..

Juyawa yayi ya fice abin sa bai sake ce mata komai ba as bata yi ilimin gaida mutum ba kamar yadda yayi tagging nata..

Bayan fitar sa sai ta sauke wani nannauyar ajiyar zuciya ta jingina da closet ɗin tana mai lumshe idanun ta sakamakon jin wani baƙon lamarin dake bijiro mata a fizge..

Tana nan tsaye idanun ta lumshe sai ga sallamar Ammy ta shigo ɗakin,a hankali ta buɗe idanun ta ta zubawa Ammy sai ta raba jikin ta da closet ɗin ta ƙaraso ga Ammy tana tambayar ta ina ta tafi tun ɗazu..

Bata amsa mata ba ta ja hannun ta tana ce mata

"Baby je ki gaida Hajja tana son ganin ki"!!kallon Ammy tayi kamar ta faɗa mata ai yaya Saheeb ya zo amma sai ta ƙyale kawai ta fita zuwa hanyar ɗakin Hajja hankalin ta na nan na tuno mata Marshall..

Sallama tayi a ɗakin aka amsa mata sai ta saka kai ta shige ba tare da ta tsaya duba wa ke gaban ta ba..

Tuntuɓe ta yi da mutum kawai sai kamar zata faɗi amma tayi saurin kama jikin ta cikin sauri ta ɗago ta kalli wa ta buge..

Ganin sa tayi zaune cikin mamakin ta itama da mamaki ta kalle sa yaushe kuma ya zo nan ɗakin?ohh ita Mufida yau ta ga abin al'ajabi yanzu yanzu ya bar ɗakin Ammy kuma har ya zo nan ita me ya sa suke haɗuwa ne da yawa haka...

"Ƙaraso mana takwara ta zo ki zauna"!!ƙarasawa ciki ta yi a natse ta sami wuri ta zauna nan kusa da Hajja sai kuwa ya miƙe dama ya gama gaisuwar tashi zai yi ya fita sai fifi ta shigo..

"Na tafi Hajja na"cewar Marshall ya saka kai ya fita sai Hajja ta juyo ta kalli fifi tana faɗin

"Kin ga ɗabi'un mijin ki ko takwara?haka yake ya cika son zaman kaɗaici kuma bai dace da lafiyar sa ba"!shiru ta yiwa Hajja kamar bata ji ta ba sai ta gaida ta itama ta tashi tayi fitar ta..

Dawowa ɗakin Ammy tayi ta sanar da ita sun gama gaisawar da Hajja sai Ammy ta ja hannun ta zuwa ƙasa,basu tsaya ko ina ba sai kitchen inda a nan Ammy ta rinƙa jan ta da labaru mostly akan mijin ta wato Marshall Saheeb ita dai fifi na jin Ammy a wasu labarun mata sai ta ga kamar da gangar Ammy ke faɗa mata su duk dan shi ɗin ɗan ta ne kuma tana nema masa shiga a wurin ta..

A kai a kai Ammy ke kuma tunatar da ita yadda mace ke karɓe mijin ta musamman ta fannin girki haka ta nuna mata nata mijin mai son abinci ne sai dai ij bai samu ba sai ya haƙura amma yana son abinci musanman na gargajiya..

Da hirarrakin Ammy wanda fifi ba amshin baki take bata ba sai uhum uhm suka kammala ayyukan suka fito da wasu yayin da yɣan aikin suka fito da sauran dan tun dawowar Marshall Ammy da kan ta take shiga ta rangaɗa mai girki da kan ta sanin duk duniya tun yarintar sa har yau da ya manyanta in har yana gidan baya yarda ya tsallake girkin ta dan yayi ranking ɗin ta a matsayin world most best a fannin girki haka ya sa even after his marriage ko da a ɗan suɓuce Muhibbah ta mai girki baya yarda ya tsallake na mahaifiyar sa bare ma ba lkcn sa Muhibbahn ke da ba...

Zazzaune suka yi a dinning table ana ɗan hira mai kama da muhawwara tsakanin Ammy da Hajja ita dai fifi nata ido,ana haka sai sallamar Saheeb ya tsaidar masu da hirar tasu..

Gaban Mufida ne ya faɗi amma bata bari ya bayyana ba,yawa yawan haɗuwar su a tsakanin jiya zuwa yau na bata mamaki da ɗaure mata kai dan tun jiyan nan har yau sam zuciyar ta ta kasa samin natsuwa bare ta tantance menene sahihin abinda ke damin ta..

Jin zaman shi kawai tayi sai ta ɗago kai a yayin da shi kuma nasa fuskar na fuskantar Ammy yana gaida ta da warhaka..

Kare mai kallo fifi ta tsaya yi tans kallon suturar jikin sa,ba wasu casual or native bane kawai khaki top ne sai wandon jeans deem blue fuskar sa ya ƙare haske sakamakon carving sajen sa da yayi compare to jiya da bai yi ba..

"Baby pls serve us muna jin yunwa"!ta tsinkari muryar Ammy na mgn sai ta juya ta kalli Ammyn sannan ta tashi ta fara daga plate ɗin Hajja ta gama ta dawo na Ammy daga nan ta juya ta kalli na Saheeb dake fuskantar su kamar jiya.

Rasa courage ɗin tmbyr sa ta yi sai ta ɗan tsaya sai kuma ta matsa daga inda ta ke ta miƙa hannu tana zuba mai chips ɗin,da ta gama ta ɗau bowl ɗin plantain chips nan ma ta miƙa hannu ta zuba mai,next scrambled egg ne ta fara zuba mai a hankali tana gab da gamawa sai bowl ɗin ya suɓce daga hannun ta ya faɗi bisa table ɗin wasu suka zuba wasu suka rage..

A hanzarce ya riga kowa fara tmbyr ta

"Are u alright"?ɗago ido tayi suka sarƙe cikin na juna sai kuma tayi ƙasa da kan ta tana gyaɗa mai kai,ajiyar zuciya ya sauke yana faɗin

"Be careful next time,glass ne it might hurt u"!!shiru wurin yayi Ammy da Hajja na kallon juna ƙasa ƙasa suna murmushi sai da suka ga kamar fifi zata juyo sannan Hajja ta riga Ammy mgn

"Takwara ta me ya same ki?ina hankalin ki yake"?shiru dai tayi ta zauna a mazaunin ta sai Ammy ta tambaye ta ko me take tunani bowl ya faɗi da fatar dai bai ji mata ciwo ba ta faɗa tana riƙo hannun nata dan ganin ko ta yanke..

"Ammy ba komai am ok"?kallom ta Ammy tayi ta ce

"Are u sure"?gyaɗa mata kai tayi sai ta karɓe spoon ɗin da fifi ta riƙe da niyar serving kan ta abinci ita ta zuba mata tana ce mata

"Baby bismillah"kallon Ammy tayi sai ta gyaɗa kai..

Ikon Allah kamar wata kurma,Hajja ta faɗawa kan ta a zuciyar ta sai dai bata ce komai ba ta yi shiru abin ta..

Duk wannan abin Marshall na kallon su yana mamakin inda hankalin fifi ya tafi har bowl ya kusa yanke ta a hannu dan ma dai bowl ɗin mai kauri ne..

Ƙala bai ce da su ba da ya gama kallon su ya maida hankali ga abincin gaban sa ya san wannan mahaifiyar sa ta yi sa ba yarinyar da ta ce ita tayi na jiya ba..

Kowa na cin abincin sa cikin kwamciyar hankali banda fifi da tsananin tsarguwa ya gama addabar ta kamar wacce tayi wani illegal act..

Sarai ya fuskanci halin da take ciki na rashin sakewar ta amma abin mamaki sai ya ɗaure fuska ya ƙi tashi ya ƙi yin hira da su Ammy ko dannita ta sami chance na cin abincin..

Sai da ta ga bai da niyar tashi a wurin kuma ba zai yi mgn da kowa ba bare ta sami damar cin abincin sai ta yi shahada ta sunkuyar da kan ta ƙasa tana cin abincin a hankali..

Ko sau ɗaya bata ɗago kan ba bare ya takura ta ta kasa samin natsuwar cin abincin..

Sai da ya ga ta ɗan sake tana cin abincin sannan ya matsar da nasa plate ɗin yana goge baki haɗe da faɗin

"Ammy zamu fita ni da Khalid zamu duba site ɗin nan na ga kamar basu saurin aikin ne"sai Ammy tayi murmushin manya tana faɗin

"Allah ya kiyaye min ku kai da shi ya sa ku je lafiya ku dawo lafiya,ka kula kar ka bari Khalid yayi tuƙin ganganci da kai dan ya saba ka ji"!?gyaɗa mata kai yayi yana tuno ranar da suka fita shi da Khalid ɗin irin tuƙin da ya rinƙa yi da shi...

Har ya juya zai tafi Hajja ta saka baki tana faɗin

"Ga takwara ta kawai ku tafi tare da ita ka rabu da Khalid itama tana buƙatar buɗe ido rabon ta da fita ya jima"!!bai juyo ba bare ya amsa shawarar Hajja,ita kuma fifi gaban ta ne ya faɗi ai da ta fita da shi gwara ta zauna a gidan,he is a matured man ba wani daɗin da zata ji ko ta fita da shi,ba sanin shi tayi ba kuma from all indications kamar moon face shi ya fi fitting nasa sama da murmushi toh ita ta yaya zata ji daɗin fita da shi?.tsintar kan ta tayi da faɗawa Hajja

"Ina da online review class by 10:30 da safen nan"!already 10:20am ne ssi ya dubi agogon sa ya ga lkc kawai girgiza kai yayi ya fice abin sa shi dama bai ɗau shawarar Hajjan da muhimmanci ba...

Kallon ta Ammy da Hajja suka yi,za su yi mgn ta tashi ta nufi hanyar sama,suka bi ta da kallo har ta shige,murmushin manya kawai suka yi suka ƙada kai musamman Hajja dake ankare da duk motsin su...

Juye juye kawai take ta yi a kan gadon tana jin yadda bugun zuciyar ta ke ƙaruwa sai dai bata san dalili ba..

Muryar Ammy ne ya saka ta tashi zaune ta dube ta,daga tsaye Ammy ta ce mata

"Baby mijin ki fita zai yi zuwa duba wani uncompleted building ɗin Abban su kuma ina tunanin sai dare zasu dawo dan ya matsu a kammala wurin kasancewar yanayin aikin sa ba sosai yake zama a nan ba kuma shi Khalid bai da wani isasshen lkcn zagawa zuwa wurin sai dai in shi mijin naki ya dawo sai ya tafi da kan sa,dan haks ina ga ki je ku gana kafin ya fita ba dawowa da wuri zai yi ba sai dare"!!abin mamaki abin dariya me ya sa Ammy ta sauya mata ne haka da yawa?kalmar "mijin ki mijin ki" duk ya addabe ta ta gaji da jin sa daga bakin Ammy sannan Ammyn ta daina bata kula ta musamman kamar yadda ta saba a baya yanzu sai dai sama sama in ta ɗan ɓata fuska sai ta rarrashe ta hakan bai hana anjima ta kuma janye jiki da ita ba...

Bata saba da yi ma Ammy musu ba sai kawai ta tashi ta nufi hanyar fita amma ta ji ƙarar abu kamar ana fetsa perf,juyawa tayi sai ta ga Ammy gab da ita tana fetsa mata turare tana murmushi,rasa ta cewa tayi sai itama ta maida mata murmushin daga haka ta fita abin ta...

A natse take takun ta har ta iso part ɗin nasa tayi sallama ta shiga,bata tsaya a waje ba ta ƙarasa ciki ta kuwa yi sa'ar samin sa a parlor yana zaune yana sipping wani abu a matsakaicin cup sai ta mai sallama ya amsa yana kallon ta..

Ganin yadda ya tsare ta da kallo sai ta gaida shi,abin sai ya ɗan bashi dariya but bai bayyana dariyar ba ya gyaɗa mata kai alamar ya ji kuma ya amsa..

Tana tsaye bata iya ce mai komai ba shi kuma bai yi offering nata kujerar zama ba,for a moment sai ya dube ta a fizge ya kawar da kai ya ce

"Lafiya"?sai ta dube sa cikin sanyin murya ta ce

"Eh"!!kallon ta yayi sai ya ƙyale ta tana tsayen shi kuma yana sipping abin kofin sai da ta gaji kuma ta zauna abin nata kamar har da yarinta a ciki ya faɗa a zuciyar sa,if not ta yaya mutum zai zo ya tsaya maka a tsaye ya ce ba komai ya kawo sa ba amma yana nan tsaye sannan yanzu ta zauna bai ce mata ya bata dama ba..

Muryar sa ne cikin sigar gar da gar babu wasa ya ce

"Ke,shekarun ki nawa"?sai tayi mamaki ta ɗago kai ta dube sa ta ga babu wasa a tare da shi kawai ta ce

"20"!!scoffing yayi na mamaki yayi tsammanin ta kai irin 25years ɗin nan ma dan mantawa yayi da lissafin sa yana ta ɗaukar ta to be a 25years old girl..

Ganin abinda yayi sai ta ayyana a zuciyar ta hala ta girma ne da yawa shi ya sa ya bata wannan look ɗin mamakin sai ta ji ina ma 19 ta ce mai dan ya san ba babba ba ce ita ɗin..

Bata san ya aka yi ba sai tsintar kan ta tayi da sha'awar tmbyr sa haka kawai bakin ta ya furta

"Kai fah"?sai ta ga ya kalle ta rai a haɗe yana ajiye kofin hannun sa,sai ta ji tsoro dan yanzu ta tuno abinda bakin ta ya furta..

Tashi zata yi sai ya umarce ta da ta zauna kar ta matsa,haka ta koma ta zauna sai ya kafe ta da ido har ta ji ta tsargu fiye da misali kamar ba zai ce komai ba sai ya ce

"Are u asking for my age"!?ya tmby yana ɗage gira ɗaya sama sai ta ji fargaba ya tsirga ta ta kasa amsa mata,yana kallon ta yana jiran amsar ta amma bata amsa ba sai ya murmusa ya ce

"Am 45"!wani irin firgita fifi tayi tayi saurin tashi tsaye tana rufe bakin ta idanu a waje ta dube sa shi kuma sai ya tsaya yi mata kallon mamaki menene na firgita?..

"What?me ya faru"?saurin girgiza mai kai tayi tana juyawa da zumar fita,ai ko ya taso ya juyo da ita da sauri suka fuskanci juna,hannun ta rufe da bakin ta har yanzu,hannun sa ya saka ya cire nata hannun daga bakin ta ya zama bata kare fuskar da komai ba..

Kallon juna suka tsaya suna yi sai da suka ɗau daƙiƙu sannan ya ce

"Me ya faru"!?cikin separate sentence ta ce

"Ba...ba..b..komai"sai ya kuma kallon ta sannan ya sake ta ta fita cikin sauri shi kuma ya tsaya hannun sa a ƙugun sa yana tunanin me ya sa ta firgita,bai sani ba amma yana mamaki..

Sallamar Khalid ne ya farkar da shi daga tunanin abinda fifi tayi sai ya juya ya ɗau wayar sa ya fito suka wuce..

A motar bai daina nemo dalilin da ya saka fifi yin abinda tayi ba haka Khalid ya rinƙa yi mai mgn amma bai bashi doguwar amsa hankalin sa na kan son samo dalilin reaction ɗin fifi..

Kawai sai hankalin sa yayi hitting nasa akan maybe shekarun sa da ya faɗa mata ne,yana wannan tunanin sai kawai ya hau yin murmushi shi kaɗai tun Khalid bai lura ba har ya fara ganewa ya rinƙa mamakin yayan nasa sai dai bai ce mai komai ba suka cigaba da tafiya..

Har suka kai inda zasu tafi suka yi abinda ya dace suka kamo hanyar dawowa around 6pm tunanin fifi da reaction ɗin ta bai daina bijiro mai ba kuma a duk sa'in da ya tuno ta toh fah dole sai ya murmusa shi dai Khalid yau ya ga ikon Allah..

Yanzu burin Marshall bai wuce su koma gidan lfy ba ya san yadda yayi Ammy ta sako ta zuwa dan ya turke ta a gaba ya tmby ta dalilin yi mai wannan abin ba alhalin ita ta mai tmbyr dan ya lura tana da tsoro sai dai kafiyar zuciya ya sa ba a cika gane tsoron nata ba,shi kuwa yau sai ya tsorata ta dan ya ga abin dariya indeed yarinyar na tattare da abubuwan ban dariya kuma yau yana son ganin iya inda nata kalar tsoron ya tsaya...

#Mamuh*23*

Fifi da tun bayan fitar ta daga sashen Marshall ta ɗan tsaya a gefe ta rinƙa dariya kamar wata sabuwar kamu,haka har ta ƙarasa sashen Ammy bata daina dariyar ba sai da Ammy ta tasa ta gaba da tmby sannan cikin dariyar da ta jima rabon ta da yi ta hau labartawa Ammy abinda ya faru tsakanin ta da Marshall nan itama Ammyn ta ɗan dara tana kuma kallon fifi da mamaki ta tmby ta dalilin ta na dariyar amsar ta shine

"Ammy he is old kamar yadda ya faɗi but he doesn't look lyk an old man wai fah 45years Ammy ki ji fah,ta yaya zan yarda?ni na san da gangar ya faɗa min shi gani yake kamar shekaru na da na faɗa mai ba gaske bane shi ya sa da na tmby shi ya amsa min haka nan amma ni na san bai kai 45 ba right Ammy"?ta tmby Ammy tana murmushi sai Ammyn ta murmusa itama tana dariyar yarintar fifi a zuciyar ta..

"Ke kuwa baby me ya sa kike tunanin zai maki ƙarya?ai duk abinda Saheeb ya faɗa haka yake baya ƙarya iya gaskiyar sa ne dan haka ki daina ɗaukar zantukar sa

da wasa iya gaskiyar sa kenan"!shiru fifi tayi tana nazarin zantukan Ammy,toh in dai da gaske shekarun sa 45 ne saura 5years ya cike 50years kenan..

Lallai Allah mai halitta wani bai kai 45 ɗin ba ma amma sai ka gan sa kamar ɗan 50 yayin da wani ɗan 50 ɗin sai yayi kamar bai ko taka layin 50 ba..

Tana iya cewa Marshall yana cikin layin waɗannan mutanin da ke da shekaru amma shekarun nasu bai nunawa ko kaɗan,but me ya sa hakan ta kasance a nasa case ɗin?shiru tayi tana tunanin rashin dacewar dariyar da ta rinƙa mai ɗazu..

Kalkon ta Ammy tayi tayi shiru tana jiran jin ko zata kuma yin wata mgn amma sai ta ga tayi shiru dan haka ta kuma jaddada mata cewar duk abinda Marshall ya faɗa mata ta ɗauka gaskiya ce dan baya ƙarya ko wasa in har akan muhimmin mgn ce,daga nan fifi ta rinƙa wasu tunane tunane kala kala har dai lkc ya rinƙa tafiya tana abubuwa ne amma hankalin ta na ga tunanin Marshall tana ganin kamar bata mai daidai ba kamar ta mai rashin kunya ne a matsayin sa na babba dake gaba da ita..

Haka dai ta ƙarar da ranar cikin tunanin rashin kyautawar ta ga Marshall har yamma tayi wankar yamma ta dawo ta natsu wuri ɗaya tana saƙa abinda zai haɗa su ta ba shi haƙurin abinda ta mai ko da zai ɗaure fuska ne...

Ammy dai ido take ta bin ta da shi tana observing ɗin ta amma bata nuna mata ta san halin da take ciki ba bare ta saka ran zata sami encouraging words daga gare ta..

Yamma lis suka iso gida duk a gajiye amma hakan bai hana Marshall saka Ammy ta aiko mai da abincin sa na dare ba a cewar sa ya gaji baya jin yana iya zuwa nan part ɗin ta sai dai ko gobe...

Tayar da fifi Ammy tayi daga ɗan taƙaitacciyar baccin da ta fara yi yanzu tana kiran ta a hankali,sai ta ɗan buɗe idon ta ta dubi Ammy..

"Tashi ki kaiwa mijin ki abinci yanzu ya dawo kuma a gajiye yake ba zai iya ƙarasowa nan ba ki je ki haɗa mai abincin sa pls yi sauri bai da jimirin yunwa"!!tashi fifi tayi zaune tana duba bed side clock ta ga 8:45pm sai ta sauko daga gadon ta ɗau hijabin ta ta saka sannan ta nufi hanyar kitchen dan haɗa mai abincin..

Dama akwai abincin a food warmers sai ta jere a saman tray sannan ta haɗa mai coffee mai ɗumi ta fito,ta hanyar baya ta fita dan ya fi sauƙi..

Da sallama ta shiga sashen nasa tayi sa'ar ganin sa a parlor yana ƙoƙarin zama..

Da ganin sa ka san yayi wanka ne dan kayan bacci ne a jikin sa sai dai akwai Cardigan a saman rigar baccin nasa sai abin ya ɗan ɗaurewa fifi kai tana tunanin yanayin garin ba wani sanyi ake yi sosai ba bare ya ce sanyin ne ya saka sa saka Cardigan ba,wata sashe na zuciyar ta ya ce mata kin sani ko shi sanyin yake ji tunda tun safe a waje suke ke kuma kina cikin gida?..

Yin wannan tunanin sai kawai ta kawar da abinda ya bijiro mata ta ƙaraso cikin parlorn tana kuma yin sallama..

Amsa mata yayi ba yabo ba fallasa kamar ba shi ba sai ta kalle sa a karkace sai kuma tayi ƙasa da kan ta tana gaida sa..

Amsa mata yayi yana kallon ta yana tuno abinda ta mai da safe sai ta riga sa fara mgn..

"Ammy ce ta ce in kawo maka abinci"!kallon ta yayi na wasu daƙiƙi sai ya buɗi baki ya tambaye ta

"Ke kullum aiko ki ake yi baki zuwa dan kan ki"?sai tayi shiru bata ce komai ba har dai ya ce da ita ta zauna,ba musu ta zauna tana ɗan kame jikin ta..

Janyo abincin yayi gaban sa ya bubbuɗe ya mayar ya rufe sannan ya dube ta ya ce

"Wa yayi girkin nan"?mamakin tmbyr nasa tayi sai dai ta amsa mai da

"Ammy ce"!ga mamakin ta sai ta ji ya kuma tmbyr ta

"Ke fah me kika yi"?a wannan karon kasa cigaba da kallon ƙasa tayi sai da ta ɗago ta kalli fuskar sa tana mamakin sa sai ta ce

"Na taya ta hira a lkcn da take girkin"!!abin dariya but ba damar yi sai ya gimtse ya buɗe food warmer ɗin ya tsaya yana kallon abincin yana kallon ta..

Tun kallon nata baya affecting ɗin ta har ya fara,ta rasa ya zata yi kuma ta rasa me yake nufi da irin wannan kallon sai da ya mata wata tmby sannan ta fahimce sa

" Je ki kirawo min masu girkin nan"!wato su su zo su yi serving ɗin sa kenan lallai al'amarim soldier sai shi..

Tsam ta tashi ta ƙarasa gare sa ta tsuguna ta fara serving ɗin sa tana yi tana tmbyr sa ko yayi,da ƙyar ma take tmbyr dan jin wani iri da ta rinƙa yi bata saba ba..

Shi dai bai amsa mata ba amma yana kallon yawan abincin da take zuba mai yana jiran ta ya ga ko zata tsaya ko cigaba da zubawan zata yi.

Dan kan ta ta tsaya dan ta san duk cin abincin sa wannan zai ishe sa sai ya maida kan sa gare ta daidai tana yunƙurin zama dan ta gaji da tsugunen..

"Na gama"!!ya kuma kafe ta da ido yana ɗage mata gira ɗaya sama wai bai fahimce ta ba sai ta dage ta kuma ce mai

"Na gama zuba abincin yayi"?sai a sannan ya dubi abincin ya dube ta ya ɗau spoon ya fara ci ba tare da ya tanka ta ba..

Ajiyar zuciya ta sauke tana jiran ya ɗan ƙara yin nisa da cin abincin sai ta sako mai mgnr dake ran ta,amma tana shakkar sa tana ganin ya wani yi mata ƙwarjinin da ba zata iya tunkarar sa kai tsaye ba amma da zama da abin a ran ta gwara ta ba shi haƙuri.

Kawai sai ta daure ta fiddo mgnr kai tsaye bayan doguwar wasi wasin da zuciyar ta ya gama yi..

"Ka yi haƙuri da childishness ɗi na da na maka da safe"!!kasa cigaba da cin abincin yayi ya tsaya yana kallon ta sai ya ce

"Ban gane ba"!oh ya salam yanzu waye zai ce bai fahimci wannan hausar nata ba? tmbyr da fifi ta yiwa kan ta kenan sai ta kuma yi mai fashin baƙi..

"Na tmby ka kuma bayan ka amsa min sai na saka dariya ka yi haƙuri Ammy ta ce min gaskiya ka faɗa min"!a wannan karon sai da ta ba Marshall dariya amma yayi murmushi mai sauti ita kan ta sai da ta ji mamakin murmushin sa dan bata taɓa gani ba tunda ta ssn shi fa ya dawo..

"Dama kin yi zaton wasa nake maki?na maki kama da mai wasa a mgn?me ya sa ke komai Ammy ce ke maki?wato ni na faɗa maki amsar tmbyr ki amma Ammy ce ta tabbatar maki da gaskiyar amsa ta unbelievable"!ya ƙarasa mgnr yana cigaba da cin abincin sa..

Shiru ta mai tana sauraron sa ganin bai wani ɗaga mata murya ba sannan in ta natsu tayi tunani kamar akwai alamar rashin lfy tattare da shi dan muryar sa ya nuna..

Bata kuma faɗin komai ba kamar yadda shima bai ce komai ɗin ba,zaman kurame suka yi a wurin har ya ƙoshi ya matsar da abincin ta zo ta hau tattarawa dan a takure take so take ta koma inda ta fi sabawa da shi wato sashen Ammy..

"Sai da safe" ta ce mai tana mai tashi da sauri bayan ta ajiye mai coffee ɗin sa,shi bai ce mata komai ba haka ta fita abin ta yana mamakin kasa tsorata ta da yayi niyar yi..

Yana nan zaune kamar mintuna biyar da fitar ta sai ya kuma jin sallamar ta abin ya ɗaure mai kai,izinin shigowa ya mata sai ta shigo hannun ta riƙe da tray tana ɗan haki..

Kallon ta kawai ysyi sai ta fara mgn on her own

"Su Ammy sun rufe sashen su ina ta sallama ba a amsa ba na yi ta buga ƙofar mai entrance ba a amsa ba,kuma dare bai yi ba fah,pls ka kirawo min Ammy da wayar ka ta sa a zo a buɗe min ban fito da waya ta ba"!!mamakin courage ɗin ta yayi sai ya tsaya kamar ba zai yi wani abu ba daga bisani ya ɗau waya yayi kiran Ammy amma bata ɗaga ba,yayi yayi har ya gaji bata ɗaga ba,sanar da ita yayi Ammy ta kwanta sai ta roƙi alfarmar ya kira mata Hajja nan ma yayi ta kiran ba a ɗaga ba..

Hamma yayi ya dube ta yana observing trembling da jikin ta ke yi kamar marar gaskiya sai ya ce mata

"Duk sun kwanta sai dai in zaki kuma komawa ki duba"!!da sauri ta kalle shi tana tsoron kuma fita it's alread past 9 ta yaya zata kuma fita ita kaɗai bai raka ta ba kuma bai da niyar raka ta.

"Ok?sai da safe"!!ya faɗa mata yana mai yin hanyar bedroom ɗin sa da sauri ta sauke tray ɗin abincin ta biyo bayan sa tana mai magiyar ya tausaya mata ya raka ta su koma..

Kamar ba zai juya ba sai kuma ya juya haka suka fito tare bayan ta ɗauki tray ɗin suka koma sashen su Ammy aka yi ta bugawa amma ba a buɗe ba,wani fargaba ne ya shigi fifi ya zata yi in su Ammy da gaske sun rufe ƙofar?ta kwana a ina?sai tayi saurin tmbyr sa

"Da gaske su Ammy sun rufe ƙofa ne"?kallon ta yayi yana tunanin anya shagwaɓa bata yi mata yawa ba kuwa tana ganin yadda yake ta ƙoƙarin ganin an buɗe ƙofar amma tana tmbyr sa wai da gaske an rufe ne.

Fasa cigaba da bugun yayi dan ko ina shitu ne daga shi sai ita a waje hakan ya sa ya juya yana faɗin

"Ina jin bacci ki zo mu tafi"!da mamaki ta ce

"Mu je ina"?kallon ta yayi ya amsa mata kai tsaye

"Sashe na in kuma kina iya cigaba da tsayuwar jiran buɗe ƙofar toh shikenan am out of here"!!ganin fah da gaske tafiyar sa yake yi kuma ko ƙarar tsuntsu babu shi a wurin sai ta ajiye tray ɗin a nan ƙasa ta biyo sa da gudu..

Hango shadow ɗin ta a bayan shi sai ya saka shi yin taƙaitacciyar murmushi ya girgiza kan sa ya cigaba da tafiyar sa..

Saurin cin mai a tafiyar ta yi sai suka zama suna tafiyar a tare amma babu mai ce ma wani komai..

Daidai sun zo apartment ɗim su Hamida kenan zasu wuce ita kuma ta leƙo dan shan iska because kasa baccin tayi abubuwa da yawa a zuciyar ta na damin ta,tana saka kai a balcony ɗin ta sai ta hango su suna zuwa,wani ras gaban ta ya bayar sai ta kuma fitowa tana kallon su har suka shige suka rufe ƙofar..

Ba ƙaramin ɓaci ran ta yayi ba wato da gangar su Ammy suka haɗa auren nan dan a ci mata fuska ko?in ba haka ba ita nata mijin yana nan yana bacci su kuma suna yawon su a tsakar gida.

Buge ƙarfen tayi da ƙarfi ta ma rasa me ke damin ta a yanzu kan ta kasa kawo mata komai yayi..

Tsaki ta ja ta koma ciki tana kallon mijin nata dake baccin sa cikin kwanciyar hankali..

Ya ta iya dole ta kwanta beside him tana mai ɗora kan ta a ƙirjin sa itama baccin ya fara fizgar ta tana son mijin ta amma a zahirin gaskiya kishin yar uwar ta ya gama rufe mata ido da bata ganin komai sama da fuskar fifi da mijin ta in a negative way.

Ko da suka shiga daga ciki duk tsoro ya gama dabaibaye fifi sai ya shiga ciki ya kawo mata blanket da pillow,bai tsaya jin komai daga gare ta ba yayi wucewar sa dan a gajiye yake bacci ke damin sa.

Haka ta kwanta bisa kujerar ta lulluɓe jiki tun tana shakka shakkar yin baccin har dai baccin ya sace ta ta bar kan ta tayi sa dan dama tana ji tsoro ke damin ta amma tunda ya tafi ta san ai ba zai fito ba..

Da wannan tunanin baccin ya ɗauke ta bayan tayi addu'ar yin bacci ta lulluɓe daga sama har ƙasa dan gudun wani abin ƙi...

#Mamuh*24*

Cikin baccin ta ta rinƙa jin numfarfashin mutum a halin wahala da azaba,kamar a mafarki sai ta juya da nufin cigaba da baccin ta amma jin numfarfashin ya ƙi ƙarewa sai kawai ta miƙe da sauri tana mai yaye blanket ɗin..

Tashi tsaye ta yi ta fara bin kusurwa kusurwar parlorn tana bin inda numfashin ke fitowa,haka ta zaga kaf dama da hagu bata ji komai ba ga parlorn ba laifi yana da ɗan girma.

Dawowa da baya tayi zuwa bayan ta ta natsu nan ta fara jin asalin numfashin..

Da hanzari ta yaye curtain ɗin wurin sai ta ga door ne da sauri ta tura ta shiga tana ɗan kalle kalle Daga can cikin lulluɓe ta hango kan sa gabaɗaya karkarwa yake yi tsabar zazzaɓin da ya addabe sa..

Bazata iya ta tancewa ba amma haka kawau ta gan ta kusa da shi cikin halin damuwa da sanyin murya ta rinƙa tmbyr sa lafiya me ke damin sa..

Nishi yake saukarwa baice uffan ba

Sam baya jin ta ko kaɗan haka ta gaji ta rasa abin yi ga ɓarin jikin nasa bai daina ba sai ma lura da tayi da kamar convulsion ke son zuwar mai..

Ganin haka ya sa cikin sauri ta sauke hannun ta daga kan blanket ɗin da ya lulluɓe jikin sa ta nufi hanyar waje a ruɗe dan tsakanin ta da Allah bata san me zata mai ba kan ta kasa kawo mata komai yayi..

A firgice ta bar sashen tana tfy tana sauri kamar zata tashi sama da hanzarin ta ta ƙarasa sashen su Ammy.

Bugun duniyar nan ta yi amma babu amsa haka har ta gama bugunta gaji bata da yadda zata yi amma abin takaici babu wanda ya motsa bare a zo a buɗe mata ta shiga ta sanar da su abinda ke faruwa da Marshall..

Da ta gaji da bugun sai ta ji wani ɓacin rai ya ziyarce ta a zuciye ta bar wurin tana tafe idanun ta na kawo ruwa tana ayyana cewa yanzu da mutuwa ce ta zo haka nan za a bar ta ta mutu kenan..

Sosai hankalin ta ya tashi,bacin su ammy duk suna sane kuma sunji bugun amma dan su cusa mata dawainiyar aurenta yasa suka ki amsa ta..

Tana dawowa sashen Marshall bata tsaya ko ina ba sai cikin bedroom ɗin sa da yake kwance,yanzu ma ɓari ya ninka na ɗazu da ta fita ta bar sa yana yi..

Wani abu ne ya faɗo mata a rai sai ta tashi kai tsaye ta nufi hanyar parlor,da kan ta ta binciko inda kitchen yake ta samo shi tayi tafiyar ta ciki Gas ce mai kai takwas sai ta nemo portable pot wanda yake sabo fil cikin kwala alamar kayan nata ne da Ammy ta siyo mata..

Wanke pot ɗin ta yi ta zuba ruwa ɗan daidai misali ta ɗora bisa gas ɗin ta zauna zaman jiran yayi zafi dan ta san ruwan in ta saka a electric kettle ba zai yi sauri ba ita kuma yanzu a uzurce take..

Tagumi tayi Tana jiran ruwan yayi zafi tana kuma nazarin kalaman Marshall ɗin na ɗazu da yake mata gorin babu abin da ta sani ta yi dan kan ta sai wanda Ammy ta ce ta yi..Abin na ta taɓa mata zuciya sai kawai hawaye ya zubo mata ta saka hannu ta goge,lallai kalaman sa sun farkar da ita daga bacci da take yi na komai bata iyayi dan kan ta sai wanda aka saka ta yi ko bari..

Aranta tace Ga tabbaci nan an kuntata ma yar uwantan akanta bata gane ba gashi a gaban ta mutum na rawar sanyi amma ta kasa aiwatar da komai ta fita nemar taimakon wasu

tuno kalaman sa ya sa ta ƙarfafawa kan ta dajin dan dolen ta wasu lokutan kai da kan ka zaka rinƙa aiwatar da abubuwa ba sai an saka ka ba..

Lallai a rayuwa kana buƙatar aboki na gari wanda zai rinƙa ɗora ka ko ya nuna maka asalin gaskiyar rayuwar ka,rashin mutumin da zai rinƙa tantance maka zaƙi da ɗacin rayuwar ka asara ce babba kuma tangarɗa ne a gare ka na mutum mai hankali da nazari...

Ƙarar zubar ruwa ta ji sai tayi firgigit ta dawo daga tunanin da ta faɗa,kai duban ta tayi ga ruwan da yake tafarfasa tayi saurin kashe gas ɗin..

Da yake hankalin ta ya rarrabu kashi daban daban kawai sai ta kai hannu directly ta riƙo handle na pot ɗin da niyar juye ruwar Ai kuwa tana taɓawa ta ji wani irin zafi ya ratsa ta har kan ta da sauri ta cire hannun ta tana yarfewa,sai a sannan ta dawo hayyacin ta bayan wasu seconds ta nemo pot holder mai laushi ta riƙe hannun pot ɗin ta fara juye ruwan a wani ƙaramin cup ɗan daidai sannan ta juye sauran a wani bowl din cikin nitsuwa..

Mayar da pot ɗin ta yi saman gas plat ɗin ta juya ta fara nemo kayan tea wayanda bata gani ba,ta dai san ba yadda za'a ce bai da su amma rashin sanin inda zata gan su ya sa ta hau dube dube..

Da ta gaji sai tayi saurin ɗagowa da niyar fita zuwa sashen Ammy wai ta tmby ta ta bata kayan tea..

Tunowa da tayi da abinda Ammy ta mata na ƙin kula ta sai ta dawo da baya kuma ta riga ta yi ma kanta alƙawarin yau babu ruwan ta da wani duk abinda ta ga ya dace shi zata rinƙa yi tunda ba ƙaramar yarinya bace ita a hakan aka mata aure kuma kula da Marshall dake a matsayin miji ya zama nata

Haka nan ta ɗauko cup da bowl ɗin ta fito ta nufi cikin ɗakin ta same sa gwanin tausayi rawar sanyin bai daina ba lallai ba ƙaramin zazzaɓi ke damin sa ba in har tun ɗazu yake ta jin zazzaɓin amma ya daure ya raka ta sashen su Ammy suka rinƙa buga ƙofa tabbas ya kokarta..

Tana ajiye ruwan zafin ta dawo kan gadon tana kallon sa cikin tausayawa ta saka hannu a hankali ta ɗan yi ƙasa da blanket ɗin tana ce mai

"Tashi ka sha warm water it will help u"!!

kasa tashin yayi sai da ta taimaka masa ya tashi da ƙyar,ya jingina da gadon yana rawar sanyin da sauri ta ɗauko cup ɗin ta kawo kusa da bakin shi tana mai sannu tana saka mai ruwan..

Sipping kaɗan yayi ya ɗago kai sai tayi saurin mayar mai da kofin bakin sa tana girgiza mai kai tabbacin wannan da ya sha bai isa ba..

Haka yayi ta sipping warm water ɗin nan har ya ƙare,sai ta ajiye cup ɗin tana hango zufar dake ɗan keto mai.

Tmbyr sa tayi inda bathroom yake ya nuna mata da hannu ta tashi ta shiga,bata da natsuwar ta dan haka bata tsaya kallon toilet ɗin ba ta nemi towel kawai..

Wasu jerin towels ta hango kusan biyar a hangers sai ta kai hannu ta ɗau ƙaramin ciki da mai bi mai ta fito da ɗan saurin ta..

Hijabin jikin ta na damin ta sai tayi tunanin cire sa tunda aiki sosai zata yi yanzu.. .

Ba tare da wani tunani ba ta cire ta ajiye a gefe sannan ta dawo gare sa tana mai ɗaukar zuwan dake bowl ɗin ta zauna bisa gadon gefen sa ta tsoma towel ɗin cikin ruwan ta matse ta ɗora mai a saman goshin sa..

Take yayi responding dan sai da ya nuna sabida ƙame jikin sa yayi,hakan ya bata damar cigaba da maimaitawa ɗin har ruwan ya salamce sannan ta sauke ta ajiye a ƙasa ta dawo gare sa tana kallon sa yana bata tausayin da bata san na menene ba...

"Ina kayan tea ɗin ka in haɗa maka ka sha tunda dare yayi babu abinci a nan"!!

kallon ta yayi da idanun sa dake nuna zazzaɓin sa sai ya kasa ce mata komai illa ɗan kwantar da kan sa da yayi yana kallon ta..

Ganin kamar bacci yake ji sai ta ƙyale sa dan ɓarin jikin ya tsaya sai zufar da yake ɗan yi..

Can cikin damuwa tace"Ka kwanta kar wuyar ka yayi ciwo ba pillow kuma position ɗin nan bai yi ba"bai ce komai ba still tazo ta tallafo sa da taimakon ta ya kwanta tayi supporting nasa kan da two pillows on both sides ɗin sa..

Bata tashi daga kan gadon nan ba sai da ta ga ya fara bacci sannan ta tashi ta zauna bisa side drawer ɗin gadon cikin rasa me zatayi tunani akai..

A yanzu ne take ƙare ma ɗakinsa kallo take yaba kyawun sa da tsarin sa kuma sai a yanzu ta gane bata da hijabi ajikinta sannan hankalin ta ya kai ga hala ganin bata da hijabin ne ya sa yake ta kallon ta dazu..

Saurin ɗauko hijabin ta yi ta maida tana mai komawa inda take zaune lokaci zuwa lokaci takan kalle sa har ta leƙe sa ta ji tausayin sa ya kuma kama ta..

Tana ta wannan abin ne bacci ya ɗauke ta ta jingina tana yi haɗe da ƙanƙame jikin ta sosai kamar mareniya.

*****

Asubahin farko Khalid ya farka daga bacci sai ya ga Hamida kwance jikin sa tana bacci but daga ganin ta ya san baccin ɓacin rai take yi,daga lokacin da suka yi aure zuwa yanzu da suka shafe watanni sama da huɗu tare ya gama karantar matar nasa,ya san komai da ya shafi halayyar ta ko da kallo ta mai ya san fassarar kallon nata haka a gefe ɗaya in aka dawo ga rayuwar ta da mu'ammalar ta da yʼar uwar ta,babu abinda bai sani ba,irin tsatssaurar kishin yʼar uwar ta da ta sakawa zuciyar

ta ba ƙaramin damin sa yake yi ba,babu wani abu sabo ba dangane da Hamida da bai sani ba akan alaƙar ta da fifi..

Ajiyar zuciya ya sauke tuno da yadda yake son fara aiwatar da nufin sa ga matar nasa dan ya wanke mata zuciyar ta akan halayyar da ta ɗorawa kan ta na kishin yar uwar tawainiyar ta..

Kissing forehead ɗin ta yayi yana shafa fuskar ta sai ta buɗe ido a hankali tana kallon sa..

Bata ce komai ba haka bata motsa ba sai shi ne ya soma tada mgnr..

Yace "Goodmorning wify hw was ur night"?kallon sa tayi tana murmushi sannan ta amsa gaisuwar nasa sai ya kuma rungume ta yana kallon ta kamar zai hadiyeta har sanda ta ce mai

"Wat"?murmushi yayi yana kallon ƙwayar idanun ta daga bisani ya amsa mata da cewa

"I just naturally luv my wife kuma ina son tasan zan iyayin komai akanta and i promise to protect her to my last breath,hamida kiban dama,inshaAllah zan cike miku wani gurbin da ba kowa zai iya ba i wll replace back ur lost love for many years,wannan alkwari ne from me to u"!!

wani sanyi hamida ta ji a ran ta da saukar waɗannan kalamai nasa sai ta kuma rungume sa tana faɗaɗa fara'ar ta bata dai ce komai ba amma ya san kalaman nasa ya ratsa ta sai ya cigaba..

"Na san kin rasa soyayyar iyayen mu daddy,Ammy,Hajja and...ur sister's care but ina so ki sani ni mijin ki Khalid na maki alƙawarin cike maki gurbin waɗannan so ƙauna da kulawar gata da duk wani abu da kika rasa da zuciya ɗaya,dan a kan ki na yarda in zama wawa in hakan zai faranta miki,i love u hamida..ina so ki yarda da ni ki bar min amanar yardar ki ni kuma zan baki mamaki da irin sigar ƙauna da soyayyar da zan nuna kuma in gwada miki"!!

sassanyar ajiyar zuciya ta sauke tana jin sabon son mijin ta fiye da kowa haka nan wani bangaren tana jin tsananin kishin Mufida mai zafi a ran ta dan idanun ta rufewa yake da kishin yʻar uwar tan da ya riga ya mata mugun shiga..

Kamar zata sauke hawaye tace""kamun alkawrin zaka kasance dani khalid bazaka ci amana ta ba !gyaɗa mata kai yayi yana mats murmushi mai ƙayatarwa haɗe da kai mata direct french kiss as good morning kiss..

Hakan ya tabbatar mata da cewa mijin nata a shirye yake, ever ready to protect and cherish her..

Sai da aka kira sallah sannan suka tashi shi da ita,tare suka yi alwalar suka fito shi ya sauya kayan sa zuwa jallabiya ya fita zuwa masallaci ita kuma tayi nata sallar a ɗaki...

Ko kafin ya dawo har ta yi yan kimtse kimtsen ta ɗin ta ta masu breakfast tayi wanka ta fito cikin ƙananan kaya da maroon kimono kan ta ta yafawa ƙaramin mayafi ta ɗan yi kwalliya ta hakimce saman dinning ɗin su tana latsa wayar ta..

Bai shigo ba sai misalin 8:30am sakamakon zama sashen Ammy da yayi suka gaisa ya kuma kai ziyara wa Hajja wacce ita ta ja sa da hira har ya daɗe..

Da shigar sa ta tare sa abin sai ya burge sa kenan kalaman sa gare ta na safiyar yau yayi tasiri a zuciyar ta lallai da haka zai rinƙa sanyaya mata zuciya har yayi nasarar yaƙice mata kishin yʻar uwar ta a zuciyar ta ya gyara alaƙar su..

Brush kaɗai ta bar sa yayi sai wanka sannan suka dawo suka fara cin abincin nasu cikin so da ƙaunar juna,yana iya faɗin rabon sa da fuskantar hakan daga gare ta wanda ba komai ya sa ta rikiɗe masa ba sai kishin fifi da ta sakawa ran ta..

Da suka kammala shi ya kwashe kayan tunda yana hutu baya on call sai ya shashance akan matar sa through out yau babu inda ya tafi yana tare da ita soyayya yake gwada mata na fitar hankali so yake ta gama yarda da shi har zuciyar ta dan hakan zai taimaka ta cire batun fifi daga ran ta dan suyi rayuwar su..

Yau Komai tare suka yi sa abin gwanin sha'awa,duk da wannan abin da Khalid ya rinƙa yiwa Hamida bai hana ta ware seconds 30 ƙwarara ba wurin son ganin baƙin Mufidah da kasawar ta,haka kawai ta rinƙa tursasa zuciyar ta da kan ta kan sai ta samo wani abu da Mufida ke lacking da zata rinƙa alaƙanta ta da shi,sai dai bata samu dama sosai dan da zarar zata fara tunanin abin sai mijin ta ya ɗau hankalin ta..

Ko da dare yayi bai bar ta tayi zaman tunanin ba ya rinƙa gaya mata sunayen wuraren da yake son su tafi a washegari sannan yana hiran yana showering nata da kisses da tickling dake saka ta dariya,da haka har tayi bacci a jikin sa shima yayi baccin cikin farincikin ganin first move ɗin sa an samu nasara.

****

A ɓangaren su fifi da Marshall kuwa da safe yayi kamar an tsungule sa ya farka ya buɗe idon sa sai ya ga haske daga curtains,juyowa yayi sai ya ga sleeping fifi,ƙura mata ido yayi yana ta kallon ta yana tunanin abinda ya faru a daren jiya,mamaki ya rinƙa yi yana ayyanawa hala Ammy ce ta saka ta yin aikin..

Ɗan taɓe baki yayi ya yunƙura ya tashi zaune yana hamma,ya ɗan sami ƙarfi kaɗan dan dole sai ya haɗa da pills but normal emergency care da ta bashi jiya ma ya taimaka masa.

Zaman kallon ta yayi yana ƙarawa sai da ta motsa a hankali sai yayi saurin kawar da kan sa yana tari..

Tarin nasa ne ya ƙarasa farkar da ita ta tashi tana kallon sa a firgice tana tmbyr me ya same sa sai ya nuna mata hanyar window..

Nan ta kai duban ta sai ta ga haske da sauri baki buɗe ta sauko daga kan drawer ɗin tana mai zuwa kusa da shi..

"Bamu yi sallah ba safe yayi"!!kallon ta yayi sai ta kawo hannu tana son taimaka masa ya tashi ba musu ya karɓi taimakon nata,suka shiga toilet da ƙyar yayi alwalar suka fito ta nemo darduma bayan ta tmby sa inda yake ya nuna mata. ...

Ta shimfiɗa mai ta miƙo mai jallabiya ita kuma ta koma ciki tayi alwalar da sauri ta fito lkcn har ya fara sallah sai ta tada nata iƙamar a ɗan nesa da shi..

Da suka idar sai tsaya jiran sa har ya shafa addu'ar sa,kawai ta ji ya kamata ta gaida sa sai ta yi ƙasa da kai..

"Ina kwana"!mamakin ta duk ya gama cika sa amma ya amsa mata sai ta kuma faɗin.

"Ya jikin naka"!gyaɗa kai yayi yana faɗin

"Alhamdulillah"fatar samin lfy ta mai tayi shiru sai can shi ya ce

"How was ur night"?kallon shi tayi ta saukar da kan ta ƙasa sai yayi murmushi dan ya fi kowa sanin ya night ɗin nasa ya kasance..

Da taimakon ta ya koma ya kwanta ita kuma ta ce mai tana zuwa..

Fitar ta bata zarce ko ina ba sai sashen su Ammy..

Ko da ta shiga sai ta gan su zaune gaida su tayi kawai ta sanar da su Marshall ba lfy daga haka ta haura ta ɗau wayar ta ta fito bayan wasu minutes har ta sauya kayan jikin ta zuwa simple gown mai ɗan kauri sbd yanayin sanyi na garin..

Mamakin ta suka ji ganin bata yi shagwaɓa ko ta tsaya tmbyr su dalilin ƙin buɗe mata ƙofa ba jiya wanda intentionally suka yi hakan duk wai dan ƙaunar ta da Marshall ya girmama..

Dawowa sashen Marshall tayi ta same sa kwance sai ta buƙaci ya bata numbern family doctor ɗin su tana so ta kira sa ya zo ya duba sa..

Miƙo mata wayar yayi bayan ya fiddo da numbern sai ta kwasa a wayar ta tayi dialing,bayan an ɗaga ne suka gaisa ta mai bayanin abinda ke damin Marshall but kasa kiran sunan sa tayi sai cewa take "yaya soldier wai dan doctorn ya gane da wanda take referring..

Shi dariya ta bashi har ta sauke wayar ta miƙo mai yana kallon ta sannan daga bisani ya ce da ita

"Ammy told u to do this right"!?shiru ta mai tana kallon sa,sai ya girgiza kai yayi shirun shi ma..

Ba jimawa Ammy da Hajja suka zo duba sa sai a nan yake jin wai rashin lafiyar nasa yanzu suke ji daga bakin fifi abin ya bashi mamaki wato ita ce dan kan ta ta ji tayi hakan kenan?lallai ashe tana da tunani mai zurfi ba yadda yayi tsammanin ta ba..

Suna zazzaune doctor ya zo ya duba sa ya mai abinda ya dace Ammy ta koma ta kawo masu abinci dan ta lura kamar fushi fifi ke yi da su ganin yadda duk ta maida hankalin ta ga mijin ta sai suka yi ta mamaki haka shima Marshall ɗin sai da suka jima sannan suka tafi ita kuma ta maida hankalin ta gare sa ta bashi magani yana karɓa yana tunanin ɗabi'un ta..

Ita kam ko a jikin ta kula da shi ta saka a gaba a matsayin abunda ya dace ba tunanin abinda Ammy take mata ba..

Ranar dai ta ƙauracewa su Ammy a nan part ɗin ta kwana dan bashi kula ta musamman kamar yadda doctor yayi ta nanatawa wanda tun su Ammy na damuwa har suka daina suka haƙura suka zuba mata ido.

Chan cikin dare tana kwance a parlor kamar jiya sai ta rinƙa tunanin rayuwar ta da na yʻar uwar ta Hamida numfasawa tayi ta juya tana mai cigaba da tunanin ta,rasa yadda aka yi ta kasa fahimtar halin kuci da zafi da Hamida ta shiga ciki tun yarintar su tayi har kawo girman su..

Ji tayi kwata kwata bata kyautawa kan ta ba ita tana ta kwace soyayya Hamida na can cikin damuwa da rashin kulawa wai amma bata taba sani ba,a duk lkcn da ta tuno wannan abin ran ta kan sosu ba kaɗan ba..

Daga wannan ranan Ta ma kan ta alƙawarin safiyar gobe a sashen Hamida zai mata tunani tayi da hala halin da take ciki rashin sauraron ta da Hamida bata yi ne ya sa take fuskantar wannan abin hakan ya sa ta yanke zuwa duba ta gobe ita ko zagin ta Hamidar zata yi ta yi in dai zata furta mata kalmar yafiya toh ita tayi alƙawarin cike mata gurbobin da ta rasa na soyayya a rayuwar ta..

*****

Da safe bayan ta gama abinda zata yiwa Marshall ta ce mai tana zuwa sai bai ce mata komai ba dan sabbin ɗabi'un nata na mai shammaki..

Gaban ta na faɗuwa ta iso part ɗin su Hamida ta tsaya ta rasa ya zata yi sai dai ta ɗan natsu ta yi sallama a hankali,sau uku tana yin sallama sannan aka zo aka buɗe ƙofar wanda fuskar Khalid ne ya bayyana..

Da mamaki ya gaida ta sai itama ta gaida sa tana tmbyr sa ko Hamida na ciki,cikin tausayin ta ya amsa mata da eh..

Hamida dake tsaye bakin kitchen tana rige rigen ɗora breakfast ita da Khalid da kamar competition ne sai kawai ta gan sa tare da fifi..

Take ta ɗaure fuska ta haɗe rai,yana kallon sauyin yanayin ta fifi kuwa da zuwa tayi saurin ƙarasawa gare ta murya na rawa ta buɗe baki zata yi mgn sai Hamida ta kawar da kan ta gefe..

Kallon ta fifi tayi

sai ta haɗiye wani abu mai ɗaci ta kuma yunƙura ta ce

"Ina kwana Hamee"!wani kallon ƙiyayya Hamida ta watso mata ta ja tsaki ta juya zata tafi sai muryar fifi ya mata amo a kunne da ɗan ƙarfi

Tace "Hamida kiyi hakuri ki sassauta min dan Allah am sorry,am deeply sorry ki yafe min,wlhy wlhy ban san ya zan hukunta kai na akan laifin da na maki ba,na kasa samin sukuni a zuciya ta am deeply blaming myself for this mistake and i swear i want to make it up to u am ready to make u happy just listen to me ko da sau ɗaya ne"!!

juyowa Hamida tayi ta kalle ta ranta na ɓaci ba kaɗan ba sai ta watsawa Khalid ɗin kallo shima sannan ta ja doguwar tsaki tayi wucewar ta..

Gwiwar fifi ne yayi sanyi nan da nan hawaye ya kawo mata sai ta dubi Khalid da idanun ta dake cike taf da hawaye ta ce mai

"Am sorry,,i truly am"...!!duk tausayin ta ya ishe sa ya san abin na damin ta sannan ba laifin ta bane laifin iyayen su ne but da alama Hamida ta gaji, wa ke da laifi waye baida shi bata dubawa for all she cares shine tana jin mummunar kishin Mufida kuma kishin nata ya fara rikiɗewa zuwa ƙiyayya...

Fita fifi tayi ta koma sashen Marshall inda a nan ta riƙe ƙirjin ta ta fara zubar da hawaye a hankali ko da Marshall ya fito a bazata dan haɗawa kan sa tea ganin bata dawo da wuri ba sai ya gan ta tana kuka..

Kallon ta yake yi daga bisani ta ji muryar sa a kan ta sai tayi saurin ɗagowa ta dube sa,da sauri ta goge hawayen ta tana tmbyr sa me yake so..

Da kamar ya kuma tmbyr ta me ke damin ta amma sai kawai ya faɗa mata abinda yake buƙata haka ta je ta haɗo mai ta dawo da shi ta bashi.

Yana ankare da ita through out yau bata da walwala duk da dai ba sanin halayyar ta yayi ba amma daga shekaranjiya zuwa yau ya ɗan karance ta..

Da damuwar Hamida Mufida tayi bacci yau kuka kam kamar yau ya fara bijiro mata dan sosai ta yi sa tana yi tana tunano lifetime ɗin su a baya,ta dai san ko dukan ta Hamida zata yi ba zata daina bibiyar ta da nemar yafiyar ta ba har sai ta yafe mata dan ita kaɗai ta san irin halin damuwar da zuciyar ta ke ciki haɗe da nauyin da zuciyar nata ke mata akan rashin kula ta da Hamida ke yi..

#Mamuh*25*

Da safiyar washegari fifi ta kuma maimaita abinda ta yi a safiyar jiya na yau ma Marshall bai da masaniya a kai ta tafi sashen su Hamida,har Khalid ya buɗe mata ƙofa sai ya tuno abinda ya faru a jiya da irin rarrashin da ya rinƙa yi wa Hamida akan ta saurari fifi ko da sau daya ne amma ta rufe idon ta ta nuna mai bata jin zata iya yin hakan duk kuwa da shi kan sa ya san abin na taɓa ta kawai rinjayar ta da kishin yayi ne ya sa take ɗauke kan ta akan abubuwan..

"Ina kwana Khalid"ta gaida sa ya amsa sai ta tmby sa lfyr Hamida nan ya ɗan yi shiru wanda ya bata amsar ta akan ba lfy ba kuma har yanzu fushi Hamida ke yi da ita..

Hawaye ne ya cicciko mata a idanun ta na tausayin kan ta da fushin da yar uwar ta ke yi da ita..

Kallon Khalid tayi sai ta ji zuciyar ta na mata zafi tana buƙatar wani wanda zai fahimci halin da take ciki..

"Khalid ai ka san manufa ta ko?ina so in gyara tsakanin mu da Hamida am deeply sorry for all my mistakes i really want to clear her mind akan alaƙar mu,na roƙe ka ka haɗa ni da ita i hv to talk to her"!!kuka me sanyi ne ya kusa cin ƙarfin ta sai Khalid ya kasa cigaba da kallon ta a haka kawai ya juya wai dan ya je ya ma Hamida mgn ta fito..

Juyawar sa ke da wuya ya hango ta tsaye bayan su tana bin su da kallo sai Khalid ya ƙarasa gare ta da sigar rarrashi..

"Hamida...Pls ki bada yar uwar ki ta gyara abinda ya faru kar fah ki manta ba itace kawai ta maki wannan laifin ba gashi ta ɗau laifin kuma ta yarda zata gyara ita kaɗai toh me zai sa ke kuma ba zaki fahimce ta ba?uhm"?kallonsa Hamida ta yi ta kuma kalli fifi dake tsaye tana hawaye ji tayi kamar tazo ta rungumeta amma tana tsoro..

Duk halin da fifi ke ciki abin na taɓa Hamida a zuciyar ta sai dai ta rasa ya zata yi controlling fushi da kishin ta akan fifi hakan ya rikiɗe ya zama kishin fifi yar uwar ta ya rinjaye ta har bata iya fasalta ƙarfin kishin nata..

Tsawon lokacin nan ace bata san da nemo min farinciki na ba sai yanzu?

In dagaske tana so na kuma ina da muhimmanci arayuwarta meyasa da chan bata iya bambamce bacin rai na da jin dadi na ba?meyasa bata karance zafi da kunan dake yawo acikin fushi na ba a duk sanda aka ware ni aka nuna min ni ba komai bane sai ita,....saida na furta?

Wannan ba kaunar mu bane,kowa kansa yafi so ya tafi kauna,dan haka nima kaunata ni kadaice bazan sake shi ba...

Kawar da tunanin da tayi yanzu ta yi ta dubi fifi dake kuka ta gasa mata kalmar nan da ke ma fifi zafi a zuciya.

"I hate liars and pretenders ki fitar min daga apartment"!

A hankli ta faɗa so calm and gentle ta yadda ta san zai taba fifin emotionally..

Ta kuwa yi nasara dan sosai fifi ta fashe da kuka mai ban tausayi haka ta juya ta fita ita kuma Hamida ta jingina bayanta da staircase har sai da Khalid ya matso ta ya rungume ta yana bata sassayanr runguma,shidai ba wai yana ƙoƙarin tursasa mata zuciya akan sai ta yafewa fifi bane a'a yana gudun kar kishin yayi yawa ya fi haka ne har ya zo ya taɓa martabar gidajen auren su gaba daya..

Gabaɗaya ranar Khalid aikin ban haƙuri da nuna ƙauna ya rinƙa yi wa Hamida tun tana ɗan kawar da kai har dai ta fara sauraron sa suka dawo daidai Yayin da fifi ta kasa samin kwanciyar hnkl tun bayan fitar ta daga sashen su Hamida daurewa tayi ta bincika kitchen ɗin ta ga abubuwan dafawa ta zaɓi wanda ya dace ta girkawa Marshall dan yanayin rashin lfyr sa..

Haka yau ma ya gan ta tana kuka amma ɗabi'ar nan ta bana shiga abinda babu ruwa na,jin kanshi yake kamar ai fifi yarinya ce ita shi kam ya haife ta ya juya ya

dubeta baya jin wani tsaurara mata tambayoyi akan dalilin kukan ta zai ƙara mai mutuncin sa instead sai dai ta raina sa dan zata ga ya damu da ita..

Haka nan itama tayi ranar kaf cikin damuwa da kuka akai akai,abu kamar wasa zazzaɓi ya fara shigar ta a hankali amma ta yi ta dannewa tana kama jikin ta tana ma Marshall ayyukan da ya dace..

Sam bata cika damuwa da auren bata kamar yadda t sa lamarin hamida aranta,tasan sun ma hamida rashin adalci kuma bata ganin laifin kowa sai kanta ayanzu

Ba abu ne mai sauƙi ba a gare ta tun tana ganin zata iya gyara komai ita kaɗai har ta fara fiddo damuwar ta sarari in Marshall ya fita zai dawo ya same ta tana kuka,ba zata jira ya tmby ta ba zata fara tmbyr sa shin bata da hali mai kyau ne,abin na ɗaure masa kai dan shi bai san sanadin kuka da damuwar ta ba kuma baiyi lokacin tambayarta ba..

Kimanin sati biyu kenan masu kyau Mufida ta ɗauka tana ƙoƙarin ɗinke tsakanin ta da Hamida amma a duk lkcn da ta kusanci inda Hamida take sai Hamida ta bata wasu irin halayyar

Munana masu zafi

Hamida ce wacce bata rasa komai daga wurin mijin ta ba dan ba ƙaramin kula da ita yake yi ba

haka fifi take ziriyar sashen ta zuwa na Hamida a kullum a ƙalla sau uku ko huɗu a rana amma zuciyar Hamida ya mata dauri me wuyan kuncewa...

Abubuwa dayawa inta tuna takanji tsanan fifi da duk wani wanda ya lalata mata zuciyan ta ya dawo baki

Rayuwa ba ƙaramin sauyawa fifi ta yi ba ba dan komai ba sai dan damuwar yar uwar ta d ta sakawa zuciyar ta gashi tayi auren da bata san ma'anar sa ba,a haka

ne rashin lafiyar ta ke ta tashi a hankali a hankali amma bata bari a gane ko shi Saheeb ɗin da take kwana tare da shi a apartment ɗaya bai sani ba..

Iyakar sa da ita shine gaisuwar safe abincin sa ruwan wankar sa sai wasu ayyukan sa da ya zama dole akan ta sai dai in tayi zaman kukan ta ya zo ya same ta ta rinƙa tmbyr sa ko tana da aibu ne shi kuma sai ya kalle ta kawai baya amsawa..

A iya zaman su fifi bata ƙara marmarin komawa sashen su Ammy da zama ba sai dai ta je ta gaida su a ɗan yi hira kaɗan da bai wuce mintuna goma zuwa goma sha ba daga haka zata tashi ta koma dan ta sakawa ran ta bata kuma nemar shawarar kowa dan inganta rayuwar ta tunda ta yi hakan a baya bata sami nasara ba..

****

Yau tana zaune a parlor sai ta ji taba sha'awar kwana a ɗaki dan duk wannan zaman nasu a parlor take kwana bata wuce nan ko dai dai da rana ɗaya Marshall bai taɓa yi mata tayin ta zo ta kwanta a bedroom ba ita kuma bata taɓa tmbyr sa ba amma yau ta ƙudiri kwanan ɗakin..

Akwai ranar da yake nuna mata wasu kayan coffee da ya sa aka siyo mai akan in zata rinƙa haɗa mai ta rinƙa amfani da su,a ranar take jin wai matar sa tayi extending dawowar ta zuwa lkcn da ta kammala abubuwan da take son yi..

Haka kawai Ta ɗan ji wani abu a ran ta da ta tuno cewa yana da mata,dan dama ita kam shaf take mantawa,yau da ta tuno sai abun ya mata wani iri,badon tanajin tana son sa ko zata so sa ba,tunani take ita wa zai so ta ya bata kulawan aure da kowacce mace take samu?babu khalid ga hamidarta ma ta juya mata baya.

Wani irin damuwa ne ya shigeta sam bata san dalilin wannan abubuwan dake faruwa da ita ba..

Tana zaune a parlor tana tunane tunanen ta sai sallamar Marshall ya doki kunnen ta,ɗagowa ta yi ta dube sa sai ta mai barka da dawowa kamar kullum shima sai ya mata barka da zama..

Saɓanin da yau sai ya zauna tare da ita a parlorn a kan wani kujera yana kallon ta sai ta ɗan tsargu har ta kasa yin shiru ta ce

"In kawo maka coffee ɗin ne yanzu"!!shi dai kallon ta yake bai ce ƙala ba har ta tashi dan halin ƙyaliyar sa ya rigada ya zame mata jiki tuntuni.. .mikewa tayi zata fice yace

"Dawo ki zauna mgn zamu yi"

..juyowa tayi ta dawo ta zauna a natse..

Sai da ya ɗau lkc sannan ya mata tmby kai tsaye.

"Me ke damin ki da kullum kike zama kina kuka ke kaɗai?

Sai yau ma ya san da haka?take ta ji hawaye na son cika mata ido,bai ce mata komai ba sai ta girgiza mai kai tana faɗin

"Ba komai"kallon mamaki ya mata wai har ta iya zurfin ciki tana ɓoye mai abu? ɗage kafaɗun sa yayi alamr abin bai dame sa ba ya ce ta je ta kawo mai coffee zai kwanta..

Zuciyarta na mata nauyi ta tashi Haka ta je ta haɗa mai tana tunane ta dawo ta miƙa mai a rayuwa tunda take bata taɓa fuskantar damuwa da shiga tashin hankali ba irin wannan,ta saba zama cikin mutani masoyan ta amma yau daga ita sai ita kamar marar hali mai kyau,wa zai fahimce ta ta sami yafiyar yar uwar ta...

Da miƙa mai ya tashi ya wuce ciki abin sa ita kuma ta jingina da kujerar tana tunanin ko ina rayuwar ta zata juya aƙala Allah ne kawai masani..

Lokuta ta asarar a tunanin nata har sai da ta ji ta gaji da zaman sannan ta tashi haɗe da kashe lights ɗin nan parlor ta wuce zuwa ciki..

Bed room ɗin is a luxurious one komai yayi daidai toh addu'ar ta ko a ƙasan ne ya bar ta ta kwanta ba sai lallai a kan gadon ba dan ta san wannan gadon ko ranar da ta hau bai mata tsawaba sakamakon rashin lfyr da yake yi ne so bata so ta fuskanci ƙasƙanci ko wulaƙancin sa akan wannan gadon ta san matar sa ce ke da damar hawa gadon..

Mamaki sosai ta yi da ta gan sa zaune saman kujera da table yana aiki ga papers nan birjik gefe ga laptop a side kaɗan ga kofin coffee ɗin sa nan..

Rasa abin yi ta yi sai ta hau kame kame shi kuma sallamar ta na fari a kunnen sa haka ya sa ya ɗago yana kallon ta sai ya tmby ta,da ƙyar ta iya furta..

"Bacci nake ji"!

funny,ya faɗa a zuciyar sa sai ya dube ta ya ƙara yana maida hankalin sa ga aikin sa kamar ba zai ce komai ba sai kuma kamar an fizgo mgnr ya ce mata

"Toh sai da safe"

da sauri ta faɗa mai a nan ɗakin take son kwanciya ba akan kujera ba batare da wani tunani ba tayi mgnr shi kuma sai yayiwa mgnr nata bahaguwar fahimta ya tsaya da ayyukan sa cak ya maida hnkl sa ga kallon ta daga bisani yayi wani tunani ya ce da ita

Ke Bazaki kwana min ɗaki na ba

"Ga ɗakin ki nan can wannan kina iya zuwa can ki kwanta"!!

gyaɗa mai kai ta yi dan dai dai da rana ɗaya bata taɓa dunfarar ɗakunan dake site dinsa ba iyakar ta parlor

kitchen,bedroom ɗin sa in ta kai mai coffee ko in ta tafi gyarawa sai guest toilet da take buƙatun ta a ciki..

Ganin ta fita bata mai gardama ba sai ya taɓe baki yana goge bahaguwar tunanin da ya fara yiwa mgnr ta ya cigaba da aikin sa..

Ita kuwa da fita bata tsaya ko ina ba sai ɗakin da ya ce nata ne,tana buɗewa ta ga daki ne mai kyau sai ta tsaya mamakin tsaruwar ɗakin nata wato har ita ke mallakar ɗai irin wannan amma take kwanciyar parlor kuma shi bai taɓa sanar da ita ba?lallai miskilancin sa ya kai matakin izgilanci dan yayi yawa..

Abubuwan ɗakin sun yi ƙura sai dai bata jin zata iya gyara sa da daren nan ko dan sbd kar ya ce ta dame sa haka ta je ta yaye bedsheet ɗin gadon ta buɗe wardrobe ta nemo wani babban blanket ta shimfiɗa kan expensive cream colour royal bed ɗin ta ta ɗau wani na lulluɓe jiki sannan ta sauya night gown ɗin jikin ta zuwa wani daga haka ta kwanta akan gadon ta lulluɓe jikin ta da blanket ɗin..

Bazata iya tuna rabonta da ta kwanta a kan gado so yau bata jima ba baccin ya ɗauke ta

*****

Kusan makara ta yi da safe yayi sai da ya ga bai ga giftawar ta ba a gidan sai yayi tunanin ya duba ta haka ya tura ƙofar ɗakin..

Hango ta yayi kwance saman gadon tana bacci hnkl kwance ƙarasawa ciki yayi ya tsaya a kan ta ya rinƙa kallon ta ya tada ta ne ko dai ya ƙyale ta ne bai sani ba,it was 7:10am sai da ya ƙare ma fuskar kallo sannan ya saka hannu ya fara yaye mata blanket ɗin dan shi dai bai taɓa jin ya kirata da sunan ta ba daga ki min kaza sai kai min kaza ko zo ko zauna,shidai sunan ta dai bai shiga bakin sa ba..

A baccin ta ji ana ja mata abin rufa sai ta riƙe wani gefe,kallon hannun ta yayi ya girgiza kai ya yaye blanket ɗin baki ɗaya.. .

Ganin surar jikin ta yayi,doguwar rigar bacci ce mai tsantsi kusan komi yana gani sai ya ɗan ɗaga idon sa daya kasa ɗaukewa daga jikin ta yana yi yana kallon fuskar ta sai da ta buɗe ido suka yi ido huɗu da shi..

A firgit ta tashi tana janyo blanket ɗin tana rufe jikin ta shi kuma ya kawar da kan sa a ɗan daburce ya juya yana faɗin

"Are u mad?..Ki tashi ki yi sallah lkc ya tafi"

daga haka ya fita ita kuma kunyar sa ya gama kama ta sai ta rinƙa jin nauyin haɗa ido da shi..

yau gaba daya haka ta rinƙa kauce mai dan kar su haɗu,ita me ya sa ma bata rufe ƙofar ba,shi kam gudun kar ta mai wani kallo sai ya rinƙa ɗaure mata fuska abinda zata ce ta jima rabon ta da ganin sa yana yi tun haɗuwar su ta fari sau biyu zuwa uku da ya rinƙa tamke mata fuska bai kuma ba sai yau..

Tana kitchen tana girkin ta har da saka lock sai ta ji ana juya handle,juyowar ta ke da wuya ta ga har an buɗe ƙofar an shigo..

Sumewar tsaye tayi ganin wani irin ƙerarriyar kaftan da ya saka,she can't judge wen it comes to kayan maza amma ko ma wani iri ne wannan ta san mai tsada ne..

bayan ƙamshin da yake yi suturar ta zauna mai hular da ya saka matching colour da kayan sai ya fito da shi a asalin magidancin kamilin namiji,gabaɗayan sa sai ta ji kamar tayi capturing nasa tayi ta kallon sa.. .

Ƙwarjini ya mata ba kaɗan ba ai tuni tsoron haɗa fuska da shi ya ɓace mata sai ta shagala da kallon sa har sai da ya ɗan girgiza mata keys ta dawo duniyar mu ta fara kame kame sai ya miƙo mata yana faɗin

"Ga keys ɗin sashen nan ki rufe in na wuce in kuma zaki shiga sashen su Ammy ne fyn ni zan tafi wni wuri ba zan dawo da wuri ba kar ki yi abinci da ni,sai na dawo"!!.

da salon gentle man ya mata bayanin sai ta ji wani abu a zuciyar ta bata san ma ta furta ba sai ji ta yi ya ce

"Amin"!!wai ashe ce mai ta yi Allah ya tsare shi kuma ya dube ta sannan ya amsa ya fita...

Bayan ya fita ne ta fara leƙen sa ta windown kitchen ɗin tana kallon sa ya shiga motar sa ta Land cruiser asalin silver colour yayi horn aka buɗe mai gate ɗin nasu ya saka kan motar ya fita aka maida ƙofar aka rufe..

Abinda bata taɓa yi ba yau ta yi wato haurawa upstairs ɗin gidan,da sauri ta haura ta tsaya a balcony inda ta hangi yadda yake tuƙin sa so gently and maturely har ya ɓacewa ganin ta sannan ta dawo ƙasa dan duba abincin ta da niyar komawa duba upstairs ɗin in ta kammala girkin ta..

Duk tunanin sa ne ya rinƙa faɗo mata ta dai ƙarasa girkin ne amma hankalin ta na ga tunanin da bata san dalilin yinsa da take yi ba,bata san matakin da zata saka wannan abinda zuciyar ta ke ayyana mata ba akan Saheeb,so ne, shaƙuwa ce ko kusanci irin na ma'aurata?..

#Mamuh*26*

Tana aiki tana jin wani sanyi yana shigarta saheeb ne yake yawan fado mata arai haka dai ta kammala aikin nata da kyar ta koma ta gyare ɗakin ta ta gyara mai nasa har bed wears ta sauya mai zuwa wasu maroon colours.

Da ta gama ayyukan nata sai ta ƙi zaman cin abinci ta nufi upstairs ɗin dan binciken me ke wurin.

Da zuwan ta ɗaki na farko ta shiga sai ta ga girman su kusan iri ɗaya da nata sai dai wannan ya fi nata girma kaɗan,komai na ɗakin mace yana nan a wannan ɗakin..

Taɓe baki tayi tana tunanin hala na matar sa ne,da haka ta kuma duba wani ɗakin nan ma ta ga kaya kamar na ɗakin farko colour ne ya bambanta su..

Dakin karshe dake saman ta je buɗewa sai ta gan sa a rufe,hararar ɗakin tayi ta sauko ƙasa abin ta zuwa kitchen..

Abinci ta ɗeba ta zauna ci amma kasa ci tayi,fitar duk sai dawo mata a kai yake yi,ɗan awowin da tayi bata gan sa ba ta rasa meya sa duk taji ta dame,da ƙyar ta tuttura abincin ba dan tana jin taste ɗin sa kamar yadda ta so yayi ba...

Sai da ta kammala cin abincin ta saka hijabin ta mai tsayi ta saka flat slippers ɗin ta ta fito,rufe ƙofar tayi ta nufi sashen su Hamida..

Sallama tayi sai ba a amsa mata ba dan haka da hannun ta ta tura ƙaramin ƙofar ta shiga.

Babu kowa a farfajiyar gidan ƙarasawa ciki tayi sai ta ga Hamida kwance ita ɗaya tana riƙe da remote tana ta sauya tashoshin tv..

Tabbacin babu kowa a gidan kenan daga ita sai ita,hakan ya ma fifi daɗi dan zasu fi samin lkcn juna sosai..

"Assalmu alaikum"kafin ta juyo ta fara amsa sallamar sai kuma da ta juyo ta ga Mufida ce sai ta ƙi ƙarasa amsa sallamar a bayyane ta amsa a ran ta.

Ɓata fuska Hamida tayi,tayi kicin kicin tana kallon fifi daga bisani ta ɗaga mata murya tana faɗin

"What?me kike so"?shiru Mufida tayi tana kallon ta,tsaki ta ja tana mai yi mata wasu irin kalamai marasa daɗin ji dake taɓa fifi ainun saidai ta san ita ta kawo kan ta dole ta jure duk abinda Hamida zata mata..

Matsowa kusa da Hamida tayi tana sauke murya ƙasa game da bata haƙuri amma Hamida ta riga ta hau dokin fushi marar dalili kuma kishin fifi ya rufe mata ido da yawa dan har ta daina jin tausayin fifin da take jin in ta zo tana bata haƙuri,ga mijin ta dake lallaɓa ta yana ririta ta amma duk lkcn da ta ga fuskar fifi sai ta ji kamar duk ririta da Khalid ke yi bai isa ba dole sai ya kara dan gani take fifi is receiving a more intensive care a wurin mijin ta akan wanda take samu sai ta rinƙa jin haushin fifin sosai..

"Kar ki ƙaraso gare ni tashi kawai ki fitar min daga gida,a kullum ke ce abin so komai naki mai kyau ne mijin ma sai da aka zaɓar maki mai kyau sannan aka baki ko ba haka ba?toh ki koma wurin waɗannan da suka tsara maki rayuwar ki suka rinƙa bi maki rayuwar daki daki suna nuna maki yadda zaki yi ki ce su samar maki abinda kika rasa yanzu dan ni kam kin ishe ni na gaji da mitar ki da kike zuwa kina min kullum,Hamee kaza Hamee kaza Hamee kaza,duk kalaman bakin ki Hamida ce ciki sbd kina da manufa da ni,in ba dan haka ba ta yaya ni ko zuwa sashen ki ban taɓa yi ba amma ke kin zo min ya fi a ƙirga,what are u up to?huh?fifi kin nemo soyayya da attention ɗin kowa a family ɗin mu kuma kin samu amma ki sani,lkc ya ƙure maki da zaki kirkiro wata soyayyar ƙarya dan ki sami nawa soyayyar,i can't believe u coz u are always pretending.

haka kike haka kika taso kuma haka kike cigaba da rayuwar ki amma ki sani not any more in dai da ni ce Hamida,lies and pretence ɗin ki ya tsaya haka dan ban da lkcn sauraron su a kunne na bare zuciya da kai na

dan haka ina baki shawara da kin zauna a inda kike kin yi rayuwar ki kamar yadda aka tsara maki tun kina yarinya kin zauna da masoyan ki zai fi miki,dan ni nan da kika gan ni,,ba zaki taɓa samin yadda kike so daga gare ni ba ki koma ki yi rayuwar ki da waɗanda suke son ki dan ni ban da damuwa a baya neda ban da kowa damuwar ki ke dami na amma yanzu da nake da miji na ya ishe ni ya maye min gurbin komai,bana buƙatar kowa a rayuwa ta ki manta ma kina da wata yar uwa a duniyar nan dan ni na manta da ke...

na manta da an haife ni rana ɗaya nida ke daga jikin mutum ɗaya,awanni ɗaya sai bambanci mintoci biyar,kema da zaki yi hakan da ya fiye maki Mufida coz i will never ever accept u in my life anymore kin taka taki rawar for long so yanzu nawa lkcn ne my husband is all i got i don't need u"!!

tana kaiwa nan ta wuce fifi dake tsaye cikin shock kamar an dasa ta..

Bayan Hamidar ta gama daddasawa fifi maganganu son ran ta ta haura sama faɗawa kan gadon ta tayi ta yi shiru tana tunanin irin kalaman da ta gasawa fifin ko sun dace ko basu dace ba..

Wani sashe na zuciyar ta ke faɗa mata tayi dai dai wani sashen na nuna mata rashin dacewar abinda ta yi sai dai mafi rinjaye ɗin ya fi nuna mata ai daidai tayi dan fifi ce ta jawo wa kan ta hakan..

Fifi dake tsaye tana halin shock ta ɗauki lkc a haka tana tunanin anya wannan Hamida yar uwar ta ce ko wata,kasa cigaba da daukar maganan fifi tayi sai ta tare hawayen da ya zubo mata da yatsar hannun ta ta juya ta bar sashen..

Hira suke yi suna dariya as family kawai ta turo ƙofar da ƙarfi ta shigo haɗe da yin jifa da wayar ta a ƙasa da ya faɗi ya tarwatse a wurin..

Take hankulan su ya dawo kan ta sai suka hango ɓacin rai mai tsanani a tattare da ita,take hankulan su ya tashi sai Ammy ta zo da sauri dan tmbyr lfy..

Ɗaga mata hannu fifi tayi cikin ƙunar zuciya da zafi rai ta kuma ɗaga ɗaya hannun ta dan ta san Hajja ce zata zo ta nan..

Hawaye ne taf a idanun ta wanda bata hana su zubowa ba ta bar su suna zubowa ita kuma tayi shiru dan zafin da ran ta ke mata in ba nutsar da zuciyar ta tayi ba kalaman da zasu fito bakin ta ba zasu yiwa su Ammy daɗin ji ba shiyasa ta ɗan tsaya na wasu lokutan sannan ta dubi wayar dake ƙasan sannan ta dubi Ammy ta kuma dubi hajja kana ta ce.

"Kun ga wannan wayar da ta tarwatse a wurin nan"?gyaɗa mata kai suka yi sai ta girgiza kan ta ta ja hanci sannan ta cigaba da mgn

Tace "nima Haka zuciya ta ta tarwatsewa,haka rayuwa ta ta tarwatse,haka dreams ɗi na ya tarwatse its all because of u people,ku kuka bada gudunmawa mai ƙarfi a lalacewar komai da ya lalace a rayuwa ta,nayi tsammanin da zuciya ɗaya kuke so da ƙauna ta har na saki jiki da ku ashe ba haka bane,kuna nan kuna koya min abinda ku kuka san ba daidai bane,menene laifi na?yarinya ce ni ban san komai ba ku ya kamata ku nuna min hanya mai kyau a layin rayuwa ta amma baku min haka ba,kuna ji kuna gani na rinƙa aikata laifi amma abinda kuka kira da "So" sai ya hana ku nuna min laifi na?

duk akan ku komai nawa ya zama wani iri na rasa abu mafi girma a rayuwa ta,gani nan ina rayuwa a duniyar nan amma kamar ban da zuciya a ƙirji na,komai nayi dan gyara kurakuran ku bai yi sai taɓarɓarewar da al'amura ke ta yi,a dalilin ku...yɔar uwar ta,jini na wacce take a matsayin komai a gare ni ta guje ni ta tsane ni ta tsani gani na duk wani abu da ya shafe ni bata son gani ko ji,kuma ku kuka jawo hakan,da gudunmawar ku kuka nesanta ni da yɔar uwa ta,da sanin ku tsana ta ya ɗarsu a zuciyar yɔar uwa ta,a yanzu,a yau Hamida ta dubi tsabar ido na ta faɗa min ta daɗe da manta ni a rayuwar ta a matsayin yɔar uwar ta ta jini kuma tana umarta ta da in manta da ita nima,wa ya janyo min??

wa ya janyo min wannan abin?me ya sa kuka min haka?kunsan soyayyar ku na iya rikiɗewa ya dawo ƙiyayya a gare ni a idon yɔar uwa ta me ya sa baku ankarar da ni ba kuka rinƙa nuna min so da bambanci a gaban Hamida?

babu abinda ni na sani akan wannan abin amma ƙiyayya ta ta gama mamaye jikin Hamida is this just?ya dace?for all those years bata taɓa nuna ɓacin ran ta ba ku kuma baku taɓa nuna damuwar ku akan ta ba sai ni ni ɗaya what if i die right now zaku iya gyara guraben da kuka ƙirƙira ne a zuciyar Hamida?

zaku iya dawo da ni ku cigaba da bani kulawar taku ne dan kar in mutu kuma?no u can't do anything kun rigada kun ɓata komai kun ɓata min matsay na a wajen yɔar uwa ta kun dasa mata baƙin tambari a game da ni a zuciyar ta da zai yi wuyar goguwa,yau an zo ƙarshe.. idan har ba zan iya gyara alaƙa ta da yɔar uwa ta ba toh i see no reason why i should continue leaving on this earth kun san me??ku manta da ni kawai i don't need u all in my life..

babu abinda soyayyar ku ta janyo wa _Ƙaunarmu_ ni da Hamidata yau bamu da wata rayuwa sai acikin ƙiyayyar mu.

dan haka ku bar ni ku rabu da ni ni na san yadda zan yi da rayuwa ta"..tana kaiwa nan ta juya da gudu ta fita..

Tana fitowa daidai balcony ɗin su Ammy sai ta ga Saheeb tsaye da alama ya ji komai,kallon sa ta tsaya yi tana numfarfashi da sauri da sauri tana jan iska da ƙyar dan ba ƙaramin nauyi zuciyar ta ya mata ba ji take kamar zai faɗo ya fito amma bata so ta cigaba da tsayuwa a sashen su Ammy bare har ciwon da take ji ya bayyana su gani su kawo mata agaji danbata nemar taimako ko kulawar kowa a halin da take ciki..

Kallon sa take yi tana kokawa da numfashin ta dake sama sama kamar zai ɗauke,ƙarasowa kusa da ita yayi sai kawai ta hau girgiza mai kai ta faɗa jikin sa cikin daƙiƙu kaɗan nan take kukan ta ya fito fili sosai sai ta sake jiki tana ta yi..

Kasa cigaba da tsayuwar wurin suka yi ta lalaɓa ya taimaka mata suka koma sashen su tana ta kuka..

Kuka sosai fifi ke yi sa sai da ruɗar da Saheeb dan bai taɓa ganin mace ma kuka irin haka dake fitowa daga zuciyar ta ba,tana a jikin sa tana kukan kamar ba zata daina ba ta rinƙa tmbyr sa

"Ina da laifi ne?sun saka tsana ta a zuciyar yar uwa ta ta ce bata sonta sake gani na,ta ce ta daɗe da goge ni a rayuwar ta a matsayin yar uwar ta i swear it wasn't my fault ya zan yi da rayuwa ta"!?da shesheƙa mai ƙarfi ta ƙarasa mgnr sai ya ji tausayin ta dama yakan lura da shigi da ficin ta kawai dai jiran lkcn da ya dace ya tunkari abin yake yi..

A jikin sa zazzaɓin ta ya tsananta dole ya nemi Dr ɗin su ya zo cikin gaggawa dan har kamar ta fara convulsing,da zuwan Dr kuwa ya ce abin ya fara tsanani dan any moment tana iya samin cardiac arrest na biyu kuma dan ta ɗan jima tana danne rashin lfyr..

Wannan abin sai da ya saka zuciyar Saheeb bugawa ya kuma duban ta tana bacci sakamakon allurar da aka mata dan yayi calming nata..

Tambayar Dr yayi ko wani abu za a zaman yi mata da zai taimaka kar ya janyo rashin lfyr nata,nan dai doctorn ya ɗan yi briefing mai abubuwan da suka dace a rinƙa yi mata..

Godiya yayiwa doctorn ya raka sa shi kuma ya dawo ciki ya tasa ta gaba yana kallon ta yana tunane tunane a zuciyar sa game da yadda zai magance wannan abin..

4 hours later

Daidai 6pm fifi ta farka daga doguwar baccin allurar da aka mata sai ta ɗan zauna tana tunanin abinda ya faru da ita nan kuwa ta fara tunowa sai hawaye ya cike mata ido..

Kamar ya sani dama yanzu ya shiga wanka a ɗakin sa sai ya fito da ɗaurin towel ɗin ya nufi ɗakin ta,da shigar sa hawayen na dropping daga idon ta..

Kallon ta yayi sai suka haɗa ido take ta ji kamar an ingiza zuciyar ta sai ta fara sabon kukan..

Ɗan ajiyar zuciya ya sauke ya ƙarasa ciki yana mai gyara ɗaurin towel ɗin ya zo har gadon ya zauna haɗe da jawo ta jikin sa ya rungume ta tsam dan ya san tana wani hali mai wuyar fassarawa..

Kukan ta cigaba da yi a jikin sa ta manta a inda take kuma a situation ɗin da shi Saheeb ɗin yake na rashin sutura a jikin sa,haka ta yi ta rusa kukan ta shi kuma yana rarrashin ta har ta ɗan tsagaita sai ya ɗago da ita ya dubi fuskar ta dake dab da nasa ya haɗa ido da ita suna kallon juna har na wasu lokuta sannan ya fara mgn cikin sanyaya murya a hankali

"Am sorry i couldn't understand ur pain".

cigaba da kukan tayi tana shesheƙa sai da tayi mai isar ta sannan ta ɗaga daga jikin sa tana share hawayen fuskar ta..

Yana kallon ta sai kuma ta ruɗe ta fara yunƙurin kawar da kan ta a yanzu da ta dawo hayyacin ta,murmushi kawai yayi ya tashi ya bar ɗakin zuwa nashi..

Around 8pm na daren still ya dawo daga masallaci ya ga bai gan ta a nan parlorn ba sai ya shiga dan duba ta,nan ya ga yadda take rawar sanyi ƙudindine cikin blanket tana ta numfashi sama sama..

A hanzarce ya ƙaraso ya zo ya taɓa goshin ta ya ji zafi rau,duba magungunan ta yayi ya ga bata sha ba sai shine yau yayi jinyar nata ya kawo mata warm tea ta sha kaɗan sannan ya ɓallo mata magungunan ya miƙo mata ta sha..

A jikin sa tayi baccin bayan wuyar da ta sha a cikin jikin ta,jingina da gadon yayi yana tunanin mafita ɗaya sahihiya dan wannan lamarin nata ya munana..

*****

Da safe ya riga ta tashi yataimaka mata ta yi wanka ta sauya kayan ta dan jikin nata da sauƙi,ya koma ɗakin sa da zumar zai je ya dawo sai ta kama hanya ta fita kamar dole tana kakkame jikin ta dan sanyi sanyin da take ji ta nufi sashen Hamida..

Yau kam Hamidar da kan ta ta buɗe mata ƙofa,tana ganin ta sai tayi wani irin murmushin is this girl for real sannan ta riƙe ƙofar nata tana duban fifin har na wasu lokuta..

"Hamida ki yi haƙuri jiya ban ji daɗin jiki na bane na so in zo da dare but ban da lfy ne shi ya sa ban zo ba"ko da Hamida ta ji fifi ta ce bata da lfy sai ta kuma duban ta a ɗan tsorace amma ta basar ta cigaba da kallon ta har ta cigaba da bata haƙuri

tana tuno mata yarintar su yadda suke komai tare akan tayi haƙuri yanzu ma is not late zata gyara komai sai su dawo kamar lkcn suna yara ba tare da wasu sun masu karan tsaye a rayuwar su ba kuma..

Hamida abin na taɓa ta a zuciyar ta amma ta rasa ya zata yi da kishin yar uwar ta da ya mata dabaibayi a zuciyar ta sai kawai ta kawar da tausayin da ya ɗan bijiro mata ta gayawa fifi mgn son ran ta haɗe da rufe ƙofar ta a fuskar Mufida..

Da rashin jin dadi Mufida ta juyo zata fara kukan sai ta ga mijin ta na ƙarasowa da zuwan sa ya riƙo hannun ta bai ce da ita ƙala ba dama da sutura a jikin ta ya kai ta hanyar shiga motar sa tana bin sa bata ce mai komai ba har ya buɗe mata ƙofar ta shiga bata fahimci komai ba shi kuma ya zaga ya shiga..

Tada motar yayi sai ta ga yayi hanyar fita a sannan ta tmby sa ina zasu cikin kuka sai ya amsa mata da..

"Somewhere far from here"!!

daga haka ya ja bakin sa yayi shiru itama tayi shiru amma kukan zuci take yi mai ciwo haka a zahiri takan goge hawaye time to time,har suka yi doguwar tafiyar da a ƙa'idance ya isa ya saka mutum bacci sbd nisan sa amma da yake ba a cikin normal self ɗin ta take ba sai bata ga nisar tafiyar ba..

Wani gida ne babba ya tura motar nasa ciki bayan an buɗe gate ɗin gidan yayi parking ya kashe motar ya dube ta yana faɗin

"Shall we"?gyaɗa mai kai tayi sai ya fito itama ta fito sai ta ga ya bada umarnin a buɗe booth a fito da kayan dake ciki nan ta ga akwatunan ta har biyu aka zo aka wuce da su ciki suna tsaye..

Daga bisani ya mata jagora zuwa cikin main house ɗin tana bin sa a baya zuciyar ta na mata wani iri kamar ba ita ba...

#Mamuh*27*

Tun da fifi ta gama maganganun ta ta tafi kaf jikin su yayi sanyi sun rasa ya zasu yi sun san su suka lalata komai kuma suna nadamar abubuwan da ya faru a sanadiyar su dan sun bada gudunmawa mai karfi a faruwar halin da ake ciki..

Hajja ce ta fara zama kan kujera tana mai dafe kan ta in soyayya na siyar komai da sun yi amfani da shi sun siyowa fifi soyayyar Hamida amma duk gatancin da suka nuna mata bai haifar mata da komai ba sama da nisanta ta da yar uwar ta da yayi ina amfanin irin wannan gatar da soyayyar?..

Ammy ce ta zo ta zauna kusa da Hajja itama tana nata nazarin da yadda zasu ɓullowa lamarin dan Hamida ta hau dokin fushi da su sam bata sauraron su ko sun tafi kuma sun san laifin su ne.

Abin ya masu yawa sai Ammy ta kirayi layin Khalid dan abin ya ishe ta haka nan duk laifin kan ta da Hajja yake dawowa..

Bugu uku Khalid ya ɗaga sai ta ce mai ya zo Hamida yanzu tana son ganin ta..

Ko da ta sauke wayar sai da aka ɗau lkc kafin Khalid ya dawo gidan sakamakon rushing da yayi ya dawo daga asibiti ya je ya tasa Hamida a gaba dan su zo nan ɗin..

Rai a haɗe ta shigo tana kawar da kan ta dan kar ma ta ji wani batun daga bakin Ammy ko Hajja game da fifi..

Gaida su tayi kamar an saka ta dole sai suka amsa mata suna kallon ta,Ammy ce ta fara bata haƙurin abinda ya faru sannan Hajja ta saka baki but duk wannan abinda suke yi bai ɗara Hamida ba so take su kai aya ta tashi ta tafi ta gaji da jin fifi fifi,imagine yardar ta da ƙaunar ta ma fifin kasa nemar sa tayi sai da ta zo ta haɗa da su..

Hajja na gama nasihar ta Khalid na sauraron su Hamida ta ce ta gode ta miƙe ta fita ta bar su da jimami,kasa haƙuri Khalid yayi ya tashi ya bi bayan ta rai ɓace ya same ta a parlor zata shiga kitchen ya fizgo ta suna kallon juna rai ɓace ya ce

"What was that Hamida"?kallon ƙwayar idanun sa tayi ta ce

"A ina"?wani scoff yayi na raina mai tunanin da tayi sai ya kuma matso ta da ƙarfi ya ce

"Hamida ki min duk abinda kika ga ya maki amma don't u ever include my mother and my grandmother,ashe haka kike?har kina iya rufe idon ki ki ma waɗannan mutanin wannan abin?duk girman laifin da aka maki baki saukowa ki dawo yadda ake so ki dawo?ke da su wa ke nemar albarkar wani dan gama da duniya lfy?ke ko su?wacece ke da har za a maki laifi a rinƙa bibiyar ki ana baki haƙuri amma kina turjewa?

.

zatayi magana ya dakatar da ita yace

Hameeda wai meye laifin Mufida a wannan abin?ita ta maki laifin ta hana kan ta sukuni ta rinƙa zarya a nan sashen dan baki haƙuri but kullum da ɓacin ran ki take komawa yet bata haƙura ba ta cigaba da zuwa wai kuma baki ji tausayin ta ba,,my god Hamida ko wanda ya halicce mu a ko wani daƙiƙa muna masa laifi kuma da baya yafe mana ko numfashin da muke shaƙa ta iska da ba zamu shaƙa ba toh dan me ke ba zaki fahimci yaruwar ki ki yafe mata ba"?kallon idon sa Hamida tayi tana jin zafin yadda yake son ɗora mata laifin komai alhalin ya san ba yin kan ta bane su suka ingiza ta yin hakan..

"Khalid ka je ka auri Mufida in ya so sai ka yi defending nata da kyau a idanu na amma wannan ba zai yi ba"! tana kaiwa nan ta buge hannun sa daga jikin ta ta wuce sa ba tare da ta juyo ba..

Abin ya ɗaure mai kai,wannan wace iriyar tsana da kishi ne ya ɗarsu a zuciyar Hamida game da Mufida?ta fara rasa tunanin ta dan tana furta kalaman da ya fita daga na masu hankali..

Ɗaga kafaɗun sa yayi ya juya ya shiga motar sa ya tada dan komawa bakin aikin sa zaman sa gidan nan bai da amfani sai dai ɓata abubuwa da zaman zai jawo dan Hamida tayi nisa ba fahimtar sa zata yi ba..

****

A natse take ta kallon parlorn kamar bata taɓa ganin gini mai kyau da tsari da ya kai wannan ba sai ya kalle ta ya mana iso zuwa wani ɗaki inda nan ma ƙarshe ne a kyau dan ya tsaru yayi kyau..

Kayan su ne a cikin ɗakin sai ta zauna bisa sofa ɗin ɗakin ta rinƙa kallon ɗakin komai maroon and cream colour tana ta kallo shi kuma yana mata murmushi..

"It's beautiful"!ta furta sai ya mata murmushin gamsarwa ya gyaɗa kan sa sannan ya koma waje dan ɗauko wasu abubuwan sa ita kuma ta cigaba da kallon ɗakin tana yaba sa..

Har ya dawo bata tashi ta ɗaga komai ba sai da ya fara gyara kayan dan kan sa sai ta tashi ta fara taya sa..

Kamar kurame suka yi gyaran ɗakin ta kalle shi tana son tmbyr sa kitchen dan ta samo masu abinda zasu ci..

Nuna mata kitchen ɗin yayi ta shiga ta ga komai na nan kamar dama akwai mace a gidan..

Nemo abinda zata dafa tayi ta fara aiki,duka duka bata ɗau awa ba ta haɗa jollof pasta da garnishing vegetables ta zuba masu a plate biyu ta saka folk da abin sha da kofuna ta fito da su zuwa parlorn..

Baya nan sai ta shiga cikin ɗakin ta mai mgn akan ta kammala girkin,barin abinda yake yi yayi ya biyo ta zuwa parlorn..

Zama suka yi a ƙasa kowa ya fara cin abincin sa,shi dai yana ci yana mamakin dama ta iya girki ne,shi yayi tunanin duk girkin da take yi ana zuwa taya ta yin sa

ne toh amma yau da babu wanda ta sani a nan ɗin kuma tayi girkin sai yayi ta mamaki har ya kasa ɓoyewa ya tmby ta..

Dariya ta yi dan tmbyr ta bata dariya sai ta dube shi ta ce

"Ni na dafa da kaina"gyaɗa kai yayi ya cigaba da cin abincin har suka kammala babu wanda ya ce komai..

Kwashe kayan tayi ta gyara wurin ta dawo tana gyara kayan ta dan ya fita zuwa masallaci...

Da ta gama ta dawo parlor ta zauna ta kunna kayan kallo tana yi tana kallon wani ɗakin dake wurin yana fuskantar wanda suke ciki ta rasa me ya sa bai buɗe wannan ɗakin ba amma in ya dawo zata tmby sa..

Bayan wani lokaci

Bacci ke damin ta sosai sai dai bata san ya zata yi ba dan yana cikin ɗakin kuma bacci zai yi toh ita kuma bata san inda zata kwanta ba sai dai ta daure ta tmby sa..

"A ina zan kwanta"!?kallonbta yayi sau ɗaya ya gyara kwanciyar sa haɗe da nuna mata inda zata kwantan da hannu,wato gefen hagun sa sai ta zaro idanun ta waje tana duban sa..

"Wancan ɗakin fah mai kallon wanna"?ta tmby sa sai ya amsa mata kai tsaye

"Ɗakin Muhibba ne wannan ne nawa dan haka a nan zaki zauna"!shiru ta mai tana tuno da matar nasada bata taɓa ganin ta ba..

Gajiya tayi da tsayuwar ta zo a hnkl wai kar ya gane ta ta hau gadon ta kwanta shiru gaban ta na faɗi,sai ji tayi ya ce

"Kin sha maganin ki na daren nan"?tsananta faɗi gaban ta yayi jin ashe bai yi bacci ba sai ta gyaɗa mai kai tana faɗin

"Eh"daga haka basu kuma mgn ba a hakan bacci ya ɗauke su shi hnkl kwance ita kuma da fargaba..

****

Kusan kwanaki biyar kenan da dawowar su wannan gida da fifi bata san sunan unguwar ba ma bare ta san layin da gidan yake..

A fannin zamantakewar cikin gidan daidai gwargwado tana ƙoƙarin yin abinda ya dace dan duk ayyukan da mace ya rataya a wuyar ta tayi a gidan mijin ta Mufida na yin su babu shayi bare wani damuwa..

Irin zaman da suke yi mutum in ya kalle sa ba zai ce da zaman nasu zaman soyayya bace amma ana iya kiran sa da zaman kulawa,dan suna kaf kaf da junan su akwai kula ta musamman da suke nunawa junan su da in wani baƙo ne ya zo ya kalle su zai yi ƙiyastin soyayya ce mai ƙarfi suke yiwa kan su..

Su kan su zaman na masu daɗi a haka shaƙuwa mai ƙarfi ya rinƙa shigar su a hnkl amma abin haushin daga shi har ita basu san so ya rusa katangar shaƙuwar tasu ya ratsa zuciyoyin su ba musamman Mufida da take ɗaukar kulawar sa a gare ta ne yayi ƙarfi amma bata kawo tunanin soyayya ko kusa a zuciyar ta ba hasalima hnkl da tunanin ta bai kai nan ba..

Haka ya danganta shaƙuwar su da kusancin da suka yi da juna ne amma batun soyayya sam bai zo kan sa ba shi gani yake ma rainon ta da yake yi ne ya sa yake iya daukar duk yarintar da take tafka masa a nasa tunanin tsantsenen ta yarinta ne..

Yau kamar kullum ta gama gyara kan ta ta zo ta kwanta yayin da shi kuma yake aikin sa a wani table mai kujera..

Har bacci ya ɗauke ta sannan ya biyo ta ya kwanta suka Juyawa juna baya kamar kullum sai dai yau abin ya gagare sa.

Rasa dalili yayi dan baccin bai zo mai ba ko kaɗan sai jin wani iri ya rinƙa yi a jikin sa,ya juya ya juya baccin bai zo ba,haka ya juya ya rinƙa kallon Mufida a natse..

Gaban sa ne ya rinƙa faɗi dan bai san ma'anar wannan abin kunyar dake shirin faruwa da shi ba,ta yaya hakan zai faru da shi..

Ɗauke kan sa yayi daga kallon ta lura da yayi da kallon nata ma daɗa tunzira sa kan yin wani abu yake yi..

Miƙewa yayi ya ɗau pillow ya nufi parlor ya kwanta yana ta juye juye kamar marar lfy mai nemar agaji..

Ƙaurace mai baccin yayi haka yana ji yana gani bacci ya ɗaukewa idanun sa,how? da girman sa da ƙimar sa a idanun yarinyar nan wannan abin ke shirin faruwa da shi,shi kan sa rabon da ya tsinci kan sa cikin wannan yanayi tun bayan haɗuwar sa da matar sa Muhibba a ƙasar Cairo da ya kai mata ziyara dan ta tafi closing wani deal a can ƙasar shi kuma yana off duty sakamakon ɗan rashin lfyr da yayi sai ya tmby ta inda take dan ya kai mata ziyar,daga lkcn zuwa yanzu kimanin watanni takwas kenan almost 9 sai kuma kwatsam wannan abin ya fara bijiro masa a inda bai dace ba.

Juye juye ya rinƙa yi yana jin abin na damin sa soaai fiye da da,tsaki yayi ta jera sa a kai a kai kuma baccin ya ƙi zuwar mai,ɗaga kai yayi ya dubi agogon parlorn sai ya ga 2pm,..

Tsaki ya ja ya miƙe da ƙyar ya dawo ɗakin ya ƙure fifi da ido kamar ya koma parlorn amma zuciyar sa ta hane sa da yin hakan..

Dole ya hau gadon ya kwanta ya juya mata baya amma abin bai mai ba dan har shivering ya fara yi tsabar yadda yake ji.

Yana karkarwar har ya zo kusa da ita ya manne da ita..

Tana bacci ta ji kamar ana jijjiga ta sai ta farka a tsorace tana dube dube a hnkl har ta juyo bayan ta ta ga mutum na rawar sanyi..

A tsorace ta juyo baki ɗaya tana zazzaro idanun ta waje..

"Me...m..me ya faru..me ke damin ka"?ta tmby sa a tsorace ganin abin na yawa sakamakon raba jikin ta da nasa da tayi dan dama haɗuwar jikin nasu ne ya rage mai rawar jikin..

Yayi nadamar zuwar wannan rana a rayuwar sa abin kunyar har ina wannan ƙaramar yarinya ta ina zata iya da shi kawai sai ya fara kawar da kan sa dan kar ta gane halin da yake ciki ita kuma a tsorace ganin tsananin abin ta saka hannuwar ta biyu ta juyo da fuskar sa tana kallon sa kamar zata yi kuka ta ce

"Dan Allah me ke damin ka kalli yadda jikin ka ke yi baka da lfy ne ina wayar ka a kirawo likata"duk ta ruɗe sai ta fara yunƙurin nemo waya dan kiran dr..

Dakatar da ita yayi ta hanyar riƙo hannayen ta biyu da wanda ta ɗora a fuskar sa da wanda take laluɓo wayar ya haɗa ya riƙo cikin nasa yana girgiza mata kai..

Kallon sa ta tsaya yi ganin mutum na ciwo amma yana hana a nema masa lfy.. .

Murya a sanyaye mai nuna alamar halin da yake ciki ya ce

"Ki bar shi i just need ur help"!!da sauri ta matso gab da shi tana tmbyr sa

"Me zan maka ka"?nauyin faɗin abin yayi sai ya rumtse idanun sa kawai ya jawo ta ya haɗe bakin su..

Dumm!!gaban ta ya bada sai ta fara son raba kan ta da shi amma ya kuma damƙe ta yana rawar sanyi..

Mufida na tsaka mai wuya ta rasa me zata yi dan ta san irin hakan bai taɓa faruwa da ita ba sai yanzu,shin abinda ke shirin faruwa da ita daidai ne ko kuskure zata tafka,hawaye ne ya sauko mata jin wasu kalamai dake bin iska ke shigar mata kunnuwa daga bakin saheeb.

"Ki yi haƙuri

I'm sorry..

hawaye ne ya kuma sauko mata tana jin shigar rawar jikin sa jikin ta itama take ɓarin fargaba ya shige ta..

Kuma tmbyr ta yayi a karo na biyu sai da ta ja fasali tana wasi wasi sannan ta rumtse idanun ta ta kaɗa mai kai dan ta gama fahimtar manufar sa tunda ita ɗin ba jahila bace daidai gwargwado tana da ilimin addinin ta da na zamani kuma baya ga haka ta san duk inda mutani biyu suka kasance na bambancin jinsi toh dole hakan ya faru da su ko da soyayya ko babu..

Tana gama amsa mai ya birkita ta ya juya ta ƙasa ya zama yana sama..

Wasu irin abubuwa ya rinƙa yi mata dake gigita ta,gabaɗaya ya caza mata tunani tun Mufida na hawaye tana mammatsewa har ta sadauƙar ya kai tana fasa kuka.

Hawaye mai zafi ne ya zubo mata daidai lkcn da Marshall din ya shigarda ita jikinsa sosai Yana zura lallausan hannayensa cikin zallar fatarta daya gama zarewa tufa ahankali cikin wani irin salon nutsuwa.

Lumshe idanuwanta tayi tana qanqamesa tareda Jan nunfashinda 'duminsa ya sauka cikin wuyansa yasashi bude jajayen idanuwansa ya Dora akan fuskarta zuwa wuyanta dasuke farare qal.

Dawo da kansa yayi ahankali Yana furta sunanta cikin wani irin yanayi ya mayar da bakinsa cikin nata tareda matsota cikin jikinsa sosai suna Jan wani irin numfashi atare..

few minutes later

Yana kwance tana jikin sa yana sauke ajiyar zuciya tana hawaye ya lumshe idon sa yana shafa bayan ta har bacci ya ɗauke sa ita kuma ta ɗago da idanun ta da suka sha kuka suka gaji ta rinƙa kallon sa tana tuno abinda ya faru a tsakanin su,duk numfashin sa da yake fita tana ji a jikin ta dan a ƙirjin sa take..

Sosai ta nutsa cikin duniyar tunani da sakamakon abinda ya faru a tsakanik su,shin shi zai daraja kyautar da ta mai ko zai wofintar da shi?ina nata makomar take a zuciyar sa?zai so ta ya ƙaunace ta ko a'a?dama abinda take ji game da shi wani abin ne na daban ba shaƙuwa ba?anya in ya dawo hayyacin sa zai mutunta ta ya ɗaukaka darajar ta a zuciyar sa kuwa?.

Kuma kallon sa tayi tana tuhumar kan ta da anya tayi abinda ya dace kuwa ta hanyar mallaka mai virginity ɗin ta?zai so ta ya kuma ƙaunace ta kuwa?..

Wani abu ke fizgar ta game da shi a zuciyar ta wanda da tana cikin daidai ne tana iya tantance menene wannan abin wanda ba komai bane sama da So.

Hawaye ne ya zubo mata jin yadda baƙon abin ke ratsa zuciyar ta da ko wani gaɓa na jikin ta..

"Allah ka taimake ni ka fi ni sanin abinda ke yawo a zuciya ta ya Allah ka min magani"ta faɗa a zuciyar ta tana kuma kallon sa tana jin baƙon abin na yawaita a zuciyar ta..

Da haka baccin itama ya ɗauke ta tana jin ciwon jiki da kasala ko ta ko ina sakamakon rashin sabo...

#Mamuh*28*

_6am_

Shi ya fara farkawa daga baccin sai ya kasa tashi ya ɗan jingina da gadon haɗe da rumtse idanun sa,shiru yayi yana tuna abinda ya faru a jiya..

Da ƙyar ya tuno gabaɗaya sai ya juyo kan sa ya kai idanun sa gare ta..

Ƙure ta da ido yayi yana ta kallon ta yana jin wani abu game da ita a zuciyar sa da bai san matsayin abin ba..

A hnkl ya kawo hannun sa ya shafa fuskar ta yana admiring beauty ɗin ta,kamar kar ta farka daga baccin dan wani irin kallon kyakyawar mace dabai taba gani ba yake mata..

Ciki cikin zuciyar sa gani yake kamar ya mata fin ƙarfi amma a wani sashe na zuciyar sa yana samin musayar ra'ayi.

Numfasawa yayi yana matsowa kusa da ita yana cigaba da kallon ta hannun sa a fuskar ta yana shafawa a hnkl yana yaba ta a zuciyar sa..

Tmbyr kan sa ya hau yi a zuciyar sa yana ganin kamar shikenan girman sa ya zuba a idanun yarinyar kuma ba zata rinƙa tsoron sa ko shakkar sa ba but abu ɗaya da ya sani shine shi da ita sun zama abu ɗaya tun jiya ko ya so ko ya ƙi ta san shi ya san ta..

A sannu ya matso gab da ita ya kawo lips ɗin sa ya mata kiss a goshin ta sannan ya dawo ta gefen sa ya sauke mata wani a cheek ɗin ta sai a sannan fifi ta buɗe sleepy eyes ɗin ta ta sauke su a fuskar sa..

Kallon juna suke ta musayar sa ita da shi wanda basu san ma'anar sa ba su dai sun san kallon na masu wani irin illah a zukatan su amma basu san matsayin abinda suke ji ba..

Shi ya kuma matsowa kusa da ita ya ruƙo fuskar ta,yʏar taƙaitacciyar murmushi ya mata murya ƙasa ƙasa ya ce da ita

"Am sorry for last night"lumshe idanun ta tayi tana tuno abinda ya farun a jiya haɗe da zafin raɗaɗin dake ratsa ta a hnkl..

Ɗago fuskar ta yayi da hannuwan sa biyu ya matso da fuskar sa kusa da nata ya haɗe..

Ba shiri ta buɗe idanun nata tana zazzaro idanu waje alamar tsorata da tayi da situation ɗin da suke ciki..

Murmushi ya mata yana kuma maimaita mata haƙurin sa da yake ganin kamar ya zalunce ta..

Kafe sa da ido tayi tana ta kallon sa,alarm ɗin ɗakin ya fara bugawa..

Da hanzari ya kai duban sa ga agogon bango ai ko ya ga har 6:30am ya yi..

Ajiyan zuciya yayi yana mai duban ta haɗe da ɗago mata gira ɗaya yana girgiza kai itama sai ta ji kunya ya kama ta har asubahi ta wuce suna nan kwance..

"U caused this"!ya faɗa yana sauka daga gadon a hnkli,da mamaki ta bi shi da kallo yayin da yake shigewa bathroom a zuciyar ta take mamakin ta ina ta zama sanadiyar makarar su sallah alhalin shi ya mata wannan abin..

Kwafa tayi ta yunƙura itama zata tashi sai kawai ta ji zafin ya ƙaru take ta sake ƙara tana kiran sunan Ammy..

.

Saheeb dake tsaftace kan sa ya jiyo ƙarar muryar ta sai ya ɗan dakata yana nazarin ta daga bisani kuma ya fito ɗaure da towel ya tsaya yana kallon ta.

Tunowa da abinda yayi a jiya ya saka sa saurin ƙarasowa yana tausaya mata dan kusan mantawa yayi da cewa jiyan budurwa ya taɓa ba matar sa Muhibba ba shi ya sa yau ɗin ya tafi ya bar ta..

Taimaka mata yayi ta tashi daga zaunen da take,yana kallon yanayin ta abin tausayi ya raka ta toilet ɗin..

Duk wani taimako na gaggawa da ya dace mace ta samu bayan irin hakan ta faru,Saheeb ya ba matar sa Mufida a wannan makararren subahi,sannan shima ya tsaftace kan sa ya fito bayan ta riga sa fita tun ɗazu..

Sauya kayan jikin sa yayi sannan ya dube ta yana mai matsowa kusa da ita ya zauna yana mai riƙo hannun ta cikin nasa yana murmushi ya ce

"Zaki iya sallar a tsaye ko sai dai a zaune"?ƙasa tayi da kan ta tana jin nauyin sa sosai..

Ɗago kan ta yayi yana mamakin wai nauyin sa take ji akasin matarsa Muhibba halayyar Mufida a yanzu yana mai wani banbarakwai dan bai san da ita ba..

"Lkc na tafiya bamu yi sallah ba amsa min"sai kawai ta girgiza mai kai tabbacin a zaunen zata yi ba zata iya tashi ba..

Rabuwa da ita yayi ya tashi tsaye ya tada sallar sa ita kuma tayi a zaune har suka idar yayi adduo'in da ya dace ya shafa sannan ya dawo inda take.

Har ta fara baccin gajiya sai ya tsaya kallon ta bai san ya aka yi ba amma kawai yana jin nishaɗi in yana kallon ta..

Kasa tada ta yayi daga baccin sai ya tsaya ƙare mata kallo ganin baccin na mata daɗi in kuma ya tada ta maybe ta sami headache sai ya bar ta shima yayi joining nata a baccin ya kwanta kusa da ita bayan ya haɗa hannun sa da nata..

Peaceful sleep ya samu da ya jima bai yi irin ta ba a rayuwar sa abin ya mai daɗi ba kaɗan ba..

2hours later

Ita kaɗai ta farka ta ga kan ta saman gado sai ta fara tunanin ina ta kwanta last,a a hnkl ta juya ta ga ba kowa a ɗakin sai ita kaɗai.

Hamma tayi tana miƙa haɗe da tashi daga kwancen da take ta duba agogo ta ga ƙarfe tara har ya gota sai ta sauko daga gadon a sannu tunanin ta zafin na nan har yanzu,sai dai ta yi mamakin jin cikin kaso mai yawa zafin ya ragu sosai..

Hamdala tayi ta sauko daga gadon completely tana takawa a sannu har ta fito ta duba babbar parlorn babu kowa sai dai hancin ta na ɗan jiyo mata wata ƙamshi ƙamshi mai kama da girki.. .

Bata tsaya ɓatawa kan ta lkc ba ta nufi kitchen ɗin tana wondering wa ke girki a gidan dan ta san daga ita sai shi ba wasu..

Tsinkewa tayi ganin Marshall da apron har da hular apron ɗin a jikin sa hannun sa riƙe da babban serving spoon ga frying pan a hannun sa yana juye wani abu da bata san menene shi ba..

Bai san ta shigo ba sai jin mutum yayi kusa da shi dan haka ya juyo sai suka haɗa ido da ita..

Shi ya riga ta mgn ta hanyar tmbyr ta ya jikin ta,sai tayi shiru tana cigaba da kallon aikin sa da yake yi na girkin,a matse take da son sanin ko me yake girkawan amma bai bari ta fahimta ba dan yana gama juyewa ya rufe ya juyo gare ta gabaɗaya..

Ja da baya tayi kaɗan tana gaida sa sai bai amsa ba yayi shiru ya juya ya kashe gas cooker ɗin haɗe da juye ruwan zafin dake tukunyar cikin kofuna biyu madaidaita..

Duk tana kallon sa kamar tana kallon abin al'ajabi wai dama ya Iya girki ne ko dai yi mai aka yi ne shi kuma yake wani ɗaga kafaɗar shi yayi..

Out of blue ta mai wata tmbyr da sai da ya ɗan dakata daga abinda yake yi ya kalle ta sannan yayi wani murmushin dole kafin ya amsa ta..

"Can u cook"?sai ya kalle ta na wasu seconds sannan ya amsa mata da

"Uhmm"bata gamsu ba sai ta kuma tmbyr sa

"I don't understand uhmm"!!kallon ta yayi sai ya bar abinda yake yi ya tako har dab da ita ya ja ya tsaya kamar gunki..

Tsoron sa ta fara ji yana shigar ta sai ta ɗago kan ta ta kuma kallon sa da kyau nan take ya mata ƙwarjini sai ta kasa cigaba da kallon sa dole ta sunkuyar da kai ƙasa..

Tana ta wasi wasi a zuciyar ta sai ta ji numfashin mutum kusa da fuskar ta,ɗagowar da zata yi kuwa ta gan sa kamar zai shige fuskar ta.. .

Kallon ƙwayar idanun sa tayi a tsorace sai ya sakar mata da wani lafiyayyen murmushi da ya ratsa ta sannan ya riƙo kafaɗun ta a sanyi ya ce

"Eh...,na iya girki,are u satisfied"?saurin gyaɗa mai kai tayi tana kawar da fuskar ta gefe..

Murmushi yayi yana riƙo hannun ta cikin nashi haɗe da da jan ta zuwa kan kujerar kitchen ɗin yana mata tayin abincin.. .

Bata mai yanga ko jan aji ba ta amsa tayin nasa ta hanyar farawa da tea ɗin da ya haɗa masu sannan ta ɗau spoons ta fara cin abincin wanda frayed plantain ne da aka yi sa da ƙwai kamar balls aka yi scrambling aka soye sa..

Matuƙa ta ji daɗin wannan breakfast ɗin dan har cinyewa tayi bata sani ba sai da ta saka spoon ɗin ta ji babu komai sannan ta ɗago ta kalle sa shi da kwata kwata bai fi spoons huɗu da yayi ba yana da kallon yadda take cin nata.. .

Turo mata plate ɗin sa yayi ya mata alamar ta ci da ido sai kuwa ta ja gaban ta ta fara ci tana murmushi..

Tagumi yayi yana kallon ta tana bashi dariya sai dai ba girman sa bane yin dariya anyhow ba sai kawai ya murmusa yana cigaba da kallon ta har ta gama sannan ta dube sa ta tmby sa..

"Kai fah?me zaka ci"?ɗage kafaɗu yayi yana mata alamar bai sani ba,ɗan buɗe baki tayi da mamaki ta ce

"Da fatar ba ni na hana ka cin naka ba"?girgiza mata kai yayi ya ce

"Kin ƙoshi"?kallon sa tayi da murmushi shimfiɗe a fuskar ta ta amsa mai da eh..

Tashi yayi yana riƙo hannun ta suka bar kitchen ɗin zuwa bedroom ɗin su sai ya bar ta a nan ya shige toilet yana mai ce mata yana zuwa..

Zama tayi a wurin har ya fito da bathrobe a jikin sa ya nufi wardrobe ya nemo kayan sa as usual kaftan da hula..

Tana kallon sa yana dressing har ya gama wani sabon ƙaunar sa na fizgar ta a ran ta da hankalin ta..

Ƙamshin turaren sa ne ya ankarar da ita ya zo kusa da ita sai ta ƙare mai kallo sama sama sannan ta sunkuyar da kai ƙasa tana jin ƙamshin nasa na shigar ta..

"Zan ɗan fita i have a meeting to attaind misalin 4 zan dawo InshaAllah and don't bother to stress ur self akwai lunch ɗin ki a warmer ɗin nan a kitchen and about dinner,i will make a takeaway for us ok"!!gyaɗa mai kai kawai tayi tana yaba manly attitude ɗin sa,bata yi zaton hakan ba daga gare sa,tunanin ta na ta bashi ba zai wani bata muhimmanci ba amma yanzu ta ƙaryata tunanin nata dan ta ga zahiri...

Juyawa yayi zai tafi sai ya ga bata biyo sa ba sai ya ja ya tsaya yana kallon ta,bata san dalilin sa na tsayuwar ba sai dai ta ƙura mai ido har ya ce wani abin

"Babu rakiya"!?a ɗan kunyace ta tashi ta biyo bayan sa ta raka sa har bakin motar sa tana ɗan takawan a sannu dan tana jin zafin na bijiro mata..

Bayan tafiyar sa ta dawo ciki ta kwanta a parlor saman kujera,tuni kewar sa ya fara mamaye ta da sabon feelings ɗin da take ji game da shi..

A haka nan ta ɓannata ranar cikin kewa da begen sa har sai da ya dawo sannan ta ji daɗin gidan..

Tun wannan rana kusanci mai ƙarfi ya shiga tsakanin Marshall da matar sa kuma ƙanwar sa Mufida,babu dai wata abin da ta sake shiga tsakanin su na dangane da rayuwar aure irin ta ma'aurata,hasalima kula ta musamman da ban mamaki yake ta bata a ganin sa shi ta fi buƙata a yanzu fiye da komai...

****

Kimanin sati ɗaya kenan da faruwar wannan ɗin haka sati ɗaya cif kenan da fara special care da Marshall ke ba Mufida abin sai wanda ya gani,Ita kan ta da ta zauna

tayi doguwar nazari da tunanin kulawar sa gare ta sai ta rasa irin mizanin da zata saka sa akai sai dai a ƙarshe,ta danganta shi da so ne mai ƙarfi burin ta bai wuce kar ya bar ta tayi ta iyo cikin son nasa ba tare da shi ya biyo ta sun yi tare ba dan da son maso wani da ake mai inkiya da ƙoshin wahala gwara son bayyane ko rashin saka kai a soyayyar wanda bai san kana mai so ba..

Tana zaune tana danna remote tana nemar tasha ɗaya da zata kalla duk bata sami wanda hankalin ta ke so ba,sai ta ja ƙaramar tsaki gashi tun rana da ya fita bai dawo ba.. .

Kwanciyar ta tayi a kan kujerar ta lumshe idanun ta har bacci ya fara zuwar mata..

Cikim baccin da bai fi 15 minutes da ɗaukar ta ba ta ji an manna mata kiss a kumatu sai ta buɗe idon ta a sannu har ta gama buɗe su tayi tozali da nasa..

Da sauri ta tashi zaune tana gyara zama haɗe da yi mai barka da dawowa sai ya zauna next to her yana tmbyr ta ya zaman kaɗaici..

Buɗar bakin ta cikin shagwaɓa kawai sai ta ce mai

"I missed u"!murmushi ya mata ya kuma maida hankalin sa gare ta ya ce

"Really?did u missed me"?gyaɗa mai kai tayi kawai da niyyar zata bar wajen sai ta ji ya janyo ta ya rungume ƙam ƙam yana faɗa mata cikin kunne

"I missed u more"!a ran ta ta maimaita "!!sai dai tayi shiru bata ce komai ba..

Sun jima a haka kafin daga bisani ya raba jiki da ita yana kallon ta cikin ido babu ɗar ya ce da ita

"I want to spoil u tonight"ya kanne mata ido ɗaya abin sai ya mata wani iri ta kalle sa da ayar tmby sai ya gyaɗa mata kai kawai ya ɗago ta suka wuce zuwa bedroom ɗin su,ko me yake faɗa mata,sai dai murmushi da take ta yi tana ƙasa da kan ta abin mamaki abin sha'awa...

bayan wasu awowi

Kwance suke kan ta a saman ƙirjin sa babu kaya a jikin sa sai blanket da rufe su su biyun,wasa yake yi da hannun sa a jikin ta daga sumar kan ta mai daƈin taɓawa zuwa gadon bayan ta..

Daga ita har shi babu mai mgn sai shi ne ma mai sauke ajiyar zuciya idanun sa na kallon sama.. ..

"Was it painful"?tmbyr da ya mata kenan ta ƙyale sa tana mai ƙara shige masa jiki,all her life bata san wannan mijin nata zai zame mata abin farinciki da jin daƈi ba dan tun impression ƈin fari da ta bashi akan tsoho ne sai ta ji bata marmarin ganin sa amma yanzu kam ta tabbatar shi ne mahaƈin sinadarin rayuwar ta babu yadda za a yi ta cigaba da rayuwa a doron ƙasar nan ba tare da shi ba

A fannin Marshall ma kusan hakan ne,ɓoyayyen soyayyar matar nasa ne ke ratsa sa sai dai yana fargabar bayyana mata kar ya rasa ta dan bai gama yarda da tana son sa ba maybe shi kaƈai ke hidima da soyayyar nata ita bata yi..

Addu'ar sa Allah ya sa kar ya zama one sided love dan in hakan ya faru,tabbas zai yi wa zuciyar sa hukuncin yi mai abinda ya mai na barin sa ya kamu da soyayyar wacce bata san yana yi ba..

Jin numfashin ta ya ƙaru sai ya leƙo fuskar ta nan ya ga bacci take yi mai nauyi sai ya murnusa ya manna mata good nyt kiss a lips ƈin ta da goshin ta sannan ya ƙara manna ta da jikin sa ya rumtse nasa idanun ko bacci zai yi nasarar ƈaukar sa..

#Mamuh[8/6, 10:58 PM] Miss Xoxo: *30*

bayan sati biyu da kasancewar su anan yau fifi kwance take a jikinshi tana karanta mai wani English novel hankalin ta kwance sai data kawo kan tsakiyan labarin sannan ya dakatar da ita ta hanyar cemata, "we are going back home tomorrow" ajiye book din tayi a gefenta sannan ta kalle sa a nitse tace "ok Allah yakaimu lafia"ba yabo ba fallasa yace ameen saidai bataji dadin hakan ba ko kadan sabida tafara sabawa da sabuwar kwanciyar hankali da kalar soyayyar dayake nuna mata anan din duk dama tasan sababin sa tausayi ne,shikuwa saheeb yana kula da mood dinta daya canza sai yakai hannunshi kan tummy dinta yace,meye ne?yunwa?Tayi murmushi ta mike xaune a kunyace ta girgixa kanta...

" kodai kar mu tafi naga kin kara kyau komi yakara cikowa"nan yafi dadi ko...sai yakare maganar da irin tsigan wasan nan Murmushi medan sauti tasaki dan ita abun daria yabata dan tasan ina maganan nasa ya dosa Hmm 3weeks kawai ya isa tadau cikine abunda tafada kenan acikin zuciyar ta?tanata murmushi haka kawai taji burin samun hakan ya mamaye ta Tunanin hakan ta mugun sawa aranta

Kamar yadda yace xasu tafi goben baiyuba wani sati guda suka kara inda babu abunda ke ninkuwa a tsakanin su sai sassanyar so da shakuwa

Kullum in tana jikinsa sai yayi ta tsokanan ta da cewa..."seriously bakiga yanda kika canza ba, inaga idan munkoma gida zamuje hospital a duba munke" dage eyebrows dinta takeyi tace, "ok" bata iya cewa komai

Kwance take sannan tamike tace bari taje tafara shirya kaya tun yanzu shima mikewan yayi yabi bayanta yace su shirya kayan atare

Bedroom dinta suka shiga suka fara shirya komi a inda yadace bayan sungama hada kayan nata sai suka wuce nashi closet din shima suka shirya komi inda ya dace da la'asar bayan yadawo daga masallaci suka shiga kitchen tare suka hada dinner saidai tun a kitchen Fifi tafara jin wani irin sauyi acikin jikinta dakyar ta iya bari suka gama aikin batare da ta nuna masa alaman komi ba...

suna gamawa tayi saurin wucewa room dinta tashiga bathroom zatayi wanka nanfa tafara jin tashin zuciya jim kadan ta soma kwarara Amai mai yawa mai gajiyarwa Sosai gaban ta ya fadi...

Nan take taji wani irin bakon yanayi ya dulmuye xuciyarta

tsoro da fargaba wanda bata san dasu ba taji yana dirar mata take gabobin jikin ta yayi sanyi sosai ba abunda take tunawa sai ranan mutuwar ta,tsuguno tayi agaban toilet tana haki,wasu silent tears ne ke ziriya daga cikin idanun ta marasa ma'ana marasa dalili..

Takanji kamar Wani bangaren xuciyarta ya amince da sabuwar zabin da Allah ya mata na samun wata nitsatsiyar rayuwa da saheeb amma takan gujewa rudin

zuciya musamman akan soyayya dan ta riga tasan iya madakatan rayuwar ta ba wani boyayyar abu bane,mutuwa ne.

Ta dade anan cikin rudanin haka,batare da sanin me zatayi ba.

Jin shirun ta yyi yawa Marshall ya biyo bayanta da sauri yashigo bathroom din ganin yanayin ta kawai yafara jera mata sannu,uhmm kawai take iya cewa harya gama tayata wanke mata jiki yacire mata atamfar dake sanye ajikinta ya daura mata wani white towel ya daukota kamar wata baby yafito da ita yadireta akan gado,a daren ranan ba karamin wahala tayiba sabida aman da take tayi ya tsanan ta wani bin sace jikin ta takeyi tayi abun ta ta dawo..

Washe gari Koda tayi sallan asuba saita koma ta kwanta sabida baccin da batayi a daren jiya ba,har cikn ranshi ya damu sai Bai tashe taba sai wuraren 10am shima yatada tane sabida su isa gida dawuri da kanshi yayi mata komi yayi feeding nata da kyar tea kadai ta iyasha

Ciwon kai da bacci ya gama kashe mata jiki

saida yasaka Duk trolley dinsu a mota sannan yadawo ya daukota a owner seat ya ajiyeta hade dayin kissing dinta sannan yamaida door din yarufe yakoma yarufe ko ina nagidan sannan yabawa gate man keys din yashiga driver seat yatada motar sukabar compound din gidan

5pm yamusu a gida suna shiga cikin compound din gidan taji gabanta yawani fadi saidai takosa sosai taga twinnie dinta sabida she have missed her so much fiye da tunanin me tunani , a bakin apartment dinsu yafaka motar da kanshi yafito yabude mata door din motar tafito sai yace mata tashiga zaishugo yanzu uhm kawai tace sannan takai hannunta kan handle din door din tabude tashiga babban falon saheeb bakinta dauke da yar karamar sallama.

A Zaune ta tadda wata mata a daya daga cikin kujerun falon sanye take da wa'insu hadaddun riga da skirt na Atamfa English Aura wax wani irin qamshin turaren Arabians na tasowa daga cikin ahankali Yana gauraya palon.

ganin kyakkyawar dirarriyar mace a zaune cikin palon saida yafadar ma Fifi da gaba duk dama bata san ta ba,dan karamar ajiyar zuciya ta sake saita dake takarasa shiga cikin falon tanajin wani rawar jikin sanyi na shigarta da tsantsar tsoro da wani tauri nason danne mata zuciya ta kakalo murmushi harta karasa inda Muhibba din take zaune tana pressing phone dinta, "asslm alaikm Ina yini" shine abunda Fifi tace a taqaice tana sake kallonta cikin tsananin sarewa da faduwar gabanta dake tsananta,

Kallonta ta sake dagowa muhibba tayi cikeda da qare Mata kallo tana qoqarin danne abinda ke taso Mata gameda fifin sbd Babu tantama wannan itace mufeeda wadda ta auri Marshall dinta Wanda ya kasance nata ita kadai....itadai Fifi murmushi tayi dan she don't really care

Wucewa room dinta tayi Muhibba tabi bayanta da harara mai zafi.

#Mamuh

[8/6, 10:58 PM] Miss Xoxo: *29*

5am ta farka da face dinshi tafara tozali sosai ta wani kafeshi da ido tana karewa face dinshi kallo soyayyar shi na huda duk wani gabobin jikinta har batasan sanda tasaki wani murmushi ba hade dakai hannunta tashafa gefen face din nashi, abunda bata saniba tun farkon tashin ta shima yatashi sai jin hannun shi tayi akan nata hannun sai tayi saurin zaro manyan idanunta hade da sauke su akan face dinshi dayake aika mata da wani rikitaccen murmushi me ma'anoni da dama saurin rintsa idanunta tayi tana boye face dinta a jikin pillow,

a hankali yakai hannun shi kan lips dinta yana shafawa lips dinta yana daya daga cikin abunda yafi birgeshi da ita Duk dashi komi nata birgeshi yakeyi, cikin yar karamar voice dinta tace, "it's already late lokacin sallah yayi" lips din nata kawai yatsirawa ido sabida yanda take motsa bakin kamar ba daganan maganar tafito ba,

"I know" shine abunda yafada hade da daukan ta cak yakaita bathroom a tare sukayi wanka suka tsaftace jikin su still da zasu fito daga bathroom din daukar ta yayi yafito da ita yadireta akan gado, sannan yace mata

"pray nima zanje na shirya nayi nawa sallan" nodding kanta kawai tayi tana wasa da fingers dinta harya fice daga dakin saita tsinci kanta da sakin wani murmushi tabbas yanzu kam tagama yarda da soyayyar Marshall yagama kama Duk wani sashi na jikinta a hankali tamike daga kan gadon takarasa gaban wardrobe tasanya hannunta guda biyu tabude inda long abayas dinta suke tacuro wata purple color

me manyan design a gaba tasaka hade da daukan hijab sannan takarasa ta dauki prayer mat tashinfida ta tada sallah,

Bayan 30min Marshall yashugo dakin zaune ya tadda ita akan prayer mat tana azkar kallon ta kawai yakeyi yanajin wani shauki akanta he loves her so much saida yakusan 5min a tsaye sannan yakarasa shiga cikin dakin yamaida door din yarufe karasawa yayi inda take hade da samun waje a bakin gado yazauna yana kallonta atare suka shafa addu'an sannan ta dago takalle shi suka sakarwa juna murmushi cikin yar karamar voice dinta tace

"Good morning" saida yakai hannun shi yakama mata nata hannun sannan ya amsa da, "Morning mon amour, how's ur night?" sosai taji dadin sunan daya kirata dashi shafa tafin hannunta daya keyi shiya hanata amsawa dawuri dan haka saida ta dauki lokaci sannan ta amsa da

"Alhamdulillah dafatan kaima katashi lafia" takare maganar da dan dagowa tana kallon shi ta wutsiyar ido,

bata ankara ba saijin mutum tayi ya sunkuceta yayi kan gado da ita saida yakwantar da ita sannan yacire mata hijab din dake sanye a jikinta ya ajiyeshi a gefe guda sannan yacire mata long abaya din a cewarshi abayan zata takura ta itadai idon ta yana rufe har shima yacire nashi jallabiyan ya ajiye agefe sannan ya janyota zuwa jikinshi hade da rufe suda blanket, yafara wasa da long hair dinta dayasha gyara harshen shi yakai cikin kunnanta yana latsawa a haka wani baccin yakara daukan ta,

8am suka farka a tare suka shiga bathroom sukayi wanka half gown tasaka mara hannu milk color saita zubo da gashin kanta har gadon bayanta sosai tayi kyau Duk dako powder bata shafa a face din nataba sai kalolin perfumes data feshe jikinta dashi tana gamawa tawuce kitchen cikin 30min tagama hada musu abun breakfast,

Arabian meal tahada musu Wraps, sandwiches and manakeesh tana son kalolin abincin larabawa sosai shiyasa ta iya dukkan nau'o'in abincin su, anan dinning table na kitchen din ta jera komi tana juyawa zata fita daga kitchen din Marshall nashugowa sanye yakeda kananun kaya black jeans da white T-shirt yayi kyau sosai har batasan ta kafeshi da idanu ba saida yakaraso gabda ita sannan tayi saurin

sunkwi da kanta tana sakin murmushi me cike da ma'anoni dayawa ita kanta ta shaida Marshall hadaddan namiji ne ita kanta tasan tayi sa'an samun gwarzon namiji kamar Marshall tana kuma jin shauki sosai a kansa,

Hannun sa yakai kan face dinta yashafa hade dacewa

"You look so cute Mon amour I like ur dress" saida takara murmusawa akaro na biyu sannan tace, "I like urs to" sannan tayi saurin karasawa taja kujera tace, "Seat" baiyi mutsu ba yakarasa ya zauna saidai Duk abunda takeyi idanun shi yana kanta harta kammala serving dinshi ta ajiye mai komi a gaban shi sannan tasaka nata taja kujera ta zauna,

saida yakalli Breakfast din sannan yakalleta sai yasakar mata murmushin gefen baki sannan yace, "so you know how to cook Arabian meals?" saida takai cinnamon tea bakinta tadan kurba sannan tayi nodding kanta tace, "Arabian Meal yana daya daga cikin favorite dina I will cook Arabian meal for dinner if you like it" tayi maganar da dage mai gira saidai kanta a duke yake,

"yeah I like it bakisan ina son abincin larabawa ba" hira sukeyi har suka kammala cin abincin a tare suka wanke dishes din suka maida komi inda yake sannan ta goge kan dinning din, yana rike da hannunta suka fito daga kitchen din a three seater suka zauna sai tayi pillow da cinyar shi suka fara taba hira kadan kadan anan yake kara sanin halinta itama tuni tagama fahimtar halinsa sabida anan zaman da sukayi ta fahimci yanada dadin zama sosai kuma baida matsala,

A cikin yan kwanakin wani shakuwa ne me karfi yakara shiga tsakanin su dan tuni Fifi tazubar da Duk wani abu tafara nunawa mijinta tsantsar soyayya shima anashi bangaren hakane dan har mantawa sukeyi da akwai wa'insu mutane a duniya bayan su sabida zallan soyayyar dasuke nunawa junan su.

#Mamuh[8/12, 12:04 PM] Nadady: *31*

Turo kofar tayi a gajiye tana maida numfashi Bata jima ba ta nemi waje a gefen gadon ta xauna a kasale,fuskar matan ne yaki fice mata arai wani irin yanayi ta tsinci kanta a ciki Wanda batayi tsammani ba.

A Sashen su ammy saheeb ya jima by 8pm kusan kowa ya fito za'ayi dinner Allah Allah Fifi take ta samu damar ganawa da su ammy gashi har cikin ranta take matukar jin muradin ganin hamidarta.

Ayanzu ji take kamar Zuciyar ta yayi sanyi,wani sashi daga abubuwan da suke yawan damun ta game da tarayyar su da hamida ba laifi sun ragu mata,bathrum ta shiga tayi wanka kasalan data ke yawanji shi ya sa ta sanya doguwar Riga pure red material and masa design da wild rose hipup belt wanda ya Dan sake ta yau batayi wani kwaliya sosai ba

Babban sashen gidan ta nufa inda Tasamu duk an zazzauna a dinning wani sanyi ne ya mamaye Zuciyar ta ayayin da take kallon su kusan kowa fuskan sa dauke da murmushi musamman hamida da Khalid Wanda Babu wani Abu daya rage ayanayin su na nuna tsananin so da shakuwa dake wanzuwaa a zukatansu.

Purple atampa ta sa Mai kyau Wanda ya dau kalar fatan kusaan kala daya da tsadadiyyar yadin vice chair man Wanda ya amshe jikin Khalid ya masa kyau sosai Shima.

Agefe da shi ammy ne da hajja wani

murmushi me sanyi ne ya kufce mata ji tayi kamar taje ta rungume su Dan bakaramin zazzafan kewarsu takeji aranta ba,a hankli ta maida kallon ta kan saheeb Wanda kallo daya ya isa yasa kasan bai Saba zaman cikin su hakanan ba dago kanta ke da wuya caraf Suka hade idanu da muhibba agefen sa irin kallon datayi mata yasa tayi saurin dauke kai gyaran murya tayi sannan ta karaso ciki a yanayin fara'a da basarwa.

" Salam alaikum"

Tace da muryan ta na da can Wanda shi kowa ya fi Sanin ta dashi, hamida ce ta soma juyo ta kalle ta cikin dakakkiyar murmushin da ya kufce mata baxata

Ammy ce ta soma mikewa sannan Hajja tabi bayan ta wani rungumar ta sukayi atare ayayin da suke gaisawa

Fifi Fifi tuni waje ya kaure da sabuwar surrutayya.

Saheeb ne kawai baice uffan ba"fifi kuwa har ta xauna Bata wani samu cikakkiyar nutsuwa aranta ba Dan rasa gane inda zata ajiye tunanin tatayi,wani bangare yanaga hamida wani Yana ga mijin ta saheeb da matar sa dataa Sha uban kwalliya tana serving kowa a nutse wacce Babu alaman kasawa ko yaranta a fuskan ta.

Normally wajen ya dau shiru kowa ya nitsu ya maida hanklinsa akan dishes dinsa ana hira sama sama,Banda hamida data fiye bada hanklin ta a kan Khalid kadai Dan in ba shi yayi magana ba Sam Bata cewa komai.

Ganin Fifi Ras fiye da yanayin yadda suka bar gidan yasa su ammy shagala,waccan yanayin zazzafan so da nuna tsananin kaunar da kulawa da suka Saba mata shiya ke fallasa kansa a duk sanda sukayi magana awajen

Babu tantama tun zamar su anan hajja take ta mata tambayoyi da wasan gata irin na tsoffi sakalci da kauna duk da ma Fifi tana basarwa Amma hamida ko ajikin ta,gani take inda sabo to ta Saba muhibba ce Abun ya mata banbarakwai sabida ji kawai tayi Abakin hamidar Amma Bata tabbatar ba Sai yau dataga cewa kusan hanklin kowa akan dinning din akan Fifi yake

Hirarrkin ma It's all about her, duk abubuwan da fifin tayi sabo sanda basa Nan seda sukaso suji duk dama ita fifin tana hankalce da furucin ta na rashin son bayyana wani Abu daxai sake kawo wani tsabanin fahimta tsakanin ta da yar uwantan.

hakan yasa taki Jan magana kwata kwata baifi Tace eh aa ba ko ma tayi dariya ba.

Duk da hakan ba shi ya Hana hamida Sanin cewa fahimtar juna ya samo mafaka tsakanin su da saheeb ba Allah Allah take Subar wajen ta samu ganawa da muhibba Dan tun xuwarta gidan suke kulla maganan a tsakanin su batare da kowa yasani ba

Tun ranar da su ammy suka sanar da muhibba cewa tana da kishiya Hamida ta gane cewa muhibbar mace ce me tsananin kishi musamman reaction din ta nuna lokacin da akace mata tare sukaje hutu

Kwanan muhibba biyu agidan Amma Babu Wanda ya gane kanta face hamida da tasanya mata idanu tana karantar abubuwan dake wanzuwaa a zuciarta na fushi da tsananin kishi hade da boyayyen damuwa.

A da can ko gaishe da su ammy Bata son fitowa tayi,tanan ne hamidaa ta shige ta da sigar nuna cewa tana tausaya mata duk dama muhibbar Bata amshe ta lokacin guda ba Sanin cewa ita taawainiyar kishiyaartan ne

Amma daga bisani hamidar ce ta wayar Mata da kai,ta cusa mata wani rufaffiyar ra'ayi me shiga har Zuciya a dunkule...

Duba da cewa Auren rufin asiri akayi ma Fifi da saheeb yasa su ammy basu bude ma muhibba komai da komai ba Sabanin nuna mata da akayi cewa Auren dangi kawai aka musu wanda aka barshi a matsayin Qaddara ne ya hada.

Hamida kuwa fede Mata biri tayi har wutsiya tayi cikin salon yaudara sanda ta cimma wani boyayyen manufarta.

Ta fara ne da nuna Ma muhibba yadda kowa

Da komai yake komawa na Fifi,ta hanyar Bata labarin yadda kowa agidan yake daukakata ake Fifita ta ake son ta fiye da komai.

Tace dama wannan ciwon shine makamin ta wajen kwace komai na jin dadi a ryuwar wani nikaina danake yar uwanta Saida 'ta kwace min nawa rayuwar,na wajen iyayen mu kakanin mu kawayen mu ke har mijina ma Saida taso ta juya masa kwakwalwa,arayuwa Fifi tafison kowa da komai ya zame nata ne ita daya

..koda akayi Auren ai mijinki bai kwatanta cin amananki ba Ina lura ya kama kansa duk dama yasan lankaya masa ita akayi,amma yarinyar Nan waini take so tayi amfani Dani Dan cimma manufarta akan saheeb sabida na nuna musu cewa na gano mugun halayyarta na son Kanta da son Zuciyarta,inkina so kiga munafukar mace inkika hadu da Fifi kinsamu kankat.. duk yadda naso ace su ammy sun gane menake nufi Amma sun ki, gani suke kamar karya nakeyi bansan meye asali a Zuciyar Fifi ba,ba gashi Nan a bayyane ba?kawai tasan nafi Karfin ne shiyasa take

nuna kamar tayi nadama but ni nasan da ciwon Nan nata take harin gamawa da mijin ki Shima.

Ko ke baki gane bane? in har dagaske akaina take cikin wancan damuwar da Zama zatayi Dani Dan In Yafeta bawai tace mijin ki xata bi wani waje ba,to wayasan Me taje ta aikata Masa ko wani irin karya ta shimfida Masa Dan ta shiga rayuwar sa ta janye ra'ayin sa makanta ita daya.

Kedai kiyi hankli da ita ni kadai nasan halayyar fifi daga ta cimma burin ta akan saheeb to babu me sake kallon ki ko jinki,sannan a gidan nan for 23yrs ana nunamin cewa fifi bata lefi bata kuskure kuma duk abunda take so nata ne, ina guje miki shiga kunci da damuwa irin nawa,compare to me aike tamkar bare ce in har anmin to kowa ma za a masa,dan haka bana cire tsammnin cewa duk wata mace me tsananin kishin mijin ta kamar ki zata iya rayuwa a tarkon fifi.

"Nice tawainiyatta kuma nice nafi kowa sanin komai akanta ln kina son kanki da lpy sai ki bani hadin kai wajen kwaco yancin mu da farincikin mu,nikam na kwace miji na a tarkon ta saura ke,in bazakiyi wani abu ba wannn ya rage miki.

.

Wayannan munanan maganganun Muhibba take juyawa aranta ayayin da dukanin hanklin ta gaba daya ya koma ga kan su fifi da ammy da shikansa saheeb daya tsoma baki a hirar su ta yanxun dake hirar ya shafi lapiyar fifin ne

Banda boyayyen kallon kallon da sukeyi a sace Wani shiru muhibba tayi tana kan fahimtar gaskiyar maganganun hamida data sha gaya mata akan fifi, ta dade cikin wannan yanayi

can tayi boyayyar ajiyar xuciya ta tabe baki a hankali bata ce uffan ba.

Fannin fifi kuwa tun Daga yanayin bayanan saheeb da tambayoyin da ake mata tana amSawa Khaleed ne ya soma fahimtar cewa ciki ne ya shige fifi.

Bayan sun koma sitting room duka akan za'ayi musu nasiha Cikin salo sanda khaleed yasa kowa ya fahimci hakan su ammy da hajja ina Kasaka da murna,alkwarin so da kulawa babu wanda basu bayyyana shi ba fifin dai batace

uffan ba ayayin da saheeb ya sulale ya bar wajen dan dama shikam ya gane abun tun jiyan datake ta laulayi.

Yana barin wajen muhibba tabi bayansa

Ita kuwa fifi a Duk murnan da akeyi hanklin ta nakan yar uwanta ne,sakamakon wani bangaren zuciyatta yana alfahari da cikin wani kuma yana kinsa da jimamin kada yar uwan ta ta sake alakanta hakan da samun fifikon da zai sake haddasa wani kiyayya da damuwa aran yar uwan tan.

Tana cikin wannan tunanin hamidar ta mike bayabo ba fallasa tayi musu sallama,a gurguje fifin ta mike tabi bayanta tanata kirar sunan ta gasunan daf da daf amma hamida ta sakai bata juyo ba bare ta amsa hakama ta rufe kofarta agaban idanun ta batare da ta ce mata uffan ba.

A sanyaye fifi take kallon kofar wani karayar xuciya da gabobin jiki su suka lullube ta sai tayi shiru bata dawo hayyacin ta ba sanda taji gyaran muryan khaleed ta bayan ta

Yace yadai Mufida baki shigaa ciki bane?

Matsawa baya kadan tayi cikin boye damuwarta tace

"ah'a yanxu na fito..im just abt to leave.

Ajiyan zuciya ya sauke

yace "ohh to shikenan..

kwayar idanun su suka hada atare tayi saurin kawar da nata gefe kureta da idanun sa yayi yanata kallon ta bakinshi da zuciyar sa cike da ababen cewa

"gudnite.. ta furta slowly batare da ta jira amsar sa ba ta bar wajen da sauri bayan ta yabi da kallo yana me lumshe ido can ya sauke ajiyan xuciya ya shiga room din su.

Kwance ya tarar da hamidar idanun ta a lumshe tayi shiru dan haka ya shirya da sauri shima ya biyota kan gadon.

Wani wawan runguma da zafafan smooches ya bata wanda yasa tuni suka dulmuye juna cikin shaukin so da raya daren su cikin kyakwar shakuwa

Can Bayan sun kimtsa ne yake tambayarta ko dagaske sun gana da fifin,eh kawai tace masa batare da nuna masa komai ba.

Yasan matsayin fifi a zuciyar hamida dan haka yaso yaji ko maganan cikin ma ya dame ta amma haka fir taki ta bayyana masa komai.

Fifi kuwa tana barin wajen su ammy suka rike ta da sabuwar hira da tarairaya dan samu tayi har hajja ta kira daddyn su tana kai masa gulman

Sosai tayi farinciki dan acewarta murnan ta kashi biu ne,musamman in ta tuno da yadda akayi auren,da tunanin cewa yau ko fifi ta mutu abunda ke cikinta zai zame musu sassaucin jin zafin rashinta a duniya da zasu zo suyi

itama fifi karban wayar tayi tafi awa suna hira me dadi da shi su hajjan na tayasu musamman da kowa ya san cewa by now saheeb yana tare da muhibba ne so Anan site dinsu ta kwana.

****

Bangaren saheeb

Suna shiga dakin muhibba ta hade rai ta kau da fuska tayi zaman ta a bakin gado batare da tace masa uffan ba,kallon ta yakeyi direct dan gaba daya alamomin fushi da zafin kishi sun bayyana a fuskan ta amma dake halayyar sane kamewa da shan qamshi sai yaki yace mata uffan

shima,wani zaman kurame akayi a dakin shiru ne ya ratsa tsakanin su ko minti biyar basuyi cikin hakan ba ta mike fuuu ta wuce bathrum tana me buga kofar da dan karfi kayan jikinta ta sauya zuwa towel ayayin da kuka me tsuma da cin rai ya kufce mata kan gwiwarta ta sauka tana zubda hawayenta sosai tana kuka tafi awa guda a hakan

saheeb dake zaman jiran fitowar tan Tun baijin sautin kukan har ya tsinkayo Da kamar bazai je ba can dai ya daure ya kai kansa bakin door din bayabo babu fallasa ya kira sunan ta amma ko sau daya bata kulasa ba

Sunfi mintuna talatin ahakan har abun ya dame sa sosai dan dolen sa ya Soma halayyar maza na rarrashi wanda sam bai saba ba.

Wai meke damunki haka ne?

"Can u please come out lets talk?

Wai miye hakane muhibba,i hate wen u act childish...open the door

Tanajinsa tayi shiru abun ta Da can kamar zata amsa sai kuma ta tuno da cewa ranta a matukar bace yake a yanzu,tana bukatar nitsuwa da samun kyakkyawar ganawa da hamida kafin ta san matakin da zata dauka me gaba daya.

Jin har yanxu bata kula sa ba yasa ya harxuka tsaki yaja ya bar mata dakin ya nufi nasa yayi kwanciyar sa se can ta fito ta kimtsa ta hau gadon ta ta kwanta abunta

Juyi take acikin ranta cikin tunani me xurfi babu wani abunda take s akawa face yadda zata bullo masa da Shi da matar sa ta hanyar da zata fi iya cimma burin ta cikin sauki.

#Mamuh

[8/12, 12:08 PM] Nadady: *32*

Washe gari da safe koda ya dawo duba muhibba ya samu kofarta a kulle Tsaki yayi Bai sake dawowa Nan ba direct ya nufi sashen su ammy ya gaida su tare da duba lapyar Fifi wacce take Nan lafiya lau Dan bakaramin kulawa da ita yau akayi ba tsaban zumudi har sun shirya lokacin da zasu je asibitin Dan Khalid yace zai duba ta acan.

Suna ta shirmen su Dan haka Bai wani jima anan ba ya fice da sojojin sa daganan basu sake jin duriyar sa ba itama fifin anan tayi zaman ta saidai duk Abunda ake Mata na nuna tsaninin kula da gata Bai wani dame ta ba Ayanzu ba.

By 4pm suka dawo daga asibitin bayan Dan karamin yawon bude Ido da sukaje dukan su su ukun ita da ammy da hajja, khaleed yana asibitin sa ita Kuma hamida tana gida tare da muhibba Babu Abunda sukeyi yau Sai kulle kullen su na Sanin Abunda zasuyi akan fifi

Kuma duk tarayyar sun Nan Babu Wanda ya sani sabida hamida takan nuna ma kowa cewa ita Sam Babu ruwan ta da rayuwar kowa face na mijinta ta khalid Dan haka wani bin ma ko cikanki Bata cewa muhibba a fili.

Itaman muhibbar dake ba sarar su bane ko a shekaru Sai rashin kula junan sun Bai Ba kowa mamaki ba Amma a zahiri kusan hamida ce me asalin dorata akan gayyar kishi dake tsokalarta a xuciyarta

Tsaf suka kammala hade haden su ayayin da kowacce ta koma site dinta tana abubuwan daya dame ta.

fannin fifi kuwa a fili ne kawai take yawan murmusawa Amma aranta wani uban kadaici takeji me nauyi She really feel alone,har cikin zuciyarta take jin kewar rayuwarta na da can Wanda Babu fargaba ko kiyayya rayuwar da Bai nisantar da ita da soyayyar yar uwanta ba

Bayan ta idar da ishai Wanka tayi a site din hajja ta sauya shiga xuwa simple white Milano gown marar nauyi ta sakaya hular sakanta shima white wani boyayyr damuwa rashin jin saheeb tun safe shiyake cike mata kirji Yana damun ta har kwakwalwa tanajin zafin Abun Yana shiganta a hankali

Numbar San ta dada dialing daga bisani ta jefar da wayar tabi lapiyar gado tana me lumshe idanun ta sosai Jin kamar baxata iya dauriyar ba ta bude Tex messg ta soma rubuta mashi Sako'

Hy can u please come home Ina son ganin ka,Sai ta goge ta rubuta Salam,kana lafiya pls wen r u coming back? ta rubuta messages yafi sau goma tana gogewa

gaba daya sai ta rasa me xata ce Wani baccin baxata ne yayi awon gaba da ita da wayar a hannun ta hajja ce ta rabata da wayar Bayan ta Gama karance sakon ta na karshen da ta rubutu Bata goge ba murmushi tayi sannan ta gyara mata kwanciyarta.

Wajajen karfe 10 saura saheeb ya dawo sashen sa ya nufa straight ya kimtsa kansa cikin kananan kaya sannan ya taho ya same hajjan dake yau ita daya ya samu tana zaune ta toshe da medicated glass da qur'ani a hannun ta tana dubawa.

A ladabce ya rusuna ya gaida ta ta amsa Masa cikin faraa,duk daama tasan baxai wuce aiki ne ya Sha kansa ba Amma sanda tamai tambayar hakan..

Ce mata yayi muhimmin meeting ne ya ritsashi yau da ogogin sa ko lokacin kansa Bai samu ba

Tace Allah ya bada sa'a yace amen zai mike yay waje ta sanar da shi cewa Fifin tana Neman ganin sa Amma tana bacci ayanzu karamar aajiyan Zuciya ne ya kufce masa tuno da condition dinta Sai baice uffan ba yayi murmushi can yace abarta tayi baccin ta zai zo ya dubata gobe.

Sallamar su ke da wuya ya nufi dakin muhibba Wanda ya same shi a wangale Abun ya basa mamaaki Sanin cewa Bata Saba hakan ba

Muhibba mace ce Mai strict mind Ita irin matan Nan ne da suka taso cikin Sanin aikin da ke gaban su mace ce kamar maza,kusan Kowani lokaci inta xauna tunanin Abu daya ne ke xuwa a mind dinta wato business din mahaifin ta Daya Dora ta akai tana juyawa,saidai ayau labarin Tasha bambam dan kuwa bakaramin tsananin kishi ta sa aranta game da Fifi ba

Gani take Kamar ita daya ce macen da kawai zata iya rayuwar ta da saheeb batare da rayuwarta Dana familynta ya ruguje ba,ayanayin data ji labarin Fifi Sai taji aranta Sam Bata bukatar wacce zata zo ta mantar da saheeb tsawun rayuwar da suka Gina na hakuri da juna da burin ta na son xuciya data Dora Auren nasu akai.

Dan jitayi Kamar ma baxata sake iya komawa aikin ba Kuma da ta rasa saheeb wajen fifi kamar yadda hamida ta fada gani take gwara duk Abunda xai faru ya faru.

Can cikin wannan tunanin taji sallamar sa akanta,mikewa tsaye tayi batare da ta amsa ba ta kallesa cikin wani yanayi Mai nuna zafin fushin dake aranta..

Inba dan burin mahaifin ta ba da saheeb shine Abu na farko a rayuwarta

Dan bakaramin kaunar sa takeyi ba

How can she loose him?tana furtaa hakan aranta ta dada harde rai batare da ta kulasa ba ta taho xata wuce ya jawota baya suna kallon juna yace

Nayi sallama baki amsa ba and where are you going?

Kanta ta kawar gefe ya bata rai yace pls..bana son shashancin muhibba wai meye aka Miki ne?

Tun dawowarki ma munyi magana ne

Hannun ta ta fauce anashi slowly ta kallesa da wani irin yanayin dayaji Babu dadi aransa Sai taja baya dashi kadan tana maida ajiyan xuciya"ta masa kallon me zance maka?

Can Tace ok happy married life..end.

Xata fixge jiki ta fice ya dawo da ita a Dan fusace yace ohh dama Abunda ke damunki kenan?su ammy basunyi Miki bayani ba?what....bai kareba ta tsare sa

"Ba su ammy nake aure ba saheeb bazaman su nakeyi ba meyasa Kai bazaka tabayin Abun da ya dace arayuwanka ba

U asking me to act matured?baka taba gayamin kayi auren soyayya ba u Neva Care abt my feelings Mr matured.

A fusace ta furta hakan cikin bacin rai fuskanta a matukar bace

Sai ya Bata ransa sosai yayi shiru

..kuka me sanyi ta fashe Masa da shi cikin kukan Tace dama nasan Daren dadewa hakan xai faru Amma ba damuwa ta bace dan kanuna gajiyar xamanka da ni cikin sauri haka

Jajeyen idanun ta ta Dora anashi muryan ta na rawa sosai tana tsuma

Saheeb xaka haifu da wata mace?tun kan ya amsa tace oh well congrats,irin dariya Mai cin rai din Nan ta karashe da shi alokaci guda tana kan tuntudo da hawayen ta masu rauni..tace

Ashe har xaka iya min hakan saheeb?mekake Shirin aikata ma rayuwata

A dame Yace muhibba menayi?nima fa cemin akayi na taho za'a min Auren nan I Neva even know anything wai meye haka?

Tace Babu..Auren da baka sanda shi ba gashi har xaka haifu ko? nikuma matarka ka hanani haihuwa,saheeb u encourage me

To plan na dauka rashin Samun nitsuwa a matsayin muna aurata shine dalilin mu Ashe Abun ba hakaa bane,Abun Isa ne,fifiko ne da nuna bambancin dangantakar da ke tsakani Wanda ni bani da shi dakai

A hankli Ya furta ya subhanallahi,u completely misunderstood me muhibba duk abunda kikagani qaddarar Allah ne kawai I didn't plan anything

Tace yes. U didn't nagane ai,anawa fannin ne ka tsara komai amma Kuma ana wata Allah aka barma ya tsara

Yayi firzan iska

" ya kike magana Kamar bani dake muka tsara maganan haihuwar mu why r u blaming me now

Tace,eh nidakai mun tsara hakan amma ai haihuwa zakayi da wata yanxu kuma gani nake Kamar nawa mahaifar ya same matsala saheeb pls u can't do this to me

"Kasan Auren ka baxai dameni ba Abunda ya dameni shine mahaifata da kabada gudumawar muka lalata sa.

I can't bear seeing my life childless musamman in wata mace xata haifa maka da a duniya kasa hannu ka karba.

Wani runtse idanun sa yayi yana jin tambayoyin ta suna fitowa cikin rawan murya a raunane

"What abt me?bazan haihu ba kenan?ka cuceni kenan?..kuka me Karfi ta rushe da shi sanda ya ji gaba daya hankalin sa ya tashi sosai xuciyansa na bugawa.

Babu irin maganganu marasa dadi da Bata furta Masa ba,gaba daya kansa ya daure ya rasa lefin sa ne ko nata,har kasan xuciyan sa ya soma jin Babu dadin abubuwan datake furtawan

Yasan dai da can sunyi cewa baxasu haihu a gantalallen rayuwar da sukeyi ba Kuma yasan a tare sukayi shawaran yin planning amma Bai taba kawowa aransa cewa zai mata wani illa ba

Dake ma cewa tayi tana ganin mahaifan ya lalace Sai ya sa aransa cewa ai bata tabbatar ba Dan haka yaki ya kula Abun sosai duk dama Abun ya taba sa sosai

Musun wazai dauki laifin yaki ci yaki karewa a tsakanin su ayayin da muhibba take nuna Masa cewa ya nuna mata rashin adalci butulci da warayya ne karara.

Kada kansa kawai yayi ya ja tsaki ya wuce ya dawo dakin se sai can around 12 ya nufi waje domin duba dakin fifin take dake baccin wuri tayi se ta farka Fitowar ta kenan daga bathrum daure da towel Tana shirin tsame jikin ta da Shike baiyi sallaman da karfi taji ba a tsorace Ta sake towel din Yayi kasa Baki daya... Ayayin da yayi sauri ya karaso gaban ta

Kafin tayi wani kyakwan motsi Ganin sa tayi agaban ta shima a durkufe.

,..wani kunya ne taji ya lullabe ta,sai tayi saurin kare kirjin ta tana mai rusunawa da kyau itama zata daga towel din Sanyin Dayan Hannun shi taji akan nata tukun ta lura ashe Hannun nashi ya riga nata isa kai.

.

Dik da haka sai tarike towel din itama,Ji tayi ta kasa dago kanta bare su hade

ido"kyawawan White hazel eyes dinsa ya dago ya kalle ta alaman ta sakar masa..

bata yi musu ba ta sake ta mike tsaye,jikin ta har rawa yake dakan sa Duk sai taji ta rasa yadda zata yi, gaba ne ko baya zata juya masa ta inda bazai ganta ba,..

Wani nauyin shi take ji Ahakan hannu ta sa ta rufe idanun ta kawai tayi shiru Shikuwa mikewa tsaye yayi da towel din a hannun sa

Wani miskilin murmushi yake yana yabin surar jikin ta da ido

,.kusa daf ya matso ya warware shi tsaf kamar wanda zai daura mata,sai ya zago dashi tun daga kan waist din ta da duka hannun sa dake rike da towel

din,...wani lumshe ido tayi tana shakar qamshin sa...

Lumsashun idanun nata ya kare ma kallo tukun,ya tallafo ta kusa da shi"A hankali ya dora palms dinsa agadon bayan ta ya shiga shafowa daga kasa xuwa sama wani lalatacen nishi ta sake mishi 'a dan rude tace Pls ka bari"..

..dumin hannunsa akan sassaynr jikin nata ke isar mata salon sakon shi har cikin jinin ta

A hankali yake round da fingers dinsa A bayan ta har ya dawo kan kugun ta bata hankara ba taji hannun shin dake yawo anan din ya sake mata dan karamin tickles mai dadi wanda ya sa ta dan zabura ta sake hannun ta dake kare kirjinta

Shima cikin wani nau'in kallo mai kashe jiki ya Dada matso ta fuskan sa sai suka hade ido cikin ido "sun kai 5mints a haka Suna kallon Idanun juna...

hannun ta dafe kan kirjin sa girar sa ya daga mata fuskan sa dauke da wani salon murmushi kanta ya kau gefe tayi Tsiririn ajiyan zuciya bata san lokacin da ta mayar masa ba..

Shall we dress Up,ko yau Ranar ganina ne?

Dan zumburo mai bakin tayi ta sake runtse idanun ta Tace 'ohh,.. ni dai katafi. ..Bai ma ji ba cos can kasan makoshi ta fada

hannun sa ya dora duka biyu biyu ya tallafo fuskan ta yana kallon ta

,..'dada runtse idon tayi din Bata so ta cigaba da hade ido da shi..

"Open... Ya fada yana mai hura mata iska a fuskan nata baki daya...

Wani irin yarrr take ji na bin jikin ta...,bai daina ba har saida long eye lashes din ta suka fara shaking

Idanun ta suna struggling zasu budu dan kansu

Dan karamin kiss ya dora ma gallant lips din ta, Hade da towel din gaba daya

Sungumo ta yayi suka koma gefen dresing mirror

tana hannun san,bai sauke ta ba ya zauna da ita akan cinyar sa A Saman vanity table stool dake gaban mirror.

Da hannun sa guda ya tallafo ta kan kirjin sa..,Lafewa tayi tana jiyo shaukin dake tafiya da yanayin su.."Yanayin ta yana nuna Masa tsoron sa Dake Cin ta arai mammatse Kafa take Tana nokewa..

Murmushi yayi ya tabe baki cikin ransa yana cewa zaki ma Gaji ki dena

Kallo yabi tender hands din na ta daya damke masa rigar sa,Dada matso ta yayi jikin sa sosai sai da taji gaban ta ya fadi ,goga fiskan sa ya shiga yi daga gefen wuyan ta zuwa kan kafadun ta yana shunshuno daddan natural scent din ta idanun sa a lumshe,riko sa tayi dam cikin fargaba Wani kwalalan

Sauke ajiyan zuciya ta shiga yi Tana jin numfashin ta na shirin daukewa

Daga gefen kunnen ta ya maida lips dinsa

..karan hancin sa ya shiga goga mata a neckline din ta,rawa jikin ta ya soma Yi,a firkice ta Shiga kokawar zamewa daga jikin sa

bai sake ta ba Sai ya kama fatar kunnen Ta da lips dinsa gently yana zagawa da tongue dinsa..

'Tare suke dauke numfashi sai ta kamkame sa sosai..Tuni jikin ta ya Dada Shiga Vibratiion,hannun ta rawa Yake dakan sa,..jin zata sakar masa kuka Sai ya Dago ta,Tare da aje ajiyan zuciya ya Rungumo ta yana mai dora kansa akan kirjin ta

,.wani irin shiru yayi kamar neman nitsuwa makan sa....

bugu kirjin ta yake kamar zai fito,..sai chan ya janyo ta tare da sauke ta akan kafar sa tsaye ya mike hannun ta cikiN nashi

....Sit,..ya fada mata a kunne yana nuna mata stool din daya tashi..ba musu ta zauna a gaban mirror Shi yana bayan ta,nan itama take noke kai tana satan kallon fuskan sa ta cikin Mirror

...har cikin ranta nauyin sa take ji amma Taga shi ko ajikin sa yadda yake bin ta da ido ko ita ma kanta tasan bata taba kare ma halittan ta kallo kamar na yau ba

Zagowa yayi ya maida hankalin sa gaban mirror..

Mayukan shafawan ta masu sanyin qamshi ya fara dagowa,aduk sanda suka hade ido sai ya dage mata gira ko ya sakar mata wasu miskilan murmushi,nan ya taho gaban ta ya Rusuna, mulmula face cream a palms dinsa yayi ya shiga shafa mata shi a fuskan ta

...kallon shi kawai take yi Jikin ta ne

yake sacewa da kansa yana mutuwa..haka ya sake mulmulawa ya shafe mata gadon bayan ta

Lumshe ido tayi tana jiyo salon yawon hannun sa Anan mai tafiya da duk wani kasala anan wasu asirtatun nishi kawai take sakar mashi.

Dada rusunawa gaban ta yayi ya durkufa gwiwan sa,...zai dago legs din ta,ta sake kara Ta danke Hannun shi..murya na rawa tace pls stop...

dan hararar ta yayi ya dago kafar Sama, sai da taji sanyin dakin yadan doke ta.

cike Da Fargaba da tsoro ta rintse ido tana jin sa har ya gama shafe ta tsaf sannan ya dawo sama ya warware towel din data rufe suman kan ta..

Bayan sauke ajiyan zuciya,A hankali ta bude sauyayyaun idanun ta ta cikin mirror Ta kalle sa

Wani irin radadin dadi da ajijiyan sakonnin Da hannun san Ya aika ma jikin tan ne yake mata yawo A kwaKwalwa.....

Shima kallon ta yake hannun shi na yawo akan flat tummyn ta da babu wani alaman da zai sanar maka cewa akwai wani hallita aciki

Warware ribbon din nata yayi ya aje shi agefe "With much seriounes tana kallon sa cikin ranta tayi murmushi"

Tunani take Tace "ai Gwara ma shafa mai,amma har yaushe ya iya gyaran gashi!sai kawai tayi shiru

sake masa jiki Tayi dan yau so take Ta ga yadda zai iya gyara mata gashin,l

To her surprise bayan ya warware Suman combing ya fara yi slowly and carefully kamar wanda baison taji zafi,dan kadan yayi wet oiling Ya yi massaging sannan ya kunna hair dryer ya busar Ya dada mikarwa yaymata parking Dinshi tsaf.

Sosai ya bata mamaki,a 'duk dama tana kallon abunda yake yi amma so take ta taba taji da hannun ta,dan haka ta kai hannun ta zata Shafa Tana kuwa kaiwa yadan buge .

Yace daga min

'uchhhhh..tace kasan makoshi ta yarfa hannun tana dan bubuga kafar ta akasa A shagwabe

"Hey,..Do not touch Again, ko ce miki akayi ban iya ba?

Tace,ai baka da Gashin...ya za'ayi

Ma ka iya?..Ni daI zan taba ta turo bakiA fakaice ta dubi mirron ta ga yadda ya gyaro ta tayi kyau Daya dan juya zai nufi wardrobe

Itama A sace ta lafe tana kallon sa,har cikin ranta taji ya burge ta sosai wani ssbuwar son shi takeji aranta

Wani pink shot marar nauyi ya hada da wani mini half vest mai siririn hannu ya taho Mata da shi..."cikin ranta cewa take yau dai naji jiki..

Haka ya matsota Cikin salo shi ya saka mata Kayan yana yi hannun shi na aiko mata sako har cikin kwakwalta lumshe ido tayi Ta Kame Sa

Yace

Kinyi sallah ko?dazu nazo kina bacci..Ya tambaye ta sai ta gyada kai batare da ta bude idon ba

Sungomota yayi ya ajiye ta akan gado a mike ta gaba flat bayan ta yana resting tana kallon shi,hannun shi ya mIka kan lamp ya rage wutar dai dai yadda take bukata

haka ya dinga mata yawo da yatsun sa a ciki har bacci mai nauyi yayi awon gaba da ita Dan kadan ya juya ta gefen dama yana mai gyara mata kwanciya

Bayan shafe ta aduoi..Kiss ya dora mata a goshi sannan ya janyo Comforter ya rufe ta da shi Sannan ya koma room dinsa.

#mamuh*33*

Lokaci na tafiya kwanaki na ja watanni na matsawa rayuwar cikin gidan su Ammy komai na samin sauyi,yadda lkc ya ja,haka abubuwa suka yi ta faruwa dan kuwa bayan sa'insar da Saheeb yake samu da matar sa Muhibba a boye ta kuma dago wani rikicin da sai da dan dole ya saka ta tafiya asibiti dan a duba ta.

Da ta shirya ta tafi sai ta kasa aiwatar da komai dan dama uterus din nata yayi weak ne amma bai lalace ba kamar yadda take ta ririta laifin Saheeb akai ba..

Sai da ta kira Hamida a waya ta fada mata abinda ake ciki sannan suka yi kuleleliyar su suka samo mafita wanda Muhibba ta yi na'am da mafitar har ta hau kan koyarwar mafitar..

Ko da ta isa ga doctor,ra'ayin ta ta fada mai sai suka yi abinda zasu yi ta karbi maganin karya na depressant wanda inta sha zai taimaka wajen nunawa kamar bata da lpyar da wani shiryayyen written document lafiyar ta lau ta dawo gidan da shi tun shigowarta take masa bayani.

Da fari Saheeb bai so ya saurare ta irin sosai din nan ba dan shi kan sa abubuwa sun mai yawa ya rasa ta ina zai fara tunkarar abin but seeing and reading her health profile sai ya ji wani karamar tsoro ya shige sa,abinda ke ciki shine wai ta sami matasala da mahaifar ta ya lalace ba zata taba iya daukar ciki ba sannan samun wannan matsalar zai iya haddasa mata damuwa sama da shekaru but ayanzun ma damuwar bai kai wani mataki mai tsanani ba

har sai a yan kwanakin nan da saheeb bai nuna damuwar sa akai sosai ba,tasha maganin saka damuwa sosai dan haka ta zama kamar me boyayyen brain trauma kuma she is affected emotionally and psychologically tace masa akan haka za'a bata magungunan da zasu taimaka mata ta sami natsuwar zuciya dan batun haihuwa babu shi a gare ta dan ba yi zata yi ba...

Fifi tana laulayi sosai dan haka take rigata fitowa tayi aikin komai badon Allah ba saidan ta cusa ma saheeb jin cewa ta zama abar tausayi mara amfani a tsakiyar su

Duk iya nuna rashin kulawar sa sanda abun yazo yana damun sa sosai

Muhibba ta faɗa cikin mata masu matsala tana buƙatar kulawar mutane musamman shi da ya ɗora laifin a kan sa kusan completely tunda shine mijin, tun farko da bai bada yardan sa ba da babu abunda zai faru.

Bayan wata uku ta turo likitan ta wajen sa da bayanai masu tsoratarwa burin ta baifi ta datse tarayyar dake bunkasa cikin sanyi tsakanin sa da fifi ba

Da Saheeb ya gama ganin doguwar sharhi sai kawai ya rusuna kai gaban Muhibba dake ta kuka mai tsuma zuciya tana nuna nadamarta da ciwon rasa gurbin haifar nata dan a duniya,rasa me zai ce mata yayi sai kawai ya rungumo ta ya hau bata haƙuri da nemar yafiyar ta sannan ya nuna cewa laifin sa ne ya kuma yi mata alƙawarin ba zai taɓa barin ta ita kaɗai tana jin raɗaɗin wannan rashin haihuwar ba dole su yi sharing tare dan ko masana da suka yi mgnan su akan family function ba iya ga mai cikin suke nufi ba actually akan family burden da matsala suke nufi shi ya sa suka ce responsibilities of a pregnant woman is shared between all sundry toh ba mai ciki kaɗai ba har da member dake cikin matsala kenan

tun wannan rana Muhibba abin nema ya samu,ko girkin ta ko ba nata ba zata san nayi har sai Saheeb ya kulata yanzu baya son ganin tana cikin damuwa dan haka bai cika yin nesa da ita ba,hakan ya mata daɗi dan ko ba komai tana samin attention ɗin mijin ta..

A fannin fifi dayake saukin kai da sassaukan zuciya ne da ita sai bata dauki abin komai ba,gashi ya saba mata komai da kanshi sai kuma ya zo a daidai lkcn da ta fi buƙatar shi sama da kowa a duniyar shi kuma ya fara juya mata baya.

A kullum tana ƙara son sa tana ƙara ƙaunar babyn su dake tare da ita sai dai tun abin baya damin ta har ya kai ya kawo abin ya fara ɗaga mata hnkl..

Kishi ne me zafi yake cinta, A ganin ta ba komai Saheeb ke nuna mata ba sama da tausay,dan tana ganin yanzu matar sa ta dawo so bai da lkcn ta ita sai na matar nasa,dan har a wurin cin abinci yana kafa kafa da Muhibba wannan dalili ya sa ta rage zuwa wurin cin abincin dan kar ta rinƙa ganin abinda zai riƙa ɗaga mata hnkl..

Takan zauna tayi kuka ta roƙi Allah ya yaye mata wannan damuwa nata haka zalika takan zauna ta rinƙa tmbyr kan ta ko laifin me tama Saheeb ɗin da ya daina kulawa da ta sosai haka..?

Sai yanzu take gane zafin son da baida amfani,ciwon dake cikin kyaliya sharewa juya baya da wahalan dake cikin nuna fifiko wayanda ta saba da sabanin su tun farin rayuwarta..

Wani lkcn zataji kishi sosai, zuciyar ta kan bata amsa da ai tunda kin fara nauyi hala shi ya sa ya daina sauraron ki dama fah kar ki manta auren haɗi aka maku ke da shi ba soyayya kuke yi ba..

A kullum in ta tuno hakan sai ta ji zafi a zuciyar ta ta kuma rinƙa ganin laifin zuciyar ta da ya bar ta tana makahon soyayyar da bata san kansa ba..

Dai dai da rana ɗaya Saheeb bai taɓa yunƙurin zama da fifi dan sanar da ita komai ba musanman akan current health situation ɗin Muhibba,dalili kuwa shine shi yana da miskilanci da ganin in mutum ya ga abu ya faru ai ya san da dalili ba sai ya bi mutumin ya mai bayani akan abinda ya farun ba kuma,sannan yana ganin shi ɗin ba yaro bane da zai yi ta bibiyar yara kamar bai san me yake yi ba..

So duka waɗannan tunanin su suka taru suka bada gudunmawa mai ƙarfi wurin nesanta muamalr su sannan zargi mai ƙarfi ya ɗarsu a zuciyar ta ta yadda take ganin kamar yana so ya ci amanar soyayyar ta ne dan ta daɗe da gane ƙarya yake mata ba son ta yake ba wani abu yake so a tattare da ita da ya janyo sa gare ta...

Duk kuwa yadda su Ammy da Hajja ke bata kulawa da kariya daidai gwargwado hakan bai ishe ta dan duk daɗin ka da mutani in har kana da matsala da gidan auren ka toh babu wani daɗi..

Tana nuna jin daɗin hakn amma aranta ta fi buƙatar shi mijin nata kusa da ita sama da kowa da komai sai dai hakan bai yiwu ba dan ganin sa ma sai yana so ya zo ya zame mata da ƙyar.

Rannan tana zaune a garden ɗin gidan tana aikin kullum wato tunanin sa da rayuwar su sai hawaye ya fara zubo mata dan bata saba da rashi ba,kamar tana son abu amma ta rasa sa,sam bata saba ba komai take so ana mata shi saidai a yanzu auren da tayi tana buƙatar abubuwa da dama daga cikin sa amma an kasa sama mata shi ta kasa samin waɗannan abubuwan dama da gaske in har mace tayi aure gatan ta ya ƙare dole ta fuskanci gidan ta ita kaɗai?in haka ne ita zata bada lbrn faruwar hakan dan dai gata iya gata babu wanda bata samu but cikin gidan ta ya zame mata kamar wuta bata iya kashe wutar sai dai in guje mai da ta yi dan komawa sashen su Ammy da zama tayi ba kasafai take zuwa nan nata sashen ba sbd gudun ɓacin rai...

Hannu ta ji a kafaɗar ta sai ta ɗago ta kalli hannun sannan ta kalli fuskar mamallakin hannun take ta kawar da kan ta tana cigaba da zubda kwallar ta..

Ta gaban ta ya zago ya zo ya zauna a kujerar dake fuskantar ta haɗe da riƙo hannayen ta yana murzawa..

Tana jin abin amma ta ƙyale sa bata tanka mai ba shi kuma bai hana ta kukan ba dan a yɗan kwanakin nan yana ɗan lura da halin rashin natsuwar zuciyar da take ciki sai ya daure ya binciko ta inda ya gan ta a nan garden ɗin ya kuma ƙudirta sanin matsalar ta..

"Me ke damin ki"?tmbyr da ya mata kenan sai ta kalle sa irin u are bluffing ɗin nan sai ta kawar da kan ta tayi shiru.

Juyo da fuskar ta yayi suna kallon juna for a while sannan ya furta

"Am sorry"a hnkl abin sai ya bata mamaki wato ya san ya mata laifi kenan..

"I truly am".ya kuma maimaita mata sai ta cigaba da yin shiru har dai dan kan sa ya fara rarrashin ta da alƙawarin making up mata da haka dai ya kalailaye ta a sannu har ta sauko daga dokin fushin ta saurare sa.

Tsakanin Mata da miji sai Allah,kalau suka shirya ranar haka tun safe har yamma fifi ta kasance cikin annashuwa da farinciki duk da bai zo inda take ba hakan ma yayi tunda ya bata tym da attention ɗin sa a ranar...

Sannu sannu rayuwa ke ta tafiya ahakan Saheeb yayi ta disappointing fifi kullum tana saka shi abu bata samun yadda takeso haka zata gaji ta cire tunanin a ran ta shi kuma bai taɓa tunanin ya take ji ba in bai nuna mata komai ba..

A ɓangaren su Hamida da Muhibba kuwa abubuwa sai gaba suke yi kamar ba za a daina numfashi ba dan kullum sabbin abubuwa suke ƙarawa akan na da sun yi nisa basu jin kira kuma duk wannan abin babu wanda ya san suna yi daga su sai su..

A kwanakin nan ne Muhibba ta fara jin wani irin abu a jikin ta kamar dai bata lfy,tun tana ɗan daurewa da kawar da kai har abin ya fara fin ƙarfin ta dan kuwa matsanancin ciwon ciki ke tasa ta gaba ba kaɗan ba amma bata da yadda ta iya dan dole ta kuma samin attention ɗin mijin ta wanda hakan ya kuma datsawa a rayuwar auren Saheeb da fifi

abubuwan sun kacame ma fifi ta yadda hakan yake nufin tana buƙatar attention ɗin wani da shawarar wani,but wa zata fuskanta ne bata sani ba..

Tana zaune wata ranar alhamis sai ta ji tana son ganawa da yaɾ uwar ta duk munin naka naka ne ko da korar ta zata yi zata tafi ta faɗa mata damuwar ta maybe ta sami mafita..

Fita tayi zuwa sashen Hamida inda da ƙyar ma ta sami attention ɗin Hamidar,abu na farko da ta fara shine kuka mai tsanani da ratsa zuciya sai Hamidan ta natsu ta fara sauraron ta inda ta rinƙa karanto mata damuwar ta..

Gwanar tausayi Tace "Hamee am not happy wit my marriage,rayuwar aure na bai min yadda ya dace komai nawa ya fitar min a hannu na rasa ya zan yi,yaya Saheeb baya bani lkcn sa,bana samin kulawar sa,Hameda ban san makoma ta ba ban san laifi na ba,haka tawa jarabtar take ni kuma?fixing aure na kan sa na kasa yi?am pregnant but the father of my baby isn't ready to take care of me and our baby ya zan yi hakan ni kaɗai?bani da uwa i don't have any one sai ke" bzan iya kai damuwata wajen su ammy ba hamida,Hamida ki taimaka min dan Allah..

."da kuka mai taɓa zuciya fifi ta ida mgnr..

Sosai jikin Hamida yayi la'asar ta kasa haƙuri har ta janyo yaruwar nata tayi hugging nata tightly tana petting bayan ta cikin tsananin tausayi tana fidda sautin

"shhhh" a hnkl..

Kuka sosai fifi ke yi kuma kukan na ɗan taɓa ta a zuciyar ta ba kaɗan ba sai dai abinda bata sani ba shine,shin ta taya yaruwar ta yaƙin samin natsuwar mijin ta gare ta ne ko dai a'a ta bar ta ta cigaba ne ita kaɗai ba tare da ta taimaka mata ba?

#Mamuh

******34*

Murya ƙasa ƙasa kamar mai tsoron yin mgn Hamida ta fara yiwa yar uwar nata kalamai masu daɗi da sanyaya zuciya dan ba ƙaramin tausayin ta ta ni ba duk da yadda take ji a game da fifin bai sauya ko kaɗan ba a zuciyar ta but tana ganin kamar in ta ƙyale fifi cikin damuwar da take ciki akwai matsala..

Ɗagowa fifi tayi tana kallon Hamida dake ta rarrashin ta,mantawa tayi da Hamidar tana fushi da ita sai ta kuma faɗa mata wani sashe na halin Saheeb wato rashin kimanta adalcin da yake yi a cikin gidan tsakanin su matayen sa..

Hamida da hnkl ta ya koma kan ƙulalliyar da suke yi ita da Muhibba akan yadda zasu takura fifi sai ta ji gaban ta ya faɗi ta rasa inda hnkln ta ya tafi kawai sai ta ji ruwa ya ciko mata a ido sai dai ta danne bata bari ya zubo ba ta kuma rungume fifi tana ce mata

"Na maki alƙawarin taya ki addu'a da samin yancin ki a gidan mijin ki i promise u"

Ba ƙaramin daɗi Mufida ta ji ba sakamakon jiyo waɗannan kalamai daga bakin yar uwar ta after many months of shunning her..

Da kalamai masu daɗi Hamida ta kwantarwa fifi hnkl har ta raka ta zuwa bakin gate ɗin sashen ta ta komo ciki ta zauna tana ta tunani ita kaɗai akan abubuwa da dama..

Fifi kuwa ɗakin ta ta nufa dake sashen su Ammy ta kwanta shiru tana shafa cikin ta,cikin ya fara girma har ya bayyanu ta yadda duk wanda ya gan ta ya san mace ce mai juna biyu..

Sanyayyan hawaye ne ya zubo mata a kumatun ta ta saka hannu ta goge tana gyara kwanciyar ta,a ran ta take ayyana dama zata iya juya hannun agogo baya da ta juya ba dan komai ba sai dan ta goge sashen Saheeb dake cikin shafukan rayuwar ta.

"Ina ma a ce zan iya,ina ma a ce ni Mufida zan iya goge ka gabaɗaya a rayuwa ta yaya Saheeb,ina ma a ce zan iya ciro zuciya ta in wanke inda sunan ka ya taɓa a zuciya ta sannan a mayar cikin ƙirji na,ina ma a ce ina da iko da zuciya da zan bata umarnin daina haska min kai da take yi a kai a kai,da da yadda zan yi da na yi ko dan in yaye ka a rayuwa ta dan ni kaɗai ke iyo a zurfaffen ƙaunar ka kai baka yi,ni ke soyayyar ni ke ƙaunar haka ni ke fuskantar hukuncin _Ƙaunarmu_ isn't it too much for me all alone"?ta ida mgnr tana mai fidda kuka mai sautin gaske da tsantsar tausayin kan ta..

Tana ta kukan har bacci ya ɗauke ta mai tsanani,Hajja dake bakin ƙofar ta tana ta jiyo shesheƙar ta haka tana sauraron maganganun ta ta turo ƙofar ta shigo a hnkl ta isa inda fifi ke kwance a kaikaice.

Kallon tausayi ta ma fifi sannan ta matso dab da ita ta mata addu'a ta gyara mata kwamciyar a hnkl gudun kar ta tashe ta daga baccin kar ciwon kai ya dame ta...

******

A ɓangaren Hamida abubuwa babu sauƙi dan ranar a wani yanayi ta yini har mijin ta ya dawo ya same ta a haka nan ya tmby ta damuwar ta but ta kasa ce mai komai sai langaɓeai da take ta yi a jiki,duk ta yi sanyi hnkl ta baya jikin ta halin da ƴar uwar ta ke ciki ba ƙaramin takurawa zuciyar ta yake ba..

Haka dai Khalid yayi ta fama da matar nasa hatta da abinci sai da ya karɓo masu a cikin gida dan kasa aiwatar da komai tayi,kkrin da tayi na girka abincin sai da ya ƙone ƙaurin sa ya cike gidan kaf da rana shi ya sa da yamma ya shiga wurin su Ammy ya karɓo dinner...

*****

kamar ƙiftawar ido cikin Fifi ya kai wata shida gab da na bakwai,babu abinda ya sauya a zamantakewar ta da mijin ta Saheeb,alƙawarurruka kam ta sha ta har ta gaji har ma ta daina yarda da shi da kalaman sa dan faɗa yake yi baya cikawa..

Sashen Muhibba kuma rashin lfy sai daɗa gaba yake yi ciwon ciki matsananci kullum cikin ta take na yau na ɗare na jiya,sannan depressant da ta karɓa tana sha bata daina sha ba..

Gani take kamar duk sakamakon damuwar da ta ɗorawa kan ta akan raahin haihuwar ne,ta kasa gane illar maganin da take sha ne ke haifar mata da ciwon cikin sai ta rinƙa ƙara yawan maganin madaɗin biyu a rana sai ta maida shi huɗu a rana ta sha biyu safe biyu yamma..

Saheeb kuwa ya kasa samin natsuwar sa dan in ciwon cikin ya motsa mata sai ta yi kamar zata tafi tayi ta juyi haka zai ta kula da ita..

A lkcn da ya nemi Khalid a abin sai Khalid ya mai nuni da su tafi asibiti a duba mata mahaifar nata ƙememe Muhibba ta ƙi yarda dan ta san blackmailing Saheeb da tayi kuma take kanyi in ta tafi asibiti za a iya sanin gaskiya ita kuma batajin zata iya karawa da Mufida..

Haka nan Saheeb ya bar ta dan ta ce ita gynaecologist ɗin ta zata tafi ta gani in ta shirya..

Sosai take cikin matsala amma ta ƙi zuwa asibitin ga ciwon na daɗa gaba amma taurin zuciya irin na Muhibba bai bar ta ta tafi ganin likita ba ta yi ta managing kan ta..

Wani rana haka da dare misalin ƙarfe tara bayan Saheeb da Muhibba sun sami sa'insa da junan su sai ya fitar mata a ɗakin ya koma nasa baidai sami kwanciyar hnkl ba sai ya fita ya bar sashen ma gabaɗaya ya nufi sashen su Ammy..

Ko da ya shiga duk sun kwanta sai ya nufi ɗakin fifi dan dama niyar sa washegari ya zo duba ta but yadda Muhibba ta ɗaga mai hnkl haka ya sa baya jin ya cigaba da zama a sashen dole ya zo ya ga fifi duk kuwa da ya san yaata laifi but he want to impress her today ta hanyar nuna mata sincere apology ɗin sa...

Da fari da ya shiga ɗakin sai ya ga duhu ya mamaye ɗakin so yayi switching wutar ɗakin,ga mamakin sa sai ya hango ta jingine da gadon ta ta haɗe kai da gwiwar ta,hasken da ya mamaye ɗakin ne ya saka ta ɗago kan ta..

Tana ganin sa sai ta zuba mai ido kamar bata taɓa ganin sa ba sai yau,shi kuma ya ƙarasa shigowa ciki a sannu,idanun ta na kan sa haka shima nasa idanun na kan ta..

Da ya ƙarasa shigowa ya zo dab da ita sai ya zauna kusa da ita,sunkuyar da kan ta ƙasa tati ta mai shiru,bai san ta ina zai fara ba amma yana so yau ya kasance tare da ita ya faranta mata ya saka ta jin daɗi kamar yadda ya dace..

Hannun sa ya saka ya riƙo nata,bata ce mai komai ba tana bin sa da kallo har ya kwantar da ita tana kallon sa ya dawo ta dama ya kwanta haɗe jawo marufin gadon ya lulluɓe su..

Mamakin sa sosai ne ya kama ta ganin yadda yake mata abu kamar kurma,jan ta zuwa jikin sa da yayi ne ya saka ta lumshe ido dan dole ta kasa buɗewa..

Kunnuwar ta ne suka jiyo mata sautin muryar sa yana bata haƙuri kamar kullum,ran ta a ɓace ta fara jan jikin ta amma ya matse ta dan ya fi ta ƙarfi ta ko ina..

"Ki kula kar ki bige min baby".dakatawa tayi daga fizge fizgen da take yi ta natsu tana numfarfashi kamar tayi gudun tsere..

Hannun sa ya kai kan cikin ta da ya fara girma sosai,zagayawa ya shiga yi da hannun nasa bisa cikin ta ba tare da ya ce komai ba..

Da ya gama yayi ƙasa da kan sa ya sumbaci cikin nata sannan yayo sama ya rungume ta tsam a jikin sa,ƙala bata ce mai ba sai da suka share wasu lokuta a haka sannan fifi ta fara yunƙurin raba jikin ta da nasa amma ta ji ya kuma riƙo ta ƙam..

Bata ankara ba ta ji ya fara janta a sannu ba da zafi zafi..

Tun bata biye masa har ta sauko ta biye mai abu kamar wasa sai ga fifi manne da Saheeb ana zuba love abin gwanin burgewa..

A nan ɗakin nata ya kwana bayan ya gama cika mata brain da alƙawarurrukan daga yanzu bai kuma yin nesa da ita ya mata alƙawarin tare zasu raini unborn baby ɗin su..

Tare suka yi wanka da asuba suka yi sallah tare suka kuma komawa baccin safe again bayan yayi showering nata da salon soyayyar sa mai ɗauke hnklin ɗiya mace...

****

A sashen Muhibba kuma tun safe da ta farka ta duba bata gan sa ba ta shirya hnkl tashe ta fito,kamar ta fara tsayawa a sashen Hamida sai kuma ta fasa ta wuce zuwa sashen su Ammy..

Babu wani walwala sosai a tattare da ita so bata wani jima ba tare da su ta tmby yaɾ aikin gidan ko Saheeb ya shigo amma ta ce mata bata sani ba.

Hnkl ta na bata Saheeb na nan tare da fifi kamar ta je kamar kar ta je sai ta miƙe ta haura saman gabab ta na ɗan faɗi..

Bata san me zata gani ba in ta shiga ɗakin fifi but bata dai son ta ga abinda ran ta ke raya mata..

Da isar ta ɗakin ta ɗora hannu a handle ɗin ta murɗa ta tura a hnkl ta sa kai..

Wani faɗuwar gaba ne ya riske ta ba dan komai ba sai ganin Saheeb da tayi tare da fifi kwance cikin tsantsar jin daɗij yanayin su..

Juyawa tayi idanun ta rufe da kishin mijin ta da ɓacin rai ta bar sashen tana ta nanata dama yana son yarinyar nan amma kullum baya admitting ya saka ta ta rinƙa jin kamar daga ita sai ita a rayuwar sa dama ƙarya yake mata..

Bata tsaya ko ina ba sai a sashen Hamida da yanzu ta dawo daga rakiyar mijin ta zai tafi aiki..

Sallama tayi a bakin ƙofar parlorn,bata jira an bata izini ba ta saka kai ta shiga,daidai Hamida zata zauna kenan ta ga Muhibba kuma da ganin ta ka ga wacce ke cikin tashin hnkl..

Bata ba Hamida damar yin mgn ba ko uffan bata ce ba Muhibba ta riga ta da baki cikin fushi da ɗan zafin rai..

"Ke Hamida tare da ke muke komai Amma ashe wannan yar yarinyar mai ƙoƙarin amsa sunan matar Saheeb na can na kalaikaye min miji ni ina nan ina tinƙahon miji nawa ne ni kaɗai nagama da shi?,for goodness sake is that girl so dump and foolish just look at me na yi kama da wacce zan haɗa miji na da wannan yar yarinyar"?

Hamida na shiru tana jin zafin kalaman Muhibba ga yar uwar ta..

"Kina ji na kuwa Hamida?ki bani mafita ta yaya zan ɓullowa wannam yarinyar na ƙi jinin in gan ta kusa da miji na"!

Dakatar da ita Hamida tayi ta hanyar ce mata

"Me ya sa"?rai ɓace ta bata amsa da

"Because he is mine and all mine alone"!

Murmushi Hamida tayi ta koma ta zauna tayi crossing ƙafar ta ɗaya kan ɗaya tana karkaɗawa tana duban Muhibba dake tsaye tana bin Hamida da kallon mamaki..

"Meye haka ina nemar mafita ta yadda zamu kawar da lbrn wannan yarinyar a rayuwar miji na ke kuma kin zauna kamar ba kya ji na"!da ɗan ɗagon murya Hamida ta ce

"And why should i help you Muhibba?for crying out loud ke baki da brain ɗin tunanin kan ki ne sai na baki mafita?waini nace miki tsanarta nayi ne uhm?shawara fa nabaki..go ahead and use ur head mana..kema ki samowa kan ki mafita as far as

am concern ke ɗin ai babba ce kin girme mu so use ur big head and find a proper solution for ur self

"Arazane Muhibba ta bi Hamida da kallon mamaki..

Karkaɗa ƙafa ta cigaba da yi tana duban Muhibba sai kawai Muhibba ta mata wani tsawa itama ta miƙe tsaye ta mayar mata da martanin tsawar nata.

"ai ban yi ƙarya ba ki je ki samowa kan ki mafita na gaji da duk wannan abin am out...kiyi waje

ɗora hannu a ƙwanƙwaso Muhibba tayi tana kallon Hamida da tsantsar mamakin ta..

Kalamai marasa daɗi ne ya fara fitowa daga bakin Muhibba zuwa ga Hamida,itama Hamida cikin rashin haƙuri ta hau maida mata martani har da gori da tunatar da ita ita ta kasa bada farinciki a rayuwar mijin nata sai hassada dan ta ga nata twin sister ɗin ta bashi farinciki..

A sannu duk suka gama tonewa kan su asirin shirin su da suka yi ta yi a ɓoye ba tare d wani ya sani ba gori akan gori,faɗa sosai suka yi mai muni,tas suka tonawa kan su asiri kamar ba a taɓa zaman mutunci ba..

Turo ƙofar parlorn aka yi da ƙarfi alamar duk wanda ya turo ƙofar ya ji every single part of their conversation,a tsorace Hamida ta juyo hakama Muhibba duban su suka kai ga wanda ya shigo dan ganin sa..

Zazzaro ido Hamida tayi sakamakon ganin wanda ya shigo ta juya ta kalli Muhibba da itama ita take kallo lokaci guda suka juya kallon ƙofar..

#Mamuh*35*

Ƙarasa shigowa yayi take Hamida ta shiga taitayin ta ta ɗan koma da baya yayin da Muhibba ta ƙare masa kallo ta juya ta kalli Hamida ta ɗan ja ƙaramin tsaki ta sa kai ta fice ta bar sashen..

Gaban ta ya zo ya tsaya cak yana ƙare mata kallo daga sama har ƙasa,irin wannan disgusting looks da yake mata na ruɗa ta..

Da ƙarfi ya riƙo kafaɗar ta cikin tsantsar ɓacin rai da tir da halin matar nasa ya fara mgna cikin bacin rai, cikin ɗagon murya da hargowa..

"Ki Tabbatar min da gaskiyan wannan hirar naku da na gama ji yanzu da bakin ki"!!

a tsorace Hamida ta dundunce cikin tsoro da fargabar me zai biyo baya ta hau in'ina tana ƙoƙarin fizgewa khalid ya kuma matso ta dab da shi..

"Khalid you are hurting me let go off me"!.kamar zatayi kuka ta furta hakan

daka mata tsawa yayi yana ce mata

"Yes i wanna hurt u so that u will feel d pain u hv been making ur own blood twin sister experiencing,hamida ba zan ga laifin ki ba dan dama wanda bai so ka ba tun asali ba zai taɓa son ka ba har abada ko ya zo ya ce yana son ka toh da manufa ne,now i get it,you are a selfish person,kin cika son kan ki da yawa,just imagine,Hamida haka kike ashe?ki haɗa kai da wata wai Muhibba da duk kusancin ku bai kai girman kusancin ki da yaɗar uwar ki ta jini ba,hnkl kwance ki yarda tana cin ma burin ta akan yaɗar uwar ki and d most provoking part of all shine da sanayyar ki hakan ke ta faruwa"..?

Zafafan Hawayen sa daya ke dannewa su suka kwace mishi suna gangarowa a hankali muryn sa yayi wani irin sanyi yace

"Hamida Me ya sa kika canza halayyar ki kika zamo kamar wata muguwa marar imani?huh?sbd Allah Hamida duk waɗannan munanan abubuwan da kan ki da hannun ki kika yi su?in fact ke ce mai coming up da idea ɗin?.yʼar uwar ki ta jini kika haɗawa waɗannan abubuwan?common Hamida u weren't lyk dis. meye ne ya sauya ki kika zamo haka?duk ƙoƙarin da nayi ta maki ashe abinda kika saka kanki a kai kenan?

Kuka ta fashe dashi batace dashi uffan ba

shiru yayi yana watsa mata kallon banza ita kuwa banda kukan babu abinda take yi..

Haɗa ta da wall ɗin parlorn yayi yana kallon ƙwayar idanun ta,tas tana hango tsantsar ɓacin ran da yake ciki..

"So u two have been blackmailing my brother huh?kai Hamida how many evil hv u done?ashe tuntuni kun daɗe da sanin juna ma sanin da yayi zurfi har ke kina iya bada shawarar ga abinda ya dace a yi?kun saka shi zama cikin zargin kan sa akan laifin da bai sani ba ku kuna nan kuna arranging plans ɗin ku shi yana can yana kwantar mata da hnkl yana nesanta kan sa da yʼar uwar ki matar sa kuma kina ankare?ke ce a gaba mai jagorantar komai ma"!!

A raunne ta dago Zatayi magana yace baison ji

Sosai Hamida ke kuka tana nadamar wannan rana da ya zo mata a haka

kwata kwata ba haka ta shirya faruwar Abun ba so tayi daga wannan argument ɗin da suka samu tsakanin ta da Muhibba shikenan ta fitar da ita a rayuwar ta ta koma ga yʼar uwar ta but unfortunately Khalid ya gama jin komai bata da yadda zata kare kan ta komai ya ƙwace mata...

Sakin ta Khalid yayi ya juya baya yana furzar da iskar takaico da ɓacin rai,yana mamakin yadda zuciyar Hamida ya ƙeƙashe ya bushe haka har akan kishin yʼar uwar ta take iya haɗa kai da Muhibba su cuci yʼar uwar nata...

Nade hannayen sa yayi a ƙirji ya juyo ya dube ta da kyau sannan ya ce mata cikin murya mai firgitarwa da tsoratarwa.

"Tun yaushe kika fara zaluntar Mufidan?saurin duban sa tayi gaban ta na faɗi cikin kuka sai ta girgiza mai kai tana faɗin

"Wlhy ban taɓa shirya zaluntar ta ba ruɗin zuciya ne ya shiga tsakani na da Mufida amma Ƙaunarmu na nan a zuciya ta"!!shutting nata yayi ta hanyar ce mata

"Ƙarya kike yi karki ce min akwai ƙauna a tsakanin ki da Mufida after all these conversation da na ji da kunne na,har kin ba Muhibba shawarar karɓar wannan maganin da take sha,well for ur information maganin nan na nan na haddasa mata illa,illah mai tsanani,ɓoye ɓoyen ku wata rana zai ƙare but kin san me?

"am leaving,am leaving u na har abada.. coz ba zan iya cigaba da zama da mace irin ki ba, duka soyayyar da na nuna maki,da irin zaryar kai komon da Mufida ta rinƙa yi maki duk dan ki yafe mata ku shirya amma tun asali da yake ba son ta kike ba sai kika rufe idanun ki kika rinƙa bin abinda zuciyar ki ke raya maki yake bijiro maki,so am getting out of ur life hamida ki je Muhibba ta zame maki abinda ni da yƙar uwar ki muka kasa zame maki"!!yana kaiwa nan ya ingiza ta ya wuce ya shiga tattara kayan sa..

Faɗi ƙasa tayi tana kuka mai haɗe da shesheƙa tana maganganu ita kaɗai tana nemar yafiyar Khalid bai kulata ba har ya gama yaja jakar sa ya fita..

Bata kuma tsorata ba sai da ta ga da gaske tafiyar zai yi dan ya fito da akwatin san rai ɓace ya xubasu s booth ya rufe..

Tana kuka ta taso ta zo zata riƙe shi,wani tsawar da ya mata sai da ta ja da baya jikin ta na ɓari tana kuka mai tsanani tana nemar yafiyar sa haka ya ya shige ya ja motr sa ya fita a gidan..

Kamar zata haukace haka ta rinƙa yi ita kaɗai tana aibata ranar da tunanin haɗa kai da Muhibba ya bijiro mata,tunda take a rayuwar ta bata taɓa ganin Khalid yayi fushi mai tsanani irin wannan ba sai yau,kenan ya tafi ya bar ta kenan?hukuncin da ya zaɓi yi mata kenan?..

Surutai dai babu wanda Hamida bata yi ba tun tana ganin abin kamar hasashe har dai ya tabbat Khalid ya tafi ya bar ta shikenan ita bata da wani gata,garin nemar gira ta rasa ido,ita ina zata kalla ta ji daɗi a ran ta...

Haka ta yini tun safen nan har dare bata sami kan ta ba abin kamar wacce ta rasa hankalin ta haka tayi ta yi,kiran tayi har ta gode

Allah bai ɗaga ba daga bisani ma kashe wayar yayi gabaɗaya,text msgs kuwa sun fi a ƙirga da ta aika mai da shi but babu reply,kwanar kuka da nadama tayi tana da ta sanin rayuwar ta...

*****

A fannin Muhibba da ta bar sashen Hamida bayan kallon banzan da ta ma Khalid,sashen ta ta nufa ta shige ɗakin ta ta saka mai lock..

She is weak already bata da wata dabara da ta rage mata tunda dai har Khalid yaji abin da ya faru tsakanin ta da Hamida toh ta san Saheeb ya gama jin komai...

Kai kawo ta shiga yi a ɗakin tana saƙa da warwara,rikicewa ƙwaƙwalwar ta yayi ta kasa lissafin komai dan dama in dai irin wannan ne toh Hamida ce mai bata mafita toh yanzu sun ɓaci babu jituwa a tsakanin su..

Furzar da iska tayi tana cigaba da kai kawo at same tym da take takura brain ɗin ta ya bata mafita a same time ciwon cikin ta na addabar ta dama daurewa tayi ta tsaya ta yi wannan faɗar da Hamida amma tana jin ciwon sosai...

Zama tayi a kan sofa ɗin ɗakin nata tana ta nemawa kan ta mafita but sam bata samo komai ba haka ta ɗau wayar ta ta rinƙa kokarin kiran Saheeb sai tayi dialing sai ta kashe dan bata san me zata ce mai ba in ya ɗaga kiran.

Gabaɗaya Muhibba ta rasa natsuwar ta da tunanij ta a ranar ga Saheeb ɗin bai ko waiwayo ta ba bare ya san halin da take ciki

Daɗin daɗawa ma ga fifi ta dawo part ɗin dan ta ji hayaniyar mai aikin su Ammy na tmbyr ta ko ta tsaya ta taya ta girki amma ta ce a'a ta tafi kenan shi Saheeb ɗin ne ya ce mata ta dawo dan ya rinƙa ganin ta da kyau yana nuna mata so da kulawar sa ita kuma ko oho..

Har dare tana part ɗin ta bata fito ba haka Mufida bata haura ta duba ko lafiya bata gan ta ba toh dama babu ruwan ta da Muhibban,mijin ta ne a gaban ta kuma duk inda yayi nan itama zata yi bata jin tana da lkcn wata Muhibba bare ta sakawa ran ta damuwar ta,ta san days ɗin ta are numbered dan sarai doctor ɗin ta ya faɗa mata komai game da rayuwar ta da na babyn ta sai dai bata sanar da Saheeb ba dan bai san tana da wani doctorn ba all he knows shine Khalid ke kula da ita bayan hakan bai san komai ba...

*****

Kusan kimanin sati biyu kenan rabon Khalid da Hamida sai dai ya zo ya gaida mahaifiyar sa da kakar sa,in yayan sa na kusa su gaisa in baya nan yayi tafiyar sa.

Duk wannan mu'amalar nasu da Saheeb ko da wasa bai bayyanawa ɗan uwan nasa abinda ya jiyo Hamida da Muhibba suka aikata ba haka bai sanar da mahaifiyar sa ba bare kakar sa Hajja..

Hakama Hamida na nan na ta targeting nasa in ya zo amma bata taɓa sanin lkcn da yake zuwa har ya tafi sai dai ta ji an ce ai Khalid ya zo har ya wuce..

Kwanar kuka take yi a ranar da ta ji hakan sai dai bata san wa zata tunkara da damuwar ta ba yar uwar ta da ta ha'inta zata tunkara ko wa,bata sani ba amma matuƙa abin na damin ta a ran ta...

Wata ran tana kan share hawayen ta bayan 111 missed calls da ta bar wa Khalid sai ta tashi wuf kamar an tsungule ta ta yafa ƙaramin mayafin ta ta nufi sashen Mufida dan ba sau ɗaya ba ba sau biyu ba fifi na zuwar mata hira sai dai bata taɓa faɗa mata abinda ke damin ta ba hasalima in ta zauna sai ita ta tashi ta ce bata jin daɗi zata kwanta,tmbyr inda Khalid yake kuwa fifi ta mata shi sau nawa amma amsarta shine ya tafi aiki so daga haka fifi zata ja bakin ta tayi shiru..

Haka ko da Saheeb da Ammy suka so sanin me ya sa ya tafi aikin ba tare da matar sa ba sai ya nuna masu so yake y barta da fifi tunda sun fara shiri yanzu,so kowa ya yarda da dalilin sa ban da Muhibba da ta san kwanan zancen..

Waya take yi da daddyn su tana ta murmushi sai ta an turo mata ƙofa dan haka ta kai duban ta ga ƙofar sai ta ga Hamida duk hnkl tashe idanun ta cike taf da hawaye ta ƙarasa shigowa bedroom ɗin Mufidar abinda bata taɓa yi ba kenan tunda aka masu aure sai yau..

"Daddy i will call u back ina zuwa"fifi ta faɗa tana kashe wayar haɗe da dubar yar uwar nata..

Hnkl tashe ta tashi ta ƙarasa gare ta tana tmbyr ta lfy,kuka ne ya ci ƙarfin Hamida sai kawai ta ɓalle da kukan sosai,hnkl fifi ya tashi sosai sai ta riƙo ta suka zauna a gadon ta saka hannun ta cikin nata tana tmbyr ta me ya same ta..

Da kunya ciki a zuciyar ta ta zayyanewa Mufida dalilin tafiyar Khalid sakamakon abinda ya jiyo,da mamaki fifi ta tmby ta me ya jiyo nan matsanancin kunyar fifi ya mamaye Hamida amma haka ta daure din dai ta fayyace mata komai daga fari har ƙarshe...

Wani mamaki ne ya kama xuciyar Mufida sai da ta ɗau lkc tana ƙaryata kunnuwar ta amma Hamida tayi ta nanata mata ai hakan ne ita dai ta yi kuskure babba Mufida ta dube ta da idon rahama ta yafe mata ba zata ƙara ba...

Kallon ta kawai fifi tayi ta yi ta rasa me zata ce,ƙirjin ta ne ya mata wani irin nauyi sai tayi shiru har Hamida ta gama surutan ta tana kuka...

Rungumo ta fifi tayi tana fidda hawaye daga idanun ta tana jin zafi a ƙirjin ta sai dai ta kasa furta komai har sai bayan wasu lokuta sannan ta rarrashi Hamidan a nitse.

"Is ok Hamee na maki alƙawarin zan taimaka maki mijin ki ya dawo maki InshaAllah!

a firgice Hamida ta ɗago tana kallon fifi da mamaki

murmushin da ya fi kuka ciwo fifi ta mata tana gyaɗa mata kai ta kuma rungume ta batace komai ba..

Ba ƙaramin guilty conscious ne ya addabi Hamida ba tunanin ta in ta gama faɗawa fifi gaskiyar ƙulalliyar da suka mata from a-z fifin zata bada negative reaction sai ta ga akasin hakan..

A nan part ɗin fifi Hamida ta yini dan tayi yadda zata yi ta sa Hamidan ta sake jikin ta kafin daga bisani ta raka ta har sashen ta suka yi sai da safe ta dawo part ɗin ta...

Kuka ne mai ƙarfi ya kama Mufida tana yi tana danne ƙirjin ta dan nauyin da ya mata ba kaɗan bane,tana ta son ta karyta zancen cewa Hamida ce ta aikata mata hakan sai dai ya faru ko saura a gyara gaba..

Ciwon ta ne ya so tashi cikin dare dan Saheeb baya nan ya ɗan je wani tafiya haka tana jin nauyin faɗawa Ammy wannan abin so ta barwa kan ta,in da wanda zata faɗawa bai wuce saheeb ba toh baya nan dole ta jira har ya dawo sannan dan kar ta ɗaga mai hnkl,kuma daga baya tayi tunanin kawai ta fasa faɗa mai ɗin ita tayi yadda zata yi dan Khalid ya dawo ga matar sa...

****

Washegari fifi da kan ta ta kira Khalid bata bari ya riga ta da baki ba ta nemi alfarmar da take nema daga gare sa sai ya rasa abin faɗi kawai ya ce mata ya ji zai dawo nan da kwanaki uku,gudun kar ta takura mai da yawa sai ta mai godiya kawai suka yi sallama ta fita dan zuwa ta ma Hamida albishir..

#Mamuh*36*

Kamar yadda Khalid ya faɗa haka ya cika,danna daidai 3rd day ɗin da suka yi waya da Mufida ya dawo gidan..

Ranar Hamida sai da tayi kukan murna ta rasa me zata mai dan ya ji daɗi sai dai bai bi ta kan ta ba ya bar ta kamar bai yi kewar ta ba..

Kasa aiwatar da komai Hamida tayi har dai ta kira Mufida a waya wacce daidai lkcn kuma tana waya da mijin ta,ganin kiran ƴar uwar ta ya sa ta katse nasa kiran ta ɗau na Hamida..

Da shesheƙa Hamida ta fara mata bayanin ƙyaliyar da Khalid ke mata,haƙuri kawai fifi ta iya bata ta ce ta ɗan bar sa zuwa washegari hala ya sauko..

A haka dai Khalid da Hamida suka kwana a part ɗin su,shi ya kwana a ɗakin sa ita kuma ta kwana a ɗakin ta abinda basu taɓa yi ba tun auren su..

Ita dai bata yi baccin kirki ba dan kewar mijin nata ne kawai ke mamayar ta but bata da yadda zata yi haka nan ta kwana cikin kewar sa idanun ta buɗe duk sun kumburo...

Da safe misalin ƙarfe shida ta farka ta haɗa ma Khalid breakfast duk da ciwon da kan ta ke yi haka ta daure ta girka mai wani da zai tafi da shi office ta je tayi wanka ta dawo ta shirya cikin shigar atamfa ja mai ratsin fari fari ya mata kyau ta ɗan yi makeup kaɗan tayi ɗaurin ta ta fito ta zauna a dinning table ɗin tana jiran sa...

Fitowar sa kenan cikin shigar tafiyar aiki yana gyara necktie ɗin sa sai ya hango ta kan ta haɗe da table ta tallafe kan da hannayen ta biyu tana bacci..

Wani tausayin ta ne ya ratsa sa sai ya ƙaraso gare ta,a hnkl ya saka hannun sa yana shafa bayan ta but kamar yana petting nata ne..

Cikin baccin ta ta ji abinda yake mata sai ta ɗan ɗago da baccu bacci a idon ta,ganin sa sai ta wartsake gabaɗaya ta tashi..

Saurin maida ta yayi ta zauna shima ya jawo kujerar kusa da ita ya zauna suna fuskantar juna,for a while bai ce komai ba sai daga bisani ya fara mgn..

"Na san na maki hukunci mai tsauri ta hanyar ƙaurace maki but ki sani,hakan ba yana nufin ban yi kewar ki bane ko ban damu da rashin ki a kusa da ni bane,i did what i did to wake u up from ur challenged future,ba zaki cigaba da rayuwa a duniyar nan da ƙiyayyar yar uwar ki ba,but am happy ganin abubuwa sun daidaita a tsakanin ku kuma kuna getting along da juna,i pray that it will continue all through"!!gyaɗa mai kai tayi da sauri tana jin sanyi a ran ta..

Hawayen dake tseren zubo mata ne suka sauko sai ta share da yatsar hannun ta tana kallon sa..

Murmushi ya mata sannan ya nemi da ta mai alƙawarin ba zata kuma ƙulla wata alaƙa da Muhibba ba..

Alƙawarin ta mai tana tabbatar mai da cewar in har ya ga tana kusantar hakan toh ya jawo hnkln ta but bata fatar kusantar hakan kuma..

Daɗi ya ji da ya iya tsawatarwa matar nasa ta dawo kan hanya,maida duban sa yayi ga abincin ya umarce ta da tayi serving nasa..

Da sauri tayi hakan,fried chips ne da scrambled egg sai quacker oath da ta haɗa masu..

Ya ji daɗin breakfast ɗin dan haka ya cinye duka yana santi haɗe da yabawa hannun nata da ya girka abincin,daɗi sosai Hamida ta ji har ta rasa ina zata saka kan ta...

Tare suka fito bayan yayi feeding nata itama ta ƙoshi sai ta ɗauko mai food flask ɗin sa na abincin da ta mai..

Nan ma wani yabon ta sha shine ta rako sa har mota,suka yi warmly goodbye sannan ya tafi ita kuma ta nufi sashen fifi...

Da sallamar ta a baki ta shiga parlorn sai tayi tozali da Muhibba dake fitowa daga kitchen cikin sauri cikin shigar blazers da wando ta ɗora wani summer cardigan,kan nan babu mayafi sai wani turban,handbag ne a hannun ta da car key,ƙafar ta ya sha heels ne baƙaƙe..

Kallon wofi Hamida ta mata itama ta maida mata da matarni har da ɗorawa da

"Ina cikin hanzari ne amma ki bari in dawo zan yi fixing naki inda kika dace"!!ta faɗa tana tafiya..

Cikin sauri Hamida ta maida mata amsar da ya saka ta juyawa dan kallon Hamidar da kyau but sai ta ga har ta wuce ta..

Abinda ta ce mata kuwa ba wani abu mai tsayi bane sama da

"Kullum cikin hanzari kike shi ya sa kika kasa ba mijin ki farinciki har ya samo wacce ke bashi,that's why u always behind,hanzari!!!hanzari!!hanzari,too bad"..

Ba ƙaramin ƙonawa Muhibba rai waɗannan kalaman Hamida suka yi ba sai dai bata ce komai ba illa ƙwafa da ta yi ta juya ta fice...

Kai tsaye Hamida ta shige bedroom ɗin fifi sai ta gan ta zaune da towel babu kaya a jikin ta tana ta positioning wayar ta kamar dai video call zata yi..

Murmushi tayi ta ƙaraso ciki,sai a sannan fifi ta gan ta sai ta kife wayar a kan gadon ta fara yunƙurin tashi dan tarbo Hamida but Hamida ta hana ta ta hanyar ƙarasowa ɗakin da sauri tana riƙo hannun ta game da furta..

"Don't take d trouble sweet"faɗaɗa murmushi fifi tayi sai ta zauna suna fuskantar juna..

Gaisawa suka yi irin ta yɗan uwa a nan Hamida ke shaida mata yadda suka yi da Khalid sai fifi tayi murmushi kawai tana sha'awar rayuwar su dan suna burge ta,kullum suna tare da juna unlike ita da suke raba mijin sannan bai cika zama ba,a ƙalla cikin sati biyu yayi tafiya ya kai uku,bai da wani lkcn isasshe da yake spending ɗin sa da ita..

Hirar su suka yi har Hamida ta taya fifi gyare gyaren inda bata gyara ba kafin ta koma apartment ɗin ta tayi girki mai ƙara lfy a jiki da kyaun kallo ta cika sa cikin food warmer tayi blending fruits ta tace ya zamo kamar fruit juice sannan ta haɗa su a wani basket ta dawo sashen fifi da su...

Abin ya ma fifi daɗi dan dama ƙiwar girkin take yi dan a yɗan kwanakin nan aiki na mata wuyar yi kuma ta ƙi yarda Ammy ta turo mata ɗaya daga cikin ma'aikatan ta haka ta ƙi yarda a rinƙa kawo mata abinci daga sashen...

Har dare suna nan tare suna ta hirar su,wanda cikin hirar ne Hamida ta kawo wata shawara da tayi tasiri a zuciyar fifi har tayi tunanin ɗabbaƙa shawarar immediately sai dai ta bari har mijin ta ya dawo sannan ayi mai yiwuwa..

Shawarar akan daddyn su ne da rayuwar zaman kaɗaicin da yake yi na rashin mace,sun gama tsara komai yadda zai kasance,lkc kawai suke jira su fara aiwatar da plan ɗin nasu...

Wayar Hamida ne yayi ƙara kamar ba zata ɗaga ba sai ta ɗaga ta kai idanun ta kan wayar..

Sunan dake haskowa ne a screen ɗin wayar ya saka ta buɗe baƙi cikin mamaki tayi saurin ɗaga wayar tana faɗin

"Am on my way luv ina wurin Mufida ne"!!tana gama faɗin hakan fifi ta saka mata dariya ganin duk ta ruɗe..

Bata bi ta kan ta ba ta tashi abin ta tana mata sai da safe,sauri sauri ta dawo apartment ɗin ta inda ta gan sa yana cire necktie ɗin sa a gajiye..

Saurin ƙarasowa gare sa tayi tana bashi haƙuri haɗe da taimaka mai ya cire necktie ɗin ta kwashe duk kayan da ya cire da hannun ta ɗaya,ɗayan kuma tayi wrapping round his waist tana mai yi mai sannu.

A haka suka ƙarasa sama inda bedroom ɗin su yake ta taya sa yayi wanka itama ya saka ta yi na dole,tare suka ƙarasa wankan bayan an gama romancing kamar ba za a bari ba sannan suka fito...

Abinci ma yanzu tare suka ci suna feeding junan su da love and care,a wurin kwanciya kuwa,yau sai da Hamida ta tabbatar mijin nata yayi kewar ta itama haka,dan basu wani runtsa da wuri ba sai cikin dare sannan baccin ya ɗauke su...

****

Yadda Allah ya so haka yake kasancewa,yau da gobe sai mai duka,a kwana a tashi ga mai tsawon rai cikin Mufida ya shiga wata takwas cif cif sakamakon scanning ɗin da tayi na ƙarshe ya tabbatar da hakan...

A lot has happened kamar yadda Hamida ta tsayawa Muhibba a ido kamar matsala ta ƙi yarda a cigaba da cutar da ƴar uwar ta,dan har threatening Muhibba Hamida tayi akan in ta ja abin da nisa toh kaf zata zayyanewa Marshall gaskiyar zance dan Khalid bai faɗawa kowa abinda ya ji suna discussing akai ba ranar...

Sosai tsoron Hamida ya ɗarsu a zuciyar Muhibba dan ta san da zarar bakin ta ya buɗe shikenan maybe ta rasa Saheeb ɗin na har abada kenan because in har yayi realizing cewa she has been blackmailing him for long toh ba ƙaramin zafi zai ɗauka da ita ba sai dai ta kasance cikin matsalar ita ɗaya

Sannan a fanni ɗaya tana fama da health condition ɗin ta,dan duk da tayi stopping maganin da take sha completely,babu abinda ya sauya game da lfyr ta,yanzu tana normal anjima zata rikiɗe kamar ba zata yi rai ba...

In ta zauna takan ji mamakin yadda ita Muhibba Hamida ke wa gashin ƙuma da mummuƙe,tana ganin Hamida is too small for her to handle amma ashe mightiness da Hamida ke da shi ya sha gaban tunanin ta...

Dai dai da pretence ɗaya in Muhibba tayi Hamida na wurin toh sai ta razana ta da kalamai masu tsoratarwa dan Hamida gani take yadda fifi ta dawo mata da annashuwar ta rayuwar ta wic is her husband,toh duk wani abinda zata mata a yanzu bai biya fifin ba shi ya sa take dagewa da strength ɗin ra take sokawa Muhibba mgn cikin mgn dan ba zata yarda yar uwar ta ta cigaba da fuskantar cin zarafin kishiya ba alhalin ta san komai na kishiyar...

Ga Muhibba kuwa babbar regret ɗin ta a rayuwa shine yarda da tayi da Hamida har Hamida ta san sirrin ta yanzu gashi tana mata barazana,abin kan dame ta ba kaɗan ba...

Thursday morning

Duk suna zaune ana breakfast a part ɗin su Ammy as family,kowa cin abincin sa yake yi ba tare da ya tanka ba,sai da aka yi nisa sai Muhibba ta fara jin wani iri a jikin ta,sincerely tana jin pains kamar kullum but fear ɗin ta shine kar ta buɗe baki ta furta Hamida ta taso ta gaba akan she is lying,dan yau ɗin girkin fifi ne wacce ita duk wannan bidirin da ke faruwa tsakanin Hamida da Muhibba bata da masaniya all she is after shine rainon cikin ta da lfyr jikin ta kafin ranar haihuwar ta dan ta sani,Dr ya sanar da ita bai ɓoye mata ba akan zai yi wuya ta rayu in har tayi experiencing labour pains,but ya bata option akan ana iya yi mata surgery a ciro babyn in kamar saura satittuka kafin EDD ɗin ta but sai ta ƙi yarda ta ce tana so ta ji zafin da mahaifiyar ta ta ji a yayin da ta haife ta kafin ta bar duniya,sbd believe ɗin ta shine duk mace da bata san zafin haihuwa ba toh ba zata mutunta kyauta da baiwar da Allah ya mata ba na bata kyautar haihuwar,so she choose to undergo the labour pains...

Duk motsin Muhibba a kan idon Hamida har dai Muhibban ta gaji da mutsu mutsu ta tashi ta bar wurin,murmushi Hamida tayi ta cigaba da cin abincin ta yayin da ake tmbyr ko lfy ta tafi,Ammy ce ta tashi ta bi bayan ta dan duba ko lfy su kuma sauran suka cigaba da cin abincin su except Saheeb da ya bar abincin ya bi Ammy dan duba Muhibba bcoz yana da tafiya yau mai muhimmanci..

Kasa natsuwa fifi tayi sai ta tashi da ƙyar ta bi sa,a hanya suka haɗe sai ya ruƙo ta a jikin sa suna takawa a sannu har suka ƙaraso ciki...

Ganin Ammy a parlor tana ta kiran sunan Muhibba ya saka Saheeb tmbyr me ya faru nan Ammy ke shaida mai wai Muhibban ce ta ce ta tafi bata son ganin ta...

Abin ya ɓatawa Saheeb rai mahaifiyar sa ce matar sa bata son gani,so annoying sai ya ja ƙaramin tsaki,ya ce da Ammyn ta tafi bayan bata haƙurin da yayi,shi da fifi suka shige ɗakin fifin inda ya ɗau bag ɗin sa da ba zata iya ɗaukar mai ba,suka fito da ƙyar ta raka sa ya shiga mota,ya ɗan leƙo da kan sa ya manna mata kiss a goshi a sannan yayi waving nata ya tafi itama tana waving nasa kafin ta koma ciki cikin tafiyar ɗai ɗai tana mai jin kewar sa tun yanzu..

#Mamuh*37*

Rayuwa ta sauya sosai a cikin gidan dan komai na tafiya normal fiye da tunanin mai tunani,rayuwar farin ciki ne kawai ke wakana a cikin gidan..

Soyayya kam tsakanin fifi da Marshall sai abinda yayi gaba,har ga Allah basu taɓa tsammanin shaƙuwar su tayi ƙarfi haka ba da komai ya faru da ɗaya sai ɗaya ya ji alama a jikin sa..

Wasa wasa ƙauna mai ƙarfi ta shige su sosai,duk da fifi ta fi dangana kusancin nasu a matsayin shaƙuwar rabuwa dan ta san days ɗin ta are numbered already..

Yayin da shi Saheeb yanzu yake kuma jin soyayyar ta a ran sa sai dai bai da wani tym na nuna mata ɗumbin soyayyar sa gare ta sakamakon yanayin aikin sa da bai ba shi isasshen lkcn spending tym ɗin sa da ita ba..

Ita kuma gani take kamar rashin amincewa da ita da bai yi bane a zuciyar sa har yanzu ya sa baya wani nuna mata soyayya ƙarara yadda ta daɗe tana dreaming...

A rayuwar Muhibba kuma lamuran ta ta fawwalawa mai duka bcos komai ya tsaya mata cak,bata isa ta bugi ƙirji ta ce zata yi wani abu ba sai Hamida ta ɗora alamar tmby a behaviour ɗin ta..

Sannan Saheeb,ba wani daɗin sa take ji ba dan yadda take stressing nasa in suna tare ko kuma suna waya,abin dai sai a hnkl..

Hamida kuma da Khalid zaman su abij sha'awa dan tun wannan matsalar da suka samu bata kuma yarda wata kafa ta shiga tsakanin su ba,kullum tana kafa kafa da gudun zuciyar sa musamman in mgn ta kama irin ta argument ɗin nan,toh bata wani ja sai ta karɓi laifin dan dai kar su sami saɓani..

Khalid bai da wani complain sosai yanzu a rayuwa dan matar sa na masa duk wasu abin da ya kamata,haka akwai fahimtar juna sosai tsakanin sa da fifi haka nan ma tsakanin matar sa Hamida da yʼar uwar ta fifi..

Duk da tight schedule na Saheeb,hakan bai hana sa yin alherin da ya saba ba ga mabuƙata in buƙatar hakan ta taso ba,kuma yana ƙoƙarin sauke haƙƙoƙin sa as a husband of two wives...

Ammy da Hajja ba abinda ya fi masu wannan daɗi ganin kawunan yaran a haɗe,kuskuren da suka yi a baya ba su fatar kuma tafka wannan kuskuren ever again a rayuwar su,dan duk inda mutum ya kai ga hassadar sa toh in ya ga bond dake tsakanin family members ɗin nan toh dole ya kawar da kan sa dan relationship ne mai ƙarfi..

Cikin fifi na shiga watar haihuwar sa wato wata na tara,Ammy ta fara bata special care kusan yini take yi a sashen fifi,wacce tayi nauyi zama da ƙyar tashi da ƙyar,bata fuskanci matsalolin early pregnancy ba but yanzu da ta shiga last trimester ɗin ta sai ta ga kamar yanzu take fuskantar matsalolin early pregnancy ɗin..

Kama daga ruwan wanka,abinci,kula da ita,komai Ammy ke mata shi bcos Hamida have to take care of her husband as well,in aka bar ta da ɗawainiyar fifi da na mijin ta abin zai mata yawa,dalilin da ya sa Ammy ke kai kawo a sashen fifi kenan,moreover Saheeb is always busy a yʼan kwanakin sai da ƙyar ma take iya ganin sa kuma baya kwana a tare da ita,ko girkin ta ne ko ba nata ba dan Muhibba na fuskantar matsanancin ciwo mai barazanarwa ga rayuwar ta...

Ita dai fifi ta san musabbabin matsalar Muhibba but da yake ba saka kan ta take a lamuran ta ba,sai ta ƙyale ta maida hnkl ta ga nata health ɗin dan tayi alƙawarin kula da babyn ta har ranar da zata haifin babyn kafin ta bar duniya...

Fargaba sosai ke sabunta a zuciyar fifi a duk ranar da ta farka a sabon rana ta tuna kwanakin haihuwar ta matsowa yake which is equivalent to ranakun mutuwar ta dake gab..

Ba kasafai Saheeb ke bibiyar scanning ɗin ta ba wanda hakan ya bata damar ganawa da likitan ta secretly bcos shi Saheeb ya san ya damƙawa Khalid ne kula da lfyr ta wanda daga shi har Khalid ɗin babu wanda ke da masaniya akan likitan da take gani a ɓoy,duk kuwa da Khalid yana iya ƙoƙarin sa na ganin ya bata extra care but bata yarda ko secretly ba tare da sanin Hamida ko mijin ta ta sanar da shi conditions da doctorn nata ya bata ba game da yiwuwar haihuwar ta...

Lyk always yau ma tayi shirin ta cikin maternity gown ɗin ta ta saka ƙaramin hijabi ta tako da ƙyar ta fito zuwa farfajiyar gidan tana duba motar da driver ke jiran ta dan zata tafi ganin likitan ta sbd Saheeb baya nan kuma a nan gidan ta sallame su ne akan wurin Khalid zata tafi dan a mata dubiya ta musamman dan ta ƙi yarda a kawo mata scanning machine ɗin gidan dan in hakan ya faru ta san zai yi wuya ta haɗu da likitan ta da suka haɗu a yawon binciken ta ta waya har dai abin ya kai su ga haɗuwa concurrently...

Motar ta nufa ta shiga tana ajiyar zuciya kamar tayi gudun tsere dan cikin ya mata nauyi ga matsalar cardiac disorder dake damin ta wato health issue ɗin ta..

Jan motar yayi suka fita,sai dai yau bata bari sun fara zuwa wurin Khalid ba ta ce mai ya kai ta ɗaya wurin da yake kai ta in sun baro wurin Khalid..

Juya kan motar yayi suka nufi asibitin likitan ta inda ya duba ta ya kuma bata shawarwari da gargaɗin kar ta rinƙa ɗaga hnkl ta dan the more tana ɗaga hnkl ta the more damuwar ta zai yi muni,haka dai ta karɓi drugs ɗin ta ta koma mota suka tafi asibitin du Khalid inda nan ma ya bata kula ta musamman kafin su dawo gida...

****

Tunda fifi ta shiga satin haihuwar ta fargabar ta ke gaba gaba,ba laifi tana samin kula daga wurin Hamida da mijin ta Saheeb sai dai kular ragagge ne dan ba wani enough tym gare sa ba,a wannan yanayi ta fi buƙatar sa sai dai ya mata nisa dole ta haƙura wasu lokutan ya rinƙa attending travelling ɗin sa dan suna da muhimmanci duba da matsayin sa...

Suna zaune a parlor suna hira,Hamida,Ammy da fifi wacce jefi jefi take saka masu baki dan bacci baccin dake ɗibar ta..

La'akari da baccin da ta fara yi ne ya sa Ammy yi ma Hamida alama da su ƙyale ta ta huta,daga nan suka fita suka bar mata parlorn inda ta cigaba da baccin nata bisa wani ƙaramin mattress da ta maida sa abin kwanciya in ba ɗakin ta take ba...

Cikin baccin nata ta ji muryar Muhibba na maganganu wanda bata gane ba sai ta daure ta buɗe idanun ta,nan ta ga tana ta kai tana komowa ita ɗaya,waya sagale a kunnen ta tana mgn da alamar damuwa a muryar ta...

Bin ta da kallo fifi tayi kawai ta maida idon ta ta rufe dan in da sabo ta saba da halin i don't care da Muhibba ke nuna mata ita da unborn baby ɗin ta,duk da tana ganin kamar Muhibban ta san very soon zata mutu ta bar mata mijin nata su cigaba da rayuwar su kamar yadda kullum take nanatawa kan ta...

Jin muryar ta tayi tana faɗin

"Ban sani ba amma zafin da nake ji yanzu ya fi na da doctor,ka taimake ni pls,i don't wanna die soon"..

Gaban fifi ne ya buga jin kalmar mutuwa daga bakin Muhibba wic means ciwon da take yi yana iya yin sanadin rasa ran ta kenan...

Kamar ta tashi amma ta fasa ta bari akan zata ma Hamida mgn in ya so sai a sanar da su Ammy abinda Muhibba ke fuskanta dan kar ayi rashi biyu..

Ta tausayawa Marshall ba kaɗan ba tayi zaton ita kaɗai ce ke cikin matsala da damuwa ashe damuwar Muhibba ke ciki itama kawai dai nata tana ɓoye sa ne dan ita babba ce kuma babu wanda ya sani cikin iyayen su...

A daren ranar suka yi waya da Saheeb ta ji kamar ta sanar da shi amma ta fasa,sai da suka gama sannan ta kira Hamida ta mata bayani sai dai to her greatest surprise sai ta ji Hamida ta ce mata

"Sweetheart pls ki kula da kan ki before anyone else,it's all about u and no one but u,ok so good nit je ki kwanta"daga haka ta kashe wayar..

Haka fifi ta kwanta cikin jimami da zullumin me zai zamo sakamakon rashin lafiyar su su duka kuma ya Saheeb zai ji in ya san duk ciwon da suke yi na ajali ne..

#Mamuh[8/24, 8:12 AM] +234 808 540 5215: *38*

Tun daren jiya fifi ke jin ta aani iri wanda ba komai bane sama da labour pains dan kuwa ranar ta gabato but sai tayi ta sharewa dan da ya mata sai ya tsaya,ganin haka ya sa ta kyale abin kawai ta sha pain relief ta kwanta tayi baccin ta..

Da gari ya waye sai ta ji sayau babu ciwon babu alamar sa sai ta ɗan yi ayyukan da zata iya yi kafin daga bisani ta tafi tayi wanka..

As always yau ma maternity gown ɗin ta ta saka na atamfa ta saka hijab ta fito tana tafiya a hnkl har ta iso sashen su Ammy...

Da Hajja ta fara cin karo wacce take zaune bisa three seaters tana danna counter dake hannun ta,tana sanye da hijabi..

Saurin taro ta tayi tana mata faɗar karambanin da tayi na zuwa nan sashen alhalin ta san ba wani lafiya ne da ita ba..

Murmushi kawai tayi ta zauna da ƙyar suka gaisa da kakar nata inda ta tmby ta me take buƙatar ci sai ta ce mata duk abinda ta ci itama shi zata ci..

Kiran mai girkin su tayi ta umarce ta da ta kawo ma fifi kunun accan da ta mata da alale kuma ta saka man shanun da ta saka mata..

Murmushi fifi tayi ta shiga zolayar kakan nata tana ce mata ta fiye kwaɗayi duk ita kaɗai ta ci wannan abin..

Dariya kawai Hajjan ta mata tana ce mata lallai tayi ƙwari tunda ta iya tsokanar faɗa.

Suna zaune a wurin aka kawo mata abincin ta zauna ta ci sosai har ta kammala sannan ta dubi Hajja ta ce mata

"Hajja ƙila fah abinci na na ƙarshe kenan a duniyar nan,kamar ta ƙaro min"!!wani faɗi gaban Hajja yayi dan straight foward person ce fifi bata ɓoye ɓoye shi ya sa ta faɗi abinda ke ran ta...

Matsowa kusa da ita Hajja tayi sai ta rungumo ta ta gefe tana mata kul da kuma nanata wannan kalmar but fifi insisted ta cigaba da furta mata kalmar rabuwa..

Sosai ta karya zuciyar Hajja har hawaye ya cicciko mata a ido but bata bari sun zubo ba sai ta aika a kirawo mata Ammy...

Ammy na zuwa da yar fara'ar ta sai ta ga mahaifiyar ta na ɓoye fuskar ta kamar kuka take yi..

Da sauri ta ƙaraso ta hau tmbyr ba'asi inda Hajja ta nuna mata fifi,ita kuma ta maida idon ta ga fifi...

Ko kafin ta ce zata ce wani abin har fifi ta fara yi mata mgnr mutuwa kamar dai yadda ta ma Hajja..

Zuciya a karye Ammy ta matso ta rungume ta tana kuka tana faɗa mata InshaAllah she will pass through da yardar ubangiji,kuma zata raini yar ta ko ɗan ta da kan ta..

Ita dai jin su kawai take but ta san abu ne mai wuya bcos likitan ta ya faɗa mata kuma ita kan ta ta san tana ji a jikin ta komai ba lfy bane sai dai ganin halin da suka shiga ciki sai bata cigaba da kira masu kalmar mutuwar ba ta dai yi shiru...

Ta jima a nan wurin su Ammy suna ta nan nan da ita dan dai kar ta kuma tado mgnr mutuwar nan,Ammy kam sai da ta ɓoye kan ta a ɗakin ta tayi kuka sosai dan ta san gaskiya fifi ke faɗa,bcos an sanar da su,Khalid ya faɗa masu a scanning ɗin ta an gano tana da matsalar zuciya kuma ba lallai bane ta iya haihuwa da kan ta ba but ita ta ce ta fi so a bar ta tayi labour da kan ta..

"Wannan masifa da me yayi kama,tun haihuwar yarinyar nan har yanzu rayuwar ta a stalk yake,rayuwa take yi a duniya amma lfyr ta bai da inganci,yanzu da ta ɗan fara jin daɗin rayuwar nata kuma,mutuwa zai yanke mata shi"..Ammy ce ke kuka tana mgnr ita kaɗai bayan fifi ta bar su ta nufi sashen Hamida..

Har dare dai bata wani sami sauyi ba dan jikin ta duk yayi sanyi,tsoro ya shige ta,fargabar rabuwa da fifi bai bar ta ba,sai a yanzu ma take jin sabon shaƙuwa na shigar ta akan fifi..

Sallar dare tayi ta musamman dama ta saba amma na yau daban ne,ta jima tana roƙon Allah akan ya rangwama ma fifi ya ji ƙan ta ya kawo mata komai cikin sauƙi ya shigo lamarin su..

Haka ma Hajja ta kwana tana ma fifi addu'a dan zuciyar ta ya karye akan wannan abin..

Bayan fifi ta fita daga sashen su Ammy sai ta nufi sashen Hamida inda nan ma duk kalmar mutuwar ce,sai dai ita Hamida bata yarda memory ɗin yayi lasting a kan ta ba dan bata yarda fifi zata mutu ta bar su ba,ta yarda cewa in har fifi zata iya riƙe babyn ta for good 9 months toh ta san da hukuncin ubangiji she will pass through her labour successfully..

Ƙarfafa mata gwiwa Hamida tayi ta yi har Khalid da ya dawo daga aiki yayi joining nata suna ta ba fifi mgn da ya sanyaya mata zuciya but a can ciki,ta san me zai faru a ƙarshe...

Har bedroom Hamida ta rako fifi ta taimaka mata ta sauya kayan ta zuwa comfortable night wears sannan ta mata duk abinda ya dace kafin ta tafi dan ta ce a nan zata kwana but fifi ta ƙi yarda ta ce ta tafi kawai in ba haka ba toh kuka zata saka mata,jin haka sai Hamida ta rarrashi fifi ta ce amma ba bacci zata yi ba zata je ne ta rinƙa leƙo ta..

A hakan ma da ƙyar fifi ta yarda sannan Hamida ta kashe mata wutar ɗakin ta tafi..

Bayan tafiyar Hamida ne fifi ta ciro wayar ta tayi dialing numbern daddyn su inda bayan ringing huɗu ya ɗaga suka gaisa ya tmby ta ya jiki ta ce mai lfy take..

Suka ɗan yi hira kafin daga bisani suka yi sallama,instead tayi bacci sai ta hau kiran layin mijin ta but duk ringing ɗin da yayi ta yi ba a ɗaga ba,haka hnkl ta ya tashi har ta tura mai saƙonni babu iyaka ko zai kira ta ko ya maido mata da reply but bai turo ba bai kuma kira ba sai ta daure ta ajiye wayar ta rufe idanun ta dan yin bacci...

****

Misalin ƙarfe uku na dare ta ji wani abu ya murɗa mata cikin baccin ta but bata buɗe idanun ta ba sai ta ɗan gyara kwanciyar..

Can kuma ta ji wani azababben ciwo a ƙasan marar ta nan take ta buɗe idanun ta ta fara salati a ran ta,tana nan a haka kafin ta tashi ciwon baya ya riƙe ta,tun tana iya resisting ciwon har ta kasa ta fara addu'ar a bayyane,da abin yayi tsanani ko ina ya amsa yana mata ciwo da raɗaɗi sai kawai ta tsala ihu..

Ihun nata ne ya doki kunnen Muhibba dake faman murƙususun ta a ɗakin ta dan dare ne kuma babu hayaniya so ko spoon ne aka yi dropping mutum na iya jin ƙarar sa bare wannan ƙara ce mai sauti...

Ɗan dakatawa tayi daga juye juyen ta ta tsaya shiru duk da zafin da take ji haka ta tako a duƙe ta fito zuwa hanyar ɗakin fifi..

Ihun ta kuma ji a karo na huɗu nan take ta ruɗe ta fara yunƙurin kai hannun ta ƙofar ɗakin amma ina,juyi cikin ta yayi wanda ya haddasa mata faɗi wurin ƙasa tana ta riƙe cikin tana numfashi sama sama...

A nan ɗakin fifi kuwa zafin da take ji bata taɓa jin sa ba tun da ta shigo duniyar nan sbd zafin is irresistible..

Hannun ta ta kai ga side drawer ɗin ta ta laluɓo wayar ta,ga ba haske ga halin da take ciki...

Bata ma san numbern wa ta kira ba ita dai tayi dialing number,wayar na ta ringing sai daga baya aka ɗaga..

Tana jin an ɗaga sai ta fara mgn a wahalce da rashin sabo da yanayin dan har ta fara kuka,tunanin ta mutuwar ce zata yi

"Hamee...ham...Hamee ki zo. Pls ki zo..am gonna die..pls come"ta ƙarasa mgnr tana jan kalmar come ɗin haɗe da tsala wani ihun...

Wayar ta wurgar ta faɗo ƙasa tana ta juye juye tana kuka tana nemar agaji da tallafin mutani...

Kusan 5 minutes bayan ta yi kiran tana durƙushe sai ta ji hayaniya daga haka ta ga an buɗe ƙofar an kunna wuta..

Already ta fara fita hayyacin ta dan haka bata san wa da wa suka shigo ba sai dai ta ji ana kinkimar ta ta mutani biyu a hanzarce...

Muhibba dake sume a ƙasa bakin ƙofar ɗakin fifi Khalid ya kira mai gadin su da ya je ya buɗe mai gate haka ya kai ta motar sa bayan motar su fifi ya tafi wanda Hamida ce ke jan motar dan ba zasu iya jiran driver ya zo ba..

Wsni irin speedy driving Hamida ke yi a kan titin cikin wannan tsakiyar daren tana yi tana kuka tana juyowa tana kallon fifi dake ta juye juye..

Ammy da Hajja dake riƙe da ita kuwa cikin su babu wanda gwiwar sa bai sage da al'amarin ba sai tofa mat addu'a suke ta yi...

Haka Khalid ma yayi ta banka gudu a kan titi yana bayan su Hamida,dai dai inda hanya ta raba nan suka rabu,motar su Hamida yayi dama nasa kuma yayi hagu..

Suka cigaba da gudu har dai motar su Hamida ya iso wani babbar asibiti inda nan Khalid ke aiki wato National hospital dake garin abuja...

Da sauri Hamida ta fito a birkice ta shiga ta kirawo su su zo emergency ne,sannan suka zo da gadon ɗaukar patient aka fito da fifi daga motat aka ɗora saman gadon aka yi wheeling nata zuwa ciki..

Shigar da ita E&O unit aka yi aka dakatar da su Ammy dake yunƙurin shiga ciki...

Card aka buɗe mata sabo fil sannan aka tmby Hamida wasu informations ɗin fifi while ana ciki ana ƙoƙarin stabilizing fifi...

Duk a rikice Hamida take sai kai kawo take ta yi a nan ta nemi da a ara mata waya zata kira mijin ta a nan yake aiki ta faɗa masu sunan sa sannan suka bata waya...

Kiran layin Khalid tayi wanda shima yana can wani asibitin an shigar da Muhibba ɗakin emergency tana numfashi sama sama da ƙyar...

Haɗa sa da likitan da aka kira tayi inda ya mai bayanin komai dangane da fifi sannan suka ajiye wayar...

Duk inda natsuwa take toh ta ƙauracewa wannan ahali a wannan dare..

It's already 4:50am kusan 5am na asuba but babu wani improvement a condition ɗin fifi abinda ya tsorata su kenan dan sau biyu ana so a mata shirin shiga theater dan ceto rayuwar babyn but ta tmby su har wani lkc bavyn zai rayu suka faɗa mata sannan ta tmby har wani lkc labour ɗin zai kai ta suka faɗa mata sai ta ce toh su bar ta dan tana so ta haihu da kan ta...

Duk yadda suka nuna mata haɗarin hakan sai ta nuna masu ta fi su sani dan ita ke da ciwon a jikin ta kuma ko a yi aiki ko ta haihu da kan ta ta san mutuwa zata yi dan haka ta ce su kirawo mata yar uwar ta...

Duk wannan mgnr ya gudana ne bayan ciwon ya ɗan lafa mata but sai basu kira Hamida ba dan suna ganin hnkl ta zai tashi in ta ga condition ɗin ta...

Ai kuwa ciwon na dawo mata ta fara kiran sunan Hamida,sai nanata sunan take yi har dai suka fito suka yi requesting Hamida ta shigo...

Da gudu ta shigo ɗakin ta ƙarasa ta rungume fifi dake kwance akan couch ɗin haihuwa ta fashe da kuka tana faɗin

"Mufida pls fight it...ki yi yaƙi ki tashi kar ki bar mu,..ki tuna fah yanzu Ƙaunarmu ke ƙaruwa,yanzu ne Ƙaunarmu ya kamata ya taimaka mana ya kawo mu kusa da juna ba wai mu rabe ba,Mufida ki tuna fah in baki yi fighting ma rayuwar ki ba this baby will be motherless ya kike so babyn nan ta ji ko ya ji?kina son babyn ya taso ko ta taso cikin rashin mahaifiya ne?ki duba ɗumbin mutanin dake son ki pls Mufida ki tashi kar ki bar mu"!!kuka sosai Hamida ke yi wanda fifi ke taya ta dan ta san ba rai zata yi ba tana ji a jikin ta...

Riƙo hannun Hamida tayi cikim azaban raɗɗin da take ji ta fara mgn

"Ko na mutu Hamee..na baki kyautar abinda zan haifa..ki ɗauka,ki kula da shi..ki kula da shi yadda in ina raye zaki kula da ni...ki bashi duk soyayya da ƙaunar da ba zan ba shi ba...pls promise me...promise me that u will fulfil my request"!!da sauri ta gyaɗa mata kai sai tayi murmushin da yafi kuka ciwo sannan ta ce da Hamida

"Kuma kar ki manta da alƙawarin mu na daddyn mu kin ji?kar ki manta ko bayan na mutu ki tsaya ki cika mana alƙawarin mu ok"?kuka kawai Hamida ta fashe da shi tana daɗa rungume Fifi..

Sai da kukan yayi tsanani sannan aka zo aka fitar da Hamida tana fizgewa tana faɗin a bar ta ta gana da ƴar uwar ta but ina,haka aka fitar da ita tana kuka..

Bayan misalin awa biyu,Khalid ya dawo nan asibitin da fifi take ya sanar da su ya kira Saheeb ya faɗa mai an yi admitting Muhibba a asibiti kuma dama yanzu ya dawo so zai tafi can wurin Muhibba..

Ammy ce tayi saurin tmbyr sa ko ya faɗa mai har fifi sai ya ce a'a sai ta ce mai a bar shi kar a faɗa mai tunda su suna nan zasu iya tsaya ma fifi shi kuma ya tsaya da Muhibba kar su yi son kai...

****

After lyk 5 hours da zuwan su fifi asibiti an ɗan tsumayi haihuwan but babu wani cigaba sai kawai Khalid yayi signing ya ce su shirya ta a shiga da ita theater a mata

aiki kawai dan situation ɗin fifi na deteriorating ga matsalar cardiac disorder ɗin ta ga na babyn dake jikin ta dake shiga distres..

Wata sabuwa ce ta taso dan ana ta ceton ran ta su Ammy na can na kuka a waje da Hajja,ga Khalid dake cikin firgici but haka fifi ta ƙi yarda a shigar da ita ɗakin theater ta ce sai mijin ta ya zo sun gana sannan ta yarda a shigar da ita..

Duk yadda suka yi haka ta ƙi yarda dole aka fara nemar layin Saheeb wanda sai ringing yake ta yi ba a ɗaga ba..

Hankula ne ya kuma tashi dan fifi bata yarda a shigar da ita ba ana ta addu'a a waje ita kuma sai nanata sunan _"Gentle"_ take ta yi wato Saheeb sai daga baya ma ma'aiakatn suka gane waye gentle ɗin nan aka zafafa kiran Saheeb but bai ɗaga ba,ga fifi na jin jiki ga Hamida na kuka a jikin Khalid...

#Mamuh

[8/24, 8:12 AM] +234 808 540 5215: *39*

On the other side kuma,bayan Khalid ya kira Saheeb ya sanar da shi abinda ake ciki sai ya tura mai adireshin asibitin da take..

Already dama suna gab da landing dama tafiya yayi kusan 6 days ago toh a yau zasu dawo shi ya sa yana dawowa ya nufi asibitin ba tare da ya sauya kayan jikin sa ba...

A lkcn da ya ƙaraso asibitin har Khalid ya tafi,so he appears so shattered kamar marar lfy,haka ya nemi ɗakin da take aka nuna mai sannan ya tafi hnkl tashe..

Yana shiga ya hango ta kwance kamar marar rai,nan hnkl sa ya daɗa tashi ya kasa natsuwa sai da ya ƙarasa gare ta ya durƙusa ƙasa..

Fuskar ta dake lulluɓe kusan duka cikin abin bada numfashi(oxygen)ya kalla ya kawo hannun sa ya fara shafa fuskar nata har ta ɗan motsa ta buɗe idanun nata da ƙyar cikin wahala..

Ganin shine sai ta ƙara buɗe idanun ta da kyau dan ta gan shi shima ya gan ta,hannun ta na rawa ta ɗora saman nasa..

Da sauri ya maida idanun sa kan hannun nata ya kalla sannan ya kalli fuskar ta da ya sauya yayi fari kamar wacce bata da isasshiyar jini a jiki..

Wani tausayin ta ne ya kama shi mai tsanani sai ya ɗan kawar da fuskar sa dan zuciyar sa ya karye for the very first tym Saheeb ya tsinci kan sa da zubda hawaye akan rashin ƙwarin gwiwar ciwon matar sa...

Murya a disashe can ciki yana rawa ta fara mgn tana jan numfashi da ƙyar tana ajiyar zuciya..

"Miji na...ka zo ashe...ban san..ban..ban san zaka zo nan kusa ba..na daɗe ina ta jiran ka ina ta ce masu su kira min kai amma...babu wanda ya gwada kiran ka...but a yanzu da na gan ka na ji daɗi"!da ƙyar ta kai ayar zancen sannan ta ja numfashi da ƙarfi kafin daga bisani ta dakata...

Kallon ta yake yi cikin halin tsantsar tausayin ta ya matso kusa da ita suna kallon juna..

Shafa fuskar ta yayi yana manna mata kisses a kumatun ta hawaye na zubo mai ya kasa mgn sai hawaye dake ta fito mai...

Hannu na rawa ta kawo ta shafa fuskar sa tana goge mai hawayen da ke fito mai tana girgiza mai kai alamar ya daina kuka sai dai shima girgiza mata kan yake yi akan ba zai daina kukan ba..

"Miji na ka yi shiru ka saurare ni..tun ɗazu nake jiran ka ka zo,i hv been fighting with this feelings dan ka zo mu gana,ganawa na ƙarshe"!!saurin rufe mata baki yayi da hannun sa yana girgiza mata kai but ta ɗan fizge ta cigaba da mgnr ta..

"Saheeb am dying...i am dying...it is certain..su kan su likitocin sun gani sun faɗa min..but ina ta daurewa dan ka zo in gan ka ganin ƙarshe kafin in mutu...na riga na gama ganin all signs of death Saheeb kuma na san at any moment...zan tafi in bar ka ba dan ina so ba sai dan ya zama dole...Saheeb bana son ka dakatar da ni daga mgnr da zan yi,i know it will hurt u but ka yafe min dan in sami rahamar ubangiji"..

Ɗan numfasa tayi kuma tana jan iska da ƙyar kamar zata tafi sai tayi yunƙuri ta cigaba da mgnr dan nauyin da take ji a ƙirjin ta ya wuce misali..

"Miji na...na zauna da kai sama da shekaru goma,baka taɓa min abinda zan ce ka zalunce ni ba..baka taɓa min abinda bana so ba,ka yi ƙoƙarin ka wurin ganin ka sauke haƙƙin ka a matsayin ka na miji na,and am proud of u for that..komai ka min a rayuwa sai dai ka san me"??ta tmby tana ɗage giran ta biyu sai ya girgiza mata kai yana kuma damƙe hannun ta cikin nasa yana zubda hawaye..

"Nayi blackmailing naka for long,..duk wasu abubuwan da na faɗa maka akan rashin lfy ta were all lies,i was sick but not to that extent,a lkcn da na tafi ganin likita..ya faɗa min cewa uterus ɗi na was weak but ba har haka ba kamar yadda na faɗa maka ba...i did what i did kawai dan in sami attention ɗin ka ne,ni na saka likita ya rubuta min abinda ya rubuta a file ɗi na sannan na ce ya bani file ɗin in kawo maka ka gani...the result was perfect na sami attention ɗin ka sai dai da yake Mufida bata da haƙƙi na..maganin da na rinƙa sha a matsayin antidepressant ashe yana min illa a jiki ban sani ba...ban daina shan maganim ba duk dan in sami attention ɗin ka,miji na...ka yafe min ka gafarta min...na san na ɗau haƙƙin ka kai da Mufida sbd selfishness ɗi na ashe ina nawa ne Allah ya tanadi min nawa hukuncin nayi tunanin hikima ta ta janyo ka gare ni ashe mutuwa ta na janyo,am deeply sorry Saheeb ka yafe min dan in sami Peaceful death,dan am dying very soon..."!!

A halin nan da yake ciki na ganin matar sa zata tafi ta bar sa bai ɗaukaka mgnr nata da ta gama yi ba sai girgiza mata kai yake ta yi yana ce mata a'a ta daina mgnr zata mutu..

Da yake ita ta san abinda take ji sai ta ƙyale sa har ta ɗan kuma gathering wani ƙarfin ta kuma nemar yafiyar sa...

Sai ga Saheeb na sharɓar kuka kamar ƙaramin yaro,daɗa damƙe hannun sa tayi ta ce

"Saheeb ka ce ka yafe min dan kar in mutu da haƙƙin ka a tare da ni,pls"!!yana kuka yana rungume ta daga kwancen da take bakin sa na rawa ya ce

"Muhibba na yafe maki..baki min komai ba,haka Allah ya ƙaddara zaman mu zata kasance,ni baki min komai ba kuma na yafe maki"!!murmushi tayi mai tafe da ciwon rasa rai sai ta ce mai

"Nagode miji na..na ji daɗi da ka yafe min..na san zan mutu a matsayin yardarjiyar mace da mijin ta ya yarda da ita..ka min alfarma ɗaya Saheeb"..da sauri ya ce

"Menene alfarmar da kike nema in maki Muhibba"?ɗan tsagaitawa tayi sannan ta ce

"Ko bayan na mutu ka cigaba da so na kamar yadda kake so na a yayin da nake doron ƙasa ina rayuwa,ka so ni fiye da yadda ka so ni while am still alive..promise to always pray for me yayin da na bar ka bana tare da kai..i know am still being selfish but son da nake maka ya kawo haka..promise me that Ƙaunarmu ba zata yanke ba ko bayan bana raye a duniya"!!yana kuka yana kissing hannayen ta ya ce mata

"Na maki alƙawari Muhibba,zan maki addu'a a ko da yaushe..ko a sallah na ko a bacci na"!!murmushi ta mai ta ce mai..

"Ka nema min yafiyar Mufida..ka ce ta yafe min pls"gyaɗa mata kai yayi sai ta lumshe idanun ta hawaye na zubo mata..

A halin gajiya da yanayin da take ciki ta ruƙo sa gagam jikin ta na rawa ta ce

"Zo kusa da ni ka kwanta while am dying,i want u next to me while i will fade away ka ji"!!ran maza ya motsu Saheeb duk ya rikice ya ruɗe ya rasa abin yi haka ya zo kusa da ita ya kwantar da kan sa a ƙirjin ta tana shafa kan sa yana kuka a zuciyar sa kuma yana jin raɗaɗi yana mata addu'a haka tun Muhibba na da nunfashi a hnkl ya fara tafiya har ya tsaya cak..

Yana jin ta sauke ajiyar zuciya mai ƙarfi da furta kalmar "sallalahu alaihi wasallam" alamar a zuciyar ta ta fara shahadar sai ta ƙarasa a bayyane..

Ɗago da kan sa yayi ya dube ta yayi zurum kamar statue sai daga baya ya miƙe tsaye ya shafa fuskar ta sannan ya manna mata last kiss a goshin ta ya fito waje...

Ko da suka ga yanayin sa su likitocin,sun san ta tafi ne sai aka shiga ciki kawai aka fara gyara ta...

Yana manne da jikin bango ya fiddo wayar sa sai ya ga kira ya shigo dama wayar a silent yake..

Khalid ke kiran sai ya ɗaga ya kara a kunne ba tare da ya ce komai ba..

Kusan minti ɗaya wayar na kunnen sa kafin ya sauke ya fito jiki a sanyaye ya shiga motar da ya kawo sa dama driver ne..

Gaya mai inda zai kai sa kawai yayi sai driver ya ja motar suka kama hanya...

****

Motar nasu na tsayawa ya fito da ɗan sauri cikin hanzari ya ƙarasa ciki yana tafe kamar zai haɗa da gudu....

Cikin sauri ya ƙarasa ciki inda da zuwan sa ya fara hango su Ammy hnkl tashe..

Ƙarasawa gare su yayi ya tmby inda fifi take nan hnkl tashe Ammy ta ce mai tana ciki tana tmbyr sa ya jikin Muhibba sai dai bai iya amsa mata ba ya wuce ciki inda fifi ke kwance ana shirya ta zuwa kayan theater..

Tana ganin sa ta miƙo mai hannun ta da sauri ya ƙarasa gare ta,abin is heart touching dan ba abu mai sauƙi bane a ce mutum ya rasa matar sa ɗaya ba cikin biyu sannan ɗayan da ta rage ma tana ƙoƙarin barin sa ba...

Durƙusawa Saheeb yayi a gaban ta yana kuka kamar dai yadda yayi ɗazu a wurin Muhibba bcos ita kan ta a nan ɗin,kalmar mutuwa take ta nanata mai sai da ya rufe mata baki sannan ta ɗan tsagaita..

Yana kukan ya rinƙa faɗa mata yadda yake son ta yake kuma ƙaunar ta,alfarmar da ya rinƙa nema daga gare ta shine kar ta tafi ta bar shi,in ta tafi ina zai fuskanta ya ji daɗi..

Yana kukan tana kukan suka rungume juna ta rinƙa nanata mai kar ya manta da ita ya saka ta a zuciyar sa duk da ta san irin son da take mai shi baya mata irin sa

amma ya mata alfarma ɗaya,ko bayan bata raye,kar ya manta da ita a zuciyar sa da rayuwar sa...

Da karayar zuci ya ce mata ta daina kiran mutuwa dan in har ta tafi shima bin ta zai yi..

"Na san ni mai laifi ne a gare ki Khadija amma ki sani tun farkon ganin da na maki..na tsinci kai na da son ki,so mai tsanani da ƙarfi haɗe da shiga zuciya farat ɗaya,ko da na rinƙa ƙyale ki ina barin ki a dai dai lkcn da kike buƙata na kusa da ke..ba yin kai na bane,Muhibba ce ke ciwo mai tsanani ban san ya zan yi,in na bar ta na dawo gare ki zata ga na so kai na da yawa tunda ke tawa ce yar uwa ta ce,wannan dalili ya sa nake ta kasancewa kusa da ita but duk da haka,hakan bai sa na bata rayuwa ba dan ina ji ina gani ta tafi ta bar ni,ta bar mu mu duka,ta bar mana duniyar,a yanzu da na san halin da kike ciki khadijah..bana so in rasa wata matar kuma..bana so in rasa ki..pls don't do this to me..i will never forgive myself in na zuba ido na kalle ki kika bar duniyar nan khadijah..ki taimake ni ki yi fighting wannan battle ɗin ba dan ni ba ba dan kowa ba sai dan babyn mu da Ƙaunarmu..ki dawo gare ni kar ki rabu da ni,i love u so very much my wife"!!ya ida yana kuka...

Itama kukan take yi sai aka zo aka fara tapping nasa akan ya fita dan har Hamida ta kuma dawowa tana kuka tana son ta shiga ciki amma aka hana ta..

Da ƙyar aka ɓamɓare hannun Saheeb daga na fifi suna kallon juna aka yi wheeling nata zuwa theater room inda suna shiga aka rufe ƙofa take wuta ya kawo mai kala..

Hankula duk a tashe,Hamida ta manne a jikin Hajja tana kuka kamar me,Khalid dake ta namijin ƙoƙari ma a yanzu ya kasa dan abin ya girmi tunanin sa dole ya zauna wuri ɗaya...

Ammy na ta addu'a a zuciyar ta da fatar Allah ya sa a yi aikin lfy,yayin da ta kalle Saheeb ta tmby sa ya jikin Muhibba..

Nan ya faɗa masu cewar ta bar su,salati Ammy ta fara yi Hajja ma haka,tashin hnkl da ba a saka masa rana...

Ana fama da ciwo ga karaya,sabon kuka ne ya kaure a asibitin shi kam daurewa yayi ta yi idanun sa duk sun yi ja jazir..

****

2 hours later

Wutar ɗakin theater ya mutu sai hnkl su ya koma ga ɗakin suka yi zurum zurum suna jiran jin sakamako..

Fargaba da zullumi duk ya addabi zukatan su musamman Hamida da ta matso gab da ƙofar ɗakin..

Bayan lyk 5 minutes Dr ya fito hannun sa riƙe da baby duk ya jigata,yana fitowa ya dubi fuskar su su duka,tausayin su ne ya kama sa ya rasa ta ina zai fara gaya masu sakamakon da suke jira,haka ya daure yayi na maza ya miƙo babyn yana faɗin..

"It's a boy"!!daga haka yayi shiru,Hamida ce ta karɓi babyn hannun ta na rawa sannan ta maida idanun ta ga Dr inda ya share zufan fuskar sa ya sauke wata nannauyar ajiyar zuciya sannan cikin tsoron ganin reaction ɗin su ya ce

"Am sorry"!!bai ƙara furta wata kalmar ba Hamida ta fara ganin duhu ko kafin a yi wani yunƙuri har ta fara tanga tanga zata faɗi..

Ammy dake kusa da ita ne ta riƙo ta wacce gwiwar ta ya gama sanyi,ta fashe da kuka tana salati..

Saheeb couldn't say or do anything but zamewa ƙasa da ya yi ya haɗe kai da hannayen sa biyu..

Khalid kuwa shi ya karɓi babyn dan tuni Hamida ta sume,already Hajja ta tsinke da lamarin a zuci take nata kukan but tana salati a hnkl a bayyane..

#Mamuh*40*

"She is in temporal comma,zata ɗau lkc kafin ta farfaɗo gabaɗaya so sai kun yi haƙuri da yanayin da ta shiga da kuma halin da zata cigaba da kasancewa a ciki for a while"!!..

Wani irin sanyi ne ya ratsa zuciyar Ammy da Hajja har ma da Khalid dake riƙe da baby a hannun sa..

Shi kuwa gogan da tun ɗazu yake durƙushe bai ɗago ba bare ya ce ƙala yana dai sauraron yadda su Ammy da sauran ke hamdala amma bai iya ɗagowa ba har sai da ya ɗau lkc sannan ya miƙe tsaye ya taka a hnkl har inda likitan ke tsaye ya tsaya a gaban sa ƙeƙam a gaban likitan yayi folding hannayen sa a ƙirjin sa sannan ya ce da likitan

"Sake maimaita abinda ka ce"shi kuwa likita tunanin sa overwhelming sakamakon nasa ya saka Saheeb har yake son maimaicin amsar da ya faɗa mai..

Gyara position yayi ya maimaita ma Saheeb sakamakon surgery ɗin,kamar ƙiftawar ido Saheeb ya shaƙo sa ya haɗa sa da bango yana shaƙe masa wuya.

A tsorace Khalid ya hau kiran sa yayi da Hajja ke mai faɗar wani irin rashin hnkl ne wannan.

Bai saurari kowa ba dan zuciya ta ɗibe sa sai gurnani yake ta yi yana kuma matse likitan,a taƙaice dai da ƙyar aka ƙwaci likitan yana ta faman tari..

Rai ɓace Saheeb ya hau shi da faɗa yana ta yi kamar ce mai aka yi fifin ma ta rasu..

"Wani irin daƙiƙi ne kai?how om earth zaka zo ma mutani da irin wannan banzar mgn as ur surgery outcome?haka kai aka koya maka ana conveying saƙo!?ko naku da dokoki ne da sigar conveying ma mutum ko patients relatives saƙon outcome ne?ta yaya zaka zo ka ba mu wannan incomplete answer ba tare da ka ƙarasa ba? dubi nan ka gani,that is her blood sister her twin sister,kana gani ai bayan ia gama faɗin banzan sakamakon ka ta sume,what if akwai mai hawan jini ko cardiac disorder kuma ya ji wannan shirmen naka ya yanke jiki ya faɗi ya mutu fah?kana fah ganin halin da muke ciki na nemar sanin mafitar wannan aikin but shi ne ka zo kana bamu irin wannan shashashar amsar"??..

Ammy ce ta tsawatar mai dan yadda yayi ta yi kamar shine mahaifin likitan ma abin was awkward..

Da ƙyar Saheeb ya daina aika ma likitan mugayen kallon da yayi ta aika mai da shi sannan ya ingiza sa ya shige cikin ɗakin da ba a gama gyara fifi ba..

Idanun sa a kan ta yana ta ƙure ta da kallo,daga inda ake gyare ta ne aka hango sa sai ya ɗaga hannu alamar su tsaya ba sai sun zo ba zai tafi..

Kusan 10 minutes yana tsaye yana kallon ta daga bisani ya bar wurin ya fito waje inda ya tarar har Hamida ta farka tana ta kuka tana kallon babyn..

Glancing fuskar babyn yayi ya sallame su akan zai je a kai Muhibba gida dan a mata wanka a kai ta gidan ta na gaskiya..

It's so touching dan haka Khalid ya bi shi suka bar asibitin dan sosai Saheeb ke buƙatar comfort amma baya cikin hayyacin sa..

Fitar su da mintuna aka turo fifi kan wheel zuwa ɗakin hutu inda aka ba su Ammy damar ganawa da ita a ɗan taƙaitacciyar lkc dan tana tsaka mai wuya ne presently yaƙi take yi da ran ta..

Da shigar su ɗakin Hamida ta zo ta zauna kusa da ita ta hau yi mata mgn tana kuka tana kallon babyn dake ta mutsu mutsu da baki,inda kusan a kashi ɗari toh kaso arba'in kawai ya kwaso na kamannin mahaifiyar sa duk kaso sittin ɗin mahaifin sa ne..

Haka Ammy da Hajja suka yi ta rarrashin ta suna bata mgn,daga bisani da kukan nata yayi tsanani ma karɓan babyn Hajja tayi ta ja gefe ta zauna tana rarrashin ɗan dan ya fara kukan yunwa...

****

An kai Muhibba gida an sanar da rasuwar ta,toh dama ba wasu yʻan uwa a kusa gare ta ba dole sai a washegari ko da zasu zo dan haka suka ce a mata sutura kawai a kai ta..

Haka aka mata wanka aka mata sallah aka suturta ta aka kai ta final destination ɗin ta..

Sai da Saheeb ya ƙulle kan sa a ɗakin Muhibba yayi ta kuka tuƙuru yana yi yana mata addu'ar rahamar ubangiji..

Sai misalin ƙarfe shida na yamma ya bar gidan ya nufi asibiti dan ganin halin da fifi ke ciki..

Dama su Ammy sun dawo gida dan karɓar gaisuwa tunda fifi na ɗaki ne na musamman ba a so a dame ta sosai sai Hamida ta tsaya tare da ita while Ammy da Hajja suka dawo gidan da babyn dan a mai wanka...

Ranar dai an ga samu an ga rashi,a wurin Saheeb da a ce babyn mace ce toh da tabbas sunan marigayiya zai maida mata wato Muhibba..

Haka nan tun ranar da Muhibba ta rasu fifi kuma ta shige comma,rayuwa ta sauya ma ahalin,wata walwala dai babu ita duk ta kau..

Rayuwar su ta sauya sosai dan daga ranar zuwa yanzu kusan sati biyu kenan fifi bata wani yi ƙwaƙwarar motsi ba sai dai in aka zo yi mata allura ta ɗan juya,da zarar an cire kuma zata cigaba da baccin wahalar da take ta yi...

Likitocin sun sanar da family ɗin fifi cewa wannan miracle ne mace mai cardiac disorder tun a yarintar ta kuma ma da shi aka haife ta ita kuma ta haihu ba tare da ta rasa ran ta ba,toh ba ƙaramin miracle bane...

Asibiti ya zama wurin zaman Saheeb har ranar da aka sallame su suka dawo gida ana bata kula ta musamman,bayan doctor dake zuwa yana duba ta,akwai wasu domiciliary nurses dake kula da ita a gida.

Duk wannan kular bai ma Hamida ba sai da ta ɗora da nata kular,bayan kula da babyn da take yi da har an raɗa mai suna while fifi is in comma..

Babu shagali da aka yi ko ɗaya duk da an yi ɗokin haihuwar amma yadda haihuwar ta zo,sai kowa yayi sanyi aka bari in har Allah ya tashi kafaɗun fifi sai ta zaɓi yadda take so a yi celebrating naming ceremony ɗin...

Babyn madara yake sha tunda ya zo duniya dan babu wani abu mafi sauƙi da zai fi zama a cikin babyn ba tare da ya mai illah ba sama da madarar..

Sunan babyn shine Abdulrahman but aka masa inkiya da Maheer duk da shi Saheeb ya ce in fifi ta farfaɗo kuma sunan bai mata ba toh dole za a sauya sunan..

Ba ƙaramin kula Maheer ke samu daga wurin aunty ɗin nasa ba wato Hamida,ita ke mai wanka ta saka mai kaya ta bashi abinci,tana yi tana kuka,tun mitsitsin babyn nan bai fahimtar Hamida har ya fara dan in yana hannun ta wani lafewa yake yi yayi ta sucking yatsar sa,alamar madarar bata isar sa..

A duk lkcn da yayi hakan toh fah Hamida kuka take yi ta daɗa rungume sa a jikin ta tana addu'ar samin lfy ga yaɾ uwar ta..

Shi dama Saheeb ya tare a ɗakin da fifi take take samin kula,duk yadda Ammy ke kula da ita in har ta ga shigowar Saheeb haka zata haƙura ta bashi wuri dan sai yayi ta kushe kular da take ma fifi,daga ya ce nan bai yi ba sai ya ce can bai gogu ba,duk kamar zautacce haka ya dawo gwanin tausayi...

Mgn kuwa ba iyaka,in fara zuba mgn shi kaɗai dan fifin dai ba jin sa take ba,abin sai ya ba mutum tausayi,dan har barin sumar fuska da na kai yayi babu gyara,duk ya sauya dan yanzu be asalin ƙaunar matar sa ke shigar sa,a yanzu da yake ganin kamar rasa ta zai yi dan kullum in ya zo toh burin sa bai wuce a ce ta farka ba amma haka zai yi zaman sa har ya tashi,ko motsu fifi ba zata yi ba...

Kalaman soyayya ya faɗe su wanda da fifi na hayyacin ta toh da zata ce maybe wani Saheeb ɗin ne ba wanda ta sani a matsayin mijin ta mai kawar da kai ba..

Kalaman ƙauna da so kala kala ko da yaushe sai ya faɗawa fifi su,duk ya zauce,ƙaunar ta mai zafi ke shigar sa..

Hamida kan yi kuka im ta gan sa a wannan yanayi,tausayin sa kan kama ta sai dai a halin yanzu,kula da babyn fifi da yi ma fifin addu'a shine abu mafi kusanci da fifin ke buƙata...

Kamar kullum yau ma yana zaune rungume da Maheer a jikin sa yaron na bacci shi kuma yana riƙe da hannun fifi yana mata kalaman soyayya da gwada mata irin ƙaunar ta da yake yi,har da alƙawarin sa na in ta farfaɗo bai kuma matsawa ko da nan da can ne sai ta yarda ta bashi izini...

Idanun sa sun rikiɗe sun yi ja dama su Hajja da Ammy basu jima da barin ɗakin ba,a kullum sai sun sanar da daddyn su fifin halin da ake ciki dan hnkln sa ya kwanta,duk da shima shirin dawowa gida nan Nigeria yake yi dan ya kasance da family ɗin sa gabaɗaya..

Dai dai yana mata surutan nasa kenan hannun ta riƙe cikin nasa sai ya ga kamar hannun na motsi,ɗan tsayawa yayi sannan ya kuma kallon hannun sai ya ga da gaske moving hannun ke yi daga haka ta fara motsawa tana nishi da ƙyar..

A 360 Saheeb ya tashi rungume da ɗan sa ya matso kusa da ita yana ta dariya mai ɗauke da kuka..

Sunan ta ya shiga kira hawaye na zubo mai kamar ba namiji ba namijin ma soldier mai matsayi kamar sa...

Da ƙarfi ya fara kiran sunan nata at same tym yana kiran sunan Ammy akan ta zo da sauri..

Ammy da zata wuce ɗakin dan duba lfyr Hajja dake fama da ciwon kai sai ta ji ana kiran ta da murya mai nuna zumuɗi..

Da sauri ta ƙarasa ta shiga ɗakin,dai dai fifi na tari mai ƙarfi kenan,da ganin haka sai Ammy tayi ƙasa tayi sujjada tana ma Allah godiya sannan ta taso a hnkl ta ƙaraso ga fifi ta riƙo hannun ta cikin nata tana kallon ta..

Rasa abin faɗi Ammy tayi sai murmushi shi kuma already ya fito daga ɗakin ya sauko yana ta faɗin ai Khadija ta farka his wife is awake,she is back to life again...

Kafin a sani tuni gidan ya hargitse da hayani ana ta murnar farkawar fifi,bayan kimanin wasu awowi aka ɗan sarara a ɗakin dan kula da ita da Hamida ke son yi kamar wanka da gyaran jikin ta...

Bata sami damar tmbyr abinda ta haifa ba,tunda dai ta gana da yʏar uwar ta sai ta ji duniyar ta mata daɗi not as she expected kamar da irin mutuwa zata yi ba zata kuma ganin su ba...

Ranar Hamida ce ta kula da ita ta bata abinci sannan ta je ta karɓo Maheer daga hannun Saheeb ta kawo ma fifi,sai daga baya su Ammy suka shigo ɗakin tare da Saheeb dake ta kallon ta kamar zai haɗiye ta tsabar kewar ta da ƙaunar sa da suka kasa barin zuciyar sa yayi saƙat...

Kallon babyn tayi ta yi tana mamakin wai ita ta haife sa kuma take riƙe da shi as his mother,me kuma zata nema a wurim ubangijin ta sama da gode mai da wannan baiwa da ya mata,dan baiwa ce,a lkcn da bata yi tunani ba bata yi tsammani ba sai gashi ta kasance tare da ahalin ta da ɗan da ta haifa da kan ta...

Har dare Hamida bata bar yʏar uwar ta ba sai da Khalid ya ja ra'ayin ta akan ta ɗan bar Saheeb ya gana da matar sa shima tunda tun bayan farkawar ta bai wani sami sararin zama tare da ita ba sakamakon cika da aka yi a ɗakin..

A lkcn itama tayi zurfin tunani sai ta ce ma fifi ta kawo babyn su tafi sai ta ce mata za a maido mata da babyn so take ta kuma kallon babyn kuma..

Da fara'a shimfiɗe saman fuskar Hamida ta fita ta bar ɗakin while fifi ta ƙurawa babyn ido tana ta kallon sa tana admiring babyn...

Tana haka sai Saheeb ya shigo bakin sa ɗauke da sallama sai ta amsa tana kallon sa..

Ƙarasowa yayi ya zauna kusa da ita suka ƙurawa babyn ido sai suka yi murmushi a lkcn ɗaya,ce mata yayi

"Welcome back mon amour"!kallon sa tayi tana mai gyaɗa mai kai kawai..

Daga haka suka cigaba da kallon ɗan har dai bacci ya fara ɗaukar ta tana rungume da Maheer,dabara Saheeb yayi ya gyara mata kwanciya bayan ya ɗauke babyn daga jikin ta..

Shima kwanciyar yayi kusa da ita sai ɗan space da ya bayar kaɗan inda ya shimfiɗe babyn a tsakiyar su ya ƙura mai ido yana ta kallon sa har shima baccin ya ɗauke sa..

Sai a washegari fifi ke sanin rasuwar Muhibba ai kuwa ta mata addu'a sosai da fatar samin rahamar ubangiji a nan kuma aka sanar da ita sunan ɗan ta sai ta ce sunan ya mata daɗi kuma bata buƙatar sauyawa babyn suna daga wanda mahaifin sa ya saka masa..

A cikin kwanakin aka rinƙa taimaka mata tana doguwar tafiya har jikin ta ya warware gabaɗaya ta fara shayar da ɗan ta da kan ta in ta gama ta aika ma Hamida da babyn..

A haka rayuwar gidan ya cigaba da tafiya cikin fahimta da kula da sanin ya kamata..

Ba a cire rai ba,itama Hamida ana mata addu'ar samin nata yayan in da rai da rabo..

*****

5 months later

Abubuwa da dama sun wanzu cikin waɗannan watannin kama daga haɗa daddyn su Fifi da Dr Fatima Yonas da su fifin suka yi dan su zama ma'aurata wanda dama dreams ɗin fifi kenan har ta bar wasiyar in ta mutu toh Hamida ta taimaka mata ta cika mata wannan buri nata,as she is still alive,sai ita da Hamida suka ɗaukaka mgnr har dai su Ammy suka ga dacewar hakan su ma..

Abu dai kamar wasa mutuntakar dake tsakanin daddyn su fifi da Dr Fatima ya ɗaukaka ya dawo babba,dan presently batun bikin su ake yi wanda ya rage nan da sati kaɗan..

A can fannin Dr Fatima kuwa da yayan ta biyu,bata da matsala ko damuwa da auren dan sun bata support ɗin su 100% as daddyn su fifi is a nice man Throughout his stay a ƙasar tare da su...

Maheer ya fara wayo kuma yanzu ne Allah ya azurta Hamida da Khalid da ƙaruwa dan she is 4 months pregnant,lbrn da ya ma kaf ahalin daɗi,dan sun fara yawa kamar yadda suke buri..

Saheeb dai dama jira yake komai yayi settling na bikin uncle ɗin nasa sai ya ɗau matar sa su koma South Africa tare in ya so sai su rinƙa zuwa visit ko vacation a nan Nigeria tunda a can yake aiki..

Bayan komai ya kammalu suka shirya dan tafiya,sosai fifi da Hamida suka yi kuka kamar sun rabu kenan na har abada,dan kuwa irin shaƙuwa da kusancin da suke yi a yanzu,ko zaman su na da da suka yi suna yan mata,basu taɓa yin sa ba,lokuta da dama ba Saheeb ba har Khalid yakan ji mamakin irin ƙarfin kusancin su sai dai in ya tuna ƙarfin jini ya fi gaban wasa sai ya share..

A haka rayuwa ta basu second chance suka fuskanci juna tsakanin su da kuma tsakanin su da iyayen su,a yanzu ne suke zaman so da ƙauna da fahimtar juna fiye da da da aka sami tangarɗa as result of ignorance da negligence ɗin su wanda basu fatar ko a wani gidan ne haka ya faru dan babbar illah ce su sun gani da idanun su..

After alk d luv and care da suka rinƙa nunawa Mufida har ya ma Hamida illah a zuciya ta so kauce hanya a ƙarshe Allah bai dubi halin da suka jefa Hamidar a ciki ba ya saka ƙaunar Mufida a zuciyar ta bayan so many attempt to get rid of Mufida..

Wannan shine clear definition na ƙauna da ake kiran sa da jini,dan ƙauna a jini yake ba kamar so ba da a baki ake faɗan sa ba wataran yana iya gushewa..

****

Bayan wasu shekaru kamar biyar a rayuwar su fifi,Allah ya azurta Hamida da yaya biyu na farkon itace mai sunan fifi na biyun kuma mai sunan daddyn su Khalid marigayi,while fifi kuma tun bayan Abdulrahman bata kuma haihuwa ba sai bayan shekaru uku inda ta haihu still through surgery kafin ma ranar haihuwar dan lfyr ta da na babyn,a wannan karon sai Allah ya bata yan biyu mata ɗaya ta ci sunan Ammy suna kiran ta da mami,ɗayar kuma sunan Hamida suna kiran ta Rayhan...

Tsakanin fifi da Nigeria shine ziyara dan tun bayan bikin dadyn su da Dr Fatima da ta zo,bata kuma zuwa ta jima ba sai dai ta zo ta ɗan yi kwanaki ita da Saheeb su koma..

Akwai shaƙuwa a tsakanin yaya su wanda hakan ya masu daɗi dan basu so rashin ƙaunar da ta so ta samo asali a nasu rayuwar ta faru a tsakanin yaya su...

Fifi kam bata da abin cewa sai godiya ga Allah swt da ya mallaka miji irin nata mijin wanda da ta so butulcewa Allah da zaɓin da ya mata but da yake matar wani bata auren mijin wata shi ɗin ne dai nata ƙaddarar sai Allah ya jefa mata so da ƙaunar sa a zuciyar ta tun bata sauraron zuciyar ta har ta natsu ta zauna da shi gashi a yau Allah ya albarkaci rayuwar auren su da abu mafi tsada da ko kuɗi bai isa ya siya maka shi ba,wato yaya..

Hamida ma na cikin gode ma Allah da ya bata nata zaɓin mijin ya kuma saka ƙaunar junan su cikin zukatan su,rayuwa mai daɗi da tsafta suke yi,kula da juna kuwa ba a mgn dan kullum cikin yin sa suke,yaya ko aikin Khalid ko nata ita kan ta aikin baya hana ta ba mijin ta kula yadda ya kamata,kamar yadda a kullum Saheeb

baya gajiya da gwada ma Khadijatul Mufidah salon son da yake mata,toh haka Khalid baya gajiyawa gurin ganin ya kuma dasa ƙaunar sa a zuciyar matar sa Ayshatul Hamida...

Duka duka a nan na kawo ƙarshen wannan lbr nawa mai suna Ƙaunarmu,inda nayi kuskure rabbi ya gafarta min inda nayi daidai Allah ya bani ladar sa,ubangiji Allah ya bar ƙauna da zumunci,taku ce

#Mamuhgee